MURYAR SHAHIDAI



# DUKUFA KA'IN da NA'IN GA YIN IBADA

Labarun Add'uoin Kullum na
MASU BANGASKIYA NA DA DANA YANZU
Daga wadanda suka sadaukar da kome
na rayuwar su domin KRISTI

*Mawallafan Littafin*
**JESUS FREAKS**
(Kungiyar 'Yan Gani Kashenin Kristi)

OVER PAGE

MURYAR SHAHIDAI

DUKUFA KWARAI GA YIN IBADA

Labarun addu'oin kullum na
MASU BANGASKIYA NA DA DANA YANZU
Daga wadanda suka sadaukar da kome na rayuwar su domin KRISTI.

Mawallafan Littafin
JESUS FREAKS
(Kungiyar yan gani Kashenin Kristi)

CONDIPRINT CONSULTANTS LTD.
Suka Fassara.

TRANSLATED BY:
Ibrahim Dikko
and
Dr. J. A. Maikano

OVER PAGE

Bangaskiya kadai ta isa. Shan wahala ta hannun mutum da wuyar jimiri. Amma idan aka gama da bangaskiya domin Kristi, wahala takan karfafa zuciyar Krista wanda yake a bude kuma cike da yarda ya rasa kansa domin ya ci ribar Kristi.

Shahidai da aka ambata a wannan littafi suna da manufa guda ta kaunar Allah. Wannan kauna itace ta rinjayi tsoron da ke zuciyar su na tunanin sakamakon abin da zai faru da su idan aka kama su suna yada bishara ta kaunar Allah ga wasu.

Watakila abinda ya fi karfafa su yazo ne daga darajar abubuwan da suke da tsada ta wajen wahalun mu, wannan yakan zama zuga-zugai na karfafa Krista wadanda suke kasashe masu mulkin duniya inda ba'a bada yancin addini. St. Augustine ya taba fada cewa "Ba wahalar ba amma dalilin shan wahalar ita take tabbatar da "shahidi" na gaske. Bisa ga kalmar Girka ta ainihi, wannan kalma "martyr" ma'anar ta "Shaida".

Shahidai da aka ambata a wannan littafi sun sami damar shaida gaskiya da kuma ikon Yesu Kristi da bakin su, suka kuma bada gaskiyar cewa ya kamata su yi shaidar wannan bangaskiya ga wasu, kome tsadar yin haka din.

A cikin littafin sa "Kisa a babbar Majami'ar T. S. Eliot ya yi bayanin shahidi a zaman wanda ya zama kayan aiki na Allah, wanda ya sa nufin Allah gaba da nasa nufi, irin wannan mutum bai yi rashi ba gama ya sami yanci wajen sadaukar da kansa ga Allah. Shahidi ba shi da sauran bukata takansa, kai ko yabon shahidancinsa ma baya sha'awa.

Zama mashaidin bangaskiya tamfar zama a bakin daga ne Pasto F. V. Hill ya taba bada labarin wata mata wacce ta zo gurin sa tace Pasto Hill, ka yi mani addu'a "Shaidan ya sani a gaba". Pasto Hill ya gaya mata" Shaidan bai sa ki a gaba ba "Ba kiyi abin daya isa shaidan ya sa ki a gaba ba" ya kamata manufar ko wane Krista ya zama "yi da gaske" domin mulkin Kristi yadda dagewarka za ta jawo hankalin shaidan ya san kana aiki domin Kristi.

A yayin da damuwa da wahalu suka zo maka a dalilin shaidar Kristi da ka ke yi fatar mu itace kai, kamar wadanda suke cikin littafin nan zaka dauki darasin daraja da ban sha'awa na mutanen da ke cikin wannan littafi "Dukufa kwarai ga yin ibada".

Kungiyar Marubutan "Dukufa Kwarai Ga yin Ibada" Muryar Shahidai.

# Extreme Devotion

## Hausa Ajami Edition

Copyright 2015 Voice Media

info@VM1.global
Web home: www.VM1.global

All rights reserved. No part of the publication may be reproduced, distributed or transmitted in any form or by any means, including photocopying, recording, or other electronic, or mechanical methods, without the prior written permission of the publisher, except in the case of brief quotations embodied in critical reviews and certain other noncommercial uses permitted by copyright law. For permission requests, email the publisher, addressed "Attention: Permission Coordinator," at the address above.

This publication **may not be sold, and is for free distribution** only.

An wallafa wannan littafi zuwa ga:

OVER PAGE

Wadanda suka gwammaci mutuwa maimakon musun Yesu Kristi. Wadanda suka zabi bangaskiya maimakon tsoro kuma suka zama shahidai maimakon juya baya. Domin dukan wadanda basu maida duniya komai ba.

Ibraniyawa 11:38

OVER PAGE

DUKUFA KWARAI
GAYIN
IBADA

Muryar Shahidai

# GODIYA

GODIYA

Hada irin wannan tsiwurwuri ya samu ne ta wurin aikin gayya ta gaske kuma akwai mutane da yawa daya kamata a gode musu.

Da farko ina so in godewa Allah domin kaunar sa da kuma jagoranci. Shine muke bauta ma kuma domin daukakarsa muke wadannan rubuce-rubuce.

Ina godiya ga dukan shahidai na da dana yanzu wadanda rayuwar su ta tabe mu ta wurin bangaskiyar su da kuma bada kansu. Da ba domin yin koyi da aikin da suka bari a baya ba da a yau majami'a zata sami rauni wajen yada bishara.

Ina godiya ta musamman ga Madaba'ar W. Publishing domin kokarin su da kuma hangen nesa. Da ba domin su ba da wannan littafi baza ta sami farin jini da ya kai haka ba.

Abin ilhama ne ganin irin sha'awar da suka yi na daukar nauyin taimakon mutane da ke da sha'awar fita daga gidajensu domin yada bishara.

Ina kuma godiya ga masu bincike da marubuta da suka yi aiki maikwazo wajen hada wadannan labaru, Ginny Clearly, Rick Killian, Todd Netlleton, Cherryl Odden da Henry "Buddy", Vaughn dukansu sun yi aiki babu kama-hannun-yaro tare da shugaban kungiyar Steve Cleary.

- Godiya ta, ta karshe ina mikata ga Mary Ann Lackland, Dave Veennan, Ashlay Taylor, Paige Divgas da Greg Longbons na Ma'aikata Livingstone, wanda ya tsara addu'oi na wannann littafi kuma yayi aiki da kungiyar 'W' wajen fitarda littafin.

Tom White
Shugaban Muryar Shahidai na Amirka.

WALLAFA

Muryar shahidai tana wallafa yar kasida wata-wata kyauta domin isarda labarun yadda har yanzu ana azabtuwa a wasu majami'u kuma ana bada shawarar yadda taimakon ka zai isa garesu.

Domin samun kasidar kana iya buga tarho ko ka rubuta zuwa:

**STEPHEN CENTRE INTERNATIONAL**
(The Voice of the Martyrs)
Sewage, Gowon Estate, Ipaja Lagos.
Tel: 0803 308 2342 0802 528 1090
0805 444 0849 0803 502 3229
Stephen Publication House,
Lagos - Nigeria.

# GABATARWA

GABATARWA

Masu bangaskiya da aka ambata a wannan littafi ba wadanda aka yi wa laifi bane amma wadanda suka ci nasara ne. Labarun gwagwamayar su ta shiga cikin tarihi tun daga zamanin Almajiran Kristi zuwa na shahidan zamani. Matsananta iri-iri ne daga Romawa zuwa Romaniyawa, daga cincirindon yan iska zuwa musulmi da kuma zamanin confuerans da kwaminisawa.

Amma ko wane daya daga cikin wadannan masu bangaskiya abin koyi ne a garemu, abin koyi na dukufa kwarai ga yin ibada ga Kristi. Labarun wadannan masu bangaskiya da za'a iske a cikin shafunan nan sun sami sha'awa mafi zurfi idan aka kwatanta da kokarin dan Adam na asali na kiyaye kansa, bukatar su itace ta bauta wa Kristi da kuma zaman shaidun sa.

AMIRKA

A daidai lokacin da muke wallafa wannan littafi muka shiga sabuwar marra a Amirka. Abubuwan da suka faru ranar goma sha daya ga watan Satumba 2001 ya sauye fuskar yanci ta duniya lokaci wanda jama'a zasu juyo zuwa majami'u domin samun amsoshin tambayoyinsu - lokaci ke nan da majamu'u zasu juyu ga Allah da sarautar sa domin samun karfafawa.

Munafar mu ita ce a yi anfani da wannan littafi wajen fadada tunanin mu kuma mu bar ayyukan mu suyi tasiri a lokacin da mu da kanmu muka fuskanci wahalu masu yawan gaske. Misali, yaya muke amsa wa wadanda suke nuna mana mugun hali? Wace irin amsa Yesu yake basu a lokacin sa? Da wane irin hali Krista na da suka amsa? Wane irin hali ya kamata mu nuna wa mutanen da ke bin wasu addinai idan suna nuna mana rashin imani a fili? Daidai ne muyi kasadar kome namu domin kokarin shaida masu kaunar Allah su wadanda za su iya kashe mu garin isar da sakon?

Wannan littafi ba zai iya amsa dukan wadannan tambayoyi ba, amma tabbas zai iya kalubalantar ban gaskiyar ka. A yayin da kake karanta wadannan labaru na Krista wadanda suka sha wahalu irin da ba'a iya bayyanawa duka a dalilin Kristi, kayi hange gaba da munanan abubuwa da suka faru domin ka gano kyawawan abubuwa dake karkashin wadannan a kunshe a cikin shaidun da wadannan yan'uw maza da mata masu karfin zuciya suka yi. Ka fahimci cewar Ruhunda ke zamne ko wanda ya zauna a cikinsu shine kuma ke cikin ka, kuma ka bada gaskiya cewa irin bangaskiya da ke cikinsu tana tare da kai ta ko wane mawuyacin hali.

A yayin da kake karatun abubuwan da aka jera anan zaka ci ribar gamsuwa da tsaurin ra'ayi na bangaskiyar su ta wurin fahimtar nazariyyar shan wahala.

Bangaren farko na fahimtar nazariyya shine na sanin cewa wadannan labaru ba tatsuniya neba na lissafta azabun da aka sha. Kuma bai nuna cewar wadannan masubi malaikune ba. Tabbas fitattu ne su wajen jarumtaka, tsayayyu ne fiye da yadda ake tsammani kuma masu bada kai ne ga Kristi ta hanyar da yana da wuya ayi bayani. Amma a zahiri su Krista ne kamar kowa (kamar mu) wadanda muka fuskanci damuwar yau da kullum.

Saboda haka menene wannan abin da ke izasu ga kaiwa wannan matsayin na dukufa ga yin Ibada? Fassara a saukake, bangaskiya a cikin yesu a zaman Ubangijinsu wanda shine dalilin shan wahalar su.

# Trukiyya: Ercan Sengul

RANA TA 1

***A lokacin da Ercan Sengul ya ba da ransa ga Kristi a kasar Musulmi ta Turkiyya, wadansu sunyi wa wannan ganin cewa ya juya wa kasar sa ta gado baya. A lokacin dayace zai iya yin ko da menene domin Allah, da gaske yake a wannan lokacin Amma yanzu fa?***

*Kuyi addu'a domina kuma, a bani ikon fadi, ina bude bakina, gabagadin sanarda asirin bishara wanda ni manzonta ne cikin sarka, domin cikinta in yi magana gabagadi yadda ya kamata ayi. Afisawa 6:19-20*

Ercan yana zaune a cikin dakin sa na fursuna a gidan kaso, mai duhu, kewaye dashi kuwa abokanj zaman sa ne laifin sa kuwa shine "wai ya yi wa Musulunci cin mutumci" Ta wurin raba takardu mawallafar Krista.

Ercan ya kai kukansa ga Allah ya na rokon a tserad da shi. Ya sani cewa baiyi wani laifi ba da zai sa a tsare shi. Kace "zaka iya yin ko mai sabili da ni" Allah ya gaya wa Ercan ta zuci "da gaske kake? Da karayar zuci Ercan ya yi kuka kuma yayi sujada ya gaya wa Allah azuciyar sa "Da gaske na ke yi".

Ercan ya fara yin wa'azi awa uku a kullum a cikin gidan kaso. Ya koya cewa Allah ya nufe shi da shiga kurkuku domin ya bashi sabon fage! Ercan ya zauna a kurkuku na kwana talatin har sai da shaidu suka fada cewa yan sanda sun tilasta musu su sa hannu a kan shaidar zur mai shari'a kuma bai sami shaidar laifi ya tabbata ba.

Wannan kamu da tsaro ya zama taki ga bisharar Ercan, sakin sa masu yawa daga wadanda suka zauna a daki daya sun ziyarci majami'ar sa suna neman sani akan Allahn sa da ya bashi salama lokacin da ya ke kulle a kurkuku. Har yanzu Ercan yana raba litattafan Krista da farin ciki duk da sanin cewa za'a iya kamashi.

Krista dayawa zasu yarda cewa shan wahala ba shi ne muka sa a rai ba a duk lokacin da muka ce muna so Allah ya yi anfani damu. Tabbas muna so mu zauna a cikin bangaskiyar mu amma ba tare da tsannani ba. Munki jinin a manta damu a lokacin karin girma a wajen aiki ko kuma rashin ba mu gayyata a wajen taro mukan ji kamar an kaskantadda mu ko ma an cuce mu. Idan kuwa muna da niyyar mu nemi Ubangiji ta wurin yin addu'a a tsakiyar dugunzumar mu. Da zarar munyi haka kuwa zamu ga yadda addu'a take sabuntar da mu. Sai mu fara samun zarafi na karuwa. Cike da bege, har mu sami alkawari cikin wuya, sannu a hankali sai mu gane matsayin da muke ciki, ko da mai sauki ne komai wuya watakila haka Allah ya shirya. Lokacin da muke yin addu'ar neman nufin Allah akan tsanani, ya kamata mu same karfin halin yin biyayya ko ta halin kaka.

# HADA KAINA KWARAI

## *Mauritania: Timothy*

RANA TA 2

***"Ka fada masa, timothy, idan ka yarda!" Inji Maura tana kara, tana rokon mijin ta "Ka fadawa gwamna inda Takardun suke a boye ka sami kanka! Ba ni da sauran dauriyar ganin dukan wadannan". Da Timothy da Maura mazauna yankin Roma ta kasar Mauritania ne wadanda suka yi aure yan makonni da suka shige kafin a tsare su.***

*Manufa ta itace su sami karfafawa a azuciya kuma da hadin kai cikin kauna.*
*Kolossiyawa 2:2*

Akan idon Maura kuma cikin razana sojoji suka cire wa mijinta idanu da karafa masu zafi, domin su karya masa karfin zuciyar sa. A yanzu kuma an ratayeshi kai kasa sawu sama da dutse mai nauyi rataye a wuyan sa bisa ga umarnin gwamnan yankin Roma Arrianus, Timothy ya saurara ko za'a cire masa abin nauyin. Tsoron da ya fara ji a farkon kama shi ya zama babu a maimakon haka sai baiwa daga sama ta natsuwa tazo masa.

Maimakon ya musunta bangaskiyar sa kuma ya bude asirin inda ya boye takardun majami'a kamar yadda Sojojin suka zata. Timothy ya tsawata mata yace, kul, ki bar kaunarki domina ya shan kan kaunarki domin Kristi. Ya karfafa Maura yana cewa a mutu domin Mai Ceton sa. Ganin jarutakar mijinta sai Maura ta dage ta karfafa.

Dagewar Timothy ta sa Arrianus ya fusata da ya ga Maura ta karfafa domin ya karya wannan karfin halin da yazo mata. Sai ya yanke mata hukumci mafi tsanani na azaba irin ta duniyar Romawa. Duk da haka bata karai ba. Ta ki yarda ta yi musun Kristi.

Bayan kowanen su ya jimre da munanan azabu sai aka giciye Timothy da Maura jere da juna.

***Yesu bai bada amanar bishararsa a hannun masu bin da ke yancin yin abin da suke so ba - ya kafa iyali ta "dan'uwa" da "yar'uwa" domin ya isar da sako cewa bai yi zaton almajiran sa ne kadai zasu yi bishara ba. Bulus ya cigaba da bisharar Kristi ta wurin umurtar sababbin tuba su taru a majami'u domin sujada. Krista suna bukatar juna musamman a lokacin jarabobi. A lokacin da mai bi daya ya fadi, masu bi sai su taimaka masa kuma su karfafa shi. Wannan shi ya sa sabon Alkawari (linjila) tana na'am da aikatawa da koyi da abin da littafi ya fada wajibi ne ga masu bangaskiya cikin Kristi. Misali guda na bangaskiyar mutum daya da jarumtakarsa yana zama ilhama da karfafawa ta hadin kai a bi sahu. Akasin haka idan mai bi daya ya gaza a cikin wahalar tsanani, zaiyi sauki wasu ma su gaza. Tarihi ya yabi hadin kai irin na Krista musamman lokacin tsanani.***

## SHIRI MAI TSANANI

### Kasar Sin: Pasto Li Dexian

RANA TA 3

***Daidai da lokacin da Pasto Li Dexian ya fara wa'azi, sai kofofin dakin Majami'a suka bankadu, sai hafsoshin ma'aikatar tsaro ta kasar Sin suka shigo cikin daki, suna yi wa kowa barazana inda suka cukume Li domin tsare shi.***

*Kamnatattu, kada ku ga abin mamaki ne tsanani mai zafi nan da ke wurinku, wanda ke abko maku domin ya auna ku, sai kache wani bakon al'amari ya same ku: 1 Biturs 4:12*

Dakata idan ka yarda ka bani dama na dau jakata" Kamar kullum muryar Pasto ga hafsoshin akwai ladabi da kamewa.

Hafsoshin sun yi mamakin wannan tambayar "me ke ciki", suka tambaye shi suna damke da bakar jaka mai zip. Li ya kama ya bude musu Jakar na dauke da bargo da yan tufafi, Li ya fada masu domin yana sane cewar za'a kama shi a ranan nan.

An sha tsare Pasto Li sau dayawa. Sau biyu ana masa duka har ga amai na jini, a wani lokaci kuma an duke shi a fuska da littafi mai tsarki. An gargadi Li cewa Yan sanda na sa ido ga kauyen inda yayi taron sa na talata. Ya sani cewa idan ya zo taron domin yin wa'azi za'a tsare shi. A yau yan Kasar Sin na iya samun hukumci zuwa sansanin Bauta na shekara uku ba tare da sharia ba.

Akwai kasada da gaske amma jakar Li ashirye take. Fiye da shiryayyar jaka, ko da shike ya rigaya ya shirya zuciyar sa. A shirye yake ya yi bishara ko ta halin kaka. Ya rinjayu da cewar Allah zai kula da shi ko da a cikin kurkuku ne.

***Zama da shiri yana nuna alamar alkawari. Alkawarin da ba shi da shirin sadaukar da kai ya zama daidata cikin shigar burtu. Misali kayi la'akkari da alkawarin aure, idan ka cika su yana zama wajibi duk da nauyin su, idan ko anyi haka sakamakon shine karfafa zumunta ta maaurata. Auren da babu shirin sadaukar da kai a ciki baya jurewa. Daidaita cikin shigar burtu yana raunana zaman tare. Haka kuma alkawarin maibi zuwa Kristi ya kan zo da tsada (wuya) don zama da daraja. Lallene mu zama da shirin gwajin alkawarin mu ta wurin tabbatarda cewa Kristi ma yayi haka. Ya ce mu bada lokaci domin addu'a ya dace a taru domin yin sujada a majami'u domin tabbatarda alkawarin mu ba tare da kwakwanto ba.***

## HASKE MAI TSANANI

### Colorado: Rachel Scott

RANA TA 4

***"Na rasa abokaina na makaranta gaba daya. Yanzu da na fara "tafiyarda Magana ta" suna yi mani ba'a" Mutanen da Rachel take marmarin ta nuna masu kaunar Kristi sun basheta kuma sun juya mata baya umma Rachel ba ta daddara ba. An karanta haka ne a dan littafin hannu nata.***

*Hakanan kuma ku bari haskenku shi haskaka a gaban r.utane, domin su ga ayyukan ku wanda ke cikin Sama. Matta 5:16*

Ba zan ba da hakuri ba don yin bisharar Yesu. Zan dauka haka idan har kawaye na suka zama abokan gaba na domin ina kusantar abokina mafi kusanci watau Yesu, in don wannan ne na gamsu da haka. Ina sane da cewar zama Krista tamfar samun abokan gaba ne, amma bar taba tunanin cewa kawaye na ne zasu zama abokan gaba na ba.

Rachel daliba ce a Columbia High School a ranar da wasu dalibai guda biyu suka bude wuta a makaranta. Wani rike da bindiga ya tambaye ta ko har yanzu tana ba da gaskiya ga Allah. Sai ta dube shi a fuska tace I har yanzu tana bada gaskiya. Sai ya tambaye ta yace me ya sa, amma bai jira amsa ba sai ya kashe ta.

Rachel Scott ta ci jarrabawan ta, dalilin cin wannan nasara ya sa hasken bangaskiyar ta ya watsu ko'ina a duniya. Ba da jimawa ba kafin wannan rana Rachel ta nuna sha'awar bada kome nata ga Kristi. Kalmomin da ta rubuta a dan littafinta shekara guda kafin wannan ranar mutawar ta ya tabbatar da alkawarin da tayi cewa ba zan boye hasken da Allah ya sa a cikina ba" I dan ma zan sadaukar da kome a shirye nake" .

***Bangaskiya itace dangantakar mu da Kristi a cikin lamirin zuciyar mu don haka ba ta ganuwa da ido. Littafi mai Tsariki ya na bayanin bangaskiyar mutane kamar haske-mai baza bege da zai shafi kowa da yake kewaye da su. Yesu ya zabi wannan misali domin haske baya tsaiduwa. Misali yin anfani da tocila a karkashin marufi garin yin karatu. Haske na tafiya ne bisa ga yadda aka halici haske, kome kckarin tare haske ba zai yiwu ba. Haka kuma damuwa yakan zo ma rayuwar masu bi a lokacin daya kamata su nuna bangaskiyar su ko kuma suyi kokarin boye ta. Tamkar kamar fitowar rana mara fashi a kullum su da suka tabbatar da shawarar su ta rike bangaskiya zasu ga hasken suna bangaskiya ya zama jiki.***

# ADDU'A MAI TSANANI

## *Kasar Sin: Sister Wong*

RANA TA 5

*Ubangiji ya ce, Tashi, ka tafi cikin hanya wadda ana ce da ita Mikakkiya a cikin gidan Yahuda sai kayi tambayar wani mutum sunansa Shawulu, Mutumin Tarsus gama gashi yana addu'a*
*Ayyukan Manzanni 9:11*

***A lokacin da hafsoshin ma'aikatar tsaro ta jama'a suka shiga dakin kurkuku, Sister Wong ta matsa ta basu guri. Wannan mugun mutumin ya sha tsare Kristoci, kuma ya nuna mata tsanani kwanan nan har ya yi mata duka wajen yi mata tambayoyi.***

Sister Wong, 'Yar'uwanta bata da lafiya ainun, duk kafafun ta sun mutu ko zaki iya zuwa kiyi mata addu'a? Wannan shine mutumin da ya kwace da ruruwa Littafi Mai Tsarki da wasu littafan Krista a hannunta? Yanzu kuma yana neman addu'a? Babu shakka hankalin sa ya dawo ga Allah.

Yan kwanaki kadan baya wannan hafsan yayi wa Sister Wong tambayoyi cike da zage-zage. Ya sami kira a tarho cewa mota ta buge mahaifiyarsa. A lokacin daya fadawa uwarsa abinda yake yi, sai tace razana Krista da yake yi shi ya kawo wannan, wannan hafsa ya maida gargadin abin canfi hadari da ya sameta.

Washe gari kuwa sai ya ci gaba da yiwa Sister Wong tambayoyi amma sai ya sami wani sakon kuma cewa dan uwansa ya sami rauni a wani hadari. Dan'uwansa ma ya bashi laifin cewa kuntata wa Krista da yake yi ne ya jawo ma iyalinsu illa. Amma a lokacin da yar'uwarsa ta shiga rashin lafiya, ya roki Sister Wong ta yi addu'a.

Sister Wong ta sami wata dama da take jira ya samu, watau damar tayi wa masu azabtarwa bishara. Allah ya warkadda yar'uwar kuma ta wurin ayyukan Sister Wong ya juya zuciyar hafsan. Hafsan ya dawo da dukkan litattafan daya kwace yanzu kuwa yana taimakawa majami'a.

***Yawancin mutane kan sami juyowa ga yin addu'a musamman a lokacin ciwo ko damuwa abubuwan da suke hana abin da ya shafi addini akan cire sune da dai dai a duk lokacin da wani ya nemi ko ya karbi cewa a yi addu'a dominsa, da wuya a sami wani wanda zai ki amsa addu'ar da aka neme shi da ita "ina addu'a dominka" yana iya zama kalmomin karfafawa da mai bi zai fada wa mara bangaskiya. Domin me? Addu'a sakon Allah ne domin sauyi tana kawo sakamako wani lokaci kuma tana sauya al'amura, wani lokaci tana sauya shawara. Galibi tana sauya wadanda suka tabu ta wurin yin addu'a Littafi Mai Tsarki ya nuna cewa addu'a ce na Tarsus wanda ya tsananta wa yawancin masu bi ya tuba.***
***Wa ya san irin aikin da addu'a zatayi ga juyo da masu tsanantawa Krista irin su "Shawulun duniya? Wadanda suka dage ga rushe addinin Krista?***

# MATSANANCIN LAIFI

## Madagascar: Ranavbalona

RANA TA 6

*Amma cikin zukatan ku ku tsarkake Kristi kamar Ubangiji kullum a shirye kuke ku amsa ma kowane mai tambayarku dalilin begen da ke cikinku, amma dai da ladabi da tsoro.*
*Bitrus ta fari 3:15*

***Ranavalona, sarauniyar Madagascar, ta tsani Krista a kasar mulkin ta. Koke-koken ta a kan Krista sun yi yawa domin sun raina gumakan ta, a kullum addu'a suke yi. A kullum zuwa majami'a suke yi kuma matansu masu tsarki ne. Ta tura hafsoshi cewa a tara dukan wadanda ake tsammanin Kristoci ne a kawo su ga tuhuma a gidan sharia.***

Masubi dubu daya da dari shida suka amsa cewa sunyi laifi a lokacin da aka karanta masu tuhumar. Ba zasu yi musun tuhumar ba dlomin yin haka zai zama musun Kristi. Sarauniyar ta sake basu wata dama na suyi musun Kristi kuma suyi ma gumakanta sujada amma kowannen su ya ki. Sai aka kai su cikin kurkuku mai duhu, da yawa daga cikin su kuwa aka kashe. Sarauniya ta fusata kwarai domin kowane Krista daya da ta kashe, guda ashirin suna bada kansu.

Daga baya sarauniya ta bada umarni a kashe Krista guda goma sha biyar. A shirya kisar ta turo su kasa daga kan dutse mai gangare su fado cikin kwazazzabo gangaren zurfin kafa 50. A ka kai gumakan sarauniya akan dutse Krista kuma aka reto shi da igiya zuwa bakin dutsen a daure da igiya. "Zaka bauta wa kristin ko kuwa allolin sarauniya? "Sojojin na tambayar kowanne Krista wanda ke reto a fuskar babban dutse mai gangare kwarai.

Kowane Krista ya amsa cikin sauki "Kristi". Da jin haka sai a yanke igiyar su fado cikin kwazazzabo. Wasu waka ma suke yi a yayinda suke fadowa. Aka bar wata budurwa wai mahaukaciyace daga baya ta gina babban majami'a.

***A kasashe da yawa akan dauki wanda aka kai kararsa a kotu cewa ba shi da laifi har sai kotu ta tabbatar da laifin. Ka'idar ita ce akwai tsarin bin doka cewa sai an sami isassun shaidu na tabbatar da yin laifin furta bangaskiya ga Kristi ya na zama yiwa gwamnati laifi a kasashe da dama inda fannin shari'ar su a birkice yake. Watau su a garesu masubi suna da laifi sai in har an sami akasin haka. Idan ko haka ne, ma'anar itace sai an yi musun Kristi shine za'a zama mara laifi a cikin bakin shari'ar dan adam. Amma fa a cikin dakin shari'ar samaniya mailaifin nan a duniya domin bangaskiyar sa, shine mai nasara.***
***"Matsanancin laifi" yana nufin samar da shaidu masu yawa na bangaskiya ga Kristi ta yadda ba za'a sami hanyar kubuta daga wannan tuhumar ba! Idan da za'a kai ka a gaban sharia yau wai don kai Krista ne, shin za'a sami isassun shaidun da za su tabbatar da laifin ka har ga dauri?***

***Mun koya cewa ba wahala ce abu mafi muni a duniya ba. Rashin biyayya ga Allah shine abu mafi muni.***

***Wani Pasto na Krista dan Vietnam wanda yayi fursuna domin bangaskiyarsa.***

***Tabbuna masu Tsanani***

## TABBUNA MATSANANTA
### Urshalima: Thomas

RANA TA 8

*Amma kai kabi koyaswata da tasarrufana da nufina da bangaskiyata da jimrewata da kaunata da hakurina. Timothawus ta biyu 3:10*

***Ya sha jin jita-jitar da gaske ma Thomas ya ji kai tsaye daga sauran almajirai wadanda suka ga shugaba da ransa. "A kalla abinda suka fada ke nan" A lokacin da naga hannayen sa kuma na sa yatsuna akan ramukan tabon inda aka huda da kusa, a lokacin da nasa hannu a wajen tabon gefen sa inda Romawa suka huda da mashi, sa'anan zan bada gaskiya cewa ya tashi" Thomas ya fadi haka.***

Ba abin al'ajibi ko wasu manyan alamu ko abubuwan mamaki Thomas yake nema ba. Kawai abinda yake so ya gani shine inda aka kafawa Yesu kusa a hannu da inda aka sokeshi da mashi in da tabon ya ke a jikin Yesu, watau alamu da zasu nuna irin wahala da yasha. Ko da shike Yesu yaci nasara da mutuwa ya kuma zauna a cikin jiki mai daukaka, amma duk da haka tabon kusa da na mashi suna nan a jikinsa abin tunawa da irin halin da ya shiga domin cetonmu.

Bayan kwana takwas yesu ya sake bayyanuwa. Wane irin wawane ni Thomas na iya tambayar kansa a lokacin da suka yi arba da yesu. Maganar da yayi wace yake zaton muhimmiya ce yanzu ya san cewa yayi wauta a lokacin da sauran almajirai suka yi masa tuni.

Duk da haka Yesu bai tsawata masa cikin fushi ba. Ya dubi Thomas a ido sai ya mika masa hannayensa, yana karfafa shi domin ya ga tabon kuma ya taba kuma ya bada gaskiya.

Tabon da suke jikin Kristi suna nan a jikinsa bayan daya tashi daga matattu. Gama ko da shike yaci nasara da mutuwa, jikin sa a duniya har yanzu yana shan wahala. Kuma yana sanne da wadanda ke dauke da tabo a jikin su ko ina a duniya a dalilin bangaskiyarsu ga Kristi.

***Tabo a jiki yana koyar da mu kuma yana mana tuni na wani abu mai ciwo da ya taba faruwa damu. Galibi ba su da kyaun gani kuma da wuya ma a nuna wa wani. Haka ma tabbunan shekarun tsanantarwa majami'a ba kasafai ake zancensu ba a taron Krista, Idan kuwa an yi la'akari da haka zamu ga karfafawa. Tsanani yana da muhammanci wajen shirya masu bi ta wurin shirin da Allah yake yi domin aikin sa a cikin dukan duniya domin duniya ta ji kuma ta karba. Yesu a fili ne ya sami raunukan da suka zama tabo a jikinsa a garemu. Yesu ma ya karfafa Thomas da ya taba da hannunsa don yayi koyi. Tabon sa abin koyi ne a garemu domin suna mana tuni da biyar fansar cetonmu. Lalle ne mu cigaba da yin koyi da wannan, amma ba waimuyi biris da irin azabar da majami'a ta sha ba domin fansar mutane daga zunubansu.***

## ZABI MAFI TSANANI
### *Ingila: John Lambert*

RANA TA 9

*Ka yafe mana laifofin mu kamar yadda muke yafewa wadanda suke yi mana laifi.*
*Matta 6:12*

***"Menene zabin ka, ka rayu ko ka mutu" me ka fada?***

***Wannan matambayin Henry viii ne, Sarkin Ingila wanda yake da ikon yin duk abinda ya ga damaryi a kasar. Mai laifin da ya tsaya a gaban da ake tuhumar baza jita-jita, shine John Lambert mutumin Girka kuma malamine mai koyarda harshen latin. Lambert don tsananin rashin tsoro ya kalubalanci Pasto akan wa'azi da yayi domin ya saba wa Littafi Mai Tsarki sai aka kawo Lambert a gaban Babban Limamin Babban Majami'ar Canterbury daga nan kuma zuwa gaban Sarki Henry. Sai ya ja nassi daga Littafi Mai Tsarki ya na bayyana harshen Girka ta ainihi. Lambert ya gabatar da bayanin sa a gaban taron manyan malaman Bishop, Lauyoyi, Manyan Alkalai da sa'aninsu, duka gefe biyu suka yi muhawara sosai akan batun ana kaiwa ana komowa har sai da Henry ga gaji da yi, sai ya gabatar wa da Lambert da zabi na karshe. "Bayan dukan wadannan dalilai da koyaswa da akayi a gaban masana irin wadannan shin ka gamsu yanzu? "Menene zabin ka ka rayu ko ka mutu"? Me ka fada?***

Lambert ya nisa ya amsa da tabbaci yace "Na danka raina a hannun Allah, amma gawata kayi abinda ka ga dama da shi" Lalle ne ka mutu" Henry ya amsa masa yana kece raini domin bazan goyi bayan jita-jita ba. Da laifin jita-jita aka daure Lambert a jikin itace duk da irin mummunar kisa a hankali da aka yi masa. Ya daga hannayen sa a sama yana sujada yana nuna cewa "Babu wani Sai Kristi! Babu wani sai Kristi".

A zamani irin na yanzu damar mu yi zabi ya wuce misali. Tashoshin Telbijin guda dari biyu damace wadda zamu iya karanta yanci dungurungum. Mu masu son zabi ne daga abubuwa dabam-dabam kuma shawarwari da yawa suna zuwa mana a kullum na abinda zamu ci tufafin da zamu sa, abin hawa da zamu tuka ko kuma abinda muke so muyi. Biye da haka mun sani a yau zabin mu ba su da adadi.

***A kasin haka yayin da muhimman tambayoyi na damuwa suka zo mana, amsa guda daya tak muke da ita da zamu bayar "Babu wani sai Kristi" ko akwai wata hanyan zuwa sama? "Babu wani sai Kristi" Shine hanya. Akwai wani muhimmanci mafi darajar rayuwa da ya dace ayi masa sujada? "Babu wani sai Kristi". Gaskiya da yace ba'a sauyata. A lokacin da muhimman tambayoyi na rayuwa suka zo maka kuma lallene zasu zo watarana, ashirye kake kayi shaida? "Babu wani sai Kristi ne zai gamsar"***

# MATSANANCIYAR CIN AMANA

## *Romania: Brother Vasile*

RANA TA 10

***An rufe majami'u a kasar kwaminis ta Romania kuma aka tsare Pastoci a shirin su na kashe ko kawarda camfi daga kasarsu a cikin wani tsarinsu na shekara bakwai.***

*Ka yafe mana laifofin mu kamar yadda muke yafewa wadanda suke yi mana laifi. Matta 6:12*

A lokacin da dan'uwa Vasile da matar sa suka fara yin taron majami'a a cikin gidan su, sun sani cewa ba zasu guje wa jawo hankalin gwamnatin ba. Vasile yana yin addua a kowane dare. "Allah idan ka san cewa da akwai aikena zuwa kurkurku" Matarsa ba ta so jin haka ba amma yaya zata yi sai ta amsa masa amin a karshen addu'ar. Anan sai sukaji labarin an kai hari gidan wani mai bi kuma an sami takardun Vasile aka kwace. Sai suka sami labarin mataimakin Pasto, abokin aikin su, ya zama dan tonon asirin su kuma ya juya wa Vasile baya.

Da karfe 1:00 na dare yan sanda suka kai hari a gidan Vasile aka tsare shi. A yayin da aka sa masa ankwa Vasile yace "bazan bar nan a cikin lumana ba sai kun bani damar yin bankwana da matata" Yan sanda suka barshi amma ba da son su ba kuma ma da shike sun san yana hannu. Vasile ya rike matarsa suka yi addu'a suka yi waka mai sosa - rai har shi hafsan shugaban ma ya yi juyayi.

A karshe aka raka shi har cikin motar yansanda matar tana gudu a bayan su a tsorace Vasile ya juyo ya yi mata kalmomin karshe kafin ya tafi, tafiyar shekaru. Yace ki mika kaunata ga danmu da kuma shi wannan Pasto da ya juya mana baya"

***Matsanacin mai cin Amana na bukatar Matsananciyar gafartawa. Idan makiyanmu suka tasan mana da zafin kiyayya, ashe bai kamata mu zama masu adalci da gafartawa ba? Idan makiyan mu sun kai ga juya mana baya ashe bai kamata mu gafarta musu ba? Yesu ya koya mana cewa gafartawa abune mai kyau a garemu. Cin amana yana iya sa mu rufe zuciyar mugu da samun koyarsawa ta wurin gafartawa. Idan ka sami kanka a zaman daya daga cikin masu wuyar gafartawa zaka sami nawayyar zuci da rashin salama domin naka zunuban, aci amanarka mugun abune. Zama cikin bakin ciki gazawane da bai kamata a sameka da shi ba. Ga wane ne zaka mika gafartawa mara iyaka yau?***

## MATSANANCIN YAR KYAUTA
## Russia: Captain Marco

RANA TA 11

*Amma ku kaunaci magabtan ku, kuna yi masu alheri. Luka 6:35*

***"Menene Hafsan Soviet Kaftin Marco ya Tambayi Yaro cikin gurnani, me kake so"?***
***Yaron dan shekaru gomasha biyu kacal, yayi karfin hali ya tsaya a gaban hafsan kwaminis. "Kaftin, kai ne mutumin da ya sa iyaye na a kurkuku. Yau ne zagayowar ranar haifuwar uwata, kuma a duk shekara na kan sayo mata furanni domin tunawa da wannan rana.***

Tunda uwata ta koya mani cewa na kaunaci makiyana kuma in rama mugunta da alheri na kawo wadannan faranni domin ka baiwa uwar yayanka. Idan ka yarda ka kai wa matarka a gida a dare yau kuma ka fada mata kauna ta a garesu da kuma kaunar Kristi.

Kaftin Marrco wanda yasha kallon yadda ake azabtadda Krista ba tare da jin tausayi ba sai ga shi kalmomin kauna da yaro yayi anfani da su sun razana shi. Sai ya fara tafiya yana zagaya teburin sa hawaye na zubowa daga idanun sa, sai ya rungumi yaron tamfar shine ubansa. Zuciyar Marco ta sami sauyi ta wurin kyautar kauna ta Kristi. Bai iya cin gaba da azabtardda Krista ba, ba da jimawa ba shi ma sai aka kamashi.

Yan watanni bayan ziyarar yara zuwa ofishinsa Marco ya yi mutunkus a cikin kazamin dakin kurkuku ga kuma wadanda ya azabtar suna kewaye da shi. Cike da hawaye yana fada wa masu bi labarin yaron nan da kyauta mafi sauki da yayi ta furarni.

***Ya nuna cewa ai wata martaba ce ma a gareshi daya sami damar yin zaman tare a cikin kurkuku da masu bi wadanda a farautar su yake yi yana kai masu hari.***
***Karimci haline da aka san Kristi da shi. Yesu ya yi koyaswa cewa za'a iya gane masu bi na gaske ta wurin nuna kauna. Kuma ba ga wadanda ke kaunar mu kadai ba. Galibi yi wa baki karimci kai har ma makiya shine hanya mafi kyau na nuna koyaswar Yesu. Wadanda suke shaida ayyukan mu, idan ba wadanda suka mori haka din ba, su kanyi mamaki da ganin haka. Me zaka ce da ma'aikaci ko ma'aikaciya da ke yi wa shugaban ma'aikata da ya kore shi ko ya kore ta daga aiki ba tare da takamamen laifiba addu'a? Ka dubi matsayi ko halin da iyayen da direba bugaggen dan giya yayi masu ta'adi.***
***Duniya bata ganewa ko menene karimci ba ko da shike mun sani cewa akwai shi duka da bayaswar mu ta karimci ba mu iya kamanta abin da Allah yake so. Allah ya ba da Dan sa tilo domin ya nuna mana kauna ta sayen ceton mu. Me zaka bayar yau da zai iya bude zuciyar wani zuwa mulkin Allah?***

## MATSANANCIYAR MAI BISHARA

## Pakistan: Saleema dà Raheela

RANA TA 12

*Ina addu'a domin ku zàma masu kwazo wajen nuna bangaskiy arku ga juna domin ku sami cikakken fahimtar lukan kyawawan abubuwa da muke dasu acikin Kristi*
*Filimon 6*

***"Idan ki kayi alkawarin daukar giciyen ki rayuwar za ta zama cike da kayayuwa, duwatsu da wahalhalu yar matashiya ta Pakistan ce tayi wannan magana da kakkarfa murya. Saleema, Kristace wadda take zaune a inda musulmi suka fi rinjaye a Pakistan, ta yi bishara ga kawarta ta makaranta, Raheela, wacce ta karbi Kristi daga baya.***

Iyalin Raheela suka tuhumi Saleema da juya musulma. Tuhuma ce da zata iya kawo shari'ar kisa a paskitan. Aka tsare Saleema da paston ta, kuma aka yi wa iyayenta tambayoyi har ma Yan Sanda suka yi masu duka. Anyi wa Saleema mummunan zagi a lokacin da take a tsare a hannun Yan Sanda, amma ba ta yi musun bangaskiyar ta ba alhali ma wakokin Krista take tayi da begen cewa yin haka zai jawo wasu ga Kristi.

Raheela tayi gudu daga gidansu, amma iyalin ta suka shiga nemanta. A lokacin da suka bata dama ta karshe cewa ta yi kalmar shahada ta dawo musulunci, ta ki yarda. A dalilin haka iyalin ta suka kashe ta.

Saleema ta gwagwarmayar shari'a iyalin Raheela sun baiwa Saleema laifin mutuwar diyarsu. Sannu a hankali sai aka janye karar. Amma rayuwar Saleema ba zai taba zama kamar da ba. Sai da aka tilasta mata ta koma wata unguwa, a Pakistan domin tsoron wasu tsagerun musulmi na iya kasheta. Duk da haka da kayayyuwan, duwatsun da wahalhalun basu dishe bangaskiyar ta ba. Alhali ma dai yanzu ta na shirin zama mai Bishara. "Tace kome girma dutsen, Yesu zai taimaka wajen hayewa!"

***Galibi akan dauki masu bishara wasu ne masu iko na musamman watau rundunar sojojin Allah na ban gaskiya wacce ba bu irin ta da take aiki a madadinmu. Gaskiyar ta ce kowane mai bi ya na zaman mai bishara. Wasu daga cikin ayyukan Allah mafi dara sa suna iya faruwa ko da akan teburin da ke wurin dafa abinci ana shan kofi ko ma makwabta. Manufar bishararmu daya ce ko da ina muka Dole ne mu yada kaunar Kristi. Ga wasu yada bishara na d wuya, ga wasu kuwa abin sha'awane. Abu mafi anfani shin anniyarmu. Anniyar ka tana da iyaka wajen yada bishara Kristi?.***

# MATSANANTAN WAHALU

## *India: Dr. P. P. Job*

RANA TA 13

***"Ji nake kamar an yanke, mani daya daga cikin hanjina" Inji Dr. P. P. Job. Wannan yana daya daga cikin wa'azi mafi wuya daya gudanar a rayuwarsa a jana'izar dansa . Muryarsa ta yi nauyi cike da sosuwar rai. "Amma ko da menene ya rage mani, zanci gaba da bautawa mulkin Kristi".***

*Yanzu nasan cewa kana tsoran Ubangiji domin baka hana mani danka tiloba.*
*Farawa 22:12*

Dr. Job shine shugaban shahidan Krista a India kuma yana daukar kasada lokaci lokaci domin ziyarar karfafa masu bi a kasashe marasa yanci. Kuma ya kan yi wa'azi a manyan taro a India, kuma yasha ganin dubban mutane suna tuba ga kristi. Ayyukansa suna fusata masu tsaurin addini na Hindu a cikin kasarsa. A watan Yuni 1999 an warwaro dutse ta tagar motarsa dutsen ya bagi Dr. Job a goshi ya yi masa mummunan rauni. Bayan mako guda karamin yaron Dr. Job mai suna Michael yana tafiya kusa da makarantar koyon aikin magani inda yake dalibbin zama likita. Wata motar Fiat ta taho a guje ta bamkade Michael ta gudu. Ba'a sameshi ba Michael ya ji ciwo har ya suma daga baya ya mutu.

Kamar yadda ya yi alkawarin rashin danda bai tsayar da shi batun mutuwar Michael, Dr. Job yayi wa'azi a manyan taruka mafi yawa, yana kawo dubbai zuwa Kristi. Wahalar da Dr. Job ya gani saboda bishara tana da yawa. Amma ba shi kadai ne ya rasa da ba. Allah da kansa ya san zafin a rasa da domin a dalilin rashin dansa Yesu ne wasu zasu sami ceto.

***Majami'ar da ake tsanantawa tana da dogon tafiya akan hanya da gangare mai zurfi kwari. Fiye da shekaru dubu biyu kenan. Dayawa mugunta ta sha masu kai a cikin gabarsu da bisharar Kristi. A zamanmu na Krista dole ne mu dau aniyar yin bishara kome tsadar yin haka lallene muyi koyi da rayuwa irin ta Ibrahim. Yayi shiri kuma ya dauki aniyar sadaukar da Ishaku - wanda ta wurinsa ne albarku zasu zo. Zama shiryayyu wajen ba da kanmu ga kristi ya na karfafa mu. Batun bada kai yana tabbatarda manufarmu. Bada kai yana karfafa halayen mu, alkawurran da suke da nauyi, sauya rayuwar mu da iyalinmu, da makwabtan mu dama rayuwar mu ta duniya domin Kristi. Sai mu koyi sanin ya ya karfin mu yake ko da shike ba mai son rasa abinda yake so sai muyi ko karin dagewa kome tsanáni.***

*Ubangiji ka maishe ni kayan aiki na salamarka.*
*Inda akwai kiyayya bari na shuka kauna*
*inda akwai rauni, gafartawa*
*inda akwai shakka, bangaskiya*
*inda akwai fid-da-rai, bege*
*inda akwai duhu, haske*
*Inda akwai cin rai, farinciki.*

*Ya Mai Tsarki ka bani ikon ta'azartawa*
*fiye da bukatata ta ta'aziyantar dani;*
*A fahimceni nima na fahimta.*
*A kaunace ni ni ma na kaunatar gama ta wurin*
*bayaswa muke karba.*
*Ta wurin gafartawa ake gafarta mana.*
*Ta wurin sadaukarda kanmu ake sake haifuwar*
*mu zuwa rai na har abada.*

# MURMUSHI MAI TSANANI
## *Siberia: Paulus*

RANA TA 15

***Wanene zai iya raba mu da kaunar Kristi?***
***Hargitsi***
***ko Wahala***
***ko Tsanani***
***ko Yunwa***
***ko Stiradai***
***ko Hatsari***
***ko Takobi.***
***Romawa 8:15***

***Lokaci na kurewa, hafsan Soviet kuwa ya azabtad da Paulus na dogon lokaci. "Ba zamu kara azabtar da kai ba kuma" Injishi, yana mugun murmushi, a lokacin Paulus ya daga kansa ya dubi Hafsan. "Za mu aika ka zuwa Siberia, wurinda dusar kankara bata narkewa. Wurine na shan tsananin azaba, kai da iyalinka za ku dace da wannan wurin"***

Mai Paulus ya nuna bakin ciki sai yayi murmushi yace duniyar gaba dayanta ta Ubanace, kaftin, duk inda ka aika ni a duniyar Ubana nake". Sai kaftin din ya dube shi, "Zamu kwashe dukan abinda ka mallaka" kana da bukatar tsani mai tsawo, kaftin domin dukiyata tana ajiye a sama". Paulus yana nan dauke da murmushinsa.

Zamu sa harsashi a tsakanin idanunka" Kaftin yayi magana da karfi da yake ya yi fushi. Idan ka dauke raina a wannan duniya, rayuwa ta ta gaske ta farin ciki da sha'awa zata fara", Paulus ya amsa masa. "Bana jin tsoron kisa".

Kaftin ya kama wuyar rigar fursuna ya yayyaga ta. Paulus ya yi ihu a fuskarsa, "Ba zamu kasheka ba" zamu kulle ka a kurkuku kai kadai mu hana kowa zuwa ganin ka" Ba zaka iya yin haka ba kaftin" in ji Paulus, har yanzu yana murmushi, "Ina da aboki wanda yana iya shiga ta kofofin da aka kulle har da karafa, babu wanda zai iya raba ni da kaunar Kristi".

***Duk da rashin sanin gobe, muna da tabbacin abu guda. Kristi yana tare damu. Ko da muna cikin jaraba ta fili ko ta boye ba kadai muke ba. Akashin haka kowane dan Ådam mai taimaka wa zai iya gazawa wasu lokuta. Akwai lokaci a rayuwa wanda mutum zai gaza a yayin da abubuwa suka yi tsanani. Yesu shi kadai yake da ikon shiga ta "kofofin karfe" da ke rufe zukatan mu a lokacinda muke cikin mummunan hali mawuyaci. Ko da shike a cikin hikimarsa, yana iya zabin barinmu a cikin irin halin da muka sami kanmu, zamansa a cikinmu zai fitar da mu da ciki. Kayi murmushi tun da ka san kana da aboki wanda ba bu wanda zai iya rabaku.***

# MATSANANCI SADAUKAR DA KAI

## Indonesia: Pasto Hendrick Pattiwael

RANA TA 16

*Don haka ina rokon ku 'yan'uwa, saboda yawan jinkai na Allah, ku mika jikinku Hadaya Rayayya, Tsattsarka abar karba ga Allah. Domin wannan itace Ibadarku ta anihi.*
*Romawa 12:1*

***Sun taru a takure cikin daki a yayin da suke jin kururuwar yan'uwansu Krista da ake wa azzalumanci tanfar dabbobi a can waje. Pasto Hendrick Pattiwael da matarsa suna taimako wajen yiwa sansanin matasa ta Indonesia Jagoranci, wannan ya sa su cikin damuwa domin matasan nan na karkashin kulawarsu.***

Wannan sansanin wuri ne inda matasan suke cike ɗa farin ciki tare da karuwa a cikin ruhaniya ta wurin yin sujada tare, kwatsam sai aka kawo masu hari. A lokacin da din bin musulmi masu tsatsaurin ra'ayi suka kewaye ginin inda suka buya Pasto Pattiwael ya fito waje. Yana jan hankalin gungun mutanen nan masu son zubar da jini daga matarsa da kuma matasan aka kuma kai masa hari a yayin da ake cikin yin haka kuwa dama ta samu garesu suka tsere.

"Yesu ka taimakeni" furucinsa na karshe kenan. Matar ba ta sake ganinsa ba sai a cikin makara. Cikin gigita da hasala matar Pattiwael tayi kuka ga Allah. Ta kaka zaka bar irin wannan abu ya faru? Me yasa baka kare mijina ba? Amma Ruhun Mai Tsarki ya tunatarda ita wasu kalmomi da mijinta yayi yan kwanaki kadan kafin wannan ranar kai masa hari. Yace, "Idan kana kaunar Yesu amma kaunar da kike yi mani ko iyali ta fi karfi to baki dace da mulkin Kristi ba".

Tunawa da wadannan kalmomi ya sa ta daina bakinciki. Har yanzu tana yin aiki a majami'ar su ta Indonesia. Shawarar da zata baiwa Krista da ke a kasashe, masu yanci mai sauki ne: "Ka nemi Ubangiji da himma domin ka iya tsayawa sosai a lokacin wahala.

***Balallene muje muna tsokanar wahala ba. Wahalarka ta al'majirasa rigaya tasan inda kake. Yesu yakan yi wa almajiransa tuni cewa jarabtar masu bi abu ne da yake tare damu a kullum. Neman Ubangiji da himma bai nuna cewa muna neman tsokanar kowa ba. A'a ribar neman kusantar Ubangiji shine zaifi taimaka mana wajen shirya mu jimre wahala ko da tazo.***
***Bamu da zabin irin wahalar da zata zo mana. Duk da haka kuma, muna iya kusantar Ubangiji sosai, wannan ya na shirya mu fustantar jarabobi.***
***Wadansu jarabobi suna iya kai mu ga rasa rayuwan mu dalilin Yesu. Duk da haka wannan ba shine sadaukarwa ainihi ba. Matsanancin sadaukarwa ya kan zo kafin, dole ne mu sadaukar da son kai a kowane mataki domin mu kara kusantar Allah da Kristi yin haka zai tababatar da yin abu maifi wuya.***

# RADADIN MAFI TSANANI
## *Sudan: Yaran Sudan*

RANA TA 17

*Amma, idan wani ya na shan wuya kamar mai bin Kristi, kada shi ji kunya, amma sai shi daukaka Allah cikin wannan suna. 1 Bitrus 4:16*

***Ku fada tare damu "sojajin suka baiwa yara umarni suna tada murya, suna shure su, suna bugunsu a fuska da ruwan cikinsu, "Allah shine God, kuma Mohammed ne annabinsa. Fadi haka!"***

Yaran Sudan kanana guda hudu sunyi kuka sunyi ihu domin iyayen su amma sunki su maimaita kalmomin da zasu kubutar da su daga sojojin amma zai zama musun addinin su na Krista. Jininsu ya fara zuba, amma suka ki musun bangaskiya ga Kristi. Sauran yara suna kallo cikin razana sun sha ganin sa'oinsu na iyali yan Kudancin Sudan wadanda mayakan Islama suna anfani da takubba suna kashe su. Yanzu kuwa suna kallo a yayinda yara kanana da ke abokansu da kuma yan uwansu wanda mafi kankanta a cikin su danshekaru biyar ne kawai suke shan duka har ga mutuwa.
Sojoji sun rigaya sun tilastawa kowane yaro mai dama daman shekaru ya kwanta akan garwashin wuta kuma aka tilasta masu suyi kalma shahada ta musulunci kuma su shiga addinin. Babu yaro guda daya daya yarda ya maimaita wadannan kalmomin duk ta tsananin azabar da suke ciki.
Akwai yara maza guda goma sha hudu da yanmata guda goma sha uku da aka kwashe a mamayar da akayi a ranar.
Ba'a sake ganin wadannan yammatan ba mai yiwuwa an sayar da su zuwa bauta ko kuma a zaman kwarakwarai a Arewacin Sudan. Dukan yara maza kuwa aka azabtarda su, amma babu wanda ya bada kai.

***Zafi ko radidi yana da dalili a shiri irin na Ubangiji. Amma ashe babu wata hanyar koyi da ta kai ga iyawarmu ta riko da maida hankali. Zafin ciwo na jiki daga wata rashin lafiya mai tsanani ko kuma jin jiki daga wata rashin lafiya mai tsanani ko kuma jin rauni yana jan hankalin mutum. Kwanya takan aika sauti ga dukan jiki domin hankalin jiki gaba daya ya komo ga rauni da aka ji. Ta haka ma damuwa mai sosa rai abu ne mai wuyar a kyale. Bakincikin rasa wani wanda muke kauna al'amura marasa dadi kamar ciwon daji ko wata cuta, ko tsanani ko da wane irin matsayi ne ya kaimu ga jin zafi ko radadi muna da zabin mu bada kai ko kuma mu kara ginuwa. Wadanda suka ji wahala suna iya zama shaidu na alherin Allah. Kamar maguji mai koyi sai ya horarda dansa domin ya kara karfi, zafi ko radadi ko wahala sune turbar girma cikin ibada.***

# KIYAYYA MAFI TSANANI

## Romania: Richard Wurmbrand

RANA TA 18

***"Ina sha'awar Kwaminisawa". Wadannan Kalmomi sun fito daga bakin Pasto da yayi shekaru goma sha hudu a kurkukun Kwaminisan, amma da gaske Richard Wurmbrand yake lokacin da ya furta haka din.***

*Kunji aka fadi, kayi kamnar makwabcinka, kaki magabchin ka: amma Ni inache maku, kuyi kamnar magabtanku, kuma wadanda suna tsananta maku, ku yi masu addu'a. Matta 5:43-44*

Kwaminisawa da yawa suna shirye su mutu domin tsare manufarsu. Sun bada kansu ga kare manufarsu fiye da wadansu da na sadu da su.

Pastor Wurmbrand dai agareshi kowane makiyi aboki ne kuma fatar sa itace mutumin ya zama Krista. Ta wurin kaunar abokan gabansa ba wai kadai ya kawo wasu ga Kristi ba amma ya kara samun budi domin yin bishara.

"A lokacinda suka hana karanta littafaina, nan da nan mutane suka fita neman litattafan don su ga wai me wannan kazamin. Yake fada 'yace ina yiwa duk wanda ya bata mani maraba. Wadansu basu da sha'awar sanin abinda zaka fada. Suna da bukatar a kalubalance su game da gaskiya kafin ka shaida bangaskiyar ka. Kuma lallene ka zama haziki. Amma a duk lokacinda zamuyi magana mu yi haka a cikin kauna. Kalamum Pasto Wurmbrand ba kalamu ne na baka kawai ba domin yana aikata abinda ya fada.

Da shi da matarsa sun marabci Hafsan Nazi a gidansu wanda yayi aiki a sansanin Bauta in da aka hallakar da dukan iyalin Sabina. A lokacin da Hafsan ya ga gafartawa su da kauna da suka nuna ma sa sai aka ci nasara da jawo shi cikin mulkin Allah. (Lura wadannan maganganu anyi sune a wata hira takarshe da Pasto Wurmbrand kafin mutuwarsa fabrairu 2001.

***Yesu ya koya mana cewa mutane zasu fahimci muke nunawa, musamman idan muka zo batun makiya, hanyar da muke bida makiya muhimmiyace. Hanyar da muke kimanta makiyanmu ma muhimmiya ce kamar dai yadda muke kimanta wadanda suke namu na cikin iyalin Krista. Alhali ma dai maida murtaninmu ga wata kushewa da akayi mana shine ginshikin nuna shaidar kirki ga addinin Krista fiye da kowane irin misali.***

***A yayin da masu bi suka yi anfani da wannan ka'ida na bangaskiyar Krista, sukan nuna irin banbancin dake tsakani shine ko ayi musun abin ko a rama. Maimakon haka masubi su kanyi kokarin fahimtar makiyansu basu nuna masu kawai ci ba, duk fiyayya da aka rungume ta ta wannan hali bata zama kiyayya ba amma takan zama wata dama ta aikata bangaskiya a kamanta yin umarinin kristi.***

# TAFIYAR JIRGIN RUWA MAI TSANANI
## Titanici: Dr. Robert Bateman

RANA TA 19

*Akwai shirye-shirye iri-iri a zuciyar mutum, amman shirin Ubangiji ne zai tabbata*
*Misalai 19:21*

***Dr. Robert bateman ya taimaki yar'uwan matarsa ya sa ta cikin karamin jirgin ruwan ceton rai. "Kada ki rude, Annie. Wannan al'amari zai gwada bangaskiyarki. Lallene na tsaya na taimaki sauran mutane. Idan bamu sake saduwa anan duniya ba, zamu sadu a sama" bateman ya jefa wa matar hankicinsa a yayin da jirgin ke nutsewa cikin duhun ruwan teku mai sanyin kankara can kasa" Ki daura wannan a wuyanki mura za ta kamaki"***

Daga nan Dr. Bateman ya tara misalin mutum hamsin a dakakin jirgin ya fada masu suyi shirin fuskantar mutuwa. Kafin wannan ranar, shi ya shugabanci sujadar da akayi akan wannan babban jirgin, sujadar da ta kare da raira wakar da ya fi sha'awa "kusanci da Allahna".

Robert Bateman ne ya kafa kungiyar Birni ta Tsakiya wato Central City Mission a Jacksonville, Florida, a amirka wacce ta zama tamfar gida mai haskakawa cike da ma'aikatan jiragen ruwa mashaya kuma bugaggu.

Ana kiransa "mutumin da ke rabawa jama'a hasken ranar mutum fiye da kowa a Jacksonville". Bateman ya tafi Ingila don yin nazari akan ayukan zaman Jama'a ta Krista kuma yana kan dawowarsa zuwa Amirka domin ya gabatarda abinda ya kawo domin anfanin jama'a.

Amma cikin daren Afrilu 14, 1912, jirgin Bateman yayi karo da dutsen kankara. Bateman ya shugabanci mutanen da ke tare da shi a dakalin Jirgin yin Addu'ar Ubangijinmu. A yayin da yan badijala suke kidi da busa ta wakar "kusanci da Allah na", babban jirgin nan titanic ya lume karkashin rakuman ruwa. An ce hanya guda daya da zata sa Allah dariya itace mu gaya masa shirinmu! A lokacin da muka karbi Kristi, muna sani cewa muna tasamma yin aiki da karfin hali, da kuru na gaske na rayuwarmu. Domin mu sami daman yin wannan mawuyacin tafiya, dolene, mu sadaukar da kanmu ga umurninsa. Shi kafin na jirgin ruwa. Shi yake sarrafa tafiyar rayuwarmu a yadda yaga ya dace, yana la'akkari da bukatun mu na ba gaira babu dalili da kuma na gaske domin cimma manufar mu. A wasu lokuta, cikin lokuta masu wuya, mukanyi tunani ko ba'a abinda ya tsara mana, ko mun kauche ko bata daga hanyarsa.

***Dawatsu masu gargada da tsaunuka suna fitowa daga gurbatattun kassai. Daren da babu farin wata yakan lullubemu a cikin duhunsa. Cikin jarabawar da muka sami kowannenmu a wannan lokaci yake samu la'akkari da yadda zamu sarrafa shirye-shiryen mu. Wannan safara ce muka fara da bangaskiya, in ma wata abuce. Shirin Allah dangane da rayuwarmu yana yi mana jagora zuwa inda mu ba mu zaba wa kanmuba. Duk da haka shi ya fi sanin komi.***

## MASANANCIN MATAKI NA BANGASKIYA

### *Misra: Shugaban Matasan Krista*

RANA TA 20

*gaskiya fa aikin abin da muke begen sa ne, tabbatawar al'amuran da ba'a gani ba.*
*Ibraniyawa 11:1*

***"Ga shirin" inji shugaban matasan Krista yana shaidawa matasa. "Lalle ne a fara raba takardun gaiyata zuwa taron a cikin University da karfe 8:30 kuma a rabar da wuri kafin yan sandan Asiri suzo su fara tambayar ku abinda kuke yi. Idan ba zaku iya baiwa wani ba, ku ajiye kawai. Allah zai kai suga hannyan da suka kamata".***

"Kana son mu rabarda takardun gaiyata kafin mu nemi izini?" Tuna min yan sandan maza da mata da ke ta faduwar gaba a kewaye da shugabansu. "Haka fa! Duba, lalle ne mu nuna karamar bangaskiya. Zamu dauki mataki na farko saura kuwa suna hannun Allah?

A Misra ana kula da duka wani taro da Krista sukeyi kuma ba'a iya yin taron sai da izini. Jim kadan bayan 8:30, Shugaban matasa ya kira yan sanda domin samun izini na taron Krista. "Lalle ne ka cika takardar neman izini, sa'anan zamu sanadda kai a cikin wata guda ko kusan haka".

"Kayi hakuri, domin mun rigaya mun fara raba takardun gaiyata na taron". Shi Krista din ya amsa wa Dan Sanda ta taraddadi. "Menene yasa kuka raba takardun gaiyata kafin ku sami izini?

Kunsan dole mu ba irin wadannan tarurukan izini. To, ina jin tunda an rigaya an raba takardun gaiyata, zan ba da izini a wannan karo".

***Daukar mataki na farko shine yin aiki da bangaskiyar mu cikin tafiyar da bamu san mafita ko abinda zai faru ba. Kamar dai yadda wasu da suka yi irin wannan tafiya zasu gaya mana, ba wai ita tafiyar ne da kanta ke da wuya ba. Amma tafiya ba "tare da sani ba" shine abin dubawa. Ba a anfani da tawwirar kasa domin tafiyar bangaskiya. Mukan yi anfanine da hasken taurarin baiwa ta Allah. Tafiya a ratse itace takan kaimu wurin da ba zamu iya hango babban hanyar ta rai. Sai da karfin hali da bangaskiya masubi sukayi kasadar raba takardun gaiyata zuwa taron da basu rashin tabbatar ko zai yiwu ba ko ba zai yiwu ba. Allah ya albarkaci matakin bangaskiya da suka dauka inda mutane dari uku suka karbi Kristi a wannan daren. A shirye kake ka dau matakin bangaskiya?***

***A lokacin yakin baya an koya***
***mana cewa idan muna so***
***mu cinma manufarmu,***
***lalle ne mu zama da shirin fadada....***
***Mun sani cewa amsa guda***
***daya ce kawai yayin da***
***kasarmu ta bukaci mu***
***tsaya mata don yancinta -***
***duk da haka a lokacin da***
***Ubangiji Yesu ya ce mu wa'azantad***
***da duniya kome wuya, a kullum***
***mukan amsa ba tare da cewa komai ba.***
***Ba zamu iya tafiya ba.***
***Mukan ce tsadar ta yi yawa...***
***Masu bishara a kullum suna***
***fuskantar abubuwa iri-iri.***

**NATE SAINT,**

***Mai Bisharar da tayi Shahada a Kungurmin***
***Dajin ekudo Rian a 1956.***

# MATSANANCIYAR DOKA

## Laos: Masubi

RANA TA 22

*Amma Bitrus da Manzannin suka amsa suka ce,*
*"*
*Wajibine muyiwa Allah biyayya fiye da mutum.*
*Ayyukan Manzanni 5:29*

***"Jan hatimi mai nahisa da aka buga a karkashin shafin wasikar yana nuna dagin ofis na kwaminis yankin unguwarsu a Laos. Ga masu bi na unguwar, kalamun da ke kunshe a takardar ya fi nahisa nakisa a garesu".***

"Idan kowane mutum, daga kowace kabila, koma kowane iyali, har aka rudeshi ya shiga wani addini kamar na Krista ko wasu, dole su dawo zuwa addinin da suka yarda dashi a da" Wasikar ta fadi haka. "An haramta yada wannan addini. A kashin haka wadannan masu bada gaskiya dole ne su tashi su koma sababbin unguwanni. Idan akwai wani kauye ko iyali wadanda suka yarda da wani addini... Mambobin kwamiti na unguwar su dauki sunayensu da yawansu a aika zuwa babban ofis domin nazari. Zamu so sanin musamman gida nawane suka bada gaskiya ga Kristi kuma su krista ne a yankin." Kwanan watan takardar Yuli 8 1996 Kwamiti ta babban ofis ce ta sanya hannu.

Ba da jimawa ba a baya an tilasta wa kristocin Laos da bakin bindiga susa hannu a takarda cewa suna musun juyawarsu zuwa addinin Krista. Gasu marasa yarda da Allah a gwammatinsu, kamar gara wasu addinai ma za'a iya saurara masu fiye da bautawa Kristi.

Baicin duk abinda gwamnatin takeyi majami'ar da ke Laos sai kara habaka takeyi a yayinda Krista suke bisharar bangaskiyarsu gabagadi.

***A lokacinda dokar dan adam tayi gaba da dokar Allah, dole ayi zabi. Ko mu hakura da dokar mutum ko kuma muyi na'am da dokar Allah kuma mu yi jiran sakamakon bin dokar Allah kome wuyar yin haka. Manufar mu ita ce salama. Bai kamata mu maida al'amuran dan adam su zama na gaba ba. Misali gwamnatin Amirka tayi doka cewa an hana yin addu'a a makarantu. Ba zasu iya dauke addu'a daga mutanen da suke so suyi addu'a ga Allah ba. Wasu suna iya yin dokar tafi haka tsauri. Amma dokar Allah ta sha kan na mutane gama shine Sarkin dukan zukata. Mu amince muyi biyaya da Allah maimakon dokar dan adam.***

## MATSANANCIN DAN FASA - KWAURI

### Kasar Sin: Mai Gadi Nee

RANA TA 23

*Sabo da wannan nake shan wahala nake fama da matukar himma wanda yake sa mini ta karfin ikon sa.*
*Kolossiyawa 1:29*

***"Mai gadi da ake kira Nee dan kasar Sin ne kuma shugaban majami'a wanda yake da sauran sa'oi shida kacal na rayuwa kafin a zartas da hukuncin kisa a kansa. Ya zama wajibi ne a gareshi da ya rinjayi mai tsaro da ke Gadi a kofar Kurkukun da ake tsare dashi ga karbar Kristi, domin wasikar karfafawa da ya rubuta na Krista da ke majami'a ta sami kaiwa a garesu a can waje daga kurkuku".***

Gwamnatin Shugaba Mao ta Kasar Sin ta fusata da irin yaduwar da addinin Krista ke yi a kasar, saboda haka abin da yaga ya kamata shine a dakatar da wannan bakuwar al'ada da ta shigo masu. Sun kori ko kuma sun kashe da yawa, da yawa kuma daga cikin shugabannin gidajen addu'a an kaisu kurkuku.

Nee ya shaidawa mai tsaron nan batun kaunar Uba da kuma yarda da yayi na bada jikin`sa da jininsa domin shi wannan mai tsaro ya sami rayuwa na har'abada a cikin aljannah. Sa'oi biyar bayan wa'azi da ya saurara, mai gadi ya karbi Kristi da hawaye sharban a idanunsa. Watau wani karin rai ya sami shiga mulkin sama, haka kuma ya zama dadin tabbatuwar isar wannan wasika da Mai Gadi Nee ya rubutawa masubi kamar yadda ya saba aikawa.

***Idan har akwai abubuwan da Shahidan Krista suka koya mana to shine cewa muyi anfani da kwakwalwa don kirkiro hanyoyi masu karfafawa domin cigaban bishara. Fasahar su, karfin halinsu kai har da azancinsu na farfadad damu garin yin sha'awar yada bishara. Ko da ya ke ba kowa ne ke samun zarafin yin fasa kwaurin litattafan bishara zuwa cikin kasashe marasa yanci ba amma duk da haka muna iya zama talikai masu marmarin mulkin sama. Yana nufin cewa azuba idanu akan hanya domin makwabta. Yana iya zama saduwa da mutanen unguwa wajen taro. Sababbin hanyoyin yada bishara na iya zama da kasada. Amma lallene mu zama masu marmarin daukar kasada maimakon daukar matsayin tsaka-tsakiya. Wannen ke bayyana rayuwarka ta yada bishara a yau mara sha'awa kuma dan tsaka-tsakiya? Ko kuwa mai fasaha da kuzari domin Kristi?***

# MATSANANCIYAR MALLAKA

## *Peru: Pasto Zapata*

RANA TA 24

***Ku kula fa kuyi nesa da kowane irin kwadayi da yawan kaya ba shi ne rai ba.***
***Luka 12:15***

***"A Peru Krista ba su sa rai ga samun wani abu domin bautar yesu", inji Pasto Zapata" Ana bukatarsu su bada wani abu". A bayan wani kauye mai dutse, Pato Zapata ya nuna wa bakinsa jeren fararen giciye da akayi da hannu, kowanne giciye guda yana a madadin Krista guda da kwaminis suka kashe. Kwance a kasa a gaban Pasto Zapata a gidansu a cikin kauyen wata gawa ce ta wani Pasto da yan Sari-ka-noke suka kashe. An rufe gawar da mayafi, kewaye da fitilun kandir kuma yan'uwa kewaye da ita suna makoki***

A waje kuma cikin ruwan sama Ikkilisiyar Paston da aka kashe suna wakokin yabo. Takalmarsu cike da tabo. Yan sari-ka-noke sun lalata majama'ar su, suka kuma kona gidajensu masu dimbin yawa. Duk da haka suna raira wakokin yabo.

Wadannan Krista ba su fita daga hadari ba, domin yan sari-ka-noke suna iya dawowa a kowane lokaci. Pastoci ake nema kullum domin sune suke karfafa kauyen gaba daya su tsaya gaba da shigowar manufar Marxist (Koyarwar cewa babu Allah).

Pasto ya tunadda masu saurare cewa littafi mai Tsarki yana yi mana kira mu bi Allah, ba abubuwan albarka da su ka zo ta hannun Allah "Don me ka sayi riga? Ya tambayi mutane. Domin yin anfani da ita. Menene dalilin da Yesu ya fansheka da jininsa? Domin yayi anfani da kai a cikin mulkinsa'

***Wadannan matalautan masu bangaskiya sun shirya domin Allah yayi anfani dasu. A duk yayin da aka tsananta mana domin bangaskiyarmu abu ne mai sauki mu manta da asarar da muka yi. Mun yi bakin cikin abokanmu na da wadanda suka kimu don abubuwan da muka gaskanta su. Muna iya rasa hanyoyin kasuwancin mu na da. Mukanji ba dadi a yayin da aka kebe mu daga cikin gajiyar ayukan alheri na yau da kullum. Duk da haka, akwai wasu dayawa da suka yi hasarar fiye da kayayyakin da suka mallaka ko kuma danganta wadda babu tasiri wadannan jajarjun masu gaskantawa sun zura idon akan abubuwan da suka rage a bayar ba akan abinda ya rigaya ya bata ba. Dayawa a cikinsu sun rasa majami'oinsu, gidaje, ayuka, da iyalansu saboda addini. Duk da haka suna shirye su bayar dayawa ta wurin hadaya domin dalilin kristi. Sun gane cewa hasarar da suka yi a duniya wata dama ce ga mutum ya sami ceto.***

## RAZANA MAI TSANANI

### Laos: Lu

RANA TA 25

***Tsarin dokoki da ke ba rubutattu ba ne na Yansanda sanannu ne. Idan an kama mutumin khumu ko kuma wasu yan kabila sun tuba sun zama Krista a kamasu. Inda an kama wani yana yiwa yan kabila wa'azi a kashe shi.***

*Ubangiji shine haskena da cetona kuma tsoron wa zan ji? Zabura 27:1*

Bayan an sa "LU" a sarka hannu da kafa kuma aka ci zarafin sa aka zagaya kauyen dashi a haka. Sai yansandan kwaminis suka jefa shi a rami. "Zamu sake ka" suka ce. "A lokacin da krista guda dari daga kauyenku suka yi musun addininku" Amma basu iya sami Krista da suka juya bayansu ga Kristi ba. Ana haka kenan sai hatsari ya auka ga Yan Sanda. Dan wani hafsan su yayi hadari ya sami karaya a kafafun sa biyu. Daya dan nasa kuma ya kwanta babu lafiya. Wannan hafsa wanda yasha azabta masubi ya sami bugun zuciya ya mutu.

Sauran hafsoshi cike da tsoro suka janyo "LU" daga rami suka bar shi ya koma gida. Masu mulki suka tsorata sosai su dau mataki akan masu bi da ke cikin kauyen ganin abinda ya faru akan shugabansu. Ganin cewa ikon Allah yafi na karfi, sai yan khumu da yawa suka tuba. Wurin da yake a ada masu bi guda dari ne yanzu sunkai dari bakwai. Har sun aika Kristoci waje su fada masu labarin Yesu. A yayin da masu mulki a Laos, suka tsorata, masu bi a maso gabas ta Asiya, sun zama nasu.

Tsoro yana daya daga cikin abubuwan da suke girgiza dan Adam. Ita take razana kasuwar duniya haka kuma farashin danyen mai. Ana iya anfani da kangararren domin yin abu mai kyau. Galibi akan fadawa gwananyen dambe cewa su ma'abotan tsaro ne. Tsoro yana iya sa su zama yan dambe sosai. Fadakar dasu. Tana gyara niyyarsu.

***Haka kuma Allah yana iya anfani da tsoron mu ya maida mu mayakan sa na gaske. A duk yayin da muke cikin jin tsoro akwai damar iya yin bazata. Me ya sa? Abinda muke ganin ba zai yiwu a garemu ba yana jiwuwa ta ikon Allah.***

***Tsoro yana iya sa muyi taimakon Allah. Tsoro yana iya sa muyi watsi da madogarar mu, a maimako kuwa mu dogara ga Allah. Ta haka matsanancin tsoro zai kai ga matsananciyar bangaskiya.***

# KAYAN ADON AINUN

## *Sudan: Peter*

RANA TA 26

***Ana kiran mari na farin karfe da larabci bacle. Peter ya rike marin a hannunsa kamar wani tsatsarkan abu. Abu ne na tunawa da tarihin iyalinsa da kuma albarku da ya samu.***

*Kuyi addu'a babu fasawa.*
*1 Tassalonikawa 5:17*

Kakansa ne yayi wannan marin amma ba wai sana'ar sa ce ba. Alhali Malaman Islamiyarsa ne suka tilasa masa da ya dinga sawa. Doka ce daga wani musulmi da ya sayeshi a zaman bawa a yayin da aka kama shi a kudancin Sudan aka kai shi arewancin Sudan inda aka saye shi a zaman bawa. Ko da shike ana kwarzabar sa ana azababtashi watau su iyayen gidansa musulmi amma bai juyawa bangaskiyarsa baya ba, ya rike bangaskiyarsa a cikin Kristi kuma tabbunan jikinsa sun tabbatar da dagewarsa. Domin kawai shi ba musulmi ba ya sa an maida shi cewa da shi da dabba ma babu bambanci. Jim kadan kafin ya rasu kakan Peter ya sa aka cire marin aka baiwa mahaifin Peter "Zuriyar mu ba za su cigaba da zaman bayi ba", in ji shi. "Amma lalle ne kada mu manta". Daga baya baban Peter ya ba shi ya dauka ya tafi da shi a lokacinda ya tsere daga gidan musulman da suke da shi, zuwa yanci. A yau, wannan marin bai kara zama shaida ta bauta ba amma shaida ce ta ce ta ikon Allah. Alamace ta hannun Allah akan iyali, ta ratsa jinsuna uku don kawo su ga yanci.

"Kada ku manta mutanena, ya roka". "Kada a daina yin addu'a domin Krista da ake wa tsanani a Sudan".

An kama kakan Bitrus a Sudan ta kudu, aka kai Sudan ta Arewa, ina aka sayarda shi, a zaman bawa. Kakan Bitrus, ko da yake malaman Islamiyya sun tsoratar da shi sun kuma gallaza masa, amman ya ki shiga addininsu. Ya rike bangaskiyar sa a cikin Kristi.

Mantuwa, itace magabciya ta farko ga addu'a. A shirye muke mu zama masu hada taimako ta wajen yin addu'oi. Amma kyawawan manufofinmu basu cika yin kyau da zasu kai mu ga cika alkawarin mu na yin addu'a domin mabukata. Menene zai iya tunatad da kai yasa kayi addu'a domin wadanda ke cikin tsanani a bangaren na kusa da kai. Watakila don karamin shaida a fuskar agogonka, zai tunasheka. Duk lokacin da ka dubi agogonka, a dukan yini zai iya zama zarafi ka tuna da wata kungiya da ke zama cikin tsanani. Ko da wace hanya ka zaba na lokaci da ka nasayir addu'a sai ka bi da shi.

***Karatun labarai akan taurarun masu bi, ba zai chanza komai ba. Amma addu'a domin masubi na kwarai zai chanza komai - watakila ko yau.***

## MATSANANCIN KARFIN HALI MACHE

### *Romania: Wata tayi Mache*

RANA TA 27

***Can kusan tsakar dare mata da ke tsare a kurkuku suka ji isowar yan kwaminis masu gadi. Sai suka yi maza suka kewaya matarda aka yanke wa shari'ar kisa wata mata mai karancin shekaru 20 kacal wacce aka zartas a kashe ta don bangaskiya ga Kristi. Suka rada mata sallama a kunnen ta Babu hawaye a idanun wannan mata yar romania. Babu kuma kuka da neman wai su tausaya mata.***

*Domina gareni, ni rai Almasihu ne, mutuwa kuwa riba ce. Filibiyawa 1:21*

Baya kadan a wannan daren tsararun sun saurareta. Fuskanta cike da kauna. "A gareni wannan kabarin shine kofa ta inda zan bi na tafi birnin dake samaniya". Ta fada masu. "Wanene zai iya bayanin kyaun wannan birnin?" Can ba'a san bakin ciki ba. Can kuwa farin ciki ne da raira wakoki. Kowa yana cikin fararen sutura ta tsarki zamu iya ganin Allah fuska da fuska. Akwai murna da farin ciki da harshen dan adam ba zai iya bayani ba. Me zai sa na yi kuka? Me zai sa na yi bakin ciki". Ana shirin aurenta amma a wannan dare abin maimakon zama da angona na duniya zan sadu da Angon Samaniya. Masu gadi marasa tausayi suka shiga ita kuwa sai ta nufo su tace mu tafi. Bayan da ta fita daga dakin ajiya kewaye da masu gadi sai ta sama haddace maganar Apostle Greet. Jim kadan hawaye cike a fuskokinsa, sai sauran tsararru suka ji karar bindiga. Masu kisan sun gama da rayuwar wannan budurwa, amma sun aikata in da zata zauna har abada a wurin mafi kyau.

***Karfin hali shine gadar da zamu iya hawa mu haye zuwa a tabbatar da begen raguwa ta ruhaniya daga wannan duniya. Su wadanda suka fahimci tabbatar rayuwar ta ruhaniya mutuwa sukan sami saukin yarda da sake halayen su da kaskantar da kai a duniya domin samun dawwama har abada a samaniya. Karfin hali ya kan sa mu bar abin duniya da suke kwadaita mana rayuwar duniya. Sai da karfin hali zamu gaskanta cewa akwai rai bayan mutuwa. Bayan haka rayuwa a duniya ita kadai muka sani sauran kuwa sai bayan an mutu. Ainihin hasken halinmu shine aiki da bangaskiyarmu da yarda cewa Kristi ya bamu ikon hayewa zuwa rai madawwami tare dashi. Da zarar munyi wannan za mu iya fuskantar rayuwa da dalili da mutuwa da karfin hali.***

***Ba addu'a muke wai a bude iyakokin kasarmu ba. Muna addu'a domin sama ta bude.***

***Addu'ar wata Majami'a dake cikin tsanani a Vietnam***

## MATSANANCIN AIKE

### *Bhutan: Pasto Norbu Promila*

RANA TA 29

*Na tabbata shi wanda ya fara kyakkawan aiki gareku, zai karasa shi, har ya zuwa ranar Yesu Almasihu Filibbiyawa 1:6*

***Pasto Norbu Promila yana cikin jin dadin wa'azi da yake yi wa jama'a lokacin sijada ga yan kabilar kauyen da ke cikin duwatsu Bhutan. Wadanda suka taru suna sauraren bishara. Amma ana cikin tsakiyar wa'azi sai ga yan sanda suna ta shigowa ta kowace kofa suka tasamma bagadi suka cafke Norbu da karfi.***

An jefa pasto Norbu a kurkuku kuma aka azabtashi kuma hukuma suka umurce shi da yayi watsi da aikinsa na yin wa'azin bishara. An yi masa mummunan raunuka kafin su sake shi. Ya dawo wajen iyalinsa inda matarsa da yayansa suka yi bacin rai daganin raunuka da jinin da yake fuskansa. Bayan kwana goma sai ya mutu a sanadin raunuka da aji masa. Magoyan bayan Pasto Promila suka ki su dena wa'azi

Bayan mutuwarsa kadan, sai suka hadu suka kira yan sa kai su cigaba da aikin Norbu a cikin yan kabilar. Mutane biyar suka mika hannu daya daga cikin hannayen na matarsa ne. Ta amsa kiran Allah zuwa bishara, yayin ta ke kula da yayanta guda biyar.

***Abubuwan da muke yiwa Ubangiji ba wani aikine kawai ba - cika umurni aiki ne ba magana ce ta mutum daya bane. Tana nufin zura ido ga Krista, da mulkin sa. Saboda haka mutumin da yake shugabantar wani aiki takamaimai a wani wuri yana iya bari, amma cikin ba zai mutu ba. Ba a taba barin aikin Allah ya lalace ba. Cigaba ya ke yi hara abada har sai an kamala. Su wadanda suke ashirye domin shan tsanani domin bangaskiyarsu suka koya mana abin da cika umurni aiki yake nufi. Sun san cewa akwai abubuwa guda biyu da ke dawwama. Aikin Allah da Ruhun mutum.***

***A lokacin muke niyyar zuba jari ranmu a cikin wadannan abubuwa muna sa kanmu ga cika umurni mai fa'ida madawwani.***

# MATSANANCIN MAI KISAN GILLA NA DAYA

## *Bangladesh: Andrew*

RANA TA 30

***Mai bishara, Andrew, ya dubi cikin ramin bindigar da aka auna shi da ita, yana mamakin abin da ya hana mutumin jan kunamar. Mai kisan gillar ya ga takaici kuma ya tsorata, daga nan fa sai ya fice daga cikin dakin.***

*Na sani ka iya yin komi ba kwa wani nufinka da zashi hanuwa. Ayuba 42:2*

Tarho yayi kara Andrew kuwa da ya sami kansa yana magana da wanda ya zo da niyyar kashe shi jim kadan baya. Shugabannin musulmi sun bani babbar lada domin na kashe, ka, inji makashin, na ratsa Bangladesh kafin in zo offishinka. Ladan nawa ne, a shirye nake nayi harbi, amma sai na kasa motsa hannu na. Na kasa matsa kunamar bindigar. Mai bishara ya yabi Ubangiji domin kiyaye shi da yayi.

Andrew ya ga abinda kamar na ban dariya. "To yanzu me kake so nayi maka?" Ya tambaye shi. "Ranka ya dade har yanzu bana iya motsa wannan hannun kuma duk a dalilin na ne! Zaka iya taimako na?"

Nan take akan waya Andrew yayi addu'a kuma nan take mutumin ya motsa hannunsa kamar da. Mamakin wannan abin al'ajibi mutumin ya koma wajen mai bishara yana tambayoyi akan "Yesu" wanda a ganinsa shugabannin musulmi suke jin tsoro. Mai bishara ya dau lokaci a tsanake ya bashi labarin kaunar Yesu, har ma ya baiwa mutumin da yazo kashe shi shayi domin ya sha.

Bayan minti 45 mutumin yayi addu'a ya karbi Yesu a zuciya tasa. A yau shi mai bishara ne a Bangladeshe.

***Shirin mutumin nan na yayi kisa shiri ne mai kuskure, da ace shiri ne na majigi da masu kallon majigin sun tafa wa Andrew a lokacin da ya shigo fili. Ranar kamar ko nene gwarzon silma Andrew ba wai kawai ya ci nasara da shirin abokin gaba ba. Amma ta gighita su har ma ya kai ga shan shayi tare da shi wanda a da yazo da niyyar yayi kisa amma sai ya zama tubabben. Wannan kuwa ba shine shirin su ba lalle ne sai da shaida ya koma ya sake wani shirin na hallakamu domin wannan dai ya sha ruwa. Andrew bai zama mai laifi a halin da ya sami kansa ba haka kaima. Idan da an harbe shine da mutuwar sa zata zama shaida haka kuma da kaine. Ba kamar shirye shiryen shaidan ba, shirin Allah domin rayuwarka baya wargazuwa.***

# MATSANANCIYAR SHELA
## *Romania: Sabina Wurmbrand*

RANA TA 31

***Sabina Wurmbrand ta tsunkuni hannun mijinta. "Richard", "ta yi kira da bacin rai, "tashi tsaye ka wanke wannan abin kunya daga fuskar Kristi. Suna tsarta miyau a fuskarsa!".***

*Cikin ikon alamu bai cikin ikon Mai Tsarki, har na yi wa'azin bisharar Kristi sarai tun daga Urshalima da kewayen ta har zuwa Ilirikun*
*Romawa 15:19*

"Idan nayi haka" Richard Warmbrand ya amsa, yana kallon matarsa da nufi, "zaki rasa mijinki".

Suka yi arbaz a idanu" Bana son rago a zaman mijina". Suna zaune ne a dakin shawara majalisar kasa ta Romania inda ake taron kasa akan addini jim kadan baya sojojin kwaminis sun shigo sun mamaye Romania.

Tarin Pastoci, Firis-Firis da Shugabannin Krista daga dakinsu dabam-dabam sun tashi, daya bayan daya suna yabon Joseph Stalin da kuma sabon shugabancin kwaminis, wadanda suka sa dubban Krista a kurkuku.

A lokacinda Richard ya tashi dayawa suna zaton wannan sanannen Pasto zai goyi bayansu. Amma maimakon yabon kwaminis, ya yabi Yesu Kristi a zaman hanya kadai ta samun ceto!" "Biyayyarmu tafarko" ya fadawa taron", kamata ga taron zuwa Allah ne ba ga shugabannin kwaminis wannan an watsa kai tsaye ta hanyar sautin rediyo a duk kasar dubban mutanen kasar sun ji kalubalan tar da Richard ya yi.

Ganin irin barnar da Richard yake yi shugabannin suka yi cha a kansa, suka ruga kan dandalin da ya ke tsaye, sai Richard ya sulata ta kofar baya, amma sai aka shiga farautarsa tun daga wannan rana. Daga baya ya yi shekaru goma sha hudu a kurkuku.

***Maiyiwuwa mafi yawa daga cikin mu ba zasu sami damar fuskatar kalubalen sanin matsayinsu domin Kristi gaban babban taro na kasa gaba daya ba. Amma an kira mu duka mununa matsayin mu dominsa a ko'ina a kowace rana. Ba yawan taron masu saurare ne maganar ba amma sahihancin matsayin domin Kristi shine makasudi. Maiyiwuya rayuwarmu ba zai ta'allaka da abinda muka fada ba. Amma ayyukan mu za su ta'allaka da shawarar mu ta furta matsayinmu. Yana iya kawo rasa dangantaka, ya na iya kawo rabuwa da iyalinmu, ta kowane hali, ya fi anfani mu jimre wa sakamako matsayin da muka dauka maimako muyi dana sani. A yaushe kuma a ina zaka sami damar nuna matsayinka domin Kristi a yau?***

# MATSANANCIN DATTAKO

## Japan: Ibaragi Kun



***Bayan ana shar'anta su duka kuma an same su da laifi, kuma aka basu hukumcin kisa, Krista guda 26 aka tasa keyar su zuwa inda wasu giciye munana ke kafe. Watanni uku baya ne aka kama su a kyoto ta kasar Japan, aka tuhume su da bin Kristi. Daya daga cikin su ana kiransa Ibaragi Kun.***

Ganin kankantar Kun wani ma'aikaci ya ja shi a gefe ya matsa masa da yayi musun bangaskiyarsa don ya ceci kansa daga hukumcin kisa. Ya dubi wannan mutumin a ido. Kun yace masa, "Ranka ya dade, zai fimaka alheri idan kai da kanka ka juyo ka zama Krista, sa'an nan zaka iya tafiya aljanna tare dani".

Wanan ma'aikaci cike da mamakin bangaskiyar yaron. A karshe sai yaron ya tambaye shi "Ranka ya dade wanene nawa giciye? Gigitaccen ma'aikacin ya nuna masa giciye mafi kankanta a cikin guda 26. Kun kuwa ya ruga a guje ya nufi gurin da zuwa sai ya durkusa ya rungumi giciyen.

A lokacin da sojojin suka fara buga kusa a hanayensa da kafafunsu a jikin giciyen, baiyi kukan zafi ba. Ya rungumi kaddara cikin karfin hali domin ya san haka. Allah ya nufa da rayuwarsa. Giciye mutanen nan Krista guda 26 a ranar 23/11/1596 shine mafarin karni na bakin tsannanin da Krista suka shiga a Japan.

***Fiye da shekaru 70 Krista da a aka kashe sun kai miliyan Kristocin Japanis sabo da bangaskiyarsu. Da yawa sun rungumi giciyansa kamar yadda Ibaragi Kun mai tsananin dattako amma mai shekara goma sha biyu kawai yayi dattako na ruhaniya ba'a auna shi da mizanin takardar haifuwa, bin yawan shekaru bashi da masaba da sanin matsayi domin Kristi. Maimako Datakas na ruhaniya ana auna shine daya bayan daya a kullum. Haka kuma ya kamata mu auna irin dattakon mu ta wurin yadda muke yin anfani da bangaskiyar mu. Ba kamar yadda ake cewa ba wai, dattakon ruhaniya ya ta'allaka ne ga zurfin sanin littafi Mai Tsarki. Mutane da ya sun san Littafi Mai Tsarki amma su baki ne ga dattakun ruhaniya. Kullum ka tambayi kana shin "yaya munyi kama da Yesu yau fiye da jiya?" Amsar mu itace ala'mar irin girman ruhaniyarmu.***

# MATSANANCIYAR YARDA

## Philippines: Budurwa

RANA TA 33

***"Zani na" yarinya tana fadan kalmomin da ba a ji sosai dai don lebunanta suna kumbure, "idan an yarda a bani zane na ina so inrike a guri na".***

*Domin Allah shine mai aiki a sukatan ku ku nufi abin dake kyakkyawan nufinsa. Filibiyawa 2:13*

Krista da suke kewaye da gadon da take kwance suna cikin bakinciki, domin irin rauni da akayi mata, likitoci basu da sauran wani taimako da zasu iya yi mata. Makonni baya masu bi sun saya mata wani farin zani domin bukin sabuwar rayuwarta a cikin Kristi Yesu. Mahaifinta bai ji dadin shawararta na bin kristi ba. A cikin buguwa wani dare ya hau diyar da duka da shuri. Ya barta a titi cikin tabo wai don ta mutu anan.

A lokacin sujada ba'a ganta ta acikin majami'a ba. Abokanta krista suka fita nemanta. Suka same ta a som a tarin farin zanin ta da aka sayo mata cike da jini da tabo. Aka kaita wajen likita, amma raunukanta masu tsanani ne. Yanzu kuma tana tambayar zaninta. Abokanta suka ce mata zanin ya lalace:. Suna kokarin dauke tunaninta daga batun zani, domin zanin ya lalace da jini da tabo zai sa ta karaya. Da bangaskiya irin ta yar shekaru goma da haifuwa, sai tayi rada, ina son in nuna wa yesu zanena. Ya zubarda jininsa domina. Ina so Yesu ya sani cewa nima a shirye nake na zubar da jinina domin kaunarsa".

Jim kadan bayan wannan sai yarinya ta mutu. Allah bashi da sha'awar iyawarmu. Gwanintarmu kan gadon mu, dukiyar mu, kurewar ilimin mu, fasaharmu, farin jinin mu, da ba da kanmu domin aikin Allah, duk da haka bai kai mu bada kanmu domin aikin Allah.

***Iyawarmu magana ce ta kanmu muna iya ganin kanmu cewa muna yin kaza da kaza domin Allah. Akasin haka samun damarmu na domin Allah yake nuna iya kwatantawa ne kawai a zuci yadda Allah zai yi anfani damu a cikin aikin sa. Bada kai cewa kana da lokaci domin aikin Allah yana nufin a shirye kake kayi biyayya ko da menene mu. Allah yana so mu bauta masa ba lalle sai ta hanyarda muka gwanace ba. Ta kaka zamu yarda muyi aikin Allah, annan din ma baiwa ce daga Allah. Shi yake bamu himma sa kai ko bukatar zama a shirye domin sa.***

## TUNI MAI TSANANI
### *Sudan: James Jeda*

RANA TA 34

*Ya kanyi wa Allah na godiya a duk lokacin da na tuna daku. Filibiyawa 1:3*

***"Debo wasu itatuwa!" Sojojin suka tsawata wa dan saurayi James Jeda a zatonsa Sojojin suna so su dafa abinci dare. Baya kadan a wannan ranar ya ga abin tashin hankali watau yadda yan ta kife na sojojin Islama suka kashe iyayen sa da yan uwansa guda hudu a kudancin Sudan. James kadai suka bari a raye domin suyi anfani da shi a zaman mai'aikaci.***

A lokacin da wutar ta kama sosa, James, yayi mamaki kuma ya razana a lokacin da suka damke shi, kuma yayi kokarin kubucewa ya gudu. Amma sojojin suna da karfi suka kuwa daure hannayensa da kafafunsa.

"Labari mai kyau dominka samari". Inji daya sojan Zamu barka ka rayu. "Amma sai ka zama musulmi" Ba zan zama musulmi ba James ya fada masu "Ni Krista ne".

Jin haushin bangaskiyar yaron, sojojin suka dauke shi suka saka shi a cikin wutar. Suka kwashi kayansu suka bar gurin da tabbacin James zai mutu.

James bai mutu ba, yayi kokari ya mirgine, daga cikin wutar ya nemi taimako. Likitoci sunyi aiki akan James har ya sami sauki, amma yana dauke da tabbunan wannan rana. Jikinsa cike yake da facin na fatarsa da ya kone kuma hannunsa daya yana kasa don tsananin kuna. A sama wadannan tabbunan zasu zama da daraja kuma abin tuni na ranar da James Jeda ya ki ya juya wa Kristi baya.

***Yawancin mutane masu sha'awar sayen kayan tsaraba, da wuya matafiyi ya kasa ratsewa ya shiga anti a filin jirgin sama ko tashar jirgin kasa ba tare da nuna sha'awar sayen wani abu dan tunawa da tafiyar. Menene zan tunasshemu mafi muhamman abubuwa da muka gani a rayuwarmu. Bada kammu ga Yesu Kristi? Wadansu zasu dubi chakin albashinsu su kuma da karin girma da suka rasa domin basa son su bada kai bori ya hau. Wadansu idan suka ga azuzuwan makarantun gwamnati za su tna inda suka fara koyon ido-ido da shan tsanani. Wasu za su ga kushewar mai bangaskiya, nan za su tuna da manufar mika kai. Wadannan tsarabe-tsaraben suna daga cikin muhamman abubuwan da suke tunashe mu dangane da halin da zamu sami kan mu a***

*Ina ji a jikina cewa ana addu'a*
*domina ko da shike*
*ba na sane da kome kuma ban sani*
*wasiku ba, na kanji dumi*
*kamar ina gefen wuta wani lokaci*
*wannan kan faru dani*
*a cikin kurkuku da yake da sanyi.*
*Na kanji kamar wani na yin*
*addu'a domina kuma yana*
*tunani a kai na.*
*Wannan ya karfafani sosai.*
*Abin na da wuyar bayani...*
*Ina ji kuma ina sane*
*da cewa ba a manta da ni ba.*
*Wannan kadai ma ya isa na*
*jimre matsanantan lokatai.*

*TRINA RATUSHINSRATA*
*CHRITIAN (POET) SHA HA*
*RARREN MAWALLAFIN*
*WAKOKIN DA AKA TSARFA*
*A SOVIET HAR 1987*

## RASHIN ADALCI MATSANANCI

### Romania: Pasto Florescu

RANA TA 36

*Ba zai fid da zuciya ko ya karai ba.*
*Kafa sa ya gaskiya da adalci.*
*Ishaya 42:4*

***Pastor Florescu ya kasa jimre ganin yadda ake yi wa dansa duka a hannun hafsoshin kwaminis. Shi kansa ya rigaya ya sha duka, kuma baiyi barci ba har sati biyu domin tsoron beraye masu cizo wadanda kwaminis ke zurawa a cikin kurkuku. Yan sandan Romania suna so Florescu ya tona asirin mambobin majami'ar karkashin kasa domin su ma a kama su.***

Da suka ga duka da azaba bai biya musu bukata ba, sai yan kwaminis suka kamo dansa Alexander me shekaru goma sha hudu kacal, suka fara dukan sa. A yayinda Florescu yake kallon dukan dansa sukayi ta jigan dansa babu tausayawa suna gaya wa pasto cewa zasu yi masa duka har mutuwa in bai fadi inda masubi suke a boye ba. A karshe a cikin fushi, Florescu yayi masu ihu don su tsaya.

"Alexander zan fada masu abin da suke so" Ya fadawa dansa, "ba zan iya kara jimirin ganin irin duka da ake yi maka ba". Jikinsa ya sha gabza daga hancinsa kuwa sai jini ke zuba har ma da bakinsa, Alexander ya dubi ubansa a fuska "Baba kada kayi mani rashin adalci zama Uba maci amana. Ka tsaya da karfinka! Idan sun kashe ni zan mutu da kalmar yesu a lebuna na".

Karfin halin yaron yasa masu gadin kwaminis sun fusata har suka kashe yaron da duka Ubansa kuwa yana kallon abin da ya faru, ba kawai yaron ya dagewa ga bangaskiyarsa, amman ya taimakawa uban shi dage da bangaskiyarsa.

***Wai shin babu adalci ne a duniya? Al lokacin da muka karanta labarin munanan abubuwa da ake yiwa mutane marasa laifi dole ne mu yi mamaki. Bangaskiyar mu tana iya girgiza duk lokacin da muka ji wahalun da ake sha a hannun mugaye. Muna iya samun karayar zuci ko damuwa idan aka sami jinkirin tallafa mana. Wai shin babu adalci ne a duniya? Domin amsa kukanmu littafi Mai Tsarki yana koya mana kaidar "I da tukuna" I wadansu mugaye sukan hadu da sakamakon aikin su ba tare da bata lokaci ba. Duk da haka shari'ar Allah wacce bata karewa kuma wacce bata da karshe, bata fado akan duniya ba tukuna.***

***Wanan abu n da Allah ya ajiye har sai karshen zamani, mun gaji da jira amma bai canja ra'ayinsa ba, kuma wannan bai canja shirin Allah ba.***

# AMSOSHI MASU TSANANTA

## *Cuba: Tom White*

RANA TA 37

***A lokacin da aka sa wa Tom White kokuwa a ka, bai sani ba ko zai sake ganin haske "Ina zaku Kaini"? Ya tambayi yan tsaron Cuba. Amma basu ce kome ba.***

*Hakanan kuma domin muna marmarinku da soyayya, muka ji dadin baku ba Bisharar Allah kadai ba amma har da rayukan mu, gama kun zama abin kauna kwarai, garemu.*
*Tass. 2:8*

Tom ya shekara bakwai yana kai takardun bishara a cikin Cuba a boye. Dashi da wasu sun zubo takardun bishara daga cikin jiragen sama zuwa cikin teku da tsibirin kwaminis. Amma bai taba samun labarin cewa takardun nan sun isa hannun Krista na cikin Cuba ba. "Allah ina rokonka" in ji Tom a cikin addu'ar sa "ka nuna mani tabbatar cewa wannan aiki da muke yi yana taimakawa".

Bayan mako shida, sai aka kaishi domin ya sadu da wani hafsan daukan labari cikin Asiri mai suna Captain Santso. Jirgin su ya fadi a Cuba, kuma Tom da matukin jirgin Mel Bailey, sun shiga hannun kuma an tuhumesu da laifin hada kai don bata zaman lafiyar kasar Cuba.

"Mutanen mu sun sami dubun dubatar takardun nan a bakin teku da kuma wasu wurare" in ji captain Santos yana magana da karfi, yana rike da daya daga cikin Pakitin da muka jefa a cikin teku shekarun baya.

Tom yayi kokari ya boye murmushin da ke ransa. "Na gode Ubangiji da ka amsa addu'ata. Na gode domin aikin mu bai zama a banza ba". Amsa addu'ar Tom tazo da tsada. Domin yayi zaman watani 21 a kurkukun Cuba. Amma a kurkukun Castro dai ya sadu da mambobin majami'a kuma ya sami sanin cewa har a karkashi Castro. Majami'ar Kristi tana habaka. Allah ya karbi addu'ar Tom. Shin masu bi sun san ko menene ma'anar amsar addu'a mai tsada? Idan mun so Allah ya amsa mana adduoin mu, lalle ne mu zama da shirin karbar amsoshinsa ta ko wane hali. Amsa mai tsada ta addu'a ita ce wadda ta shafe mu wajen yin haka.

***Mukan mika addu'oin mu ga Allah amma shin mukan mika har rayukanmu in ma ta dauro abin kai ga mutuwa? Mai yiwuwa muna yi wa wadanda suke cikin tsanani addu'a. Amma idan aka kiramu mu tafi mu taimaka akai musu abinci da kayan agaji ta hannun wata kungiya a majami'ar mu? Idan munroki Allah ya taimakenmu a lokacin da muke cikin bukata lalle ne muma mu bada kai a lokacinda yakeso mu taimaka don samin amsar wannan rokon. Akwai damuwa da kayi addu'a akai amma babu amsa? Ko zai iya zama addu'a Allah tana jiran naka shirin na ka yarda ka zama sashi na warware wannan damuwa in ta dauro a haka?***

## SHAIDU MASU SANANTA

### *Ammoria: Fursunoni guda Bakwai*

RANA TA 38

***Malaman Islama masu tsattasaurin ra'ayi sun yi kokari su rinjayi "kafirai" su bi addinin Islama har shekaru bakwai suna tsare. Amma su wadannan Krista da ke kulle a cikin kurkuku mai duhu basu juyo ba.***

*Zaku zama shaiduna kuma cikin Urushalima da dukan Yahudiya da Samaria da kuma dukan duniya.*
*Ayukan Manzanni 1:8*

"Mohammed shine mafificin annabi. Su ka yi kokarin baiyanawa su Kristan. Shin ya zo a baya bayan nan watau zuwansa ya fi kusanci damu fiye da kristi kuma shine annabin karshe na Allah?

Su Kristan suka saurare su a hankali kuma suka basu amsa "A cikin ka'idar shari'a irin taku, magana takan ta'allaka ne ga yawan shaidu. Yesu Kristi yana da shaidu na zuwansa daga Musa har zuwa Yahaya Mai Yin Baptisma.

"Mohammed shi yayi wa kansa shaida". Da suka rasa tacewa sai limaman suka yi kokari kai hari ta wata hanya. Tabbas Islama addini ne daga Allah. Domin (daularmu) kasarmu tafi kasashen Krista yawa suna fadar haka da gaskene.

"Idan haka gaskiya ne" in ji Kristan ko bautar gumaka na Misra. Girka da Roma da sune zasu zama addinin gaskiya, domin a wani lokaci tambaya, gwamnatocin ku, da dukiyarku basu zama shaidar gaskiyar bangaskiyar ku mun san wani lokaci Allah ya kan ba Krista nasara wani lokaci kuwa ya barsu a cikin tsanani da azaba.

A shekara ta 845 kusa da birnin Ammoria ta Gabas ta Tsakiya sai Musulmin suka daina tilasa Krista bin Mohammed. Duk bakwai akan fille masu kai. Sai aka jefa gawayen su cikin kogin Eupirates.

Yesu ya dokace mu da mu zama shaidunsa, ba wai mu sami dukan amsoshin da muke so ba. Kalmomi guda 3 da zaka fada wa mara bangaskiya su ne "Ban sani ba".

***Lalle ne, ya yiwu kana da amsar, ita amsar kanta amsar na wadannan tambayoyin da kuma shakku da mara bangaskiyar ya ke dasu. Duk da haka ba zai yarda da abinda ka gaya masa ba. A cikin yin shaidar ka idan ka kai wurin da ba ka san amsar ba, ka ce baka sani ba, sai ka fuskanci abu guda da ka sani za'a yi gardama a shaidar ka. Karewar ka ga Yesu Kristi, da abinda yayi wa rayukar, sun fi gaban karya tawa. Kai kafi kowa sani a wannan sashen. Bishara mafi kyau itace ta ba da labarin irin alheren da ka ke samu domin masu ji su karu da kai.***

# SAKANKANCEWA MATSANANCI

## *Indonesia: Petrus*

RANA TA 39

***Baya kadan a wata hira. Wani Krista dan Indonesia, mai suna petrus yayi magana mai firgitarwa: "Domin muna da Yesu, zama Krista ba abu ne mai uya ba, ko da shike akwai matse-machen lamba kwarai". A yayin da mu karan kanmu mun san maganarsa gaskiya ne, bin Kristi ya bukaci sadaukar da ta kai da gasket ga petrus.***

*Da shike bishararmu ba da magana kadai ta zo urinku ba amma da iko kuma, cikin ruhu Mai Tsarki kuma da sakonkan cewa karai: Kamar yadda kun san irin mutane da muka nuna kanmu gareku domin anfanin ku.*
*Tass. 1:5*

Gungun masu tsatsauran ra'ayi na Islama sun kewaye ginin majami'ar, suna kakkarya tagogi kuma suna anfani da kalmominsu na kiyayya da Krista. Mahaifin Petrus wanda yake Paston wannan majami'ar suna ciki tare da mahaifiyar sa, yar'uwarsa da wani danginsa da kuma wani ma'aikacin majami'ar , mahaifinsa yayi kokari ya kantar da hankalin gungun masallatan amma suka ki tafiya. Sai ya koma cikin majami'ar domin yin addu'a, yana rokon tsaro daga Allah da kuma taimako.
Gungun mutanen nan da yake jin ni suke neman zubarwa sai suka cinnawa ginin wuta, suna kalmomin irin nasu kuma suna jiran duk wanda zai fito sai su make shi. Yan sandan Indonesia suna tsoron daukan mataki. Sojojin kuma ba sa wurin. Wannan ya zama wani kona majami'ar a kasar kenan inda aka kona majami'u fiye da dari biyar a cikin shekaru goma da suka wuce.
A lokacinda Petrus ya iso gurin bayan yan sa'oi kadan, da majami'ar da duk abinda ke cikin sun zama toka. Kamnatattunsa da ke cikin sun kone, da ba za'a iya sansance gawawwakin ba. Daga baya wani ma'aikacin gwamnati ya baiwa Petrus hakuri amma ya karfafashi da cewar kada ya nemi yin ramako. Petrus bashi da bukatar ya rama amma ya nuna masu kauna. Bukatarsa shine ya ga cewa musulmin kasarsa sun juyo sun karbi Kristi.

***Galibi tsanani shine filin daga na karshe a tsakanin ilhama ta halin mutumtaka sakankancewa da ta ruhaniya kuma ta halin mutumtaka ba'a da wani sha'awa illa na kiyaye kai a duniya amma sakankancewa ta ruhaniya ya wuce gaban abinda muke sh'awa na mutumtaka. Kamar mutumtaka tace a dau fansa akan masu yi mana illa. Sakankancewa ta ruhaniya ta na yi mana tuni akan bukatun mu na ruhaniya game da masu yi mana tsanani. Yawancin mu bayan mun ga yadda aka kashe mana kaunatattun mu domin bangaskiyarsu. Zai yi wuya mu yi aminci irin na Petrus. Duk da haka bin wata hanyar daba ta Kristi ba yafi zama abin da petrus. Duk da haka bin hanyar da ba ta kristi ba yafi zaman mugun abin da Petrus ba zai taba yi ba. Yaya ko ace baza'a bi Kristi ba? Labarin sa yana tabbatar mana cewa sakankancewa ta ruhaniya ta ci nasara da ilhama ta mutumtaka. Wannan kuwa zai yiwu ne idan kaunar Kristi ta juya nufin mu na mutumtaka - nasara a tsakiyar daga ta tsanantarwa.***

# MATSANANCIN MAI KISAN GILLA - NA BIYU

## Bangladesh: Andrew

RANA TA 40

***Shugaban Musulmi yayi mamaki da ya ga Andrew mai yin bishara yana zaune a zauren dakinsa yana cin abinci tare da iyalinsa!***

***Ni kuwa idan an tadani daga cikin kasa zan jawo dukan mutane zuwa kaina.***
***Yohanna 12:32***

Yayi mamaki domin ya bada lada mai yawa domin a kashe wannan Krista. Sai ga Andrew a gidansa yana shaida Kristi ga iyalinsa "Me ke faruwa anan?" Yayi magana da karfi "Me wannan mutum, wannan kafirin, wannan makiyin Allah ya ke yi a cikin gidana"?

Sai surukarsa ta fara, "Nice na kira shi domin shi Yesunsa ya warkarda danka - Mijina". Ta ci gaba da bada labarinta cikin gaggawa. Yayi rashin lafiya ta shekaru 18, amma yau, wannan Krista, Andrew, yazo yayi masa addu'a. Ya dibiya hannayensa a bisa kansa, gashi kuwa ya warke! Yesu ya warkar da shi".

Malamin ya ga irin farinciki da dansa yake da shi a lokacinda yake bayanin yadda ciwon ya fita daga jikinsa. Wannan shine lokaci na farko da dansa ya sauka daga kan gado cikin watanni da dama. A lokaci na farko cikin shekaru 18 kenan da ya tashi babu jin ciwo a jikinsa. Dajin haka sai ya huce bai zabi ya karbi Kristi a wannan ranar ba, amma ya zama aboki da Krista na kewaye kuma ya taimaki Krista da yawa kaucewa kamu da tsanantarwa kuma.

Mutumin da ya bada kwangilar kashe Andrew ya zama mai marabtar sa da hannu bude.

***Kristanci addinine na "ka gani-kayi da kanka" A lokacinda Musulmin nan ya shiga gidansa. Ba wa'azi Andrew yakeyi ba akan Allah Uba, Allah Da da Allah Ruhu Maitsarki. Ba wai ko yana baiwa matar laifi ba ne tareda yayan don sun gaskanta Allah. Abinci yake ci tare da iyalin bayan yayi musu addu'a wannan gadon majiyaci da yanzu babu kowa akai tabbata ta ikon Allah gaskiya ne. Kazalika alle ne mu tuna cewa gaskiyar Allah a fili cewar, idan har zamu fadi kuma muyi abubuwanda suka kamata. Muyi abubuwan da suke daidai duk lokacin da zamu shaida bukatunsu gareshi, mu tabbatar mun bar shaidar Kristi ta gaske tayi aiki don kanta.***

# GASKIYA MAFI TSANANI

## *Romania: Pasto Kochanga*

RANA TA 41

***"Baka jin tsoron abin da zamuyi maka?" Kanar na Kwaminis ya tambayeshi, muryar sa cike da ba'a da kalubale.***

*Kowanene fa da zaya shaida ni a gaban mutane, shi zan shaida a gaban Ubana wanda ke cikin sama.*
*Matt. 10:32*

Pasto Kochanga matashin Pasto ne sau daya ya taba yin wa'azi tun zamansa Pasto, ya tsaya a gaban Kanar, yana kuma sane da cewar yana da mukamin da zai sa a kashe ko a rayar, ya amsa masa a cikin ladabi amma da murya ta karfin hali.

"Ranka ya dade, ita gaskiya bata san tsoro ba yanzu a ce gwamnatinku ta dauki shawarar rataye dukan masanan ilmin lissafi. Nawa ne biyu a tara ɑa biyu zai zama a lokacin? Biyu a tara da biyu ba zai sake ba.

Muna da gaskiya, gaskiya tamfar daidaitar jaddawali. Muna tare da gaskiyar cewa akwai Allah kuma shine Uba mai kaunarmu. Muna tare da gaskiyar cewa Yesu shine Mai Ceton duniya kuma yana kaunar ya ceci kowa, har da kai. Muna tare da gaskiyar cewa akwai Ruhu Mai Tsarki wanda yake karfafa maza da mata kuma yana basu haske, kuma muna tare da gaskiyar cewa akwai aljannah.

Ko da wane irin bulala ko kayan azabtarwa kake dashi, bazai sauya gaskiyar da ke kasa ba haka zata tabbata, biyu a tara da biyu zai cigaba da zama hudu kacal babu sakewa.

Ɗaganan aka yi wa Kochanga dukar kawo wuka har ba'a iya ganeshi kuma ba'a sake ganinsa ba. Ko da shike an bata masa fuska har ba'a iya ganeshi. A sama sanannene kuma anyi masa maraba.

***"Ka fadi gaskiya" Yara sukan ji wannan tsokaci tun suna kanana, wanan hikima bata da iyakan lokaci. Idan zamu dawo mu amsa abinda muka sani gaskiyane zamu sami abin fada a kullum idan aka kiramu muyi shaidar Kristi. Mutane da yawa sukanji kamar ba su kai matsayin da zasu shaida Kristi ba cewa basu sami "horon" yin haka ba. Mukanji tsoron ayi mana tambaya akan Tauhidi, ba mu kan san yadda zamu amsaba. Musani shida Kristi ba ya bukatar cin maki acikin aji na iya yiwa maganar Allah kariya. Abu mai sauki shine a kullum ka fadi gaskiya akan abin da ka sani. Kamar dai su wadanda suka sha tsananin addini a baya. Shaidar Kristi ba ta da wuya kamar yadda ake tsammani, dolene mu koma bin ka'idar da muka koya muna yara, an dokace mu da mu yarda da Yesu Kristi mu fadi gaskiya.***

*Sai lokacinda mutum ya gamu*
*da gaba da tsanani da hari*
*akan bangaskiyar sa'anan*
*ne zai fara tunanin ainihin*
*wannan bangaskiya tasa.*
*Ba wai sai lokacin da a ke*
*tunkarimajami'a da jita-jita*
*sa'an nan zata fara gane*
*dalilin amfanin ra'ayin rikau.*
*Galibin majami'un Krista*
*sukan nuna halin a*
*rziki a majami'unsu*
*cewa suna iya daukan kowane*
*mataki indai na arzikine domin*
*ci ma biyan bukata a kowane mataki.*

*William Barclay*
*Na Binciken Littafi Mai Tsarki a Kullum.*

## MATSANANTAN MASU BISHARA

## *Romania: Pasto Richard Wurmbrand*

RANA TA 43

*Kayi wa'azin kalma, kayi naciya ko da dama, ko ba dama ka tsauta ka kwabar ka galgadas da iyakacin jimrewa da koyaswa. II Timoti 4:2*

***A yayin da jirgin ya ja ya fara barin tashar, Krista da suke tsaye akan dakalin tashar jirgin suka fara balle anihin rigarsu ta "Kwat" suna zaro daruruwan takardun bishara, da sauri sauri suka yi ta zuba su acikin jirgin ta tagogin jirgin domin sojojin Russia da ke ciki.***

Sojojin Russia dake cikin jirgin wasunsu ma basu fi shekaru 16 da haifuwa ba suna dariya sha feduwa, musamman ga kyawawan yammata dake jefo musu takardu ta tagogi na jirgin, suka yi ta kwasan takardun suna mamakin wai me ake jefowa acikin jirgin da ke dauke da sojoji. A lokacin da shugabansu ya shigo sai suka yi maza suka boye aljifan su. Domin daga baya su karanta wannan takarda su kara sanin wani abu akan wannan Sarkin.

A can dakalin jirgi a tasha Krista sun taru suna dariya. An kira daya daga cikinsu, kuma ya bude Kwat din sa da wuri-wuri don ya san babu kome a ciki, don duk takardun da ya kawo tasha an jefa su a cikin jirgin da ya bar tasha ya nufi kasar kwamisanci ta Russia.

Ya da bishara ta jirgin kasa yana daya daga cikin dabarun da Richard Wurmbrand ya koyawa matasan majami'arsa domin kawo mutanen Russia ga Kristi. Wadannan abokai suna sace dukiyar kasar su kuma suna kashe mutanensu da yawa duk da haka Richard yana maraba da sojojin, a kowane soja yana hangen filin yin bishara kuma duk inda zarafi ya samu a shirye ya ke ya kawo wannan sojan ga Kristi.

***Sa kai ga yin bishara ya danganta ga yadda irin manufar mutum ta rayuwa take. Mai bishara ba wani bane illa shi wanda ya kudurta kuma yasa himma a cikin rayuwarsa ta kullum. Richard Wurmbrand mutum ne wanda ya tashi da himmar bishara kuma kokarinsa ya bazu a cikin matasa wadanda suka gane azancinsa. Ta haka kam dukan masu bishara wakilan Kristi ne ko da a ina ne muke bauta masa dukanmu masu bishara ne.***

***Zama mai bishara yana nufin kullum a shirye kake idan dama ta samu domin fadada mulkin Allah, ko a wajen aikin ka, ko a cikin jirgin kasa ko motar safa ko a kanti ko a makaranta, halin kirkin ka na kullum shine filin bishararka a lokacinda ka kafe domin fadada mulkin Allah.***

# MATSANANCIYAR WASIYYA

## Indonesia: Stenley

RANA TA 44

*Kune hasken duniya*
*Birni da ke kafe bisa tudu*
*bashi boyuwa.*
*Matt. 5:14*

***A lokacinda Stenley ya sauka daga cikin karamin jirgin ruwa a kan wani tsibirin Indonesia, sai yaji a jikinsa cewa akwai ruhu amma na shaidan cike da gurin. Mutanen sun shahara wajen maita kuma suna addinin Islama, Stenley kuwa ya fito kenan daga makarantar koyon aikin mai bishara. Kuma a shirye yake yayi aikin da Allah ya kirashi yayi; watau isarda mutanen ga Kristi.***

Stenley yayi wa'azinsa da karfin zuciya, yana kiran mutane da sujuyo zuwa ga Kristi su kona gumakansu da kayan tsubbunsu na tsohon rayuwa da suke yi. Wani Musulmi ya kona nashi gunkin, amma aciki akwai rubutu daga kur'ani, lokacin da yan ra'ayin rikau na Islama suka sami labarin an kona kur'ani sai suka kai karar Stanly zuwa gurin ma'aikatar unguwar, nan da nan kuwa aka tsare Stenley.

Ko da shike an yiwa Stenley mummunar duka har ya kwanta a some, maigidansa daga makarantar da ya fito, Pasto Siwi ya ziyarce shi kuma yaga hawaye na zuba daga idanunsa. Jim kadan bayan Stenley ya mutu daga raunukan da aka yi masa. Amma har mutuwa da kanta bata iya tsaikon bisharar Stenley ba. A lokacin da labarin ya isa ga mutanen kauyensa, Musulmai guda gomasha daya suka arbi Kristi ya zama Mai Cetonsu. Mutanen kauyen guda hamsin da uku kuma suka bada kansu domin tafiya makarantar koyon aikin bishara, goma sha daya daga cikinsu suka nemi akaisu yin aikin bishara a wannan kauyen da aka kashe Stenley.

Da zaton zasu iya kashe wutar marmarin kawo bishara shi yasa ma'aikatan gwamnati na kauyen suka kashe Stenley. Amma duk da tsananin yin anfani da karfi da hasala ikon Allah yana aiki. A yau bishara tana aiki a kauyen.

***"A bar fitilar tana ci" Abin da ya kamata ya zama manufar dukan masu bi suyi a lokacin da suka bar wannan duniya. Krista na gaske yakan bar fitila tana ci domin haskaka duniya da take cikin duhu. Ana kiran wannan barin wasiyya. Mukan ji wasu shahararrun mutane sukan bar wasiyya na fim ko guje guje da sauransu. Biye da haka a yayin da rayukan shahidun Krista da yawa suke salwanta ba tare da an sansu ba, fitilunsu na bangaskiya na haskakawa ko ina a duniya. Wasiyyarsu ta bangaskiya, mutunci, bege da kauna ba zasu kaiwa ba domin an kashesu. Alhali ma, mutuwarsu tana iya zama zuga-zugi na fifita harshen wutar don ta kara haske. Wasiya irin haka abin koyi ne ga wadanda suke raye kafin nasu tafiyar.***

# IYALI MASU TSANANIN BISHARA

## *Indonesia: Mahaifiyar Stanley*

RANA TA 45

*Ke mutuwa, ina nasarar ki? Ke mutuwa, ina karinki?*
*I Korintiyawa 15:55*

***Saura wata guda kawai wannan mata tare da diyarta su kammala karatunsu na koyon aikin bishara. Makarantar da suke ita ce inda dan Stenley ya yi dalibci, kafin ya tafi wani tsibiri na Indonesia yin aikin bishara. Aka kashe Stenley domin aikin bishara, amma shaidarsa ta harzuka mutane da yawa su tafi makarantar Littafi Mai Tsarki kuma su amshi kiran Allah domin shaida kaunarsa ga mutane.***

A lokacin da suka kammala karatunsu, wannan mata da diyarta suka yi shirin tafiya wannan kauyen inda Stenley ya mutu. Tana sa rai na samun damar nuna kaunar Kristi, har ga wadanda suka yi wa danta duka har kisa. Wani da ya ziyarci makarantar yaji abinda ta fada kuma yayi mamaki "Ba kya jin tsoron ki mutu"? Ya tambaye ta.

Matar ta nuna alamar rudewa da irin wannan tambaya, kamar ma ashe ba wani abune da tayi akansa ba kafin ranannan, "Me zai sa naji tsoron mutuwa", ta amsa masa a saukake.

Bangaskiyarta ga alherin Allah yana nan daram. Idan ya zabi yayi anfani, da ita a kauyen da aka kashe mata da a shirye take. Idan kuma har ta mutu acan, a shirye take ta amsa kiran. Mutuwar ta zai kai ta gaban Kristi da take kauna. Mutuwa ba hani ne ko horoba, hanyace kawai ta zuwa ga Isa ga mulkin Allah madauwami.

***Fuskantar mutuwa na iya yi mana tuni da alamar yara da ke tsaye a bakin rami mai zurfi cike da ruwa ganin haka zai tsoratar damu da rawar jiki domin rashin sanin abinda zai faru. Ko zan raunana ko zan iya? Bamaso mu muyi tsallaken farko - ba fa tare da rashin sanin abinda zai faruba. Sa'ar abin ma ba lalle ne muyi tsallen ba. Tarihi yana cike da labarin iyalin da suka yi tsallen haye iyaka tsakanin rai da mutuwa. Waliyyai ne su da suka mutu da tabbacin inda zasu. Maganar ga yarma ita ce Yesu Kristi ya tafi can wurinda babu mutumin da ya taba zuwa watau zuwa mutuwa da kuma dawowa. Kristi shugaban iyalan Krista ya ci nasara da mutuwa ya karya karinta ya kuma maye gurbin da alkawari mara shakka.***

***Ka saurari kiran ka shigo- Ruwan garau yake.***

# MATSAYI MATSANANCI
## Russia: Munafukai

RANA TA 46

***Suna raira wakoki a lokacinda sojoji guda biyu suka shigo da bindigoginsu. Aka tsaida sujada a yayinda sojojin suke hararar masu bi da idanu tamfar na dabbobi.***

*Wanda ba nawa bane gaba yake dani. Wanda kuma baya tayani tarawa, watsarwa yake yi.*
*Matta 12:30*

"Me kukeyi anan?" Sukayi tsawa "Kuna bautawa wani kagaggen Allahnku ko?" Mambobin suka tsorata suna tunanin ko akwai karin sojoji a waje dauke da bindigogi. "Dukan wadanda suke masu bangaskiya ga Allah su kama hannun dama na Majami'ar" inji daya daga cikin sojojin da fuska ta kiyayya "Za'a harbe ku domin bangaskiyar ku. "Ku da kuke so ku tafi gida ku tsira da ranku ku tsaya a hannun hagu. Su da suke da bangaskiya ga 'Allah' zasu mutu. Su da suka yi musunsa zasu sami yancin tafiya babu komi."

Minti goma da suka shige kowa na wakokin yabo dai-dai da juna. Yanzu kuwa zance ake na rai ko mutuwa. Wadansu sun tsaya a gefen hagu suna tattara fuska ko kuma daga hannu kamar na neman gafara ga wadanda suke hannun dama. Wasu sun tsaya a hannun dama da idanunsu a rufe domin yin addu'ar su ta karshe. "Ku na hannun hagu an sallameku" daya daga cikin sojojin ya fadi jim kadan. Wadannan mutanen suka fita bi da bi suna yiwa sauran duban karshe domin za'a harbe su nan ba da jimawa ba. A lokacin da na hannun daman suka rage su kadai, sai sojojin suka ajiye makamansu, "Muma Krista ne suka furta "amma munfiso muyi sujada ba tare da munafukai ba".

***Lokacin sanin matsayi yakan zo a lokacin da bamu tsammace shi ba, kuma ba zamu iya yin shiri domin yin haka ba. Dole ne mu karbe su a yadda "suka zo" muyi koyi kuma daga sakamakon. Lokacin sanin matsayi lokacine wanda yakan shafi maganar hali. Yana iya zama kawo harin masu aikata laifi da zasu nemi ayi na'am da addininsu. Ko kuma daukar shawarar fita daga dakin sinima domin suna nuna batsa. Irin amsar da zamu bayar a lokacin sanin matsayi zai nuna gefen da muka zaba Kristan gaske ko kuma gefen da ke da alamar tambayoyi. Ko a shirye ko a'a zamu san da halin mu na gaske da zarar mun dauki matsayi.***

## DADIN ADDU'A MAI TSANANI
### *Bohemia: John Huss*

RANA TA 47

*Addu'ar mai adalci tana da karfin aiki kwarai da gaske.*
*Yakub 5:16*

***"Oh Kristi mafi jinkai" haka John Huss ya rubuta a lokacin da yake jiran a yanke masa shari'ar Kisa "ka bamu ruhu mai karfin hali, domin ta zama da shiri. Idan kuma jiki yayi sanyi, bari alherinka yayi shugabanci, gama in ba tare da kai ba bazamu ta buka kome ba, fiye da haka, idan ba tare da kai ba bazamu iya fuskantar maketaciyar kisa ba. Ka bamu karfin zuciya, ta jarumtaka da tsayayyar bangaskiya, bege tabbatacce, da kyawawan halayen ba da taimako, domin mu iya ba da ranmu dominka tare da hakuri da farinciki. Amin".***

Huss ya yi kira da ayi wasu gyare gyare a majami'u cikin karni na goma sha biyu, yana yiwa firistoci masu shagwaba da suka sayar da damarsu (watau samun dama ta ayi zunubi ba tare da sakamakon horon wannan zunubin ba) kuma yana kira da asami dai-daitarda yin adalci bisa ga abinda ke cikin Littafi Mai Tsarki. Anyiwa Huss alkawarin samun tsaro ta hukuma domin ya gabatar da kariyarsa. Amma gashi yanzu a tsare yake a kurkuku yana jiran hukumcin kisa, kuma yana kai kukansa ga Allah.

Ranar 6/7/1415 aka tube Huss aka daure shi da sarka a jikin itace da aka kafa. A yayinda wutar da aka kunna ta kewaye shi, Huss yayi addu'a "Ubangiji Yesu Kristi, a dalilin bisharar ka ne nake shiga wannan hali na yanke mani shariar kisa ta hanya mafi muni amma na karba tare da hakuri da kaskantar da kai". A lokacin da wutar tayi yawa a kewaye dashi, Huss ya nunfasa a karshe ya tada murya, Kristi dan Allah Mai Rai, kayi mani jinkai".

Shaidar Huss muhimmin abune wajen dakatar da irin shagwabarsu ta bada kai ana rinjayar Kristoci su dawo bisa turbar koyaswa ta Littafi Mai Tsarki yadda ya kamata.

***Addu'a ita ce kariyar mu ta farko a wajen yaki da mugayen ruhu, amma kuma galibi sai ta baci muke komawa ga addu'a, wadanda suka shiga tsanani domin bangaskiyar su suna koya mana fifikon addu'a kalmominsu na karshe ba masu zafi bane. Ayyukansu na karshe aduniya ba na jayayyabane. Maimako, addu'a ita ce numfashinsu na karshe kafin mutuwa suna sa makasansu su rude amma suna rinjayar saura domin bishara. Idan kana cikin rayuwa mawuyaci haka kuma wutar tayi zafi zaka juya ga yin addu'a, shin za'a ganka a ranar wanine wanda kariyarsa ta farko da ta karshe shine sadarwa tare da Uba da ke cikin sama?***

# KARFAFAWA MAI TSANANI

## Vietnam: Pasto Nguyen Lap Ma

RANA TA 48

*Domin ina dokin ganinka, in ni'imta kuda wata baiwa ta ruhu domin ku karfafa juna. Wato ni daku mu karfafa juna ta bangaskiyar mu tawa dataku.*
*Rom. 1:11-12*

***A lokacinda kwaminis suka mamaye Vietnam, Pasto Nguyen Lap Ma ya ki ya mika majami'ar Hada kai ta Kristocin Mishan da ke garin Can Tho. Domin wannan "Laifi", an tsare shi da shi da dukan iyalinsa da hukuncin daurin talala a wani karamin kauye da hana shi yin tafiye tafiye da kuma hanashi karbar wasikun sa harma tsawon Shekaru gomasha biyu.***

A karshe da hukuma ta sassauta dokar hana samun wasikun. Pasto Lap Ma ya ji dadi ainun da ganin wasiku na isowa gidansa. Muryar Shahidai ta buga labarin Pasto Lap Ma da kuma adireshin gidan. Dalibai, Matan Aure, Pastoci da Yan Kasuwa suka yi ta rubuta wosiku na karfafawa zuwa gareshi tare da iyalinsa. Yan Sandan Vietnam sunyi mamaki da pasto Lap Mą ya sami fiye da wasiku dubu uku daga ko'ina a duniya.

"Na karanta kowace wasika da addu'a da hawaye", inji Pasto Lap Ma, "Na rike kowace wasika aka kuma nayi nazari akan ayoyin da aka ambata a ciki. Sa'annan na mori ayoyin nan tare da iyalina har da ma mutanen Vietnam. Mun yi farinciki kuma mun karfafa da wadannan sakonni da ke ciki".

Allah ya karfafamu kuma ya taimakemu" Pasto yaci gaba da fadi cewa lallene mu kafa begen mu a gareshi mu kuma kafa idanunmu ga Yesu. Mu bishi da jimirin giciye, raini da shan kunya har zuwa ga mutuwarsa. A lokacin da kuke rayuwa, Allah yana anfani da mu domin mu lallashi yan'uwanmu Krista da suka shiga tsanani mu kwantar musu da zuciya". Wasikun sun karfafa su a yayinda su kuma cikin farinciki suna karfafa sauran masubi.

***Karfafawa shine makamashi a gudun tsira na Krista ba idan babu ruwa, babu wanda zai jimre gudu na dogon lokaci. A yayin da muke cikin tafiyarmu ta rayuwa mun koya cewa karfafawa kamar titi mai gefe biyu yake daya na tafiya daya na dawowa. Muna bada karfafawa ga wasu haka kuma muna karbar karfafawa daga sauran masu bi kuma daga Allah da kansa. Kome kankantar karfafawa ya na taimakawa gajiyayye ko raunanne ta wanda bangaskiyar sa tayi sanyi. Galibi karfafawa ta ruhaniya da muke samu daga wadanda suke kewaye damu yana farfado damu. A wani hali ma an sami horon shekara gomasha biyu domin bangaskiyarmu, a wani matsayin kuma yana iya zama wahala ce ta rana daya wacce in akayi jimiri sai aci nasara.***

*Idan baka da shirin mutuwa*
*domin abinda ke cikin*
*Littafi Mai Tsarki, to*
*kada ka bada kudi domin*
*sayen Littafi Mai Tsarki.*
*Domin in har ka bayar,*
*mu kuwa zamuyi*
*fasa-kwaurin karin Littatafai.*
*Idan kuwa mukayi*
*haka din to tabbas za'a*
*sami karin shahidai*

*Pasto Richard Wurmbrand*
*wanda ya kafa Muryar Shahidai*

# MAHAIFIYA MATSANANCIYA

## England: Susannah Wesley

RANA TA 50

***Goma daga cikin gomasha tara na yayan Susannah sun mutu kafin su cika shekara biyu da haifuwa, kuma daya daga cikin yayanta mata gurguwace. Duk da haka ta rubuta ta ajiye cewa duk wahalun da ta sha sun taimaka wajen "Ciyarda ruhaniyarta gaba, Daukaka yana gareka ya Allah".***

*Ina tunawa da sahihiyar bangaskiyar ka, wadda da farko ke tare da kakarka Lois da mahaifiyarka Afiniki, yanzu kuma na tabbata ana tare da kai*
*2 Timoti 1:5*

Mahaifinta yaki ya amince da dokokin Ingilishi na 1662, wanda ya tilastawa dukan malaman addinin Krista da suyi biyayya da Littafin Addu'ar kowa da kowa. Krista guda dubu biyar na darikar da ake kira "Babu ruwanmu da Tijadidi" suka mutu a kurkukun Ingila domin bangaskiyarsu.

Mijinta shima dan Baburuwanmu da Tijadidi yaci gaba tare da Majami'ar Ingila. Adalilin haka aka kona masa rumbunansa, mambobin Ikklisiyarsa suka sa aka kamashi aka kaishi kurkuku. A irin wannan lokaci Susannah ta sha wahala da talauci. Harma barayi sun zo sun yanke nonon saniyarsu don dai kada su sami madara domin yanyanta.

Akwai kuma ranar da mambobi suka fusata suka kona rufin gidan dukan iyalin sun tsira daga gobarar sai John dan shekara shida, shine yayiwo tsalle daga tagar gidan kuma ya tsira daga faduwar, kuma wannan dan John Wesley ya girma har shine ya kafa darikar Methodist, wani daga cikin yayanta Charles Wesley shine ya wallafa Sananniyar wakar Kirsimeti din nani da ake kira "YAU AN HAIFI ALMASIHU" kuma wasu wakoki fitattu. Susannah Wesley tayi bayani cewa "Addini ba wani abu bane illa aikata nufin Allah amma ba namu ba. Ko Aljannah ko Jahannama ya danganta ne kadai ga wannan".

***"Dubi habarsa kamar ta Ubansa" "Kalle ta kamar kakarta ta tsarta miyau don tsananin kama" Idanu, kunnuwa, gashinta, hannye da sauran gabobin jiki suna kamaNta mu da dangogin mu wani lokaci ma da kakanni na can baya da nesa. Haka ma dangantaka ta yan'uwa cikin Kristi. A zamaninmu na Krista muna da dangantaka ta hanyoyi dabam-dabam, kamar kauna, bege, farin ciki da salama - dukan wadannan sunzo mana ne daga gadon samaniya. Ko da ace bamu da iyaye ko kakanni irin na su Wesley wadanda suka koya kuma suka rike bangaskiyar Kristi harya iso garemu. Allah shi ke bamu yan'uwan ruhaniya da zasu yi reno kuma su kaunace mu. Wa ke uwa ko uba na ruhaniya a gareka - wani ne wanda ya koya maka akan Kristi? Ga wa zaka iya zama dan'uwa ko yar'uwa ta ruhaniya?***

# DUMI MAI TSANANI

## *Russia: Nadejda Sloboda*

RANA TA 51

*Idan nace bazan ambaci*
*Ubangiji ba, ba zan*
*kara magana da sunansa ba;*
*sai inji damuwa a zuciyata,*
*An kulle ta a kasusuwa na,*
*Na gaji da danneta a cikina,*
*ba na jurewa ba.*
*Irmiya 20:9*

***Nadejda Sloboda ta kasa boye dokinta. Ta saurari rediyo mai dogon zango daga Turai inda taji labarin Kristi. Da yake ita ce Krista ta farko a wannan kauyen kasar Russia, sai ta zaku da ta gaya wa abokanta labarin Allahn da ya sauya zuciyarta ta hanyar ban mamaki. Amma ta sani cewa hukuma ta haramta ayi magana akan Allah ko kuma addinin Krista.***

Nadejda dai ta kasa hakuri, ba da jimawa ba kuwa sai aka kafa majami'a. A lokacinda Yan Sanda suka kasa tsayarda karuwar mambobi da habakar majami'ar koda shike har toshe hanyar zuwa akeyi, sai suka kama Nadejda sukayi mata daurin shekara hudu a kurkuku. Aka kwace yayanta da karfi aka kaisu makarantar koyarda musun sanin Allah wannan kuwa ya dami Nadejda. Amma sai ta kara jin kusancin ta da Allah karuwa ya ke yi fiye da da sai tayi kudirin yin bisharar Kristi ga abokan kurkukunta. Domin irin naci da take na maganar Kristi, sai hukuma suka saka ta a dakin kurkukun daga kai-sai-kai har na wata biyu, wannan ya faru ne a tsakiyar lokacin sanyin kankara kuma akan kankare babu gado. Bayan da aka dawo da ita cikin sauran fursunoni, suka tambaye ta yaya tayi har ta iya jimirin wahalar. Sai ta amsa, "Na kwanta barci akan kankare mai sanyi cikin yarda da Allah, sai naji dumi kewaye dani, na huta a hannun Allah".

***Yawancin Krista zasu iya tunawa a cikin rayuwarsu ta ruhaniya inda sukaji kamar ba zasu koshi da maganar Allah ba. Marmarin Ruhaniya abune da ya kamata ya zama jiki. Wani lokaci bangaskiyar mu takanyi sanyi. Watakila tsanani ne ke kashe mana jiki watakila wani damuwa ne, watakila ma babu wani abu takamaimai - kila abubuwan yau da kullum ne suke kawo damuwa. Wai shin wannan marmarin ruhaniya ta da ta zama babu ne? Himma ta da ta mutu ne? Akwai damar sabuntar dangantakarka da Allah. Ka rokeshi ya taimake ka sabuntar himmarka ta bangaskiya a yau.***

# MATSANANCIN GANI

## *The Ivory Coast: Chloe*

RANA TA 52

***Duka da yakeji kamar ko ta ina ma gabzarsa akeyi Chloe kuwa yayi kokari ya rufe kansa da hannuwansa domin kariya, ko da shie baisan mutum nawa nesuka kawo masa hari ba, yana jin zafin ko wanne duka da aka kawo masa a yayin da yake jin kamar zai suma, suna yi ma ihu da ba'ar bangaskiyarsa ga Yesu. Chloe yayi addu'a a zuciyarsa yana rokon Allah ya bashi karfi.***

*A kuma saku ku waye ta idon zuci Afisawa 1:18*

A kowane mako, Chloe yakan taka da kafa tafiyar mil ashirin a kasarsa ta Ivory Coast domin yin Bishara a wani kauye da ake kira Sepikaha. Akwai dan tarin Krista da sukan marabci Chloe, amma yawancin mutanen kauyen musulmi ne. Yan ra'ayin rikau na cikin musulmin sune suka yi ta dukan mai bisharar.

Aka kai Chloe a asibiti inda aka yi masa jinyar raunuka da akayi masa. Da yan sanda suka tambayi Chloe ko su wanene suka yi masa duka, sai yace bai sani ba, Chloe makaho ne tun shekaru da dama baya gani. Mako daya bayan sallama daga asibiti Chloe ya koma kauyen Sepikaha, yana sadaukar da rayuwarsa domin yayi wa mutanen da baya iya gani bishara. Idanunsa ba sa iya gani, amma zuciyar Chloe tana iya gani sarai. Zuciyarsa ta ga bukatar Yesu a wannan kauyen, kuma taga akwai yayan Krista da ke da marmarin girma a cikin bangaskiyarsu. Yayi ta dawowa daga mako zuwa mako zuwa Sepekaha. Fuskokin da baya iya gani a yanzu zai gansu watarana a sama.

***Ba lalle sai anyi anfani da na'urar daukar hoton cikin jikin dan adam sa'annan za'a gane gazawar da mutum (mace ko namiji) ke ciki game da rayuwa ta ruhaniya ba. Dadewa da akayi ana daukan guragun shawarwari baya buya tunda zaka ga damuwar a fuska. Ma'anar idon ruhaniya shine anfani da idanun zuciyarmu domin mu gano abubuwanda wadansu suke bukata. Shi kenan, ikon samun iya ganewa shine mataki na fari na sanin bambanci. Me kake gani a yayinda ka dubi fuskokin wadanda suke kewaye da kai? Waishin kakan ma duba? A la'adar mu ta yau kana iya samun mutane kewaye dakai, ko a kasa ko a tasha ko a makaranta bata re da kun hada ido ba. Kana saduwa da mutanen da ke bukatar Kristi? Shin idanun ka na ruhaniya sun sami horon da zai sa su gane wadanda ke da bukatar Kristi? Ka roki Allah ya taimakeka raya idanun ruhaniyarka domin ka gane kuma ka aikata.***

# MATSANANCIN MISALI

## *Gabashin turai Labarin Misalin Kananan Itatuwa Guda Uku*



***Wata rana a cikin kurmi, kananan itatuwa guda uku suka yarda suyi addu'a cewa sunfiso ayi amfani dasu ta haya mafi daraja maimakon su zauna haka su tsufa su rube.***

*Banda haka ma har muna sa takama da shanwuyarmu da yake mun sani shan wuya ke sa jimiri, jimiri kuma ke sa ingantaccen bali, ingantaccen hali kuma ke sa sa zuciya kuwa bata sace iska faufau, domin Allah ya kwarar kaunar sa a zukatan mu, ta Ruhu Mai Tsarki da aka bamu. Romawa 5:3-5*

Na farko yace ya fi son a yi amfani da shi a haka ya zama mazubin ruwan dabbobi watau sakarkarin da zasu sha ruwa bayan sun yi kiwo sun gaji. Allah kuwa ya albarkaci wannan itacen domin nuna irin wannan filako. Sai ya zama sakarkari na musamman - watau wanda aka kwantar da Yesu Dan Allah a lokacin haifuwarsa. Na biyu yayi addua'a da ya zama jirgin ruwa. Aka kuma amsa addu'arsa, kuma aka yi anfani da itacen ya zama inuwa ga wani fasinja na musamman - watau Dan Allah icen yaii Yesu yana tsautawa guguwa yana cewa "Salama, yi tsit".

Ice na uku kuwa aka yi babban giciye da shi a zaman kayan aiki azabtarwa Da farko itacen yayi bakin ciki da yadda aka yi anfani da shi. Amma watarana sai a giciye Yesu Banazaret ajikin icen. Abin mamaki shine giciyen baiji kuka ko nishi ba kamar yadda giciyen hagu da na damar sa sukeyi. Maimako sai yaji kalmomin kauna da gafartawa daga bakin Dan Allah - kalmomin da suka bude wa barawo mai tuba kofofin sama.

Daganan ne itace ya gane cewa anfani da aka yi dashi na giciye Yesu shi ya kawo ceto ga dukan mutanen duniya.

***A majami'un karkashin kasa na kasashen turai ta gabas akanyi anfani da wannan misaline domin karfafawa ga wadanda suke shan azaba domin bangaskiyarsu. Ana so aga cewa wadannan masubi su san makasudin abinda suka jimre dominsa. Babu shakka suna da fata ta gaske da kuma buri tun can farko da suka sa suna so ayi amfani dasu domin daukaka Allah. Duk da haka akwai alamar danniya ta shiga tsakani domin ta rabasu da shirin Allah. Me zaisa wahala maras adalci zai shigo irin wannan shirin? Kamar ana siffanta su ne domin su gamshi makasudin karshe na rayuwarsu. Ta wnnan hangen za'a gane cewa shan wahala ba tsaiko bane ga shirin Allah, a rayuwarka, amma hanya ce da za'abi idan ana aikinsa.***

# MATSANCINAN RAUNI

## Russia: Reverend Mikhail

RANA TA 54

***"Idan zaka janye bangaskiyarka, ka tattake giciyen, za'a barka ka tafi", inji Yan'daban Bolshevik "Idan baka yi ba, zamu kashe ka".***

*Amma ya ce mani, "Alherinsa ya isa, domin ta wajen rashin karfi ake ganin cikar ikona". 2 Korintiyawa 12:9*

Reverend Mikhail ya ga kisan yan kasarsa shugabannin majami'u masu ra'ayin rikau na Russia da sauran mutane da kwaminis suka yi. A tsakiyar wannan hali na azabtuwa da ila iri-iri ba sai ya tsaida magana cewa Allah in har akwai shi, to da ba bar irin wannan abubuwan bakinciki su faru ba.

"Ban gaskanta ba", yana tunani a lokacinda ya fuskanci Ẏan Daba. "Menene ma'anar giciye a gareni? Bari na ceci raiña". Amma a lokacinda ya bude bakinsa domin yin na'am da dokar Yan Daba, kalmomin da suka fito daga bakinsa ya gigitardashi "Ni na bada gaskiya ga Allah kadai, Bazan tattaka alamar giciye ba?"

Yan Daban nan suka sa buhu a kewaye da kafadar sa a zaman rigar sarauta kuma sukayi amfani da malafarsa mai gashi a zaman kambin sarauta ta ba'a irin da aka dora wa Yesu amma na kaya. Daya daga cikinsu wanda yake mamba ne na majami'asa a da ya durkusa a gabansa, yana cewa, "Agaisheka sarkin yahudawa" suka shiga dukansa daya bayan daya suna wa Allahn sa ba'a.

Reverend kuwa sai yayi addu'a a zuciyarsa, yace, "In dai akwai ka Allah to ka ceci raina in ka yarda" Da akacigaba da dukansa, sai ya sake kira da karfi, "Na bada gaskiya ga Allah daya". Nuna bangaskiyarsa ya burge bugaggun Yan Dabannan har suka sake shi. A lokacin da ya isa gidansa, sai ya fadi a rub da ciki a kasa, yana kuka yana mai mai ta kalmannan, "Na bada gaśkiya"

***Rayuwa na cike da juyi iri-iri. A mutu domin a rayu, ka rasa domin kaci nasara, ka nuna karamci don ka yi karfi. Lallene mu sani cewa idan bamayin na'am da kasawar mu to ba zamu ribatu da karfi daga Allah ba. A lokacin da kuka shiga mawuyacin hali da jaraba ko kuma irin cin zali da ake yiwa wasu daga nesa, mai yiwuwa mu fara shakkan alheran Allah, wannan mutum-taka ne. Duk da haka Allah baya yashe mu, yakan karfafa mu. Saboda haka muna iya murna da kasawar mu domin sukan yimana tuni cewa karfin mutum shine ba sai karfin Allah. Muna iya gazawa amma karfin Allah yananan. Me kake koyo akan gazawaka? Me wannan yake koya maka akan karfin Allah?***

# MATSANANCIYAR HIKIMA

## Isra'ila: Istifanus



***Shaidu sukayi shaidar zur a kansa "Mun saurareshi yana zagin Musa da Allah. Mutumin nan yana magana babu saurarawa gaba da dokokin Allah. Har munjishi yana cewa Yesu Banazare zai rushe wannan wuri kuma ya watsarda dukan al'adun da Musa ya bamu".***

*In waninku ya rasa hikima, sai ya roki Allah, Mai ba kowa hannu sake, ba tareda goriba, sai kuwa abashi. Yakubu 1:5*

Babban firis na babbar majalisa ya juya wajen mai laifi. "Me kake da shi na fada domin kare kanka?" Ya tashi a hankali kuma muryarsa mai kissa ta canza. "Kakanninku sun kashe duk wanda yayi maganar zuwan Yesu. Kuma kunci gaba da bin wannan al'ada ta addininku - ku masu cin amanar kasa, masu kisan kai dukanku. Kuna da dokokin Allah da mala'ika ya baku kyauta a nade - kuma kun banzartardashi."

Gaba daya sai suka maida murtani cikin tsawa da zage-zage, amma Istifanus bai fasa ba. Sai ya dubi sama yace "To! Na ga sama a bude sarai ga kuma Dan Mutum yana tsaye a gefe tare da Allah!" Sai suka tashe kunnuwansu da hannayen su, suka far masa, suka ja shi zuwa taje daga cikin birnin.

Daya daga cikin Farisawan da ake kira Saul ya tattara rigunan sauran domin kada jinin Istifanus ya bata kayan.

A yayinda suka fara jifar Istifanus da duwatsu, sai yayi kira yace "Ya Yesu ka karbi raina". Sa'annan ya durkusa yana addu'a da karfi yadda kowa ke ji. "Ya Yesu kada ka basu laifin aikata wannan zunubi" Kalmominsa na karshe. Sa'annan ya mutu.

Sabo: An dauko daga Ayyukan Manazanni 6:11-7 (an kirashi)

***Kwantar da hankali a fuskar mawuyacin lokaci Hikima ce mai kyau. Wasu abubuwa masu sauki kamar shiga rukukin motoci a kan titin mota, faduwa a jarrabawa ko kuma samun gargadi a wajen aiki duk wadannan suna iya sa mutum ya hasala" Mu sani cewa fita daga damuwa yana bukatar abinda yafi aiki da hankali. Ana bukatar hikima daga Ubangiji. Idan a tunkare ka da shaidar zur koma da tsorator da ranaka. Istifanus yayi aiki da hikima ta gaske. Bai raina ba. Bai zage su ba, kadai ya dogara da abin da ya sani gaskiya ne wanda farisawa suka ki su gaskanta - cewa Yesu Dan Allah ne. Shi Yesu wanda ya rungumi Istifanus bayan mutuwarsa shi kuma zai rungume ka a lokacinda kake bukatar hikimar wacce daga Allah kadai take zuwa.***

*Zanyi ta yin*
***BISHARA***
*har sai na*
***MUTU.***

***Pastor Li Dexian -***
***Shugaban wata majami'a a China wanda aka tsare domin yin wa'azi ba tare da izini ba fiye da sau ashirin.***

*Russia: Maria*

# Zuwa ga Uwata da Ubana

RANA TA 57

*Domin sau dayawa na sha gaya muku, yanzu kuma nake gaya muku, har da hawaye wai suna bin Yesu, amma su magabtan Almasihu ne.*

*Filib. 1:18*

***Ina gaisheku cikin kaunar Kristi. Ina cin gaba sarai da samun albarku. Daya daga cikin yan makarantar mu, mai suna Varia yar kungiyar matasa ta kwaminis ce wadda nake yiwa bishara, kuma a ganina da alamar nafara cin nasara a kanta. Kwanaki tayi magana tace "Bana iya fahimtarki sam. Dalibai da yawa suna zaginki, suna bata maki rai, amma duk da haka kina kaunarsu".***

Na shaida mata cewa Allah ya koya mana dukanmu mu nuna kauna, ba wai ga wadanda suke son mu kadai ba, amma musamman ga wadanda suke kin mu domin ta yin haka zasu iya ganin alherin Allah ta wurin mu. A da Varia tana daya daga cikin masu yi mani ba'a da zage zage, amma ni kuwa wannan yasa naci gaba da yin addu'a domin ta kari bisa kari.

A yau ta tambayeni ko zan iya na kaunaceta ita ma! Sai muka rungumi juna muna kuka. Na bada gaskiya tana kusantar karbar Kristi. Ina rokon kuyi addu'a dominta.

Idan ka saurari wadanda ke musun Allah a fili, sai kaga kamar haka yake da gaske. Amma rayuwa ta nuna cewa yawancinsu suna da sha'awa kwarai a cikin zuciyarsu. Kuma zaka iya jin nishin zukatansu, suna da bukatar wani abu da suka rasa amma suna kokarin rufa rufar nuna wannan rashi ta wurin rashin Allahn takarsu. Zan sako rubuta muku nan ba da jimawa ba. Ina aika kaunata ga dukan kowa a gida.

Nice Maria.

***Allah ya halicci mutum da gurbi domin ruhaniya a cikinsa, wanda kuma shi kadaine zai iya cika wannan gurbin. A yayinda muka sadu da wani wanda yake gaba da addinin Krista sai mu tunatadda kanmu irin bukatu masu yawan gaske da ke cikin rayuwar wannan mutum... Kayi tunanin gurba kirji wurin ma'ajin zuciya na aboki gabanka- jikin da babu zuciya. Wannan rashi shine yake tunzura mutane da yawa zuwa neman ruhaniya. Ko duyi na'am cikin bangaskiya, da sha'awar karba Kristi domin cika wannan gurbin, ko kuma su amsa da bakin ciki suna kiyayya da Kristi gaba daya. Galibi ganin krista yakan tunatadda makiyan Kristi abinda suka rasa a rayuwar su. Ba kai karan kanka suke ki ba. Suna kin abinda kake wakilta.***

# MATSANANTUN WASIKU (NA BIYU)

## Russia: Maria

## Zuwa ga Uwata da Ubana

RANA TA 58

*Saboda haka duk wanda ke na Almasihu, sabuwar halitta ne, tsohon al'amura duk ya shude, gashi, kome ya zama sabo. 2 Kor. 5:17*

***A cikin waccan wasika ta na baku labarin wata mai musun sanin Allah, Varia. A yanzu na mai farincikin shaida maku labari mai dadi. Varia ta karbi Kristi! Ta zama wani abu dabam domin har tana shaida bishara a fili ga kowa da kowa. Tun farko da Varia ta bada gaskiya a can cikin birnin ranta tana jin laifofinta da tayi. Ina jin tana bakin ciki domin ta dade tana bada gaskiya cewa babu Allah kuma tana fada wa mutane haka. Tana jin yakamata ta wahala tasha horo don abin da tayi.***

Tare muka tafi wajen taron masu cewa babu Allah na kungiyar matasan kwaminis. Ko da shike na gargade ta da tayi a hankali gargadin bai yi anfani ba. Bayan taki ta raira wakar kwaminisanci tare da su. Varia ta tafi gaban taro tayi musu magana. Da karfin hali kuwa ta yi wa mutane magana akan karbar Kristi ya zama Mai Cetonta!.

Ta roki kowa ya kauce daga hanyar zunubi ya zo ga Kristi, wurin kuwa yayi tsit. Bayan ta gama magana sai tayi waka da muryarta mai dadi, wakarda take cewa:-

"Banajin kunyar shaida Kristi wanda ya mutu, domin ya kare dokokinsa da ikon giciyensa". Ba abinda na iya yi sai dai kawai zuba ido a lokacinda suka kamata suka tafi da ita. Yau (C) tara ga watan biyar amma bamu ji labarin kome a kanta ba.

Ina rokon kuyi addu'a!

Maria.

***Manyan abokan gaban Krista sune ganiyar bara ta addu'a. Kamar Saul na Tarsus, abune mai yiwuwa makiyi ya zama mashahurin mai bada bisharar Kristi. Amma in ba tareda addu'a ba yiwuwar haka zai yi wuya. A maimakon muji tsoronsu ko mukisu, ya kamata mu yiwa wadanda suke tare damu a unguwanninmu, a kasarmu da ko'ina a cikin duniya wadanda suke kiyayya ainun da Kristi. A duk yayinda muka yi addu'a domin marasa bishara da wadanda basu yarda akwai Allah ba zamu yi hangen alherin Kristi maimakon kinsu. Suna iya zama masu bisharar shaida alherin Allah. Babu wani makiyin mu da yafi karfin ikon Allah, Kuma addua tana shan kansu.***

## WASIKU MASU TSANANI (NA UKU)
### Russia: Maria
# Zuwa ga Uwata da Ubana

RANA TA 59

*Amma wadanda suke dogara ga Ubangiji domin taimako zasu ji an sabunta karfinsu. Zasu tashi da fikafikai kamar gaggafa. Sa'anda suke tafiya bazasu ji kasala ba. Ishaya 40:31*

***Jiya ranar biyu ga watan takwas nayi magana da Varia a kurkuku. Ta rame kuma ta kode, amma idanunta suna da hasken salama ta Allah da kuma farinciki amma ba irin ta duniya ba.***

A duk lokacinda na tuna da ita na kanyi bakin ciki. Ita yar shekaru goma sha tara ne kawai. A zaman maibi ita jaririyace. Amma tana kaunar Ubangiji da dukan zuciyarta kuma har ta zabi hanya mafi wuya tun farkon tuba. Ina roko ayi addu'a dominta. Sun kwashe dukkan kayanta an barta da kayan jikinta kawai. Munyi karo karo mun aika mata da yan kaya, amma bana zaton ta sami kayan duka.

Da na tambayi Varia ko tana da-na-sani da abin da tayi? Tace a'a, kuma idan suka sake ni zan sake yin haka. Kada kiyi tunani wai ina wahala, ina farin cikin kauna da Allah yakeyi mani har ya bani farin cikin jimiri domin sunan sa" Ina godiya ga Allah domin muna da salamar fahimtar wannan, idan muna cikin Kristi babu wahala da zata tsaida mu. Addu'a ta ita ce ina fatar bangaskiyata tayi karfin nata a yayin da na shiga ha!i irin nata. A yanzu mun gaskanta za'a aika Varia zuwa sansanin bauta na Siberia.

***Kristanci ba kamar gudun tsere na tsawon yadi dari bane. Kamar gudun mila-milai sai mai jumiri yake yi. Ayoyi suna gaya mana akwai lokuta da muke tashi kamar gaggafa muyi gudu ba gajiya. Haka kuma akwai lokuta a rayuwar mu inda kadaici da sauransu sukan zo mana. A irin wannan lokaci mukan yi kokarine muyi tafiya ba tare da mun suma ba har sai mun kara karfi. Wannan shine matsayin da masu shan tsanani suke ciki. A lokacin tsanani koyo muke domin iya daukar matakin gaba ba tare da mun gaza ba. Jimiri babbar nasarace da take kawo daukaka ga Allah. Idan kana cikin jarabtuwa da baka gane ba ka dage. Kana karfafuwa a kowace rana - wataran ma ba tare da la'akarin haka na faruwa ba. Ba da jimawa ba sai ka sake mikewa kamar gaggafa.***

# WASIKU MASU TSANANI (NA HUDU)

## *Russia: Varia*

## Zuwa ga Maria

RANA TA 60

***A karshe dai na sami damar rubuta maki wasika. Mun sauka lafiya a sabon sansani mai nisan misalin mil goma daga gari. Bazan iya bayanin rayuwa irin na nan ba, amma na gode wa Allah da yake ina lafiya kuma ina da karfin yin aiki.***

*Ina so ku sani, yan'uwa, al'amuran da suka sameni, sun dai kasance ga yaduwar bishara*
*Filib. 1:12*

An samu a aiki a cikin wani daki mai inji ni da wata yar'uwa wacce ba ta jin dadin jikin ta. Nice nake yi mana ayyukanmu, in ko ba haka ba dukanmu zamu shiga horo.

Mukanyi aiki sa'oi gomasha biyu zuwa goma sha uku a kullum kuma cikin karancin abinci. Amma bana so nayi kara.

Ina so in fada maki cewa Allah ya yi amfani da ke domin isardani ga Kristi. Wannan shine karo na farko da nake jin rayuwa ta tana da manufa, kuma nasan domin wanene nake wahala, ina da marmarin gayawa kowa anan labarin babban farinciki na ceto. A wajen aiki sukan zage ni kuma su bani horo domin banayin shiru. Ta kaka zan yi shiru? In dai ina da ikon bude baki, to zan shaida wa kowa labarin babbar kauna tasa.

Akwai masu bi da yawa anan, mun saki jiki jiya da dare mun tafi bakin kogi, inda aka yi mana baptisma da ni da wasu yan'uwa maza guda bakwai. Bazan taba mantuwa da wannan ranaba! Ina roko kada ayi kuka domina. Dalilin zuwana nan afili yake kuma bangaskiya ta tananan da karfinta.

Kauna daga Varia.

***Mutanen sun yarda cewa akwai kaddara ko kuma rabo, to kai wanne ka zaba, mun sani cewa mutane da yawa sukan bada kansu domin aikata wata manufa da zata anfani jama'a. Krista sunsan da wannan a zaman "Kira" - Nufin Allah bisa rayuwarsu Idan muka aikata nufin Allah domin rayukanmu, mukan zama horarru cikin dayantaka. Mukan sami gamsuwa cewa ko menene mukayi kuma ko menene ya faru da mu yana ciyarda bisharar Yesu Krist gaba. Mu a hade muke, masu amfani kuma. Da farko cikin rayuwarmu, ko da menene al'amarin, mu sani cewa muna ba da taimakone ga wani abu wanda yafi karfin mu. Babu abinda zai sha gaba da ko yaci nasara da duk wanda ya rungumi wannan manufa. Me kake ji cewa shine ya zama babbar manufar rayuwarka?***

# WASIKU MASU TSANANI (NA BIYAR)

## *Russia: Varia*

## Zuwa ga Maria

RANA TA 61

***A karshe na sake samun damar rubuta maki kuma. Ina farincikin shaida maki cewa yar'uwannan da bata da lafiya ta sami sauki kuma an kaimu wani sansani dabam.***

*In sanshi, da ikon tashinsa, da tarayyar radadinsa ina nan ana ce kamantadda ni ga mutuwarsa.*
*Filibbiyawa 3:10*

A wancan wasikar na baki labarin baptismata. Amma ban sami damar na rokeki gafara ba domin dukan irin laifufuka da nayi maki kafin na karbi Kristi. Sai fa tawurin kyawawan halayenki na gafartawa ne yakai ni ga zama Krista a yau. Ina rokonki ki karbi hakuri da nake baki. Kuma ina godiya domin kunshe kunshe da kuka aiko mani. Godiya mafi yawa ga Littafi Mai Tsarki da kuka aiko. Tunda Ubangiji ya nuna mani zurfin al'ajibin kaunarsa tsattsarka, sai na dauki kaina na zama ya mafi sa'a a duniya.

Na maida wahalun da nasha a zaman alherin Allah na musamman. Ina farinciki da Allah ya bani wannan gagarumin dama na shan wahala dominsa.

Ina rokon addu'a domin bangaskiya ta ta dage harkarshe. Bari Ubangiji ya kiyayeku ya kuma karfafaku domin wannan yaki, kada ku damu sabo damu. Muna da farinciki domin ladarmu a sama babbace. Ba'a sake samun labarin Varia ba, amma kaunarta da shaidarta domin Kristi ba za'a manta suba. Mai yiwuwa mugayen nan na hukuma sun kasheta su da suka sa ta a kurkuku domin bangaskiyarta.

***Abin so shine wasikarta na bishara yana haskakawa a zukatan dukan wadanda suka karanta ko suka ji labarinta. Rayuwarta ya zama shaida tsayayya game da yadda wahala take iya karfafa dankon zumunci a tsakanin mutane. Shan wahala domin Kristi yana iya kawo kusantar mu da shi ta hanyoyin da basu samuwa da sauki. Littafi Mai Tsarki na kiran wannan Zumunta da Kristi ta hanyar shan wahallunsa - Kusantar Kristi ta shan azaba wani abune da aka fi ganewa ta irin wahalar da aka sha. Yaya kaga naka shan wahalar shin yana kawo ka zuwa kusanci domin tafiya tare da Yesu Kristi? Ta kaka wannan ya faru?***

# MATSANANTUN MATAKAI

## Sudan: Pasto Jeremiah Logara

RANA TA 62

***Jeremiah Logara bai taba sanin komabaya ba sai dai kafewa kan abinda ya yarda dashi. Sojoji musulmi sun kama yara guda shida daga majami'arsa aka kaga musu laifi wai su yanleken asiri ne. A lokacinda jeremiah Pastonsu yayi kokarin yin bayani cewa su Kristane ba yan leken asiri bane, sai sojojin suka yi sha'awarar shima a kamashi.***

*Duk wanda yace yana cikin sa, Dole ne yayi tafiya kamar yadda Yesu yayi.*
*Yohanna ta Fari 2:6*

Sojojin Islama suka daure Pasto jeremiah sau da hannu gaba daya aka rabashi da kasa a rataye misalin kafa hudu da igiya. Suka yi masa bulala kuma suka dinga masa wani abu mai zafi da ake narka mai kamar dankon zuma a kirjinsa.

Ya tuna da addu'ar Yesu a cikin gona. Yayi addu'a "Ya Allah idan nufin ka ne in mutu yau, bari haka din ya tabbata". Bazan iya jimirin gazawa a gaban masu azabtadda shi ba watau su larabawan Sudan ta Arewa, a yayinda yake tsaye a gaban matasan nan Krista masu ban sha'awa.

Amma nufin allah shine ya rayu ya zama shaidar wadannan yara matasa. An sakeshi amma an tsare yaran. Pasto Logara yana kyautata zaton cewa watakila ana tilastawa yaran koyon aikin soja. A lokacin da wannan al'amari ya fadowa pasto a rai. "Na yi tunanin mutuwar Yesu, akan cewa Yesu ya mutu domin ceton dukan duniya. Na yi tunanin cewa maiyiwuwa mutuwarta ta zama dalibin ceton yarannan a yayin da na yi koyi da matakan da yesu ya bi. Ina addu'a cewa irin wahalar da na sha ya zama misali a garesu da kuma karfafasu su tsaya akan bangaskiyarsu ga Allah.

***Yaya sukan so su gaji iyayensu, ko wajen wasa ko wajen aiki sukan so suyi abinda sukaga iyaye na yi, sukanbi abinda iyaye keyi ko da ina zai kaisu. Kazalika bin Yesu yana iya kaimu bi ta hanyar da ke cike da jaraba. Muna iya binsa ko da hanyoyin yin haka na cike da jarabobi da wahalu da bazamu so ma kanmu ba. Idan fa mun sadaukar da kai gabin Yesu to ma'ana mun bada yancinmu na zaben makarnarmu. Bin Yesu yana baiwa yaranmu kyawawan misalai da ma sauran wadanda suke ganinmu su kwaikwaya. Turbar da muke bi tana da muhimmanci. Wace irin alama kake bari a zuciyar wadanda suke kewaye da kai?***

***Banyi rokon rayuwa mai sauki ba,***
***Ya Allah:***
***Rokona shine ka Karfafani.***

***Dan Bayahude - Wanda aka tsinta a cikin tarin rusashen gini bayan Yan Nazi sun saka ma wurin bamabamai.***

# MATSANANTUN WURARE

## Romania: Pasto Richard Wurmbrand

RANA TA 64

***Richard Wurm Brand wanda yake Pastor ne kuma dan kasar Romania wanda ya sha azaba a kurkuku har tsawon shekaru goma sha hudu, ya taba bada wani labari da yaji daga wani abokin kurkuku. Wannan ya taimakeshi yin jimirin lokuta masu wuya na azabtarwa. Mutumin ya fada masa kamar haka:-***

*Masu albarka ne ku a lokacin da mutane suna zagin ku, suna nuna maku banbanci suna maku shaidar zur, suna fadar mugayen abubuwa a kanku sabili da ni. Matt. 5:11*

Na taba zuwa kallon wasan circus naga wani nuni mai ban sha'awa. Wani gwanin harbi ya dora kunnannen kandir a bisa kan matarsa daga nan sai ya fice daga tsakiyar filin wasan ya gusa can da nisa, sai ya auna kandir da ke kan matarsa ya harbeshi.

Bayan an tashi daga wasan nunin. Sai naje wurinta na tambaye ta wai shin ba ta taba jin tsoron ko kibiyan zai sameta ba? Sai ta amsa. "Me zai sa naji tsoro? Ai kandir din yake aunawa ba ni bace".

A lokacin da Pasto Wurmbrand ya ji wannan labari sai yayi tunani, "Mezai sa naji tsoron masu azabatarwa? Ba ni suke aunawa ba. Suna iya dukan jikina, amma ainihin rayuwata Kristi ne ke cikina. Ina tare dashi a cikin ikon ruhu, saboda haka ba zasu iya taba mutumtaka ta ta ainihi ba.

Ta wannan siga ina kallonsu da ganin cewa kokarinsu na hana bishara aikin banza ne" Pasto Wurmbrand yayi rayuwa a cikin shekaru masu wahalarwa kuma sau da yawa takan kaishi ga kusan mutuwa. Amma ya sami karfafuwa ta wannan dan labari mai sauki kuma ya albarkatu a ruhaniyance domin yasan matsayinsa ga Kristi tabbatacce ne, ko da me zai faru da jikinsa.

***Ko da shike azabtarwa abune mai zafin gaske amma tana da iyaka. Ko azabtarwa ta jiki ko ta lamiri ba zasu iya kawar da zurfin tunanin mu na kowanene mu ba. Abin da muke dauka da a lamirin zuciyar mu shine abu mafi daraja, watau kurwarmu. Ruhun Kristi yana zama a cikin mu kuma yana karemu daga mugayen abubuwa na fama jikin mu da lamirin mu. Gaskiya ne makiyanmu suna iya su tar mana harma su iya kashe jikunanmu. Amma, duk lokacin da makiyan mu suka tar mana a zahiri suna gaba ne da sunan Kristi - wanda yake Allahnmu. Ko da kaka kiyayyar take lalle a dalilin Kri[illegible] suke yinta. Yakin yana iya shafar mu amma musani ce[illegible] shafi yakin karfin hali mai jurewa tsakanin nagari da m[illegible]***

# MATSANANTUN FUKAFUKAI

## Russia: Mai Kusumbi

RANA TA 65

***"Nayi shekaru da yawa a cikin kurkuku da dama na Sovie haka wasikar da aka rubuta da hannu ta fara. Rubutun na da tsabta, sai dai akwai shaidar alamar rawarhannu - wanda yake tuni ne na yawan shekaru da kuma dadewa a kurkuku.***

*Haka kuma yake ga tashin matattu. Akan shuka su da halin ruba, akan kuma da su da halin rashin ruba.*
*I Korintiyawa 15:42*

"A cikin sansanin, an tilasta mani nayi aiki a karkashin kasa a cikin ramin tonon ma'adinai. Aikin yana da wuya, masu gadinmu kuwa marasa tausayi ne. Watarana a can karkashin kasa hadari ya auku, na sami rauni a baya na, kuma tun daga ranannan sai na zama mai kusumbi.

"Watarana" wasikar taci gaba akwai wani yaro da ya kura mani ido, 'Malam', ya tambaye ni, me ka dora a bayanka? "Sai nayi zaton gatse ko shakiyanci ne ake so ayi mani, amma duk da haka na amsa masa na ce 'kusumbi?

"Yaron yayi murmushi mai kyau, "yace A'a, Allah kauna ne baya baiwa kowa nakasa, wannan ba kusumbi ba ne, akwati ne aka sa a kafadunka. Aboye a cikin akwatin kuwa fukafukan Mala'iku ne. Watarana akwatin zai budu kuma zaka yi firiya zuwa sama da fukafukan ka na Malaiku. "Sai na fara kuka domin farinciki" ko yanzuma, inji wasikar, a yayinda nake rubuta wannan wosikar hawaye na zuba. Azabtattun Krista da yawa suna da tabo na irin halin da suka shiga ajikunansu. Wasu lokuta Allah yakan tunashe su ta muryar karamin yaro mara aibi game da boyayyun albarku da ke cikin wadannan tabbuna.

***Abu guda daya tak ne zai yi mana tunin duniya a sama, Yesu, a cikin jikinsa mai daraja na tashi daga matattu ma ya nuna tabbunan shan wahala akan giciye. Yesu ya nuna tabbunan gefen sa da hannayensa ga almajiransa bayan tashi daga matattu. Thomas ya taba gefen da hannayen da hannunsa. Watarana hannayensa masu tabon-kusa zasu rungume mu, muma, a lokacin da muka tafi sama. Zasu zama abin tuni na kauna wanda ya kawo albarku ta wurin wahalar da ya sha. Amma fa tabbunan jikunanmu zasu shude a yayin da muka tashi da jiki irin na samaniya. Wadanda suka yi jimirin wahalu, zage-zage da rashin adalci dominsa zasu sauya tabbunansu daya bayan daya domin albarkun Allah masu yawa.***

## DAWOWA MAI TSANANI

### *Kasar Sin: Pasto Wang Min-Tao*

RANA TA 66

***"Ba zan yarda da haka ba" Pasto Wang Min-Tao ya fada wa sojojin Japan, "Ba zan rataya wannan hoto na sarki a cikin Majami'a ta ba.***

*Ku komo wurin Ubangiji Allahnku, gama shi mai alheri ne, mai jinkai, mai jinkirin fushi ne mai yawan kauna.*
*Yowel 2:13*

Shekaru da dama daga baya, kwaminis suka umurci Pasto Wang da ya rataya hoton shugabansu, Chairman Mao a cikin mafakarsa. "Bani ma da hoton Yesu a cikin Majami'ata, inji Pasto, na ki yarda na kafa hoton sarkin Japan, kuma naki na kafa ta Mao" An kama Wang a 1955, aka azabtaddashi har na tsawon shekaru biyu. Azabar ta kusan haukatadda shi, a karshe ya rattaba hannu a wata yarjejeniyar karbar laifi da yayi wa kasar. Da wannan karbar laifin Pasto Wang ya sami saki daga kurkuku.

Amma bai sami salama ba bayan ya fito daga kurkuku, sai yake kiran kansa Yahuda Iskariot, ya kuma ce kamar Bitrus nake a lokacin da yayi musun Kristi", a karshe sai ya koma wajen yan sandan kasar Sin.

"Na janye karbar laifi da nayi", ya fada musu yace "Kuyi yadda kuka ga dama da ni" masu gadin basu gamsu da kaishi kurkuku kawai ba. Sai suka kara har da matarsa. A cikin wata wasika daga kurkuku, ya rubuta, "Kada ku sami damuwa domina, ina da daraja fiye da hankaki da yawa". Wang Min-tao ya mutu a kurkuku domin laifin kaunar Mai Cetonsa.

***Wanene ba zai so yayi jarumtaka kamar na Bitrus ba wanda ya buge wadanda suka zo kama Yesu Kristi cikin kyaftawa da bismillah? Wanene kuma zai ce baya son zama kamai Bitrus, wanda ya yi musun Kristi kusan a lokacin guda cikin tsorotarwa da ya samu ta makiya? Allah ba ya gargadaddamu domin mutumtakarmu. Ya kan karbi gazawar mu yayi aiki damu har sai mun sake jin karfi. Kamar dai yadda Allah ya farfado da Bitrus da sauran masu bada gaskiya kamar Wang Min-tao zuwa matsayin bangaskiya, zai farfado da jarumtakarmu mai karfin jiki kuma. Ko ka taba kaucewa wata dama ta tsayawa daram domin Kristi, ka roki Allah ya farfado da kai ayau. Zaifara shirya ka ko a yanzu ma domin wata damar inda zaka tsaya da karfin jiki.***

***...isti***
***...wa ya***
***...ugu.***

# HANGE MATSANANCI

## *Romania: Florea*

RANA TA 67

***"Ubangijin mu ya umurcemu da mu tuna da ranar Sabbath kuma mu tsarkake ta" Florea ya shaidawa masu gadin kurkuku a tsanake. "Ba zan iya yin aiki a wannan rana ba".***

*Ku dauki halin Almasihu Yesu, Filibbiyawa 2:5*

Ana tilastawa fursunoni suyi aiki a kullum, amma a kowane Asabar Florea ya kan ki yin aiki. A dalilin kin aikin masu tsaro sukanyi masa duka akai-akai har ya kai ga yakasa anfani da hannayensa da kafaffunsa. Kansa kawai yake iya motsawa. Da yake ba zai iya kara yin aikin bautaba. Ana tilasta wa Florea ya zauna a dakinsa duk wuni. Sai da ya dogara da sauran fursunoni domin su ciyar dashi, duk da irin wahalar da yake ciki Florea bai jijjiguba.

A lokacin da wasu fursunonin suke kuka da wahalarsu, Florea yakan karfafa su. "Idan hangen ba shi da mafita", to ayi kokari ayi anfani da duban sama, a lokacin da aka jejjefi Stephen ya dubi sama kuma ya ga Yesu a tsaye a hannun dama na Allah. Wannan ya ta'aziyantar da Stephen a zuciya kuma zai ta'aziyartar da naka ma". Ya karfafa abokan kurkunsa domin kada suyi "hange waje" akan al'amuransu, amma su "duba sama" ga Yesu.

Daya daga cikin abokan kurkukun Florea shine Richard Wurmbrand wanda ya sami saki daga kurkuku kuma ya sami dan Florea mai shekaru tara da haifuwa. Ya shaida masa irin albarku da babansa ya samar a kurkuku. Yaron yayi murmushi ya amsa "Ina da sha'awar in zama mai shanwahala kuma mai karfafawa domin Kristi kamar yadda Ubana ya zama".

***Krista bashi da wasu al'amura- Da gida maikyau kammalallen iyali, kyakkyawar lafiya, A'a Krista mutum ne mai wani irin hali game da dukan al'amura. Halayen mutum shike nuna bambanci ko da ta kowane hali ne. Halin biyayya da Allah yasa hangen sa ne ga Allah a lokacin jarabobi. Dogara ga namu wahalu yana janye hankulanmu daga duban sama. Idan muka ji nauyin damuwa, takaici, da mutuwar zuciya, akarshen haka dogara ga Allah game da damuwarmu yana kawo amincewarmu cewa Allah yana aiki dominmu. Mu natsu agaban Allah mu jira muga yadda zai sarrafa damuwar mu. Kana cikin jarabtuwa ne a yanzu? Ina kake hange? Ka tambayi Allah ya daidai ta kuzari naka domin ka iya hange gaba da damuwarka domin ka sami sanin kusantarsa da kai.***

## MATSANANTUN SARKOKI

## Cuba: Wani Krista Fursuna



***"Sa hannu kan wannan bayanin" Hafsan Cuba yayi magana da karfi, yana tilasta wa shi krista din alkalami a hannunsa "sa hannu a bayanin!".***

*Saboda haka, tunda shaidun taro shaidu masu dinbin yawa suka kewaye mu haka, sai muma mu yar da dukan abinda ya nauyaya mana, da kuma zunubin da ya dafe mana, mu kuma yi tseren nan dake gabamu tareda jimiri.*
*Ibraniyawa 12:1*

Rubutaccen bayani dake gaban fursunan yana kunshe da jamhuru akan wasu Krista. Sa hannunsa kadai gwamnati take bukata domin a kamo su a tsare. "Ba zan yarda na sa hannu akan wannan takarda ba", shi Kristan ya fada cikin ruwan sanyi yana duban hafsan a ido. "Me zai hana?" Shi Kaftin din ya tambaya cikin ruwan sanyin gaske, kafin ya fusata. "Shin baka san yadda zaka rubuta sunanka bane?" Dalilin sarkokin nan ne, abokina. Sarkokin basu bani damar sa hannu ba". Ya rarumi fursunan da karfi a hannuwansa ya daga su a gaban fuskarsa, Amma ai gashi ba a daure kake da sarka ba, kai wawa" yana magana da karfi. "Ayya, amma a daure nake". Inji shi Kristan, "A daure nake da sarkokin shaidu wadanda suka bada rayukansu domin Kristi tun shekaru daruruwa da suka shige. Ni karan kaina mahadine na wannan sarka, kuma bazan iya katse sarkar ba".

Ko da shike an tsoratar da shi kuma an jijjiga shi, fursunan yaki ya sahannu.

***Shadidan Krista sukan bar darasi na shaidar abubuwan ban mamaki acikin al'amura masu firgitarwa da suka faru dasu. Jarumtakar su tana da karfi, kalmomin su suna da hikima. Natsuwarsu bata jijjiguwa. Thomas Aquinas ya rubuta, "Kalama da shahidai suka furta a gaban hukumomi, ba daga dan adam suke ba, bayani mai sauki na rinjayar dan adam, amma kalmomine na ruhu Mai Tsarki da suka fito ta bakin masu shaidar yesu". Daga rayuwa zuwa wata rayuwar kuma daga mahadi zuwa wani mahadin, duk kalmomin da aka fadesu ta wurin ikon ruhu Mait Tsarki a lokacin da ake cikin tsanani suke zama kwararan shaidu. Kai, ma, kana da halin da zaka iya kara naka dabi cikin shafukan. Kai, ma, mahadine a cikin sarkar masu bi. Zaka ga lalle sarkan nan tama hade?***

# MATSANANCIYAR MAKARANTA

## *Lithuania: Nijole Sadunaite*

RANA TA 69

***Halin da ake ciki babu dadi, kusan ma matsanancine. Mashamanta ta Lithuania tana taro domin yankewa Nijole Sadunaite hukumci. "Laifin" ta kawai kamar dai na mutane da ma, za ma Krista akasar da ke na kwaminisanci ne.***

*Ka shiga bautata kuma ku koya a gareni. Matta 11:29*

Sa'anan akarshe mai sharia ya bata damarta yi magana. Yana dokin cewa wannan mata ma karancin shekaru zata nemia yi mata afuwa cikin kuka da hawaye. Watakila ma tayi musun bangaskiyarta ga Allah wanda a ganinsu wai shirmene. Amma aiyaga abin mamaki. Babu bawaye daga idanun Nijole Fuskarta tana haske, ga kuma murmushi, mai kyau idanunta cik da annuri kai har ga masu tsananta mata.

"Wanan ita ce rana mafi farinciki a gareni", Inji wannn mata da aka yanke wa hukumcin kisa. "Anasharantani domin manufar bangaskiya da kauna zuwa ga mutane".

A wannan lokacin fa sai dukan idanu a cikin dakin sharia suka karkata zuwa gareta. "Kaddarata abin kyashi ne, rabo mai fifiko. Wannan hukumci da aka yi mani a dakin sharian nan shine nasara ta karshe. Abinda tafiji kwarai a ranta wanda baya boyuwa shine in da tace, "Bakin cikina kadai shine gwagwarmaya ta domin mutane kadan ce. Bari muyi kaunar juna, domin dukan mu muyi murna. Wanda bashi da kauna shike zama cikin bakinciki". Sai ta juya baya ga mai sharia ta fuskance masu bi da suke dalin sna sauraren shari'artace, "Dolene muyi tir da muguntar, amma lallene mu kaunaci shi maiyin muguntar wannan kum a zaka iya koya amma sai a maarantas Kristi."

***Idan akazo batun koyo akan wadanda aka azabbtar domin kristi, a yi lura, muna iya karatun labarun shahidan Krista a cikin gidayenmu, ko ma'a unguwanninmu. Muna ma iya yin rawa a yayinda muk bude shafanan. Ammashin a shirye muke mu shiga Makarantar Yesu Kristi? Ashirye muk muyi nazari tare da su wadanda suka yi tafiyar kadaici nbe shanwahallada azaba. Lallene muyi anfani da abinda muka koya daga garesu akan bangaskiya, kauna, tsarki da jimiri. Sai fa muyi koyi da wahalun da Krisi ya sha ta wurin sanin abinda muka koya daga wasu sa'annan zamu iya kiran kanmu Krista na watau "yan kanann Kristi" sa'anna cin nasarar jamrrabawa.***

***Shan wahalayanaiya hana yin zunubi,
amma zunubi baya iya
taba hana shan wahala.***

***Sharhi da aka rubuta da hannu a
shekarun 1800 Littafin Fox Mai Suna
LITTAFIN SHAHIDA! ITA TA BUGA***

# BAYANI MAI TSANANI

## Romania: Pasto Richard Wurmbrand

RANA TA 71

***"Karya kake fadi" Hafsan soja Leftana Grecu ya daka wa Pasto richard Wurmbrand tsawa. "Kafada mana gaskiya akan ayyukanku na Krista da kuma sauran mabiya na majami'arku! Gashi ka rubuta mani duk dokokin kurkuku da kuka karya".***

*Yanzu kuma ya Ubangiji, dubi wannan kashedi nasu, ka yiwa bayinka baiwar yin manarka da iyakan karfin hali.*
*Ayukan Manzani 4:29*

Wurmbrand ya zauna shiru ya rubuta dukan dokokin da ya karya. Da ya gama, sai ya kara sakin tayi daya "Ban taba magana gaba da kwaminisawa ba Ni Almajirin Yesu Kristi ne, wanda ya bamu kauna domin makiyanmu. Na gane su kuma ina addu'a dominsu juyo su zama yan'uwana a cikin bangaskiya" sai yasa sunansa a manyan harufa a karkashi.

Grecu ya karanta "bayanin". Fuskarsa kuwa cike da murna cewa Warmbrand zai iya rubuta batun kaunar gwamnatin da ta kamashi kuma ta azabtadda shi. "Wannan kauna" inji shi "Itace daya daga cikin krista da ba za'a iya kebewa ba".

"Batun ba na kebe doka bane", richard ya amsa a hankali, "A lokacinda na zama krista sai na zama kamar an sake haifuwata, da sabon hali cike da kauna. Kamar dai yadda ruwa kadai ne ke gudu a kogi, haka kuma kauna kadai ke fitowa daga zuciyar da take cike da kauna".

A cikin watanni da suka biyo baya Wurmbrand ya yi magana akan kaunar Kristi sai tarin yawa ga Leftana Grecu, wanda sannu a hankali yayi addu'a ta karbar kristi!.

***Bayana bangaskiyarka a cikin Kristi domin wasu suji kuma su karba. Wannan bai nuna cewa kai ma son kai bane. Bai kuma nuna cewa ka zama dabam da na kullum, mai ban mamaki ba kuma mai yawan magana. Ma'anarsa kuwa shine kaifa budadden Littafine domin wasu su karanta labarin Yesu Kristi. Kuma kazama mai shirin karanta littafin da murya a duk lokacin da ta koma ayi haka. Galibi mukanyi sanyin jiki wajen shaidar kristi. Ba mu da niyar bata wa kowa, kuma bamaso akarbe mu da sanyin jiki. Duk da haka yin shiru shiru wajen shaidarmu zai sa mu rasa damar kai wani ga bangaskiya cikin Kristi. Yaya zai zama a gareka idan ka bayyana bangaskiyarka cikin Kristi a yau? Ga wa zaka nuna ma tsayinka kuma ka isar da labarin alherin Allah?***

## SADUWA MAI TSANANI

### *Spain: Antonio Herreeuelo*

RANA TA 72

***Vodashike ana kona shi a sarkaje a itace ta wurin dakar Hukumomin Spainish ne, Antonio Herrezuelo yana jin zafi a lamirin sai ya gane matarsa ta juya tayi musun Yesu domin ta tsira daga irin kisa da shi yake fuskanta.***

*Bayan wannan na duba ga wani kasaitaccen taro, wanda yafi gaban kirge, daga kowace al'umma da kabila, da jama'a da harshe suan tsaitsaye a gaban kursiyin a gaban ragon. Wahayin Yahaya 7:9*

Da Antonio ya ceci ransa da daurin rai da rai a kurkuku zaiyi kamar matarsa. Watakila ma watarana ayi masa afuwa ya sake saduwa da matarsa.

Amma yaki, kalmomin karshe da ya sani damar furtawa kafin sojojin su doke bakinsa sune rokon matarsa da yayi. Ina rokonki, ki dawo wurin Kristi a yafe maki zunubanki, zamu sake saduwa a sama "Ina rokinki, ki dawo" yayi wa matarsa magana da karfi. Ko da shike bashi da sa rai ga saduwa da ita a duniya, yana so su sadu a sama ciki rai madawami. Bayan mutuwar Mijinta, sai aka dawo da ita a kurkuku domin tayi zaman daurin rai da rai. Tayi shekaru takwas tana jayayya da Allah da kuma nata lamiri ta ransa salama domin irin shawara da tayi can baya.

A karshe ta dawo ga bangaskiya cikin Kristi, ta janye musun Kristi da tayi, ko da shike masu ganin kunta na karni na goma sha shidda sunai mata barazana Mai sharia yayi mata hukumcin kisa a daure a jikin nafaffen itace, watau hukunci na biyu kuma na karshe.

Ta kosa a zantas da hukumcin kisa domin ta sami saduwa da mijinta. Ko da shike Malama Herezuelo tana dab da mutuwa amma cike take da salama, tana tunanin kalmomin farko da zata fada mashi sune dawowarta ga bangaskiyar ta.

***Sake saduwa a sama zai zama abin al'ajibi! Dukan wadanda suka wahala suka mutu domin bangaskiyar su a cikin Kristi zasu haskaka kamar kwafsai na alherin sa da jin kansa.***

***Iyalin da mugayen hukumomi suka raba su zasu sake wanzuwa. Maza da matansu, iyayeda yayansu. Abokai da makwabta daga kasashenda aka mamaye da wadanda aka sa sukayi gudun hijira zasu sake ganin juna. Yan majami'ar karkashin kasa da mambobi na kasashen da aka sha tsanani zasu bayyana da labarunsu na ceto na biye. Labarun kadai ma zai dauki lokaci kafin a gama fadarsu shaidu daga shahidai na shekaru aru-aru, akan cikawar alkawarin Allah. Zaka bayyana a sama domin ji? Fiye da haka zaka sami naka labarin domin maima ka bayar?***

# ALHERI MATSANACI

## *Kenya: Wata Gwamruwa*

RANA TA 73

*Ku jure wa juna, in kuma wani yana da kara game da wani, sai su yafe wa juna kamar yadda Ubangiji ya yafe muku, ku kuma ku yafe.*
*2 Kolosiyawa 3:13*

***"Kafin mu karasa wannan addu'a ta jana'iza" kalmomin maganar da takeyi suna fitowa sarai sarai ga dubban mutanen da suka hallara, "Ina so in fada maku abinda mijina ya gaya mani kafin ya mutu. Yace mani in shaida wa dukan makasansa cewa ya tafi sama cikin kaunar kowa da zuciya daya har da wadanda suka kashe shi. Ya gafarta wa dukansu abinda sukayi domin Yesu yana kaunarsu kuma zai gafarta mus".***

Ta tsaya inda akwati mai dauke da gawan mijinta yake. Ga hawaye kuwa a idanunta, amma muryarta da karfi. Kukkujewan da ke jikinta yanuna wa masu makoki cewa ita ma tasha duka. Da yake ita da mijinta Kristane su, sai suka ki su dauki rantsuwar al'ada taki kuyu wanda bashi da nasaba da addinin Krista. A dalilin wannan akayiwa mijinta duka har mutuwa, ita kuwa akayi mata duka har aka kwantadda ita a asibiti.

Taro yayi tsit, kalamu masu karfi da suke fitowa daga bakinta da karfin halinta ya sa kowa yayi shiru. Mutane da yawa da suka zauna a kanya a shekarun 1969 sun sha razanarwa da hari da ake kai musu domin darajar da suke baiwa bangaskiyarsu maimakon bautawa al'adu.

"Ni a zaman gwamruwa, ina gaya muku duka, a gaban gawar mijina, cewa bana kiyayyarsu da suka kashe shi, ina kaunar makasan, na gafarta masu, sanin suma Kristi ya mutu domin su"

Babu wani a cikin wadanda suka halarci wannan jana'iza da zai taba mantuwar kalamun wannan gwamruwa kokuma darasin misalin matsanancin gafartawa da kuma alherin allah.

***Gafartawa misali ne mai tsanani na me ake nufi da zama kamar Kristi, daya fada alherinsa ga mutane. Babu wanda ya taba gafartawa fiye da yesu Kristi. Babu abinda za'a kamanta da nauyin zunuban dukan duniya akan kafadunsa a kalfari. Saboda haka lokacin da muka gafartawa makiyanmu bamu zama kamar Yesu ba a wannan lokaci. Gafartawa baya mai da kurakuran da aka yi maka su zama daidai ba. Amma gafartawa yana kwantar da zuciya.***

***Gafartawa bai nuna cewa masu aikata laifin sun kubuta kenan ba. Gafartawa yana nufin kubutadda kanka daga zurfin tnanin yin ramuwa. Gafartawa wasu kurakuransu yakan ba da dama ka haskaka domin Kristi fiye da yadda ake zato. A ina zaka haskaka fitilar gafartawa ta Allah a yau?***

# MATSANANCIN ALHERI

## Romania: Barto



*Iko kuwa kana raina yalwar alherinsa, da jimirinsa, da kuma hakurinsa ne? Ashe ba ka sani ba alherin Allah yana jawo ka ga tuba? Romawa 2:4*

***Barto ya bakin mutuwa don rashin abinci. A da shi ma'aikaci ne na siyasar kwamnis kuma lauya ne mai tsayawa gwamnati, amma a yanzu dai anga cewa ana iya yi babushi a wannan kungiyar siyasa. An yanke masu sharia'ar yin aiki sansanin kurkukun romania. A da kasashe ne kullum cikinsa cik da abinci amma yanzu sai lalacewa yake yi sabili da rashin abinci. Sai tunani yakeyi wai to har zuwa yaushe zai ci gaba da zama haka?***

Garin ramammen jikin Barto wani fursuna ya zo wurinsa yace su raba abinsa. Sai barto ya ce masa "Na gode abokina, shekaru nawa zakayi anan"? Yayi wannan tambayar a lokacin da yake cin abinsa "shekara ashirin" inji daya fursunan idanunsa cike da alamum tambaya a yayin da ya dubi Barto.

"Laifi me ka yi"?]
An sha'antanu domin na baiwa wani maigudun hukum abinci pasto ne shi kuma yana godune dan Yan Sanda suna neman su kamashi", mutumkin yayi bayani a hankali. Sai barto ya lurada cewa muryar mutumin nan bata nuna yana bakin aiki ba kamar na sauran da Batro yyi hira da su.

Wanene ya baka irin wanan mumunan horo domin kayi abin Kirki? Barto ya tambaya. Fursunan ya amsa cikin sauki kai. Ranka ya dade kaine mai kore gwamnati a wannan sharia'ar tawai "Baka iya ganeni ba yanzu amma ni na gane ka"

***Alheri shine hanyarmu tashiga zukatan makiyan mu, kuma kakan zai iyayin wani abu game da ruhunsu. Allah yana anfani da alheri a zamanshirinsa na zabi a lokacin da yake so yayi anfani da mu. Maimakon ya ba mu daidai abin daya cancance mu game da laifoinmu da muka yi masa sai ya tausaya mana. Jinkansa misali ne na yadda ya kamata mu bi da halin tausayi game da wadanda suka yi mana laifi. Tausayawa yana juwo hankalin su, don takanzo a zaman ba za's kuma shi da akeyi ma din yasan baimaci ayi masa ba amma kuma akayi. Kamar Barta tau sayawar mu ga makiyina iya farkadda yunwar ruhaniya a zaman masomin juyayin mu. Duk da haka kom menene amsar da zasu bayar dolene muyi koyi da misalan Ubangijin mu a lokacin da muke ma'ammala da makiyamu. Who needs your kindness today?***

## Russia: Iyaye da ke Fursuna

RANA TA 75

*Hakika ina gaya maku, duk wanda baiyi na'am da Mulkin Allah kamar yadda karamin yaro keyiba, ba zai shiga mulkin ba har abada". Markus 10:15*

***A kasashe marasa yanci, yayan Krista sukan sha wahala kamar yadda iyaye suke sha. Duk lokacin da aka tsare iyaye maza da mata domin laifin yin ayyuka majami'u, galibi yayan sukan zama tamfar marayu. Idan sunyi sa'a, to wasu yan'uwansu ko kuma abokai suna iya kula da su.***

***Ko kuma, in ta baci, sai a aika dasu zuwa gidan marayu ko makarantun da gwamnati ne ke gudanar da su, Babu sauran koyaswa ta Littafi Mai Tsarki kuma babu sauran addu'ar tare ta iyali kafin aci abinci.***

Wasikun da yara suka rubuto wa iyayensu da ke kurkuku ya nuna karfin hali da dgewa a yayin da suke cikin mawuyacin hali na rabuwa. Kalamansu sun nuna akwai bege na sake saduwa.

Allah ya albarkace ki masoyiyar uwarmu. Kada ki sami damuwa a dalilin wannan rabuwa namu na wucin gadi wannan rabuwa ba na harabada bane farincikinmu zai sake dawowa ba da jimawa ba, bari wannan tunanin ya karfafa ki. Mahaifiyata ba na iya kintata irin buki da zamuyi a ranar dawowarki, ina nan ina kokari a ayyukana na makaranta yanzu dare yayi gobe ma wata ranace. Muna tafiya daga rana zuwa wata ranar lokaci na ja amma na sani cewa zamu sadu nan bada jumawa ba. Ina yi maki sumba. Diyarki mai kaunarki".

Zuwa ga Uwata, idan kika dawo gida, ba zan kara tunani aka kadaicida jin zafin haka kumaba. Ina rokonki kada ki yi kuka, Uwata ina kaunarki, na rubuta waka dominki.

"Kina da zuciyar zinariya.  
Kina da budurwar zuciya ba tsofoba.  
Ubangiji yana lura da ke daga sama  
Zamu sadu tare nan ba da jimawa ba ka dani".

***Idan aka zamaganar tsanantawa musu bi a kullum yara sune na karshe a tunanin al'amuran da zasu shafe su. Ga kowane iyali da aka tsare akwai yaro ko yara da abin yake shafa. Mun sani Yesu yasha jawo hankalinmu sau da yawa cewa bangaskiya yaro tana da muhimmanci. Idan yaro zai iya nuna karfin hali mai ban mamaki a tsakiyar al'amura nasu wuya to wace hujja ke garemu? A zaman muna manya, muna kasa da zuba ido kwarai akan duka da kasalar da rayuwa yake kayowa. Akwai riba idan muka kwaikwayi yaran nan. Tawace hanya kake bukatar girma yakamata bangasiya yaran? Kafara yau tawurin tunawa da yaran.***

# MATSANANCIN ZANGA ZANGA

## Russaia: Kristocin Baptist



*Kaima sai ka zama gurbi na aiki nagari ta kowa ahanya da kuma sahiliyar magana da na za'a rushe mata badon a kunyata abokan hamayya su rasa hanyar Zarginmu*
*Titus 2:7-8*

***Wannan zanga-zanga kusan makamar duniya bata taba ganin irinta ba. Yawancin tarzoma a cikin duniya sukan zo da rikici, suna zuwa da takensu da ake rairawa ko kururutasu, ga alamu da take na tuta ana daga su, wani lokaci ma ana jifar duwatsu. Amma ranar 16/5/1966, yan Soviet da suke Baptsit sun taru a filin tsakar gida na Babban Kwamiti na tsakiya na Soviet. Amma ba kamar sauran yan zanga zanga ba, ba suyi ihun wani take ba ko na biyan bukatarsu.***

Suna tsaye ga badayansu suna addu'a suna wakoki. Georgi Vins da Gennadi Kryuchkov suka mika takardar kara ga gwamnatin Soviet a madadin su, suna nma a amince da zaman majami'unsu, roko domin gwamnati ta daina yi musu katsalandan, sakin fursunan Krista, dama domin yan kasar Soviet su koyar ko su koyi bangaskiya ta addini. Da safiyar 17 ga wata, jamian soja da na KGB suka kewaye wannan taro mara tarzoma. Wajen karfe daya na rana kuwa motocin safa suka matso sojoji kuwa suka kai wa mutane hari suna masu duka suna tilasta masu shiga motocin, babu wanda ya maida murtani. Maimako ma masu zanga-zanga suka kama hannayensu suna wakoki bayan su sojojin suna tayi musu tsawa. Duk wadannan a titi akanyisu ga kuma mutane suna kallon tsayayar bangaskiya ta Krista. Daga nan aka kaisu kurkuku.

Har a kurkuku ma sunci gaba da addu'a da wakoki, kwaminis ta ki karba rokon wadannan masu zanga-zangar lumana, amma basu karya alkadarinsu ba.

***Wadanda suka maida addinin Krista a zaman sanadi suna kasadar rikrtuta ma'anar aika-aika da kalmar biyaya. Wannan bayani haka yake. Biyaya mai tsauri yana nufin muyi kiyaya da dukkan abinda ke gaba da koyaswa Kristi. Amma kamar yan Baptist na Soviet manufar mu salama ba tayarda hankali ba. Su wadanda ake musu tsananidomin bangaskiyar su sun bar misalin zanga zanga ta lumana da kuma dagewa. Ba su taba rama mugunta da mugunta ba a kullum sukanyi na'am da abin da yazo musu cikin natsuwa shine kuma sakamakon biayyarsu ga umurnin Kristi. Idan kana so ka zam Krista mai tsaurin ra'ayi dole ne kabi dokokin Kristi a cike. A gareka me ake nufi da krista mai tsauri?***

***Dalilin, ba wahalar ba,***
***ita take yin shahidi na gaske.***

***WALIYI AUGUSTINE***

# KAYAN AIKI MATSANANTU

## *Kurkukun Kwaminis: Wani Pasto na Krista*

RANA TA 78

***"Menene ya sa Krista da yawa sukan yi wakoki sau daya kawai a mako? Idan ya dace ayi waka, to a dinga waka a ruhun. Idan yin waka ba daidai bane, to kada kayi waka a ranar Lahadi***

*Ku zo mu yabi Ubangiji!*
*Mu raira waka domin*
*farin ciki ga Mai Kiyaye mu.*
*Da mai Ceton mu.*
*Zabura 91:1*

Wannan Pasto yayi shekaru da dama a kurkuku a hannun kasashen yan Kwaminis. Aka kai shi kurkuku a dalilin bangaskiyarsa ga Kristi, kuma ko da shike yana tunawa da irin azaba da yasha a can, bai tsayar da hankalinsa, a kansu ba, maimakon haka shi maganar farinciki a gaban Ubangijinsa yake yi. Da shi da sauran fursuna da suke Krista suka kafa kungiyar sujada ta yabo a cikin tsakiyar kurkukun.

A lokacin da muke kurkuku, kusan kullum muke waka, domin Kristi yana raye a cikinmu. Kwaminisawan sun yi mana kirki. Sun san mu masu sha'awar yabon Allah ne ta hanyar anfani da kayan kida, sabo da haka sai suka baiwa kowane Krista da ke cikin kurkuku abin kida ko abin busa. Ko da shike basu bamu molo da kalangu ba domin suna da tsada ainun maimako sai suka sa mana sarka a hannayenmu da kafafunmu. Sun daure mu ne domin su kara kuntata mana. Duk da haka sai muka gane cewa sarkoki na iya zama kayan kida. Idan muka motsasu tare gaba dayanmu ko kuma kashi-kashi za mu iya yin waka "Wannan it ace ranar (sai mu motsa sau biyu) wannan itace ranar daya yi (mu motsa sau biyu) "sheidaar farin ciki ga Ubangji!

Ga wadanda basu taba shiga tsanani ba tukana, suna ganin kamar tsanani ya shafi fuskantar rashi. Rashin yana nufin rashin bege, kai har rashin rai. Saboda haka su d suka sha azaba a dalilin bangarskiyarsu a cikin Kristi, basa duban abinda suka rasa, sai dai duban abin da zai zama koyarwa a garesu. Sukan nuna jin dadin dan yanci da suke samu, maimakon yin bakin ciki akan abinda suka rasa. A wannan labari Kwaminis sun hana wa Krista yancinsu na rayuwa da na martaba. Duk da haka wadannan karfafan masu bi sun fuskanci abin day a rage a garesu watau fari cikinsu a cikin Ubangiji. Idan yana da kyau a raira wakoki ga Ubangiji a lokacin da kana da kome da kome yana da kyau kuma ka yi masa wakokin yabo a lokacinda ka rasa lome. Me ya kamata kayi ayau domin kada ka rasa farincikin ka na Krista?

# MISALI MAI TSANANI

## Colombia: Chet Bitterman

RANA TA 79

***Yan sari-ka-noke masu damara da kayan fada da kawunansu rufe da kokuwa, na Kungiyar yan tawayen Marxist da ake kira M-19, suka daure mutanennan Goma sha Biyu da yara guda Biyar wadanda aka taras a cikin ofis na Wycliffe inda ake fassarar Littafi Mai tsarki a garin Bogota ta kasar Columbia***

***"Ina Shugabanku yake? Ina Al-Wheeler?" Jagorar gungun yana ihu a fuskar daya daga cikin sakatarorin. "Muna son Wheeler"!***

*Kuyi koyi dani kamar yadda nake koyi da Almasihu I Korintiyawa 11:1*

"Kada kaji mata ciwo ya ji wani yana fadi, "Wheeler ba ya nan", Shi dantawayon Maraxist ya tashi kamar zai buge shi, amma sai ya sake shawara. "Shikenan, zamu dauke ka maimako, mutafi!"

Bukatarsu ta iso bayan kwanaki. "Idan kungiyarku bata bar Columba a 19 ga wanta Fabrairu ba zamu hallaka fursunan". Har dan-tawayen ya kira shugaba Reagan ya kuma nemi a buga manufarsu a cikin jaridun Amirka na New York times da Washington Post in ko ba haka ba Mr. Chet Bitterman zai mutu.

Da ranar ta kusato, sai aka shirya yin addu'oi. Sai aka sami sako afaifan tep na wata tashar rediyo cewa Chet yana yiwa yan tawaye bishara. Matarsa Brenda kuwa ta sami wasika ana nema Littafi Mai Tsarki cikin harshen Spanish.

Chet ya cika manufarsa ta rayuwa - na watsa bishara a duk in da ake bukata. An tsinci gawar Chet a cikin wata mota kirar bus da an sari-ka-noke suka bari. Mutane Columbia tare da Krista da ke fadin Amirka, sunyi tunawa dashi da kuma cika gurbin daya bari. Shekaran da yabiyo wannan kuwa da yawa sun aika da takardan nema domin a basu damar yin aiki da Makarantar (Fassarar) Littafi Mai Tsarki ta Wycliffe har yawan su ya rubanya.

Shugabanci ta wurin nuna misali sannane hanya ne na koyarda masu gudanarwa a ma'aikatu.

Bukatar ma'aikata akan shirya su ne bisa ga abinda aka fi bukata da fari ko kuwa cikin sauri kuma manyan ma'aikata su, ke wanzar da wannan bukata. Amma in anzo batun addinin Krista, Shgabanci ta nuna misali yana da muhimmanci. Alhalima Yesu ya bad J wannan umarni ya nuna yadda dole shagabannin Krista su nuna bangaskiya domin sauran mabiya suyi koyi. Ba koyaswarsa kadai ya bamu ba - yayi su a rayuwar sa. Mutane nawa ne cikin mu suke a shirye su rabu da rayuwar su ta tsaurin biayya ga Kristi? Idan haka ne, ba zamu yi kokarin jan ragamar kaddarar mu ba. Zamu zama misali ga wasu kamar yadda muke bin misalan Yesu. Wa ke lura da rayuwarka yau? Me suke koyo daga misalan ka kuma yaya kusancinka da yesu a wajen bi?

# SHIRYE-SHIRYE MASU TSANANI

## *Sudan: Yayan Sudan*

RANA TA 80

***Ramukan Yanyawa a cikin filin makaranta - akwai su barkatai a kudancin Sudan. A tsakiyar filin wasan da ke cike da yara suna gudu da wasa da dariya akwai wani katon karfe mai zumbutu da filafilai a wutsiyar sa rabinsa a binne a cikin kasa. Akwai tuta a kafe-inda wannan bomb yake a zaman tuni ga yaran kada suje kusa.***

*Duk wanda yake da Dan yana da rai, wanda bashi da Dan, Allah kuwa ba shi da rai.*
*I John 5:12*

Ba da jimawaba wadansu mutanen Mishan sunkawo wa wadanan yan makarantar elmantari taimako a gunduma. Kamar dai yawancin wurare a Sudan, ita wannan makaranta dakyar ake gudanar da ita domin rashin kaya da kuma malamai.

Wannan makaranta tana wuri ne wanda ita Gwamnatin Sudan ta Islama takan jefo bomb akai-akai a wannan yankin.

Wadannan yara sun tona fiye da ramuka ashirin na Yanyawa da hannuwansu a kewayen makarantar. Sun shirya wa kansu kariya ko da masu jefo bomb zasu kawo hari. Idan suka ji karar jirage masu fefo bomb sai su gudu su shiga ramukan, suna kuma maida hankali suga ina barbadin karafan bomb da ya fado ya fashe zai bi. Wadansu sukan tsere sukai bakin rami, amma wadansu ba sa kaiwa.

A lokacin da kungiyar Mishan ta tambaya ko me za'ayi a taimaki yaran, amsar tambayar mai sauki ce, "Ayi addu'a domin su sami kariya.

Littafi Mai Tsarki ya koya mana cewa masu bi dayawa a da sunyi zaman rashin dadi domin su iya kebe bangaskiyarsu a cikin Kristi.

Ga wadannan yara shanwahala ko ma mutuwa domin bangaskiyarsu abune da zai iya faruwa a koyaushe. A garemu su baraden sojojin Kristine.

Yaran Sudan ashirye suke su yi yaki anan duniya. Fiye da haka a shirye suke wata rana su shiga ta kofar sama. Sunyi irin tsaro nasu na duniya don yin kariya daga karafe masu firiya idan bomb ya fashe. Kuma bangaskiyarsu ga Kristi yana basu tsaro na har abada a wurin Allah. Watakila kamar yaran Sudan da suke wasa kusa da bomb. Ya kamata a ce ka koya cewa, galibi rayuwa ya na faruwa ne sa'adda hadari ma yana kusa. Mai yiwuwa ka dau matakin kare rayuwan ka a duniya, da fatan mafi alheri cikin rashin tabbas. Shin ko kana bin misalinsu na shirin rayuwa bayan na duniya? Kana da shiri domin rai madawami? Tawurin dayantaka da Yesu Kristi?

# MATSANACIN JUYI (NA DAYA)

## *Romawa: Kristocin Timisoara*

RANA TA 81

***A lokacinda mawallafin wakoki Contantin lioanid ya rubuta waka mai kan magana cewa, "Akwai Allah", bai taba sanin irin muhimmancin da kalamun wannan waka zasu yi wa tarihin Romania ba.***

*Zaku san gaskiya, kuma gaskiyar kwa zata yantarda ku: John 8:32*

Wata rana a cikin dare a shekarar 1989 Krista suna zanga-zanga a cikin garin Timisoara. Wani Bishop wanda ya zama tamfar Yartsana na Kwaminis ya sallami Pasto Tokes mai halin jaddadawa, laifinsa shine wai don yayi wa'azin maganar Allah da kyakkyawar aniya.

A ranar da Pasto Tokes zai bar gidan da kuma Majami'ar, sai Krista suka kewaye gidan, domin su hana Yan Sanda tashinsa. Nan da nan mutane suka taru da yawa har yakai ga jami'an soja fitowa domin a tsaida su.

Sojojin kuwa suka fara harbi kuma mutane dayawa suka mutu ko kuma suka ji rauni. Daga nan sai wani abin mamaki ya faru. Maimakon suyi fada da sojojin, dukanin Jama'ar Krista da suka fito suka durkusa sukayi addu'a. Wannan al'amari kuwa ya gigita sojojin yasa suka dakatar da harbe-harben su gaba daya.

A cikin wannan hali yasa mutanen gari gabadaya suka taru, wani Pasto da ke cikin garin yayi musu magana daga kan dakalin gidan sama na gidan wasan kwaikwayo. Sai ya fadi kalmomin wakar Dan'uwa loaned, gaba daya kuwa Jama'a suka dauka, "Akwai Allah! Akwai Allah" Takardu dauke da wadannan kalmomi da akazo dasu kuwa a ka rarabawa mutane, wadanda suka sa ita wakar kuwa sai suka fara raira wa. Jim kadan kuwa sai ga dubun-dubutar mutane suna wakar akai-akai.

Wannan wakar ita ce ta zama mafarin juyin-juya-hali na Romania da ya kai ga faduwar mai mulkin kama-karya na Kwaminisanci Nicolai Ceaucescu..

Juyin-juya-hali wani hanyane sabo domin sake tsohon ra'ayi na mutanen da ko da na yancine, ko ta martabar mutum ko mata yarda cewa akwai Allah ko babu. Wadannan fitattun ka'idodi ba sa samun sauyi a zamanai masu tsanani ko da shike sukan yi "sauki" na wani lokaci, sanin cewa akwaisu tabbas ne. Juyin-juya-hali na ruhaniya yana falkadda gaskanta akwai Allah - ko da shike Allah da kansa bai taba mutuwa ba. Juyin-juya-hali ya fara ne da bayyanuwar gaskiya ta Allah. Dukanmu muna bukatar karfin hali domin falkadda imanin mu a cikin tashe mai iko, da sake niyyarmu ta cewar akwai Alla:..

Muna shiga sahun masu juyin-juya-hali idan muka hada kai da sauran Krista wadanda suka yarda suyi rayuwar su daidai da bangaskiyarsu. Yaya juyin-juya-hali ta ruhaniya take a rayuwara?

# MATSANANCIN JUYI (NA BIYU)
## *Romania: Yara guda Goma sha Uku*

RANA TA 82

***Bayan daruruwa sun mutu a banza a Timisoara a 1989 wasu tarzoma suka fara tashi kusan a lokaci guda ko'ina a cikin biranen Romania. A lokacin wata zanga zangar wani taron yara guda goma sha uku suka hada kansu suka yi katanga da kansu suka tare hanya domin kada sojoji su isa ga taron Jama'a. A lokacin da sojojin suka fara matsowa, sai yaran suka durkusa sukayi ihu, "Muna rokonku kada ku kashemu".***

*Yace gaskiya ni ke ce muku in ba ku jure ba ku komo kamar yara kankanana ba bazaku shiga cikin mulkin Sama ba.*
*Matt. 18:3*

Sojojin suka ki sauraren yaran suka fara harbinsu. Duk da haka yaran basu ja da baya ba. Sai suka cigaba da roko, "Muna rokon kada ku harbe mu" An kafa alama ta tunawa da yaran a wannan wuri da aka kashe su.

Labari ya bazu ko'ina a Romania cewa a zahirima mala'ku ne suka fara juyi ta wurin kewaye yaran suna karfafa su a ruhaniyance domin su dage su tsaya gaba da mugu. Tankunan yaki nasoja da kuma sojoji na kowane gari sun sami umarnin su fito su tsayar da wannan tarzoma.

Amma a karshe sojojin sun ba da kai ga wannan zanga zangar lumana. A cikin garin rabin, hafsoshi da sojoji suka shiga cikin dubban Jama'a yayin da ministoci guda biyu da ke kan tankin yaki suka umurci dukan Jama'a da su durkusa ayi addu'a ashe sun gaji da gwamnatin kamar sauran Jama'a daga nan kuwa sai ya zama babu damar danne wannan bukata ta juyi.

An gaskata cewar bada kai na shahidan yaran nan shi ya baiwa kasar nasara bisa gwamnatin kwaminis mai zamani mai tsawo na tsanantawa.

A lokacin da muka zama kamar yara a bangaskiyar mu, zamuyi marmarin bukatar cika ayyukan da Kristi ya sa a gabanmu. Kamar yara lalle ne mu dauki wannan dama kuma muyi anfani da ita. Yaran Romania sun roki a barsu da rai, amma ga manufarsu kam ba su fasa ba. Akwai al'amarine ko kuma wani abu dake faruwa da yake yi wa biyayyarka barazana harga hanaka cika umarnin da ke gabanaka? Me kake shirin saukarwa domin bada kanka ga manufar Kristi?

## FITOWA MATSANANCI

## *Sansanin Bauta ta Nazi: Mary Skotsobaugh*

RANA TA 83

***"...Bakwai, takwas, tara...! Fito waje!" Mai tsaro na Nazi yayi wa matar tsawa. Kwamanda ya bada doka a kirga fursunonin kuma duk wacce ta fadi a kirge na goma tafito da ita a kashe wannan horone wai domin fursuna guda biyu sun tsere a cikin dare.***

***Ubangiji ya kayyade hanyoyin mu, ta kaka wani zai fahimci rai? Misalai 20:24***

"Ina rokon ka kayi mini jinkai! Ina da yaro, mata ta goma ta roka. Mary Skotsobaugh ta tsaya ita ce ta biye a layi. A cikin zuciyar ta Mary ta ji ana cewa, "Fito gaba kice kin yarda ki mutu a madadinta". Sai ta maida amsa ga wannan, "Domin maganar zuci din tace.

Me ita ba Krista bace. Ita Bayahudiyar Kwamini's ce. A lokacin da aka tumbuke mulkin Nazi kuma Kwaminis suka shigo, suma gidan jiya ce watau mugunta kamar Nazi."

Nanfa sai Mary ta tuna wannan rana itace ranar tunawa da giciyen Yesu, sai muryar tace, 'a wannan ranar ce na mutu, ba domin masu kyawawan hali ba amma domin masu mugayen halaye domin masu zunubi". Sai Mary ta fito gaba "Ina so in mutu".

Hafsan yayi dariya "Indai har wawancinki ya kai ki ga son ki mutu a madadin ta, shikenan, fito gaba. Na ta lokacin zaizo ba da jimawa ba". A lokacinda Mary ta tafi wajan da za'a kashe ta kuma a konata a cikin tanderun wuta, ta fadi masu. Lokacin da Allah ya fitarda mutanen sa daga kasar Maar yana rubuce a Littafinmu Mai Tsarki cewa yayi tafiya a gabansu a zaman ginshikin wuta. Ina addu'a a lokacin da za'a kona jikina bari shi zama ginshikin wuta da zai nuna maka hanyar zuwa wurin Allah?"

Daukan mataki gaba, yana iya nuna bambanci, galibi Krista suna zaman rayuwarsu tamfar tsakani zaman lafiyane da kuma rashin sa. Su wadanda suka yi kuru suka fito gaba zuwa rashin sani kaka zata kaya lafiya ko babu, a kullum sukan sami amincewar Allah. Nuhu, Musa, Ibrahim, Deborah, Ruth, Maryamu da Bulus. Jimlar misali daga Littafi Mai Tsarki suna nan barkatai. Ban da ma sannanun mutane. Kana sauraren kira daga Allah na ka fito gaba cikin bangaskiya a yau? Ka na jin muryarsa a zuci yarka? Ka saurara kayi shirin yin gaba, dan karamin taku gaba zai iya nuna wa wasu hanyar zuwa ga Allah.

*Shahidi shine wanda ya zama kayan aiki na*
*Allah wanda ya sadaukar da nufinsa*
*ga nufin Allah bai rasa shi ba amma ya same shi.*
*Gama ya sami yanci ta wajen sadaukarda kansa ga Allah.*
*Shahidi bashi da sauran bukata ta*
*kansa har ma daukakar cewa shi shahidi ne*

***TOS. ELIOT:***

***KISA A CIKIN MASUJADA)***
***Book title: (Murder in the Cathedral)***

## HALIN ASIRI MAI TSANANI

RANA TA 85

*Gama ba abinda ke boye, sai dai domin shi bayyana, babu wani abinda aka asirta sai dai domin shi tonu*
*Mark 4:22*

***An san Krista na farko da abubuwa biyu: addu'a a karkashin kasa da kuma shan tsanantawa a doron kasa. Sanannen abu ne cewa dukan duniya suna gaba da Krista a zamanin Mulkin Romawa. Marcus Aurelius Antonio ya rattaba hannu a wata dokar soja a Shekarar A.D. 162 cewa, "Dukan wanda ya karbi addinin Krista doka ta tsara ayi masa kisa ta hanya mafi muni!" Wani zamani mai tsawon Shekaru 400 na halin asiri mai tsanani ya fara kenan ga Krista.***

***Majami'a ta koma karkashin kasa gaba daya wanda kuma shine ya kirkiro abinda ake kira Roman Catacombs.***

An shirya jeraru kuma hadaddun dakuna da aka gina a karkashin kasa a Rome domin bizine matattu. Duk da haka wannan su suka zama masujadun boye na majami'un farko. Masu bi suna samun wuri inda suke yin sujada babu kuntatawa.

Catacombs ya nuna irin bada kai da masu bi na da sukayi na samun wurin da suke bauta wa Kristi. Kasusuwan mamata da aka kakkarya kuma aka kona, kaburburan sun nuna alamar irin tsananin da sukasha.

Watakila abu mafi muhimmanci shine wadansu sakonnin asiri a rubuce na nasara da kuma salama ta wurin giciye.

Ba abin mamaki bane a ga rubuce-rubuce kamar haka a jikin kaburbura: "Nasara cikin salama da Kristi" ko "Da yake an kira shi, ya tafia cikin salama "ko" ga Maria a kwance, wacce aka sa ta yin barci a cikin mafarki mai salama" Mabudin nasararsu ba a boye yake ba. Kammalalliyar salama a cikin Kristi Yesu.

Mutane da yawa sukan boye bangaskiyarsu duk tsawon rayuwarsu. Sukance addini abu ne na zuci-abune tsakaninsu da Allahnsu kawai. Amma fa abin ba haka yake ba can farkon majami'a. Masu bi suna ma'amalla a fili akan bangaskiyarsu shi yasa ma ake gane su cikin sauki kuma a azabta su. Anyi anfani da Roman Catacombs a zama kebabben na yin sujada, amma in aka fito kan doron kasa daga ramin, biyayyarsu ba ta boyuwa. Shi yasa da yawa cikinsu suka yi shahada domin bangaskiyarsu, na cewar su da addu'a a fili a can karkashin kasa shine yake basu salama da suke ji a tsanantawar in sunfito waje. Shin ko bangaskiyarka tana "karkashin kasa" a dukan rayuwarka na Krista? Lokaci yayi da ya kamata asirin ya fito, ko da menene zai zama sakamakon, kada ka boye Kristancinka.

# AMINCEWA MAI TSANANI

## *Birnin New York*

RANA TA 86

***"Kuma ina so ku sani yan'uwana maza da mata, cewa dukkan abubuwan da suka faru dani sun taimaka wajen ya da bishara. Kuma a dalilin zuwa na kurkuku Krista da yawa sun kara amincewa kuma sun zama masu karfin zuciya wajen shaida Kristi ga wasu. Gama ba damar gaskanta Yesu kadai aka bamu ba amma harda damar shan azaba domin sa (Filibiyawa 1:23, 14, 29 NLT)***

*Muna kuwa da irin wannan amincewa ga Allah ta suna wurin Kristi.*
*II Cor. 3:4*

Idan da masu bi na Amirka suna da kwazo wajen yada bishara shin zasu ga karin tsanani a kasan" Metro Ministries, Kungiyar Bishara ce da take Birnin New York sun ga haka a kungiyar su. Yada bishararsu na kara zurfi cikin lungu- lungu da sako-sako kuma suna kara samun masu taurarewa. Wasu ma'aikatansu ma sun sha duka, suka da wuka har da fyade a lokacin da suke aikin su. Har an kashe musu ma'aikaci.

Shugabansu Pasto Bill Wilson ya sha duka da sukar wuka sau da dama. Duk da haka tsoratarwa ta mugun bai saya ja da baya ba daga mutanen da yake kauna, kuma tarin fuka ya kamashi a lokacin da yake tare da marasa galihu yana masu bishara.

Debbie yar shekara gomasha biyar da ke zaune a unguwar marasa galihu ta Brookyn a New York ta fadi abinda matasa da yawa sun san haka dinne, domin sun dandana tsanani a kasar Amirka. Tace "yana da wuya ka fito fili ka ce kai Kristane a makarantata. A kullum damuna ake ana matsamani wai ina shiga daya daga cikin irin kungiyoyinsu".

A cikin kasashe marasa yanci da yawa ana tsanantawa krista ba domin sun bada gaskiya ga Yesu kadai ba amma domin suna shaida wa wasu akan Kristi a cikin kasashen su, yin Bishara yana kawo tsanani wanda yana kawo shaidu su karfafa domin Kristi. Abinda ake zato zai hallakasu sai kuma ya kara sa su, su karfafa su fi dagewa.

Haka kuma bishara a Amirka da sauran kasashe masu yanci ba abune mai sauki ba. Duk da haka kamata yayi sanin haka ya kashe mana jiki? Kasa irin Amirka da aka kafata ta yancin addini bata saba da wahala ko tsanani ba maimakon yin anfani da wannan ka'ida a zaman makari, kamata ya yi mu dangana a kai don mu sami karfin zuciya. A zaman mutumin da ke zaune a kasa mai yancin dimokradiyya kana ma da karin dalilin da zaka shaida bangaskiyarka da karfin zuciya da rashin tsoro. Zaka bude baki yau?

# MATSANANCYIYAR KALLAFARWA

## India: Gladys Staines

RANA TA 87

***Gladys Staines tana da kwakkwaran dalilin nuna bakinciki da kuma yin fushi. Da tabar India ma da babu wanda zai ga aibunta. Amma a lokacinda yan Hindu masu tsaurin ra'ayi na cikin garin Manoherpur suka kashe mijinta da yayanta maza guda biyu, Gladys da diyarta yar shekaru goma sha uku, mai suna Esther, suka yi shawarar cingaba da zama. Kuma zata cigaba da aikinta a cikin kutare na wannan yankin.***

*Amma wadanda ke bisa tabi'ar ruhu, alamuran ruhune.*
*Rom. 8:5*

Mijinta mai suna Graham, da kananan yaransu maza guda biyu, Philip da Timothy, an kashe su ne a lokacin da suke barci a cikin motarsu kirar Jeep a cikin harabar da Majamilar take.

Sun ziyarci majami'ar domin yiwa ikklisiyar hidimar bishara. Amma, kafin rana ta fito a wannan bakar safiya, kungiyar yan daba na Hindu wajen mutum dari suka bullo suka watsa fetur akan motar suka kunna mata wuta. Yan Hindu din suna dauke da bakankuna da kibau suka kewaye motar don su hana na ciki tserewa.

Gladys tace Graham bai taba yin bishara ga yan Hindu ba. Ya tafi can ne kawai don ya nuna kaunar Kristi. A sakamakon yin haka, wannan iyali daga Australia sun sami masu tuba zuwa Kristanci kuma suka kona gumakan su. Hadarin da ke gabansu wajen kai bishara bai taba hana su cin gaba da nuna kaunar Yesu Kristi ba.

Gladys da Esther sunyi waka a bukin tunawa da Graham, Philip da Timothy, wakar tana cewa:-

Zan iya fuskantar gobe, domin Yana da rai. Dukan wani tsoro babushi, domin yana da rai. Domin na san shine ke da gobe.

Kuma rayuwa ya wajaba ne kawai don Yana raye.

***"Domin yana da Rai" William J. Ya tsara tareda Gloria Gaithar Muryar Noka - William J. Gaither sake wallofa 1971 William J. G. Inc. Dukan damar wallafa na karkashin gaither Copyright Management.***

Matsananciyar kallafarwa ba zata taba tsaiduwa ba kome hadarin da ke gaba, damuwa ma bata rage mata karfi. Kallafarwa abu daya ta sani - aikin da aka sa a gaba. Ga mutane da yawa rasa iyalansu ta hannun abokan gaba na wata Kasa zai iya zama kwakkwaran dalili na yin watsi da aikin dake gabansu.

Ba haka yake ba ga wadanda suka kwallafa ransu kwarai da anniya. Koda shike zasu girgiza da irin wannan jaraba dagewarsu na cingaba da aiki baya tsaiduwa Allah ne kadai ke iya bamu karfin hali a ruhaniyance wanda zai iza mu gaba ga yin aiki duk da abin bakin ciki da ya samemu. Ko ka sami kanka cikin shawarar zuwa ko rashin zuwa yin aikin Allah? Akwai abinda ya faru da zai iya ya shaitse ka? Ka roki Allah ya baka kwallafawata kullum domin mannewa aikinsa.

## MATSANANTAN MASUNCIN NASARA
## *Romania: Pasto Richard Wurm Brand*

RANA TA 88

*Yanzu dai bangaskiya da bege da kauna sun tabbata su uku amma mafi girman su kauna.*
*I Cor. 13:13*

***"Matata tana barci a daya dakin domin ba ta da lafiya", Pasto Wurmbrand ya fara magana. "Da ita da ni dukan mu daga zuriyar Yahudawa ne. An hallaka iyalin ta a Sansanin Bauta ta Nazi inda kake yin fariyar kashe Yahudawa yanzunnan har da cewa wadansu ma suna rungume da jarirai a hannayensu. Watakila ma kaine ka kashe iyalin matata".***

Da jin haka, bakon Pasto, wani soja yayi fushi ya tashi tsaye da niyyar fita. Amma Richard ya tsaida shi. "Ka jira ina so in gabatarda wani gwaji. Ina so in gaya wa matata ko wanene ne kai da abinda kayi. Amma matata ba zata zage ka ba kuma ba za tayi fushi da kai ba. Zata karbeka".

Sai mutumin ya zauna da baki bude, amma babu magana.

Pasto yaci gaba, "yanzu idan matata, da take yar'adam ce amma ta iya gafarta maka - Balle ma fiyeda haka Yesu zai kaunace ka kuma ya gafarta maka?

Mutumin ya rufe fuskarsa da hannayensa. "Me nayi? Ta kaka zancigaba da rayuwa cikin irin wannan laifin zubar da jini? Yesu, ina rokonka ka gafarta mani". Sojan ya bada kansa ga Kristi.

Sa'anan Richard ya shiga ciki ya tada wa Sabina. "Ga wanda ya kashe yan'uwanki maza da mata da kuma iyayenki, ya gabatarda mutumin. "Amma yanzu ya tuba." Ta rugumi mutumin nan kuma tayi masa sumba a kumatu.

"Kauna ta ci nasara da dukan komi wannan sananniyar kalma ce da ake anfani da ita. Amma Krista sun san gaskiyar wannan tun farko. A duk lokacin da muka fusata, sai mu cika da kiyayya. Amma duk lokacin da muka barwa Allah (wanda yake shine kauna) shugabancin rayuwarmu, sai mu gane cewa halayyen mu ta halitta kamar yin fushi abune da ya kamata mu bari mu yi biyayya gareshi.

Ba mu kara jin marmarin yin fushi akan abubuwanda ke sa muyi fushi a da. Lalle ne kauna ta ci nasara da duk abinda yake akasi ne ga halaye irin na Kristi. Sakamakon haka shine mu zamana cike muke da kauna yadda har makiyanmu ma zasu anfana daga sakewarmu. Shin ko kana jin cin nasara bisa bakinciki da ramako? Ka roki Allah mai kauna ya sa kaci nasara da fushinka a yau.

# TAUSASAWA MATSANANCI

## *Cambodia: Yarinya Matashiya*

RANA TA 89

***Sojojin Khme Rouge suka shigo cikin daki, suna barazana da makamai suna zage-zage suna tsoratarda mutane. A lokacinda Khme Rouge suka kwace mulki a 1975, an kashe dubun dubatar Krista. Kananan yara kuwa sai jefa wa Kaduna ake yi wai ai" bata harsashine a harbesu"..***

*Idan fa da kuttawa a cikin Kristi idan da taimakon kauna, idan da zumuntar Ruhu idan da Juyayi da Tausayi, ku cika farinciki da kuma in hankali daya kaunarku kuma daya, zuciyarku daya hankalinku daya.*
*Filib. 2:1-2*

Babu wani memba da ke cikin taron daya motsa. Sai wani hafsa ya tafi gurin Pasto, ya wa wuri Littafi Mai Tsarki da yake karantawa ya jefar a kasa. "Zan bari ka tafi". Injishi, "amma na farko sai ka tsarta miyau akan littafin karya. Dukan wanda ya ki yin haka kuwa za'a harbe shi".

Wani sojan kuma ya cafki hannun wani ya taso shi gaba. "Fada, ina rokon gafara", yayi addu'a a yayinda yake durkusawa kusa da Littafi Mai tsarki da aka jefar a kasa sai ya tofa miyau kadan akai. "Yayi, kana iya tafiya". Sa'annan hafsan ya nuna wata mata. Ita ma ta durkusa a wurin Littafin. Ta jika Littafi Mai Tsarki a yadda zai gamshi hafsan.

Kwatsam sai wata matashiyar yarinya ta tashi tsaye ta tunkari inda Littafin yake. Idanunta cike da hawaye ta durkusa ta dauki shafin rigar da ta ke saye da ita ta kade kuran jikin Littafin. Me suka yiwa maganarka? Inji ta, "ina rokon ka ka gafarta musu Sojannan ya auna ribalbarsa a keyar yarinyar sai ya ja kunamar bindigar.

Krista da aka bari su tafi tun farko aka dawo dasu aka harbe. Tsorata da sukayi har yakai su ga tofa miyau a jinkin Littafi Mai Tsarki bai cecesu ba.

Halin tsaida shawara na mutum guda tana iya karfafa zuciyar taro ko Jama'a fiye da yawan nuna halin cin amana. Wannan matashiya ta cikin wannan labari ta hamzartadda wani budi na fahimtar me ake nufi da dayantaka tare da Kristi. Maimakon kwabar yan'uwanta maza da mata masu sanyin gwiwa, sai ta yi anfani da misali ta wajen yadda ta dauki Littafi Mai Tsarki ta tsabtace. Ina ma da dukan Krista da ke wurin sun yi kamar na ta. Ai da anga shaida ta Kristi! A duk lokacinda muka hada kai ga yin abubuwa tare, mu kan fi karfi. Tausasawa tareda juyayi, hadeda kwakwaran misali zai haifarwa wadanda suke da sanyin gwiwa karfafawa domin badakai ga aiki tukuru. Idan kanajin takaicin wasu da suke fama wajen bada kansu, ka tuna Allah yana kiran ka da ka hada kai da wadanda ke da rauni domin a taimakesu su karfafu.

***Batun Azabtar da Krista ba batu ne na yancin dan Adam ba, Amma aukuwa ne da yakan zo kuma ya wuce.***

***Steve Cleary***

## HAKURI MAI TSANANI

### Korea Ta Arewa

RANA TA 91

*Ku al'ummai, ku dogara a gareshi a ko wane loto.*
*Zabura 62:8*.

***"Wannan kyauta taka ce".***

"Menene ne" Mai bishara ya tambayi abokinsa a lokacinda yake cikin shirye-shiryen tafiya cikin kasar Korea ta Arewa.

"Kai dai ka karba. Zaka san yaushe ya kamata ka bude".

Yayi shiga irin na yan kasuwa ya batar da kamanninsa, ta haka Mai Bisharan nan ya tafi Korea ta Arewa. An shirya masa jagora dan Kwaminis mai yawan yin barci.

Ganin wannan dama ta samu, Mai bishara yayi sanda ya bar "Hotel" masaukinsa a lokacin da jagorarsa ya ke yin abinda ya saba, watau bari. Ya shiga wani kauye da ke kusa ya sadu da wasu masu bi. Da suka gane cewa Mai bisharannan nadadden Pasto ne sai suka ce, "lalle ne kayi mana baptisma! Mun sha jiran wani ya zo yayi mana baptisma.

A cikin kasa wadda mallakar Littafi Mai tsarki laifi ne da ke tattare da hukuncin shekaru goma sha biyar a kurkuku yin baptisma kuwa hukuncin sa kisa ne. Ba tare da samun taki ko Kogi kusa ba, sai mai bishara yayi addu'a akan masu bi da ya bayan daya a zaman shaida ta bangaskiyarsu. Amma abin daya bashi mamaki shine sun nuna rashin gamsuwarsu." Munjira shekaru arba'in kenan domin cin jibin Ubangijinmu Yesu".

Daya daga cikin masubin ya fito da wainar shinkafa. Mai bishara yayi tunani a ransa yace "Sunyi baptisma babu ruwa kila zasu iya cin jibi ba tare da abin sha ba". A nan ne ya tuna da kyautar da abokinsa ya mika masa kafin ya tashi zuwa Korea Ta Arewa. Nan da nan ya dauko jakarsa ya fit da kunshin - kwalbar ruwan anab. Mamaki ya hana su magana sai hawaye ke zuba a idanun mutanen kauyen nan suna kuka a fili, suna yabon Allah domin wannan kyauta da tazo akan kari.

A yayin da yawancin mutanen zamani ba zasu iya jure rayuwa ba in babu kalanda na kwanan wata da kuma agogo don sanin lokaci, Allah yana lura da nashi lokaci. Rashin bin ka'idar mutum baya tunkude shirin Allah. Saboda haka dole ne mu koyi yin hakuri domin mu sami rayuwa ta farinciki a cikin shirin lokacin irin na Allah. Ma'anar yin hakuri shine yarda da cewa Allah yana aiki domin mu, ko ma da bamu ga alamar haka din ba. Ka'idar samun sakamako na biyayya ga Allah kome dadewa itace hakuri. A lokacin da muke jiran albarkan Allah a cikin rayuwar mu, mukanji dadin su kwarai. Duk abin da muka yi jira kwarai a kansa, mukan fi bashi muhimmanci. Ko da cin jibin wainar shinkafa ce ko kuma wani kayyadadden bukata na rayuwarmu. Shirin lokaci na Allah tabbatacce ne. Menene batun da ya dameka game da lokacin shirin Allah a cikin rayuwarka? Lokaci yayi da zaka amince dashi?

# BISHARA MATSANANCIYA
## *Uganda: Bishop Hannington*

RANA TA 92

***"Hanya kadai da ma'azabci zai sami ceto tana iya zama ta hannun fursunan Krista. Basa zuwa majami'a kó karanta Littafi Mai tsarki. Amma fursunan Krista yana iya yin maganar kauna dasu, kai harma a lokacin da ake yi masa duka" Wannan maganace da wani dan majami'ar karkashin kasa ya amince da ita.***

*Gama bishara ba abin kunya ba ce agareni gama ikon Allah ke zuwa ceto ga ko wane mai bada gaskiya. Rom. 1:16*

Wata mata da tayi shekaru tana bautawa Kristi cikin hadarin shan azaba tace. "Cikin dukanin tarihin majami'a, fursunonin Krista da yawa sun kawo ma'azabtansu ga tsira. Akwai allon da aka kafa na nunawa a cikin kurkukun Rome na sunayen mutanen da suka tuba a lokacin da Bulus yake cikin kurkuku a wurin. Da ba domin Bulus yayi musu magana a kurkuku ba, da basu da ceto. "To dakata kadan, "Ban damu da insha wahala ba in har sakamakon yin haka zai zama ceto ga masu azabtarwa".

Bishop Hannington ya san akwai kasada ainun a lokacin da yayi shawarar kawo bisharar Kristi ga nyamnyam na kasar Uganda. Bayan yan makonni da isarsa, nyam-nyam suka ki karbar sakon sa suka kashe shi.

Kafin Hannington ya mutu, mutanen sunji wadannan kalamu da babbar murya. "Ku kaunaci makiyanku... Kuyi addu'a domin wadanda suke yi muku hassada, suna anfani da ku kuma suna a zabtadda ku".

Wannan sako na Bisho shine kuma yayansa maza guda biyu suka dauka tare dasu a lokacinda suka tafi wannan kauyen dai inda aka kashe mahaifinsu. Sun dage da cingaba da yin bishara ga wadannan mutane dai da suka kashe Ubansu.

Wadansu sun dauki mutuwar Kristi da tashin sa tatsuniya ce kawai na rudi da masu tunanin son zuciya domin suna so a dinga tunawa da masoyinsu, malami. Amma idan haka ne za'a yi bayanin shahidancin yawancin almajiransa da yawacin sauran shahidai bayansu na shekaru daruruwa? Akwai ma'ana idan suka yi na'am da wawancin su a lokacin da aka kama su da kuma sanin mutuwa zasuyi? Me zaisa su yarda su kai ga irin wannan hali idan har zancen na rudi ne? Alhalima dai, tarihi ya fada kokarinsu na juya ma'azabtansu har zuwa karshen lokacinda suke da damar yin haka. Wannan tsananin yin bishara ta na shaidar tabbatar bangaskiyarsu. Wannan shine ainihin bisharar Allah. Yaya tsananin amincewarka take game da bishara? Ashirye kake ka kai bishara a ko'ina kome tsanani?

# FILIN BISHARA MATSANANCI

## *Japan: Francis Xavier*

RANA TA 93

***Japan, kasa ce da ke kewaye da duwatsu masu ban sha'awa, an albarkace ta da bangaskiyar wadansu jaruman Krista maza da mata wadanda sukayi shawarar yin kasada domin su zama na farkon masu kawo bisharar Kristi ta kauna da gafartawa zuwa Japan.***

*Hakika idan kuna da bangaskiya kwatancin kwayar zarra sai kuce wa wannan dutse ka kawu daga nan koma can sai shi kawu.*
*Mat. 17:20*

A shekarar 1549 ne Francis Xavier ya zama mai bishara na farko zuwa kasar Japan. A karkashin gudanarwarsa da yawa sun karbi Kristi kuma majami'a ta girma da sauri. Amma sai hukumomin Japan suka yi wa wannan ganin barazana, daga nan kuwa sai mumunan tsanani ya fara gaba da kristanci kamar gobara, a lokacin abin ya sha kan masun bi. A birane irin su Unzen, ana tafasa krista a cikin narkakkiyar wutar da duwatsu ke amayowa da ake kira Lava.

Wasu kuwa giciyesu akeyi akan itace a cikin birnin Nagasaki. Sojojin Japan sukan farma dukanin Krista da aka sani, a shekarar 1637 sun kama dubu talatin kuma sun kashe dukansu.

Sakamakon wannan hali sai majami'a ta shiga karkashin kasa da fatar kare rayukan wadanda suka tsira daga kashe kashen. Majami'a tayi gwagwarmaya ta shekaru da dama. A karshe kuwa sabili da Alherin Allah Majami'a ta tsira. Tsayayyun masu bishara basu daina zuwa ba. Sun sami labarin tsanani a tsaunuka kuma suka amsa kiran zuwa su ciyadda yan kalilan na masu bi da suka rage.

A yanzu haka Japan tana da mabiya Kristi guda 1.7 million da suke aiki ainun, kuma masu bi na karuwa a kullum. Xavier da kuma masu bishara na yanzu suna kamar kwayar zarra da ya zama wata dama kasar ta sami sauyi.

Rayuwa cike yake da matashiyar hange, masu bi galibi suna fuskantar gagarumar kiyayya daga yan'uwa na jini wadanda basuyi na'am da bangaskiyarsu ba. Krista da yawa sukan yi karo da tudun kiyayya na masu cewa babu Allah a wuraren aikinsu. Ga tuddai masu tsawon gaske na tsanani da gwamnatocinsu suna shan kan masubi a kasashen da babu yanci. Amma duk da haka akwai hange mai ban sha'awa a hayin dutsen ko tudun da yake fuskantar majanu'a a yau. Filin na dubun dubatar mutane ne maza, mata da yara wadanda suke yinwar bishara. Bangaskiya tana iya share hanya domin wasu ma su sami ceto. Shin zaka cigaba da aikin da suka bari tare da bangaskiyar da zata ratsa duwatsu? Wane dutsen zaka fuskanta yau?

# MATSANANTUN WURARE

## *Russia: Zoya Krakhmalnikova*

RANA TA 94

*Kayi kokari ka mia kanka yardaje ga Allah ma'aikaci wanda babu da lilin kunya gareshi kana raraba kalmar gaskiya sosai. II Timoti 2:15*

***Wani fursuna wanda yake a da Priest ne a kurkukun Russia yaci amanar Zoya. Ya dora mata laifi domin wai ko a sake shi daga kurkuku don ya tsere wa azaba. A lokacin shari'ar, Zoya ta ki ta fadi ko da kalma daya ne marakyau a kansa. Ta ce, "A lokacin da Yahuda Iskarioti ya ci amanar Yesu, shi mugun mutum ne. Amma Yesu ya kira shi aboki a Gethsemane. Bai kamata muyi koyi daga misalan Kristi ba kuma muyi wa wadanda suka ci amanar mu haka?"***

Zoya Krakhamalnikova tayi shekara shida a kurkuku somin shaida Kristi ga wasu. Lokacin ya bata damar sanin maganar Allah da yadda abin yake game da wuyar rayuwa na ainihin abubuwa da ke aukuwa a zahiri.

A kurkuku kowane kofar daki yana da karamin rami da aka huda na leke anakiran shi ramin yahuda. Ta wannan yar kofa masu gadi suna lura da mutane duk minti biyar. Suna kallon mutum kuma suna bada umarni.

Wannan ya taimakeni gane ko kwaminis suna da kwazo ko himma akan sa mani ido, "Allah da malaikunsa ba zasu sa ido akaina da himma fiye da nasu ba?" Zoya tana iya bari bakinciki yarinjayi zuciyarta. Amma sai ta dauki darasi daga maganar Allah kuma tayi anfani da su akan rayuwarta. Darasi ne mai wuya amma sun taimaka wajen haskaka rayuwarta da ma na kewaye da ita.

Shirin yin doguwar tafiya ba tare da Kristi ba shirine daya isa ayi wa mutum ba'a a kansa. Wanene zai yi doguwar tafiya ba tare da shiri ba? Duk da haka Krista sukanyi tafiya ta ruhaniya a kullum ba tare da isashen shiri na ruhaniya ba. Muna da bukatar mu shirya kanmu da maganar Allah a zukatan mu domin mu iya anfani da su idan bukatar yin haka ta taso. Yawancin mu mukan yi fama garin neman cin nasara domin bamuyi nazarin ka'idodin Allah tun da wuri ba. A karshe mukan kare da rashin nasara maimakon cin nasara kamar Zoya ta wurin anfani da maganar Allah a cikin al'amuranmu. Bangaskiyar ka a cikin Kristi zai iya kai ka wurare masu tsanani. A shirye kake domin wannan tafiyar? Ka tabbata kayi damara da maganar Allah - zaka bukace ta.

# MATSANANCIN DAN-SARI-KA-NOKE

## *Peru: Juan*

RANA TA 95

*Duk da wannan abubuwa da suke ribobi a gareni, wannan na lisafta su hasara sabilida Kristi. Filib 3:7*

***An daure Juan shekaru goma sha biyar a kurkukun Miguel Castro domin ayyukan sunkuru. Juan yasan irin tunanin da yan sunkuru kanyi. Shi soja ne na Kungiyar Kwaminis da ake kira "Shining Path". Babban aikinsa shine koyarda wasu yadda za suyi kisa ko barna. Shi mairike da babban mukami ne kuma kwararre ne wajen fada da nakiya, makamai da rushe rayukan rundunar mutane. Aikin sa ya bashi tunani na sanin akwai kaddara.***

Juan yaci gaba da aikinsa har a cikin kurkuku ma. A lokacin da yake kokari ya shigar da wani saurayi mai suna Fernando a cikin kungiyarsu ta soja sai ya gane cewa dayawa daga ra'ayoyin su na Marxist basa shiga ma saurayin. Maimako ma sai Fernando ya tambayi Juan wata tambaya maishiga kwakwalwa. "Idan ka mutu yau da darennan, abokina, a ina zaka dauwama".

Juan ya ga ko kuma ya zama sanadin mutuwar mutane dayawa, amma bai taba yin tunani akan tasa mutuwarba. Tambayar Fernando ta fara cakunarsa. Fernando ya ci gaba da magana da shi a kowace rana akan kaunar Kristi da mutuwarsa. A karshe Juan ya bada gaskiya.

Fernando ya karfafa wannan sabon tuba "Kamar yadda ka bada ranka ga kungiyar juyi, a yau ka bada wannan zuciyar ga Kristi Ubangijin ka".

Sannu a hankali Juan ya shugabanci ikklisiya a kurkuku. Game da rayuwarsa na baya, yana dauka mutane a cikin makarantar soja ta Kungiyar su, a kurkuku kuwa yanzu shirya Sunday School yake yi. Aikinsa na kisa ya sauya zuwa aikin taimakon wasu domin su sami rai na har abada.

Abinda mutane suka fi sa rai ga so yakan basu tunani na azanci da kuma sanin akwai kaddara wadansu mutane masu son aikinsu na kwarai, wasu kuwa iyalinsu ne suka fi so kwarai. Har yanzu wasu kuma babban son su shine duk abin da ya shafi kiyayya da al'amarin Kristi shi sukafi sa wa a gaba. Su wadanda suke azabta Krista ba za'a basu laifin nuna wariyar al'umma ba. Da sunyi amfani da dagewar su babu sassantawa wajen aikata alheri maimakon azabta Krista da abin ya zama da sha'awa amma ina. Allah yana cikin aikin sauya tsohon rayuwarsu zuwa sabuwar rayuwa. Duk da haka da tsananin so ya rungumi Maxist a da. Juan ya fara daukan mutane domin Kristi. Allah ya dauke tsananin so na kangara ya juyashi ya zama tsananin so na Kristi. Yi addu'a domin Allah ya juya dukan wani abu da zai yi gara da ibadarmu ta ruhaniya. Mu roke shi domin ya bamu zukata masu kuna da zamu cigaba da sha'awar ciyarda mulkinsa gaba.

# WANI ZABI MAI TSANANI

## *Kansar Phillipines: Peter*



***Peter yayi tunani yace wannan kasada ce amma dalilin yin kasadar ya dace. Shi mai sha'awar tafiye tafiye ne tare da kawunsa Micheal, wani mai bishara a kasar Phillipines, zuwa cikin kauyuka inda mutane ke marmarin jin maganar Kristi.***

*Idan kowane mutum yana da nufi shi aika nufin Allah, zai gane ko Koyaswa daga Allah Yake ko kuwa ina Magana don kaina ne. Yoh. 7:17*

Tafiye tafiye zuwa kauyukan akwai kasada da hadari, tafiya ta cikin tsakiyar kurmi na tsawon lokaci. Mutanen kasar Philippines sun sha samun hari daga yan tawaye na shekaru da dama wanda New Peoples Army suke kai masu, wani bangare ne na Jamiyyar Kwaminis. Da Peter da Kawunsa wani lokaci buya suke domin guje wa hadari. Peter yana son yara kuma yakan ji dadin ganin hasken idanunsu a yayin da suka gane cewa Allah yana kaunarsu.

A ranar Good Friday, su New Peoples Army suka yi shawarar kawo karshe ga yin bisharar kawunsa Michael, saboda haka sai suka kama Peter suka yi barazanar kashe shi idan kawunsa bai daina yin maganar Kristi ba. Iyayen peter suka bada amsa, "Ba zamu iya fada wa Michael cewa ya daina aikinsa ba, amma muna rokonku ku dawo mana da dan mu. Bai yi laifin kome ba."

A karshe hannayensa a daure ta baya, Peter ya saurari iyayensa suna gaya wa sojojin. "Rayuwa Kristine mutuwa kuwa riba ce." Da waddanan kalmomi, Peter ya tafi gida don ya sadu da maicetonsa a wannan rana ta Good Friday, Kawunsa Michael yana zuwa kauyen cikin duwatsu yana musu bisharar ikon Kristi na kauna haryanzu kuma yana gaya musu labari na saurayi mai aminci dan danuwansa mai suna Peter.

***Maganar kasada batu ne na zabe, wadansu sukan so suyi kasada da dukiyarsu, ta caca akan abin duniya. Sakamakon buga kwallon kafa, ko wanda yaci tseren gudun dawaki. Ko kuwa cin kwallon kwando. Wadansu ma sukan yi kasadar ransu ta wurin zaben abin yabo na duniya wanda bashi da wani muhimmanci game da gobe kiyama wadansu ma sai kwayoyin sa maye da kuma barasa. Yesu yana kira zuwa ga wani zabi dungurungum, Ya ce lalle mu zabi yin kasadar tsaro irin na duniya domin mu ribatu da ladar samaniya garin cika nufinsa. Cika nufinsa yana kawo lada mafi daraja da ba za a kwatanta da yan kudi da za'a ci a filin sukuwa ba ko kuma buguwa da kwayoyin zamani. Ko ka sami ladan Yesu ta wurin yin kasada da bangaskiyarka? Me yasa ko kuma me ya hana?***

RANA TA 97

***Ba ma yin addu'a domi mu zama Krista da suka fi kowa ba amma domin mu zama irin Krista kadai da Allah yake nufinmu da mu zama, waṭau Krista masu kamanta Kristi da zasu dauki giciye da yardar rai domin daukakar Allah.***

# *Korea Ta Arewa: Kauyawan Goksan*

RANA TA 98

***Yarinya mai kasa-kasan idanu ta daga kai ta dubi uwarta Wace shawara uwar za ta yi?***

Can dasafe kafin wannan lokacin, uwar wannan yarinya, Pastonsu da wasu mabiya guda ashirin da shida yan kauyen Goksan ta kasar Korea ta Arewa da aka kama su aka daure aka kaisu gaban taron yan kwaminis da suke ta kururuwa.

Daya daga cikin masu tsaro ya umurci Pasto Kim da sauran Krista. Ku yi musun Kristi, ko ku mutu" wadannan kalamu sun bata sanyin jiki. Ta kaka zasu gaya mata wai suyi musun Yesu? Ta sani a zuciyarta Yesu yana da rai. Dukansu kuwa su ka ki. Dan tsaro na Kwaminis yayi tsawa yana fuskantar Krista da suke manya a cikin taron. "kuyi musun Kristi ko mu rataye yayanku" Kalmar yarinyan nan ta daga kai ta dubi uwarta, sai ta kama hannunta sanin irin kaunar da uwar ta ke yi mata. Uwarta kuwa ta sunkuya. Da karfin zuciya da salama ta fada mata. Kaunatacciya ta, yau zamu sadu a sama"

Aka rataye dukan yaran. Sauran masu bi kuwa aka fito da su kan wani dabe aka tilasta musu su kwanta a gaban wata babbar mota ta dankare dabe (steam roller). Yan kwaminis suka basu dama ta karshe, "Yi musun Yesu ko a ragargaza ku" Wadannan Krista sun rigaya sun bada yayansu, babu sauran gudu babu ja da baya.

A yayin da matukin wannan babbar motar aikin hanya ya tada inji sai mutanen kauyen suka fara daga waka a hankali. "Karin kauna a gareka."

***Kari. Abin da Allah ya bayar kenan a lokacinda ya aiko da dansa. Aka giciye shi. Kari, abinda Yesu ya bayar kenan a lokacin da aka giciye shi. Kari, abinda Masu Ban Gaskiya suke bayarwa kenan ta wurin kaunar Kristi. Suna so su kara bayarwa ga wanda ya bayar da yawa a garesu. A cikin shekarun zamanin nan da ake darajanta bayarwa shine abin yi domin karin kauna a gareka yafi kalmar baki kawai na yin waka. Wannan halin rayuwa ne mara iyaka a ko wace rana, dama ce ta gano yadda zamu bada karin kauna ga Yesu Kristi. Ga wadansu masubi, wannan turba ya kai su ga mutuwar su. Ga wadansu "Karin kauna zuwa gareka" yana nufin sadaukarda kai ta hanyar kudi. Manene "karin kauna a gareka yake nufi bisa rayuwarka ta kullum?***

*Gama Allah ya yi kaunar duniya har ya bada dansa haifaffe shi kadai domin dukan wanda ya bada gaskiya a gareshi, kada ya lalace amma ya sami rai na har abada*

*Yoh 3:16*

# MATSANANCIN MAJIGI
## Pakinstan

RANA TA 99

***Yanzu dai kowa yana so yayi kallon wannan maijigi. Rada ake a koina a cikin kasuwa har a cikin masallaci, "Akan menene aka tsara magajin,wai abin akwai muni ne kwarai, da har za'a tsare duk wanda yake da shi?"***

*Gama tunanina ba tunaninku bane, haka ma dabi'unku ba nawa bane in ji Ubangiji*

*Ishaya 55:8*

Magijin da ake magana akai,shine Yesu ingantaccen majigi da aka tsara mai tsada wanda yake nuna rayuwa, aiki , mutuwa da tashin Yesu Kristi. An yi bayanin shirin ceto a allon majigin, wannan ya kawo labarin Yesu a fili ana kallo kamar a raye. A Jalalabad kasar Pakistan an tsare mutane biyu domin raba wannan majigin da kuma wasu takardun Krista. Anyi musu duka kuma malaman Islama na kewaye watau shugabanninsu na Islama. Suka zuga cewa ayi chajinsu da kuma sauran wadanda suka shafi rarraba majigin. Suka ma yi gaba da karfafa musulmi su dau mataki akan Krista. Jim kadan kuma sai akayi wa wani pasto sata, kuma aka yi harbi kusa da wata makaranta. Da alamar garin yana dab da barkuwar fitina.

Amma fa sai abubuwa suka fara sauyawa. Maimakon a gujewa wannan majigin kowa da kowa a cikin gari na marmarin ganin wannan "Majigi mai zunubi" suna so suga duk korafin da akayi da kansu. Kasuwar bayangari ya fara tashi, sannu a hankali sai aka nuna majigin a gidan talabijin na kasar.

Babban mai shari'a na birnin ya kalla ya kuma yanke shari'a cewa majigin bai nuna wani abin gaba da Islama ba.

***Ta wurin kokarinada ba su yi niyyar yi ba malaman Islama (mullah) sun taimaka wajen bishara ga dukan yankin su. Sunyi shiri su kauda majigin Yesu daga kasarsu. Duk da haka hanawar su ya zama tallatarda bishara. Allah baya mai da mugu ya zama nagari. Yakan albarkaci kokarin bayinsa, amma ba ta hanyarda muke tsammani ba. Krista da suke kasashe marasa yanci suna samun darasi ma mawuyacin hali. Amma sukan yi farinciki da ganin alajiban Allah na aiki a kasashen su. Allah yakan yi mana hanya harma ta inda muke zaton babu ma'ana. Akwai lokuta da mukan ga kamar komai na tabarbarewa. A wadannan lokuta kake kara karfafa amincewa da Allah? Ya san abin da yake yi koma da kai baka sani ba.***

# GAFARTAWA MAI TSANANI

## *Peru: Ricardo*

RANA TA 100

***Takardar bata da tsafta, gefen ta kuma a yayyage. Bakar tawada ta bazu a cikin shafi ta yadda karanta takardar za ta yi wuya. A karkashi kuwa sai ga sa hannun Ricardo***

*Idan wani yace "ina kaunar Allah" amma yana kin danuwan sa, shi makaryaci ne. Gama duk wanda baya kaunar danuwansa wanda yake gani ba zai kaunachi Allah ba wanda ba ya gani.*

*1Yoh 4:20*

Ina rubuta wa ne daga Sansanin Yan-Sari- Ka-Noke na Kwaminis a Peru. Kwanaki, na lalubi wasu shirye shiryen radio domin nadan sami fara'a a zuciya ta. Wannan shiri na bakar-kiyayya irin ta abokina faloko suke a gareni. Daga nan ne nayi kicibis da shirye-shiryen radion ku. Bishara a cikin harshen Marxist. Kun ce Yesu, babban malami yayi magana akan gafartawa abokan gaba.

Wannan shiri ya shiga lallokin rayuwata. Nan take salama ta zo mani kuma na yi kuka kamar dan yaro. Ban gane abinda ya faru ba.

Masu sayar kasa sun zalunci iyayena, shi ya sa nake kin ma'azurta duk rauyuwata. Amma bisa wasu dalilai, na daina kiyayya, kuma bana iya bayana dalili. Shin abu ne mai yiwuwa na iya daina yin kiyayya?

Wannan lokaci shi ne na farko da na saurari shirinku. Kuma kar kaji irin farincikin da nake da shi yanzu, bazan kara barin wani shirin ya wuceni ba. Inaso in karanta littafin da kuka yi magana akai".

Daga baya Ricardo ya bar Yan Sari-Ka-Noke ya hada kai da wata majami'a, bayan shekaru biyu sai ya koma sansani, da fatar zai fadawa abokansa na da game da Mai Ceton sa. Ba'a sake samun labarinsa ba. Idan mutuwa ce to ya yi haka ne da kaunar wadanda suka kashe shi.

***Daya daga cikin halayyar dan adam mafi dafi ita ce kiyayya. Ana kwatantata da gubar acid da ke cinye mazubinta. Wadanda ke kiyayya sukan hallaka kansu ta wurin bakin cikin su. Amma mai bi yana da rayuwa ta ruhaniya da ke cin nasara da son yin abu na mutumtaka. Yesu ya nuna wa mutane yadda zasu kaunaci makiyansu, kuma sakamokon yi musu haka ya sabunta su. Sauyi ko sabuntarsu na iya aukuwa cikin sauri da mai tubar zai ce ina ne kiyyaya take? Tunanin yin ramako yana hana ka barci? Ka juyo wurin Yesu domin samun warkaswa daga kiyayya. Ka gafartawa masu yi maka laifi yau domin ka sami bege a gobe.***

## MATSANANCIYAR DUKIYA
### *Romania: Kauyawan Dobrogea*



**Nicholas Ceaucescu ya bullo da wani salo da ake kira "tattarawa". A zaman sa na mugun mai mulkin kama karya na Romania, watakila yana zaton tunani ne mai kyau a sa mutane su mika dukan abinda suka mallaka don radin kansu ga hukuma domin amfanin kowa da kowa**

*Gama kai al'umma mai-tsarki ne ga Ubangiji Allahn ka ya zabe ka ka zama al'umma kebabiya a gareshi, gaba da dukan al'ummai da ke bisa fuskar duniya.*

*Fubawar Sharia 7:6*

Manoma, masu gidaje da talakawa a koina sun rasa mallakarsu, gonaki, tumaki, shanu, gidaje, dawaki da tebura. Shaharar bunkasa ta aikin gona da akasan Romaniyawa dashi ya zama babu. Kowane manomi a yanzu ya zama bawa ga kasar, suna aiki a gonaki akan albashi mai ban tausayi a gonakin, da suka zama na kasa. Yanzu sai iyali sun shiga layi ake basu burodi na kalachi

Domin ya ga lalle mutane basu yi tawaye da hanyar da yake bi da su ba, sai mai mulkin kama karyan nan da kansa ya taimaka a wajen kaddamarwa ta farko. A yankin Dobrogea ta kasar Romania an tara mutanen kauyen a dandali aka kuma tambaye su da su bayarda abubuwan da suka mallaka da yardar rai. Akayi shiru babu wanda ya fito. Ceaucescu ya harbe mutum goma da bindigarsa. Sai aka sake kira "su wanene suka yarda su bada dukan mallakarsu?"
Suka fara sa wakokin sa kuma suna yabon Kwaminisanci, aka tilasta wa mutane suyi rawa, aka dauki hoton video ana nunawa ana tallar cewa mutane suna haba-haba da kwaminisanci. Wani manomi da ya rasa dukan mallakarsa ne ya bada rahoton haka. Suna zaton sun kwashe komai da komai. Amma sun bar wani muhimmin abu-litattafanmu na raira wakoki.

***Mutane sukan je wurin wasanni domin su yi cudanya da jama'a kuma su kara sanin juna. Tambaya mai waye kai ita ce wane abu guda daya zaka kawo idan ta dauro ka makale akan wani tsibiri in da babu wani mahaluki, mutane dayawa sun rasa shawara da ya kamata su yi sai da aka tunashe su cewa fa ai wannan wasa ne.***

***Amma mutanen Romania basu wayi gari suna cewa nasu al'amarin na wasa ne ba. Suna ganin abin a zahiri. Gwamnatinsu bata bar masu kome ba a mallakarsu. Duk da haka kauyawan sun gane muhimmancin litattafan wakokinsu da aka barsu dasu ya kawo musu farinciki a kauyen wanda yanzu ya zama kamar tsibirin da aka watse aka bari babu kowa. Mutanen sun aminta litattafan wakokin, Allah Kuma ya aminta mutanen***

# BAYASWA MATSANANCIYA

## Lebanon: Mary

RANA TA 102

***Ko yazama ana tsiyaye ni bisa hadayata ta bangaskiyar ku da hidimatta na yi murna na yi farinciki kuma tare daku duka***

***Filibbiya 2:17***

***Mary tana yar shekaru gomasha bakwai ne kawai da musulmi masu tsattsaurin ra'ayi suka kai hari a kauyen su a kasar Lebanon. Aka fuskanchi Mary da iyayenta da suyi zabi "ko ku musilinta ko a harbeku"***

Da karfin hali Mary ta gaya wa mutumin, "Na zabi Allah. Ka ci gaba da harbi" Aka harbe Mary da iyayenta aka barsu da tsammanin sun mutu. Bayan kwana biyu, Kungiyar taimako ta Red Cross ta iso kauyen suka taras da abin al'ajibi, Mary tana da rai har- sashin ya nakasa ta.

Cikin tsamanin zafin ciwo Mary ta dagewa bangaskiyar ta tayi addu'a. A karshe sai tayi salama a zuciyarta, salama ta ban mamaki. Sai ta kudurta a ranta ga Allah cewa:

Kowa yana da aikin da ya kamata ya yi. Bazan taba iya aure ba ko yin aikin karfi. Saboda haka zan bada rayuwata domin masallata, kamar irin wadanda suka kashe iyayena, kuma suka yi kokarin kashe ni. Rayuwata zata zama addu'a a domin su.

Addu'oin ta da kuma shaidartar kin yin musun Kristi ya kawo masallata da yawa ga bada gaskiya ga Dan Allah.

A Lebanon shekarar 1990 ita a mafi muni a cikin shekaru gomasha biyar na yakin basasa da da akayi. An kashe dubban mutane kuma dubu-dubata sun kaura cewa kasar garin gudun hijira.

Amma irin hali da Mary take ciki ya karfafa Krista da yawa akan su zauna su dau matsayi domin Kristi.

***Bayaswa mafi girma kwarai ga aikin Allah ba zai dauku a cikin farontin yin baiko na majami'a ba. A lokacinda muka dubi rayuwarmu kacokan a zaman bayaswa ga Allah, dabarun mu na taimakawa mulkinsa ba su da iyaka. Da yawa da aka azabatar kamar Mary suna dauke da labaru makamantan haka.***

***Sun kanci gaba da bada rayuwarsu domin yi wa wandanda suka tsananta musu hidima a zaman yin sujada. Therese ta Lisieux ta taba cewa "shan wahala da aka dauka aka domin wasu yakan kawo tubar mutane fiye da yin wa'azi da baki" Krista mafiya yawa sukan sami kawo hajjar kin bada kansu cewa "aiki yayi sani cewa Allah yana iya bayyana hanyoyin na musamman na yadda zamu iya bayyana hanyoyi na musamman na yadda zamu iya zama shaidunsa.***

# BAKINCICI MATSANANCI

## Romania: Archmandrite Ghiush

RANA TA 103

***Kurkukun kwaminis na Jilava yana da tsanantawa na musaman. Pasassun tagogi suna bari iskar hunturu mai kankara ya shigo dakuna. Wadansu fursunoni ma sanyi ya kashe su. Babu tausayi ko kadan ga masu bi a wannan kurkukun Jilava. Alahali ma, jimrewa munanan duka da maketatan jami'an tsaro suke yi masu.***

*Yanzu murna nakeyi, ba domin bata zuciyar ku ba, amma domin bacin zuciya irin da Allah ke sa ayi maku domin kada kusha hasarar komi ta wurinmu.*

*2 Korint 7:9*

Daya daga cikin sababbin fursunoni, Archmandrite Ghiush pasto ne a birnin Liberty ta Romania. A lokacinda Archmandrite yake marmarin dube duben sabon mahalli da aka kawoshi, sai ya ga sananniyar fuska ta mutuminda sukayi aiki tare a Liberty. Shine Pasto Richard Wurmbrand. "Takaka za'a ce haryanzu yana raye? "Archmandite yana tunani, babu wanda ya sami labarin sa yanzu kusan shekara takwas" Pastocin nan guda biyu masu karfin hali suka rungumi juna. Archmandrite yayi murmushi ta godiya domin ya ga tsofon aboki da zai taimakeshi jimrewa bala'in wahala da zai shiga.

Amma Pasto Wurmbrand baiyi murmushi ba. Yayi bacin rai da ganin irin wannan Pasto mai kokari a kurkuku. Sai ya fara nuna damuwa a kansa. Shin zai iya rayuwa ya fita daga wannan azaba?, Ko zai haukace ne kamar wasu da ya gani?. Bayan shekara takwas a kurkuku Wurmbrand yasan abin da yake tafe.

Abokan nan biyu suka zauna shiru na wani dan lokaci. A karshe Richard ya katse tunanin da suke jujjuuyawa a zukatansu, kuma a hankali ya tambaye shi. "Kana bakincikine? "amsar da ya bayar yace, "danuwa bakinciki daya ne na sani. Watau shi ne rashin cikakken zama tare da Yesu".

***Abu ne mai wuya a karanta ainihin labarun Shahidan Kristi ba tare da tsigar jikin mutum ya tashi ba. Bisa ga mutumtaka, mutum yakan yi bacin rai da kuma jin tausayi ga wanda aka yiwa mummunar kisa ba tare da yin laifi ba. Amma su jaruman wadannan labaru zasu fi son akasin haka. A lokacinda suka bada kansu, sunyi ne da fatar wannan bada kai zai sa a zuciya kuma ya karfafa wasu ga yin haka in ta dauro, amma ba don a tausaya masu ba. Tabbas mutuwar su na taba mana zuciya. Amma a fahintar kankantar bangaskiyarmu kamata yayi muyi nadama. Wannan shine abin bakinciki kana samun kalubale game da jin tausayinka irin na duniya tare da tuba domin sakacinka? Shin kana da tunani na kwarai domin dagewa a zaman sakamakon karatun wannan labari? Ka roki Allah ya***

*Ban gaskiya ba ta ma da kimar*
*sunan sai in ta barke ga*
*yin aiki tukuru.*

**CATHERINE MARSHALL**

## TSANANIN GAFARTAWA

### Romania: Demeter

RANA TA 105

*Kuna hakuri da juna, kuna gafarta ma juna, idan ko wane mutun yana da raganar kara game da wani: kamar yadda Ubangiji ya gafarta maku, hakanana kuma sai ku yi.*

*Kolossians 3:13*

***Demeter ya sha wahala na shekaru a kurkukun Kwaminis. Duk da haka yana cike da karfafawa a ruhaniya a lokacin da yake tsare, amma jikinsa ya fara nuna gajiya. Akwai wani ganduroba wanda yake cikeda nishadin dukan gadon bayan Demeter da guduma, wanda ya gurguntadda shi na din-din-din.***

***Amma halin kamanta Kristi bai taba rabuwa da shi ba, kuma akwana a tashi sai ya sami sallama daga kurkuku.***

Shekaru ashirin daga baya ya ji an kwankwasa kofar gidansa. Yayi mamakin ganin shi wannan ganduroba wanda ya doddoki gadon bayansa har ya nakasa shi a shekarun baya gashi kuma tsaye a gabansa. Haryanzu dai Demeter bai sauya daga bangaskiyarsa ba.

Kafin ma Demeter ya mika masa gaisuwa, tsohon ganduroban nan yace. "Na lura da cewar bazan iya samun gafartawa ba na abinda nayi maka. Abin ya cika muni. Amma ina roko ka saurari kalmonina na ban hakuri sa'anan zan tafi."

Demeter ya dakata na wani dan lokaci a lokacin da yake.duban mutumin da tausayi da kuma mamaki, sai ya amsa masa a hankali. "Shekaru ashirin kenan a kullum ina yin addu'a domin ka. Na sha jiranka. Tun shekaru ashirin da suka wuce ne na gafarta maka. Idan muna da niyyar nuna kauna da gafartawa ga kowa-harma da wadanda suka nuna mana tsanani-Ashe kuwa kaunar Kristi za ta ci nasara akan duka.

***Mafi yawan mutane ba zasu taba yarda susha azabar ganganci ba. Amma raunukan da wasu suke yi mana yakan jimana.***

***Tunawa da kalamu marasadadi, aboki ya ci amanar aboki, mutuwar aure, duk wadannan suna tare da mu duk tsawon rayuwarmu. Muna iya ma mu kullaci, ko kuma ma mu yi kokarin rama wa wandanda suka yi mana laifi. Gafartawa baya zuwa mana ta halin mutumtaka, amma ba'a iya raba ta daga ikon Allah. Idan har mun dandana alherin Allah, to sa'anan ne zamu iya bari wasu su ribatu da gafartawa ta Allah. Gafartawa bata dangana da cewar sai mai laifin ya roka ba. Wannan aiki ne na biyayya, da kuma bangaskiya. Ka roki Allah ya bude zuciyarka zuwa al'ajibin gafartawa.***

# ZIYARA MAI TSANANI

## Gabashin Turai: Jon Lugatanu

RANA TA 106

***Wani matashin Krista a Gabashin Turai, Jon Lugajanu, an dawo dashi kurkuku bayan sauraren shari'arsa. Abokan kurkunsa suka yi marmarin tambayarsa, "Menene ya faru"?***

*Yasha azabar mutuwa domin tawurin alherin Allah ya dandane mutuwa domin kowa.*

*Ibraniyawa 2:9*

Ya amsa, "Abin kamar ranar da malaika ya ziyarci Maryamu, uwar Yesu, sai ga ta nan Baiwar Allah a zaune ita kadai cikin halin yin ibada, a lokacin da mala'ikan Allah mai haske ya bata labari mai ban al'ajibi cewa zata yi cikin dan Allah.

Dokin sanin yadda wannan labari ya shafi abinda akayi a cikin dakin shari'a da Jon sauran fursononi suka saurara domin suji.

Jon ya tafi domin ya bada bisharar salama ta wurin bada labarin Maryamu. Duk da irin farinciki da haifuwar Yesu ya kawowa Maryamu. Ashe wata rana zata tsaya a karkashin giciye ta gani da idanun ta yadda zai sha wahalaha ya mutu domin zunuban duniya. Allah ya tada Yesu , inda yake mulki yanzu a sama. Maryamu ta sani cewa da zarar ta je sama, zata sake ganin Yesu ta kuma yi farinciki na har abada".

Sauran fursunoni suka dimauce. "Amma mun tambaye ka ka fada mana abin da ya faru a dakin shari'a, suka tunashe shi.

Jon ya dube su, fuskasa tana haske da salama, "Jon ya gane cewa labarin da mala'ika ya baiwa Maryamu gashi da dadi, gashi kuma da dachi-bayan Yesu ya wahala za'a sami farinciki a sama. Yana dokin samun nashi farinciki madawwami a gaban Yesu.

***A cikin al'adu da yawa na duniya ba'a cika son yin zancen mutuwa ba , wadansu ma sun canfi yin haka, wadansu ma sukan dauki duk matakinda zasu iya dauka domin yiwa kansu kariya, daga abinda ansan dole ne ya faru watau mutuwa. Sukan so suyi amfani da kalmomi kamar. "Lokaci yayi" maimakon kalmar ya mutu".Mukan yi kiwuyan yin wasiyya ko kuma sayen inshora ta rai, da tunanin. "Ai bazata faru da ni ba". Manyan ma'aikatu sukanci riba mai yawan gaske suna sayar mana abubuwan da zasu tsare mana tsufa dawuri. Allah bai bamu zabin cewa mu manta akwai mutuwa ba, amma ya bamu sirrin fuskantar mutuwa. Mala'ika bai boye wa Maryamu abinda zai faru da Yesu akan giciye ba. Amma kuma tana sane da zaici nasara da mutwa wanda zai kwantar mata da damuwa.***

***A zaman Krista alkawarin Allah na rai na harabada yana taimaka mana muyi na'am da tamu mutuwar a zahirance kuma da karfin zuciya.***

# KARIYA MAI TSANANI

## *Russia: George Jeltonoshko*

RANA TA 107

***George Jeltonoshko ya sani gwamatin sa batason mutane suyi shaidar bisharar Kristi, amma yana da niyya mai karfi ta biyayya da umarnin Kristi- koda ya zama gaba da dokokin kasar ne.***

***Kamika kanka ga Ubangiji ka dogara a gareshi, zai kuwa taimake zaisa maganartar ka ta hashaka kamar tsakar rana.***

***Zabura 37:5-6***

Bai zama abin mamaki a gareshi ba a lokacin da Yan Sanda suka isa kofar gidansa. Ya rigaya lissafafta cewa dole ne hakan zata faru cewa zasu yi bincike akan aikinsa na bishara a dalilin takardu da yake rabarwa. A ranar da shari'arsa ta zagayo sai aka bashi lauyan gwamnati dan kwaminis, George ya fada wa alkalin da karfin zuciya cewa. "Banason lauya inaji a dai dai nake kuma gaskiya bata bukatar kariya."

Alkali ya tambayeshi, "Ka amsa laifin ka?"Ya amsa yace "A'a yada kyawawan labaru na kaunar Allah alhaki ne na dukan Krista".

Alkali yace in haka ne sai ka hada kai da "majami'un da gwamnati ta basu izini" wadanda ke bin umarnin gwamnatin kwaminis. Amma George ya ki. Irin wadannan majami'u suna bin umarnin kasar ne amma ba dokokin Allah ba. Alkali ya fara fusata. "A ina kuke taronku na sujada? "Ya tambaya. George ya amsa. "Masubi sukan yi sujada a ko'ina".

Aka daure shi shekara uku a kurkuku inda George yaci gaba da aikinsa da kuma sujada. Haka ne gaskiya bata da bukatar kariya.

***"Yin abu daidai" yana iya zama sanannen take, Amma wannan fada ne ba yi ba, domin abinda yake daidai a gaban Allah galibi yakan yi karo da abin da mutane sukafi so. Rashin jituwa tsakanin yi daidai da akasin haka yakan fito fili a cikin aji, ko wajen aiki kai har a dakin shari'a ko majami'a. Ba zamu iya dogara ga kewayen mu ne ya gaya mana gaskiya ba.***

***Mutane suna iya rinjayarmu su rudar da mu akan sanin me ke daidai a cikin al'amuran mu. Maiyiwuwa wasu ba zasu gane ko su yarda da zabin da mukeyi ba. Amma Allah yayi alkawarin yin na'am da bada kai da muke yi na yin abin da yake daidai. Wadanda suka zuba mana ido zasu ga haske kuma suji domin ayyukan mu na gaskiya.***

# MATSANANCIYAR WUTA

## Siberia: Victor Belikh



***Tare da hasken wuta ta kauna da Yesu ya kunna a zuciya ta nasa kankarar Siberia ta narke hallelujah!***

*Domin allalin mu wuta ne mai cinyewa.*

*Ibran. 12:29*

Fuskar Bishop Victor Belikh ta haskaka a lokacinda ya furta wadannan kalmomi. Ya sami sanin kwakkwaran sirri na barin jagorancin zukatan mu ga Allah ko da cikin kowane irin hali muke. Ya azabtu har na tsawon shekaru ashirin a kurkuku a kasar kwaminis ta Russia ba tare wani ya ziyarce shi ko samun labarin iyalinsa ba, ko kuma abokansa.

Akan shinfida katifan ciyawa da ake kira, "Bakya- zuwa- tasha" a cikin dakinsa kowace yamma. Akan barshi yayi barchin sa'oi bakwai kafin azo a dauke shinfidar. Sauran sa'oi goma sha bakwai na kowace rana kuwa yana yi ne ta wajen zagaya dan karamin cikin dakin, idan ya tsaya ko ya gaza sai masu tsaro suyi masa duka ko su watsa masa ruwa har sai ya ci gaba. Bayan shekaru ashirin na irin wannan azaba sai aka kaishi sansanin aikin gwalegwale na wani karin shekaru hudu a Sibeia ta Arewa inda kankara bata taba narkewa. Ya tsira amma ba domin kome ba sai dai don ya bada dama ga wutar Allah ta narkadda dukan bakincikinsa da fushinsa.

Matsayinda Belikh ya shiga ba kasafai ake samun irinsa ba, amma dagewarsa ta wurin Yesu Kristi a bude yake ga dukan wanda yake shan wahala. Yesu ya zuga wutar kauna da ke cikin zuciyar Belikh zazzafan murhu mai dumi daga Allah da ya duma shi har na tsawon shekaru ashirin.

***Wuta, Jin saunan kadai zai baka tunanin abu mai zafi. Idan aka kira sunan da karfi a cikin taro na ginegine to kowa zai maida hankali akan cewa ko gobara ce. Tana kawo shakatawa idan dumi ake nema a lokacin sanyi. Ana danganta wuta da abu mai karfi misali "wuta wuta "watau mai zafin-nama. Ana kuma amfani da wuta domin tace ko kuma kara kyau na wani abu kamar karfe ko a haskaka ko a taurare karafa. Wuta tana haskaka ko kauda duhu. Duk cikin wadannan abubuwa, abu daya ne bai sauya ba. Wuta tana da dagantaka da sauyi kamar ma'amala da wuta, ma'amala da Allah abu ne mai sa sauyin rayuwa sauyin rayuwa . Shin kaunar Kristi. Mai wuta- ta kunna, ta taimaka aci gaba banda kasawa, tace ta ta'azantar kuma a karshe ta yantar da kai kamar yadda ta yantar da Belikh?. Muguntar dan-adama ba zata taba iya kashe wutar kauna ta allah ba. Shin ko wutar kauna ta Allah tana ci a cikinka?***

# MATSANANCIN SUNA

## *Urshalima: James*

RANA TA 109

***James "adali" yayi aikinsa da aminci a mukamin shugaban sabuwar majamaia. Bà da jimawa ba bayan tashin Yesu daga matattu. Babu wani maraban gaskiya da ke jure wa wa'azinsa ba tare da tuba ko arcewa daga gabansa ba.***

*Saboda haka duk shan wuya biasa ga nufin Allah su danka ran su ga mahalicci mai aminci suna aikata abin da ka daidai*

*I bitrus 4:19*

Sabili da haka, babban malamin da sauran shugabanin Yahudawa suka dora James a kan hasumiyar majami'a kuma suka ce yayi musun Yesu da tashinsa daga matattu a gaban taron ja'ama ko kuma a jefo shi kasa. Wannan awa a gurin James dama ce ta yin wa'azi ga taro irin wannan. "Ku saurara jama'a! Yesu shine mai ceto da aka alkawarta ma duniya, Dan Allah, kuma mai ceton mu!" Yana zaune a hannun dama na Allah kuma zai sake dawowa duniya domin ya shar'anta masu rai da matattu!. "A can kasa wasu suka fara yabon allah suna daukaka sunan Yesu, wasu kuwa suna mamakin karfin zuciyarsa da kuma amincewa. Lalle mutumin nan adali ne! Nan da nan suka turo shi daga sama-ya fado kasa ya mutu.

Taro yayi tsit sai wani ya tada murya, "Duba, yana da rai! James bai mutu ba ya durkusa ne garin yin addu'a. Da yawa sun debi duwasu domin su jefeshi,

Sa'anan daya daga cikin malaman yayi gaba ya roki jama'a. "Me kuke yi? "Adali" yana yi mana addu'a kuma me kuke so kuyi masa?" Yana fadar haka sai wani ya zo ta bayansa da katon karfe ya makawa James aka. Ya kashe shi nan take. An binne shi a wannan wuri da ya fadi.

***A bayan kowanne al'amari da aka karanta labarinsa a tarihi, akwai labari. Wannan labari akan James ya zama ai'nihin irin mutumin da James yake da kuma shaidar Yesu da yakeyi. Su da suka sanshi sosai sun san bada kai da yake da shi ga Kristi. Wadanda basu sanshi ba sunji labarin halinsa da shahararsa a zaman mai wa'azi da karfin zuciya. Mutuwarsa wata karin shaida ce ta tsayayyar bangashiya na mabiyan Kristi. Tarihin kristanci yana tabbatar da bangaskiyar masubi da shaidu na gaske. Menene tarihi zai fada a kanka? Wane labari zaka bari a baya domin jikoki da tattaba kunne game da bangaskiyar ka?.***

## BAPTISMA TA KWARAI

## *Slovakia: Annmarie*



***Annmarie wata matashiyar Krista,' tayi zaman kurkuku watanni domin huldar ta da majami'ar karkashin kasa. A kan kaita wani daki akai akai inda masu tsaro suke yi mata duka domin su sami labarin sauran Krista da ke majami'arta.***

*Baptisma kuwa wadda it ace kwatacin wannan, ta ceceku a yanzu, bata fitar da dauda a jiki ba, sai daita wurin ikon Allah da lamiri mai kyau.*

*1 bitrus3:21*

Ta wurin ikon Allah kuwa ta jure har ma tayi amfani da wannan zarafi tayi wa masu tsaron bishara akan kaunar Yesu. Mai tsaron yayi mata ba'a "Idan baki gaya mani asirin majami'ar karkashin kasa ba zan yi miki dukan da zai kawasda dukan kaunar da kike ji kina da"

Annamarie ta amsa masa. "Ina da aboki maifi dacewa. Shi kaunane, kauna bata neman nishadi amma takan nemi ta cika mutane da farinciki. Tun lokacin da nasan wannan abokin. Ni ma, kauna kadai na sani. Kai mai kaunar kiyayyane amma yanzu ina rokanka ka kaunaci kauna"
Mai tsaron nan don bacin rai yayi ta marinta har ta suma. Da ta farfado sai ta ganshi a zaune shiru kamar wani da ke cikin zurfin tunani. A karshe ya tambaya "wanene abokin naki?" Annmarie ta bashi labarin Yesu da dalilin zuwan sa a lokacin da ya tambaya yace takaka shima zai maida Yesu ya zama abokinsa, sai ta gaya masa dole ne ya tuba daga laifofin sa kuma ayi masa baptisma. To in hakane ayi mani baptisma yanzu yanzu in ko ba haka ba zan harbe ki. Ya umurceta.

Annmarie ta yi masa baptisma, daga baya kuwa shi ma ya zama fursuna tare dasu wadanda yayi wa duka.

***Idan mutane suna cikin yin soyayya, sukan bari kowa ya sani. Sukan shaida wa iyalinsu, abokai, makwabta da ma duk wanda zai saurare su. kauna takan sa su daure, rashin fadawa idon sani. Cewa kana tare da Kristi da kuma jama'arsa da ke kaunarsa. Yin baptisma ga mutum alama ce ga duk wanda yake shaidar yin hakan- in ma da wani fursuna ne a cikin hurkuku- wannan a shirye yake ya yabi Kristi ko ta halin kaka. Kaunarmu ga Kristi yana zuga mu domin mu yi shaidar ba da kanmu a duniya. Ko da ba a tsoratar da mu ba shin muna da karfin zuciya na shaidar kaunar mu ga Kristi?.***

***Bangaskiya ba ta taba zama babu aiki ba takan nemi amsa. Takan bukaci aikata manufa. Takan nuna cewa ikon Ruhu Mai Tsarki na tare damu.***

***Pastor Richard Wurmbrand.***

# KARFIN ZUCIYA MAI TSANANI

## Romania: Wata Uwa da 'Yarta

RANA TA 112

***Dukan fursunonin sun nuna bacin rai da ganin wannan yar yarinya a kurkuku tare da uwarta. Har shugaban kurkukun ma yace, "Me yasa ba zaki tausaya wa diyarki ba? "Idan da za ki hakura da zama Krista, sai kuyi tafiyanku gida".***

*Ashe ban umurce ka ba? Kadage kayi karfin hali, gama Ubanjigi Allahn ka yana tare da kai duk in da zaka.*

*Joshuwa 1:9*

Abin yayiwa matar zafi a cikin birnin ranta, an kaita kurkuku tare da diyarta bayan ta nuna rashin yarda da tsare pastonta, amma gashi ta yarda ta yi musun bangaskiyarta domin ta fitarda diyarta daga shan wahala.

Bayan makonni biyu, kwaminis suka tilasta mata ta hau wani dandamali a gaban taron mutane wajen dubu goma tayi magana da karfi tace, "Na janye bangaskiyata, ni ba Krista bace daga yanzu".

Bayan da suka dawo gida, diyarta ta jiya wajen uwarta tace, "Mamata Yesu bai gamsu dake ba yau". Uwar tayi kokarin tayi mata bayani cewa wannan tayi ne dalilin kauna. Diyarta ta dubeta da wani irin kallon amincewa fiye da na yawan shekarunta tace, "Nayi alkawari idan muka sake shiga kurkuku domin Yesu bazanyi kuka ba".Uwarta tayi kuka, cike da girman rai da kauna ga diyarta da kuma fahintar ta, ta ganin gazawarta. A yayain da take rokon Allah ya bata karfin zuciya a mayuancin lokaci na tsaida shawara, sai ta koma wurin shugaban kurkukun ta ce, "Ka rinjaye ni da nayi musun bangaskiya ta a dalilin diyata, amma tafini karfin hali. "Dukansu biyu suka koma kurkukun, yar yarinya kuwa ta cika alkawarinta.

***Joshuwa ba Israile ya fuskanci mawuyacin kalubale cigaba da jagoran Israi'la daga inda Musa'ya tsaya. Akwai hadari? Ko shakka babu. Yana taka tsan-tsan? Watakila Joshuwa ya karbi alkawari daga Allah cewa zai bi tare dashi, kuma ya baiwa Joshuwa amincewa Kaman wannan yar yarinya na wannan labarin. Da Joshuwa da wannan yar yarinya duka sun gane tun da wujri a cikin rayuwa cewa zasu bukachi tarayya da Allah kafin suci nasara. Allah yana umartarmu da muyi wa kanmu tasmahara da karfin zuciya da sani cewa bazai taba yashe mu ba. Idan muka fuskanci jarabobi, galibi karfin zuciya yakan gudu. A lokutan hargitsi, ka zabi yin dogaro da alkawarin Allah nacewa yana tareda kai.***

***Ka zama mai biyayya kuma mai karfin zuciya yau.***

## SHAWARA MATSANANCIYA

## *Albania: Valerii Nasaruk*

RANA TA 113

***A cikin kasar Albania, kasa ta farko da ta nada kanta kasar-da-bata-yarda- akwai-Allah-ba a duniya. Akwai wani matashi Krista mai suna Valerii Nasaruk da aka tsare domin yayi zanen alamar giciye a hannunsa. Yana so kowa ya sani tun daga farko wajen shan hannu ta gaisuwa cewa shifa ya mannewa bangaskiyar sa ga Allah. Valerii mutum ne da ke cikin damuwa domin ba'a yarda ya furta bisharar kaunar Allah da bakinsa ba.***

*Amma ni ko kusa bazen yi fariya ba, sai dai da giciyen Ubangiji jin mu Yesu Almasihu wanda albarkacin mutuwarsa a giciye ne nayarda da sha'anin duniya kuma ta yarda sha'a ni na*

*Gal 6:14*

A dakin shari'a alkali ya shaida wa uwarsa, "ki fadawa danki ya sauya tafiyarsa, domin ya sami yancin tafiya gida".

Tayi tunani na wani lokaci kafin ta bada amsa da hawaye cike a idanunta, "Valerii shawarata zuwa gareka shine ka tsaya da karfi kada ka yarda kayi musun Kristi, ko ma da yin haka zai kawo mutuwarka".

A cikin wasika da ta rubuta wa majami'ar karkashi kasa bayan shari'ar ta ce, "Na halarci shari'ar, wacce ta zama abu mai takaici a gareni. Na gwammaci na dauki matsayinsa a lokacin, Abu mafi bakinciki shine lokacinda suka tambaye ni a dakin shari'a wai na shawarci Valerii ya sauya bangaskiyarsa, amma ban iya yin haka ba. Duniya tana bamu laifi mu iyayensa, cewa fada da muke da ita gareshi ita ta jawo aka yanke mashi wannan hukumci. Har wasu Krista ma sun kasa gane dalilin da yasa nayi abinda nayi, amma a sa'annan ni kaina na tuna Yesu ma da kansa basu fahimce shi ba. A lokacinda nake fare da damuwa. Nayi mani tuni da Bitrus inda ya baiwa Yesu shawarar tsinar da rayuwarsa, Allah shi ke bada ikon jurewa komi. Ina roko kuyi addu'a domina".

***Allah yana kaunar mu, kuma yana da gagarumin shirye shirye domin rayukanmu. Abin damuwar shine, kana ma sane yana shiri domin mu? Yi wannan, yi wancan, jarraba wannan, jarraba wancan.***

***Kalamun bada sharawa suna nan barkatai amma lokaci yakanzo da za'a iske wasu kalamun suna da nauyi. Duk lokacinda wani maibi kamar mu ya karfafa mu da mu ci gaba da aikata nufin Allah a cikin rayuwarmu komi rintsi, mu sani cewa munji ne daga mutumin Allah. Akasin haka kuwa, kome kyaun anniyar ba shawara ce da ta dace ba. Wa kake saurara wa domin samun shawara ta ruhaniya ka tuna kuma ka rubuta shawara daga wani amintaccen abokonka. Kayi amfani da wannan shawara yadda ya kamata?***

*Zanyi ta yin*
***BISHARA***
*har sai na*
***MUTU.***

***Pastor Li Dexian - Shugaban wata majami'a a China wanda aka tsare domin yin wa'azi ba tare da izini ba fiye da sau ashirin.***

# HANGE MAI TSANANI
## *Kasar Sin: Me Ling*

RANA TA 114

***Na tace tsoron mutane daga zuciyata, kuma na koyi fuskantar Allah.***

*Ku kalafa ranku ga abubuwan da ke bisa, ba wajenna kasa ba.*

Me ling tana da karancin shekaru a lokacinda aka tsare ta domin ayyukan ta na Krista a Kasar Sin ta Kwaminis.A lokacin da akeyi mata tambayoyi, sai Yan Sanda suyi mata azaba wai don ta tona asirin abokanta na majami'ar karkashin kasa. Da farko Me Ling ta razana kwarai da gaske, kuma ta kasa ganin manufa da Allah yake dashi dominta a wannan mugun wuri. Amma sai ta tuna da koyaswar paston ta wanda yace, "Shan wahala na gaske yakan dore ne na gajeren lokaci mai cetonmu".

A lokacinda aka tambaye ta yaya ta yi ta dage har abin baikaita ga haukacewa ba, sai ta amsa, "Idan na rufe idanuna, ba na ganin fuskokinsu na rashin imani ko kuma kayan da suke amfani da su wajen azabtarwa. Nakan kuma maimaita alkawarin Kristi akai akai domin tunatadda kaina. "Masu albarka ne su da suke da tsattsarkar zuciya, gama zasu ga Allah" (Matta 5:8). Na kuma gane a lokacin da na tace tsoro daga zuciyata. Na yi koyi sosai na ganin Allah. Na sami karfin zuciya ta daga dukan su da suka rigayemu kuma na zaba idanu a gareshi da kome da kome sun shude. A lokacin da ma'aikatan suka ji labarin kariya ta, sai suka gane ina da kariya ga manufa ta.

***Mukan yaba wa mutanen da aikinsu ya ke bukatar tara hankali wuri daya. Gwanin likitan fida, gwanin dan wasan guje guje na Olympic da ma'aikaci mai hange manufarsu guda ce. Cin ma abin sa aka sa a gaba. Horon cin nasarar abin da aka sa a gaba ya wuce batun basira, kuzarin dan guje guje ko kuma farin jini. Idan ba da sa fuska ga cinnasarar da abin da aka sa a gaba ba, mutanen nan za su zama kawai masu zafin jini ne. kokarin su na dagewa shi ke taimaka wa nasarar da suke samu. Dagewa irin ta duniya takan kawo nasara irin ta duniya, amma kaka batun gobe kiyama? Idan ka dage wa abin duniya mai wucewa, zaka rasa cin nasara Me zaka iya yi yau domin ka tabbatar da dagewarka ga Kristi da kaunar yada bisharar sa?.***

# WASIKU MASU TSANANI
## *Kasar: Ukraine*

RANA TA 115

**Jaridar Soviet maisuna Molodoij Gruzii ta buga rahoto a kan wasu Krista guda uku da aka tsare a kurkuku. Laifin su shine wani shiri na musamman da suka yi na raba wasiku domin taimakon mutanen cikin dukan fadin Kasar Soviet su fahimci koyaswar Yesu Kristi.**

*Maganarka tabbatacciya ce ya ubangiji, a kafe take a sama.*

*Zabura 119:89*

Rashin samun damar wallafa Littafi Mai Tsarki da sauran takardun Krista, sai suka fara aikawa da dinbin wasiku kuma suna shaidawa wadanda aka aika masu wasikun cewa suma su juya a wasu takardu su ma su aika wa wasu.

Ta wurin wannan dabara ta yada bishara dubun dubatar wasikun sun isa loko da sako dabam dabam na Kasar Soviet.
Musamman ma yara sunyi na'am da wasikun domin ba a basu damar zuwa majami'a, dalili kenan da wasikun na nan suka zama hanyarsu ta samun koyon maganar Allah.

Bugu da kari wadannan wasiku sun taimaka wajen karfafa bangaskiyar Krista cikin fadin kasar a wannan lokaci. Bayan shekaru da dama da gwamnati take musu danniya da katsalandan a majami'un su, a shirye suke su jarraba wasu sababin hanyoyi.

Sunyi shiri ne na gaske domin kowa ya sami jin labarin kaunar Allah, kuma baicin ta kura su da akayi, saukin kansu da fasahar su ta sa bisharar ta yadu ko ina cikin garin Tbilisi har ya zarce zuwa wasu yankunan Ukraine!

Wani labari kuma ya fada a jarida cewa "Kristoci sun mamaye garinmu da rubuce rubucen su, "Tayi bayanin wannan kokarin hadakai a zaman, "Wani hari ne daga Kristoci".

Wanene zai iya kintatar adadin da jerin rubutattun wasiku zasu yi?

***Bayan shekaru hamsin na kuntatawa Krista, hukumar Soviet ta tsoranta da jerin wasiku. Amsarsu a tsorace kana nuna iko dake cikin maganar Allah. Duniya ba ta bada kai ga kokarinmutum. Bata sanyi dajin tausayi. Kadai takan ki yarda maganar Allah mai cike da iko- da ke mai rai kuma yana aiki a cikin rayuwar masubi. Shaidan yakan yi- makyarkyata idan aka ambaci iko da ke cike a cikin maganar Allah. Wai muna sane da wannan iko kamar yadda magabtan mu suka sani? Idan har ya dau wani lokaci rabon ka da kaji tsoro ko fargaba a lokacin da kake karatun maganar Allah, ka roki Allah domin ya baka wata damar. Ka rokeshi ya nuna maka ikonsa domin kaji maganar Allah na aiki a rayuwarka yau.***

# BADA KAI MATSANANCI

## *Kasar Sin: Yar'uwa Kwang*

RANA TA 116

**Bayan fama da aiki mai tsanani kuma na dogon lokaci abincinda ake bayarwa baya isa ko kadan, yan China masu tsaron kurkuku suka nemi wani ya bada kansa domin tsabtace gidan wanka a kullum. Babu daya daga cikin mata fursuna da ta budi baki.**

*Kuma dukan abin dakake yi ko tawurin magana ko ta wurin aikatawa kayi su duka a cikin sunan Ubangiji Yesu tareda yin goldiya ga Allah wurin sa.*

*Kol 3:17*

A karshe, Yar'uwar Kwang ta yiwo gaba ta bada kanta domin yin wannan kazamtaccen aikin. Tayi hangen cewa wannan zai bata damar tattaunawa da sauran matan kurkuku game da shaidar bangaskiyar ta wandanda in bata bi wannan hanyar ba, ba zata ma sami saduwa da su ba. A lokacin ta na zaman kurkuku ta kawo daruruwan mata ga Kristi.

Dukufar Kwang ga yin sujada sanannen abune ga dukan wadanda suka santa, amma fa irin wannan sani yazo ne ta hanyar shan wahala. Kafin ta shiga kurkuku, ita da mijinta sun bada kai domin shirya kungiyoyin masu yin bishara wadanda da suke tafiye tafiye a cikin Kasar Sin suna kafa kananan dakunan sujada.

A lokacinda kwaminisawa suka gano ayyukan Kwang, sai suka yi wa danta dan shekaru gomashabiyu duka har sai da ya mutu. Amma duk da haka taki tayi musun Kristi, sai ma ta ci gaba da kafa kungiyar masu sujada ta gida bayan da aka saketa.

A karshe cikin 1974 kwaminisawa suka yi shawarar nuna misali da "Mama Kwang" sunan da ikklisyarta suka santa dashi. Aka daure ta rai-da-rai a kurkuku aka sa ta a wani killataccen kurkuku a karkashin kasa da bokitin ba- haya kuma ana ciyar daita da kazamar shinkafa.

Ta sami saki na ban al'ajibi bayan shekara goma, akullum kuwa takan waiga ta tuna da zamanta na kurkuku da cewa wannan zaman kaso baiwa ne- dama ce ta musamman na more kaunar Kristi ba tare da mutane wadanda da ba domin haka ba da maiyuwa ba zasu taba jin labarin Yesu ba.

***Ba da kai ya zama sana'a ga wadansu mutane. Sukan bada ki a makarantar yayansu, sukan taimaka a kungiyar iyaye da malamai kuma sukan taimaka a kungiyar iyaye da malamai kuma saukan koyawa yara kwallo. Bada kai ga yin abubuwanda basu da farinjini sun ki bada kalubale. Galibi kuzarin bada kai yakan yi sanyi. Ma'aikatun asibiti, gidan marayu ba wurareno kowa yake sha'awa ba wari, takaici da ke kewayen da sauran abubuwa marasu dadi yakan kori mutane da. Amma a zatonka a ina Yesu zai so yin anfani da lokacinka? Kusan dukan inda aka bada kai akwai aikin yi mai anfani da ban sha'awa, amma ka saurara a hankali domin samun dama. Kayi kokari na zama mai bada kai na farko a yace da damar yin haka ya samu.***

# MATSANANTUN MASU SAURARO
## Romania: Pasto Richard Wurmbrand

RANA TA 117

**Ko da shike an tsare Pasto Richard Wurmbrand a dakin kurkuku na daga-kai-sai-kai wurin da babu haske sai duhu kuma babu wani mahaluki kusa ballantana aji sautin dan adam ko motsin wani abu, duk da haka yaci gaba da yin bishara ga masu sauraron da ba'a gani.**

*Baku dashi domin laku roki Allah ba.*

*Yakub 4:2*

Bayan shikarsa ta ban mamaki daga kurkuku da kuma kaurarsa zuwa Amirka, Pasto Wurmbrand ya rubuta litattfai da dama inda ya bayyana irin halin da yashiga da kuma irin wa'azin da ya wallafa kuma ya haddace a lokacin da yake zaman kason daga kai-sai-kai. Bayan yan shekaru kuwa sai ya sami wannan wasika.

Zuwa ga Pasto Wurmbrand. Na samu reno kuma na yi girma a hannun iyali masu tsoron Allah amma sai na ratse a karshe ma dai har ta kaini ga shiga kurkuku a nan Canada. Ina so na koma ga Allah amma ban san hanyar da zanbi ba, saboda haka sai nayi addu'a. Allah idan akwai wani a cikin duniya ko ina wanda yake cikin fursuna ne shima kuma cikin kadaici wanda kuma ya sanka ina rokon ka ka kawo mini tunaninsa. Naji wata murya a cikin birnin raina tana gaya mini na zauna shiru kuma da karfin zuciya cewa Allah zai isa gareni.

Abin mamaki sai na fara ji dare bisa dare ana wani abu kamar wa'azi kuma ina ji kamar yana zuwa daga wuri mai nisa. Sai na furta laifofina na tuba bayan sallamata daga kurkuku, na karanta littafin ka. Wa'azi a kurkukun daga-kai-sai-kai a kantin litattafai na Krista. Nan da nan kuwa na gane wadannan wa'azi ne da naji a lokacin da nake kurkuku. Na gode sabili da wadannan bisharu da ka bayar.

Pasto Richard Wurmbrand ya sami wasu karin wasiku biyu daga kasashe dabam dabam wadanda suka yi kama da juna wajen labarunda ke kunshe a wasikunsu. Tabbas mala'iku sun dau wannan wa'azi zuwa wasu wandanda suke kira ga Allah.

***Rashin tsayayyas ban gaskiya ta Krista ta maida malaiku tamfar marasa aikin yi. Yawancin lokaci masu bi sukan fi gamsuwa da rayuwan annashuwa mai albarka amma sa'i amma Allah maison bamune fiye da abubuwan da muke ganin kyawawa ne a garemu. Shi mai son ya kai mu ne ga abubuwa mafiya kyau, ya kebe albarkunsa mafiya kyau domin wadanda suka roka cikin bangaskiya.***

***Me zai sa mu roki Allah, idan har ya riga yasan bukatun mu? Lalle ne mu roka cikin bangaskiya domin mu nuna dogaro da muke dashi gare shi. Shin ka sami gamsuwa da kyawawan abubuwa da Allah ya baka? Idan haka ne ka roki fiye da haka tare da bangaskiya ka nemi abubuwa mafiya kyau daga gareshi domin rayuwarka.***

***I dan da dukan yan Adam masu adalchine sai mutum daya ne mai zunubi har ila yau da Kristi yazo domin ya jure wa azabar giciye domin wannan mutum dayan. Shi mai kaunar kowane mutum ne.***

***AUGUSTINE***

# MATSANANCIN MATSORACI

## *Tarsus: John Mark*

RANA TA 119

**"Ba zai iya zuwa tare da mu ba" Bulus ya nace. "Shi matsoraci ne kuma ba shi da anfani ga kungiyar."**

*Ka dauko Markus ku zo tare, gama yana da anfani gareni wajen yi mani hidima*

*2 Tim 4:11*

Barnabas ya maida murtani, "Mai yiwuwa ka fitarda rai game dashi, amma Allah bai Fidda rai ba".

Paul dai ya dage haryanzu, "Ba zaka iya sani a dole ba, Barnabas. Mutanen da zan iya dogara dasu, sune Kadai mutanen dazan kawo tare dani. Ban yi masa maraba a wannan tafiya ta yada bishara".

Idan hakane nima ba a marabceni ba kenan. Shawarar ka ce, Paul. Allah ya nuna maka alkibar tafiyar bari mu rabu cikin salama. A lokacin da majami'a take shakkarka, ta wurin alherin Allah nazo wurinka, kuma na nuna masu cewa zakayi kasaitaccen aiki domin mulkin Allah. Irin wannan kira ne kuma Allah yayi wa John Mark". Paul ya dan yi shakka, amma dagabaya sai yace, "To bari ya zama haka. Ina fatar cewa zancen ka daidai yake tsofon abokina, ko da shike ni dai ina jin kamar ban gaskanta ba a karan- kaina ". Ta haka kuwa Paul da Barnabas suka rabu. A kwana a tashi kuwa da Paul da John suka kare a kurkuku tare a birnin Rome kuma Paul ya tabbatarda dagewa da amincin cikin Kristi na wannan matashin aboki nasa amintaccen bawa ne na Kristi. John Mark shine ya rubuta Bishara ta Markus kuma ya tabbatar da kansa azaman-matsoraci a yayin da shi da Paul suka fuskanci gwagwarmayar wahala irin ta kurkuku.

A zamansu mai wahala na kurkuku Mark ya dage babu gazawa, wanda Paul ya tabbatar da wahalar wasika zuwa Timothy jim kadan kafin mutuwarsa.

***A wasu lokuta Allah yakan jarrabamu domin tabbatar da gaskiya guda biyu: Ya kanyi anfani da gwadawa domin ya nuna mana kuma mu san irin cigaba da mukayi da kuma matsayin mu a ruhaniyance ko kuma ya bada damar shigarmu cikin wasu al'amura masu wuya domin mu samu sanin a ina da kuma yaushe ya kamata muyi aiki da su domin samun girma cikin ruhaniya.***

***Rikidar John Mark daga sanannen matsoraci zuwa tsayayyen mabiyi yana yi mana tuni cewa girma cikin ruhaniya al'amari ne na yau da kullum. Amma ba lalle ne ayyukan mu na baya su shafi abin da ke zuwa a gaba ba. kamar da John Mark, shin kana bukatar wata sabuwar dama domin ka nuna bada kanka ga Kristi? Yi addua'a domin samun dama da zai taimakeka yin girma a cikin ruhaniya.***

# MATSANANCIYAR HUDUBA

## *Kasar Sin:*

RANA TA 120

**"Harbe su, mu kuma zamu barka ka rayu".**

*Kuyi wa juna kirki, kuna tausayi kuna yafewa juna kamar yadda Allah ya yafe maku ta wurin Almasihu*

*Afisawa 4:32*

Pasto ya shirya ma'amala da yan kwaminis a cikin kurkuku mutanen kasar Sin inda ake tsare dasu. Amma wasu yan-matan Krista guda biyu da suke tsaye a gabansa sun dage sun ki yin musun bangaskiyarsu. Wani fursuna wanda ya ga wannan yayi bayanin cewa ya ga wannan mugun abu da ke faruwa yayi bayanin cewa ya ga fuskokin yan'matannan a kode amma kyawawa abin sah'awa fiye da misali- ga bakinciki a fuskar amma kuma ga wata alama mai ban sha'awa. Sun kafe da shirin fuskantar mutuwa maimakon juyawa Kristi baya.

Pasto yayi tunani, "Me zaisa dukanmu uku mu mutu? Idan na kashe ku kuma aka barni na rayu, kun ga sai naci gaba da aiki a tsakanin majami'u". Yan matan suka yi masa magana a hankali. "Kafin ka harbe mu, muna so muyi maka godiya domin abinda ka zama a garemu. Ka kawo mu ga Kristi, ka yi mana Baptisma, kuma ka ciyar da mu da jibin Ubangiji. Bari Allah yabaka ladan ayyuka masu kyau da kayi. Kuma ka koya mana cewa a wani lokaci Krista yakan rasa karfin hali har ya kaishi ga aikata munanan zunubai, amma za'a iya gafarta masu kuma. Idan kana yin nadamar abin da kake shirin yi mana ne ka da ka karai kamar Judas Iskariot amma ka tuba kamar na Bitrus. Kuma ka tuna cewa wannan rabuwa da zamuyi na karshe, tunanin mu gareka bana kiyayya bane ko na fushi, amma na kauna ne da gafartawa. Dukan mu mukan ratsa lokatai halki mawuwata. Muna mutuwa da farinciki.

Amma zuciyar wannan pasto ya rigaya ya taurare, sai kuwa ya harbesu. Nan da nan bayan haka kuwa sai yan kwaminis suka harbe shi.

***Mutanen da suke cikin halin fuskantar shiga halin mutuwa suna iya shiga tunani iri iri. Wasu suna iya yin tunani rayuwar da sukayi can baya. Irin wannan ma da ban mamaki domin wani ne da aka dauka cikakken aboki wanda ya bashe su. Za'a dace idan har suka ji haushinsa, sukayi fushi dashi? A zaman mu na Krista lalle ne mu zabi mika hannun gafartawa cikin dukan al'amaruran mu ko da ya shafi rai ko mutuwa. Kamar dai wadannan yan'mata a wannan labari, mai da murtanin ka ga wani mugun abu da akayi maka ya kan zama kasaitaccen wa'azi. Ta kaka hanyar da ka zaba ta gafartawa zata zama hanyar nuna hasken Kristi ga wani wanda ka sani?.***

## GARKUWA MATSANCIYA

## Pakistan: Tahir Iqbal Da Raymond Lully

RANA TA 121

**Zanyi wa igiyar sumba amma kada ka taba yi mani musun bangaskiyata!, inji Tahir Iqbal. Sojojin suka daga gurgun pasto daga kekken guragu da yake bisa kai sai suka saka masa igiya bisa wuyansa. Yau zai yi yawonsa babu tsaro tare da Kristi a aljannah.**

*Banda wadannan kuwa ku dauki garkuwar bangaskiya wanda zaku iya kashe dukan kiban wutar mugun nan da ita.*

*Afisawa 6:16*

Wani kwararren pasto yayi harbin bindiga a kusa da gidansa a cikin kasar Pakistan. Harsashin ya kuskure shi ya huda bangon gini bayan kujera da yake zama a kai. Yayi godiya ga Allah domin bashi wannan rana da zai iya yin bisharar Kristi ga wannan kasa da musulmi suka fi rinjaye.

Rayuwan lully ya bar matsayi mai maiko a zamam Parfeso na Jami'ar Oxford kuma yayi anfani da yawancin rayuwarsa yana shan wahala domin yada bishara. Ya rubuta. " da ni mai abin hannuna ne kuma ina more jin dadin rayuwa yadda na ke so. Amma sai nayi murabus daga wadannan domin samun damar yada sanin gaskiya. Na sha shiga kurkuku, an shayi mani tsangwama yanzu, ko da shike na tsufa kuma bani da kome. Ban fidda rai ba, a shirye nake idan nufin Allah ne in yi jimiri har mutuwa".

Masu bi irin wadannan suna da fahimta ta musamman na abin da ake kira. "Garkuwa ta bangaskiya". Sun fahimci cewa ba lalle ne ya hana shan wahalar su ba, amma yana basu karfin zuciya su fuskanci haka din in ta dauro. Garkuwa bangaskiya ta basu yanke shawarar cewa babu ja-da-baya wajen yi wa ruhaniyar Kristi yaki ko ta halin kaka a nan duniya.

***A zaman karni na farko kayan yaki da ake anfani da su sune garkuwa a hannu daya da takobi kuma a daya hannun. Daya,na kaiwa abokin gaba harine da takobi kuma a daya hannun. Daya, na kaiwa abokin gaba harine na kariya. Game da namu kayan yaki irin na ruhaniyya a yau, shin zamu sami "garkuwar bangaskiya" cike da kura ? Wacce aka ajiye can awani lungu ? Duk yayin da muka fice daga karkashin tsaron da Allah yake bamu ta wurin garkuwar bangaskiya mukan zama da wuyar tsaro daga harin abokan gaba. Idan ba tare da bangaskiya ba babu yadda zamu iya kaucewa tsaro da razana. Daga samun hamayya sai kaga mun dena yada bishara. Me yake dakatar da kai daga yada bishara a kewayen da aka sanka? A ina kake so kayi anfani da garkuwarka ta bangaskiya ko da a tsakiyar yan'hamayya masu tsoratarwa ne?***

# MATSANANCIN ALHERI

## *Romania: Pasto Richard Wurmbrand*

RANA TA 122

**Pasto Wurmbrand ya ratsa sauran fursunoni ya kutsa har wajen wani pasto da yake zaune babu motsi akan dabe. Ba a jima ba da kawo shi cikin dakin kurkuku. Ya sha mummunar duka. Wurmbrand bai iya sanin ko zai rayu har safiya ba domin irin dukar da ya sha.**

*Ku tafiyar da al'amuran ku da hikima cikin zamanku da marasa bi, kuna matukar anfani da lokaci*

*Kol 4:5*

Tare da tausayi da kauna Pasto Wurmbrand ya durkusa a gafensa kuma ya tambayeshi, "Dan'uwana zaka iya fadar wannan addu'a. "Uba ka gafarta masu?"

Mutumin yayi kara ta ciwo, ya na taba kumburin dake fuskarsa, yin magana ma yanayi masa wuya. Kalmomin ma sai a hankali suke fitowa, "Bana iyawa"

Pasto Wurmbrand ya fara tausayawa mutumin sai ya fara magana kuma. Da hawaye a idanunsa yace, "Addu'a ta bata cewa a gafarcesu bane, Addu'a ta ita ce.... Uba ka gafarcesu harda ni, idan da ni pasto ne fiye da haka, watakila da masu azabtarwa da yawa sun tuba.

Wannan gajiyyen pasto don tsanannin shan duka ya furta damuwarsa domin akwai dama da ya rasa da juyo abokan gabansa ga Kristi. Sai pastocin duka biyu suka gane akwai wani saurayi dan kungiyar matasan kwaminis ta Romania wanda aka taba tsarewa kuma aka yiwa duka na rashin tausayi, wai kuma wani hafsan dan sanda Krista ne yayi dukan.

Wannan abu da ya faru dashi sai ya sa ya taurare zuciyarsa game da Kristi duk sauran rayuwansa. Wannan dama da aka rasa ta yin bishara shi yazo ya zama mai mulkin mallaka na kasar kwaminisanci ta Romania. Nicolai Ceausesai shine ke dahakin azabta Kristoci masu dinbin yawa har da Pasto Richard Wurmbrand da abokin kurkukunsa pasto da ya sha duka.

***Babu na'adamar da tafi takasa anfani da wata dama da ta samu. Amma haka rayuwa take. kamar halfuwar jariri da dai sauransu. Kasa yin anfani da wata dama da ta samu domin sauya rayuwar mutum ta kaddara. Ba zamu iya sanin irin abin da na zaune kusa da kai a cikin jirgin kasa zai iya domin Kristi a cikin duniya ba-kamata yayi dai mufurtabishara muce wani abu, haka kuma yana iya yiwuwa furucinmu ya juyo da hankalin mabiyin Kristi. Kana iya lissafta dama da suka subuce a baya. Amma kana iya gyaran na gaba ta wurin yin anfani da damar da ka samu a kowace rana domin shaida bangaskiyar ka.***

## KWALLAFARWA MAI TSANNANI

### *Kasar Sin: Liu Xiaobo*

RANA TA 123

*Ku sawa masu zagin ku albarka, masu wulakanta ku kuma, ku yi musu addu'a*

*Luka 6:28*

**Liu Xiaobo yana ta fushi a cikin dakinsa na kurkuku, baya tunanin kome sai irin zunuban da matsanantan Kwaminis ke aikatawa. A zamansa na shugaban zanga zanga da akayi a dandalin Tiananmen kasar Sin, addu'arsa ita ce a saki majami'ar kasar sin, addu'ar sa ita ce a saki Majimi'ar kasar Sin daga tsauraran dokokin gwamnati. Yayi hangen cewa shaidar kauna da jinkai na Allah da Krista sukeyi zai ci gaba da Kwaminisanci. Amma karshen abin baiyi kyauba.**

Daya bayan daya yayi ta ganin abokansa masu karfin zuciya suka tashi tsaye har zuwa mummunan karshe mai tashin hankali. Gashi kuma anbiyo sawayensa an kama shi. Ta kaka Allah zai bari irin wannan mugayen abubuwa su same su? kokarinsu bai haifar da abin da tunanisa na mutumtaka ke tsammanin zasu yi ba.

Daga nan ne karfafawa ta Allah ta zo masa ta hanyar wani Krista da ke kurkuku tare da shi. Bayan da sukayi hira sai ya gane zanuban sa, ya rubuta yace, "Ta kaka mutumin da bai san zancen zunubi ba zai taba jin muryar Allah? Maimakon a yi fada da kwaminis domin suna aikata abubuwan, zunubi. Lalle ne in kallafa raina ga juyosu zuwa ga Kristi, Koda haka din yana nufin mutuwa ta ce an buga wa Yesu kunsoshi a kan giciye domin kaunar da yake yiwa masu zanubi. Dole ne in kallafa raina ga kaunar yan kwaminis. Idan ko bahaka ba dukanmu zamu kare a karkashin tudun maimakon hawa zuwa kan-kolin bisa".

***Wasu mutane suna zaton da zarar mutum ya bada kansa ga kristi, rayuwa zatayi sauki. Suna iya zato cewa rayuwa zata bi yadda suke so. Tun da mai aikin Allah suke yi", haka ne? M eyasa al'amuran su ba zasu ci nasara ba? Ba da Jimawa ba kuwa sai ga damuwa ta zo. Tana iya yiwuya ma yi masu rauni a dalilin bangaskiyarsu. Yayin da muka zabi ayi lissafin mu a cikin wadanda suke Krista, mukan gane ko makiya nawane Kristi yake da su. Yesu ya yi alkawari cewa za'a kimu a dalilin sunansa. Yadda muka zabi mu maida murtani ga makiyanmu shine gwawdwarmu ta kamanta Kristi. Kana shirye ka kaunaci makiyanka ta wurin yin addu'a domin cetonsu? Zaka shaida masu bisharar Kristi? Idan mu bamu koya wa masu tsananta mana labarin Kristi ba shin wa zai yi?***

## BAMBAMCI MAI TSANANI

## *Russia: Claudia Vasilevna*

RANA TA 124

*Don ku zama marasa abin zargi, salihai, ya'yan Allah marasa aibu a zamanin mutane karkatattu, kangararru, wadanda kuke haskakawa a cikin su kamar fitilu a duniya.*

*Filib. 2:15*

**Wasu takardan sirri na yan sandan Asiri na Soviet sun nuna cewa a wata unguwar waje ta birnin moscow da ake kira Butovo an harbe mutane dubu arba'in da hudu a asirce, ta wurin tara mutane kamar dari biyu sa'annan a harbe kuma a tara a birne. Wani dare a lokacin wannan kisangilla, Claudia Vasilevna ta bude wa wata firgitaciyar mata kofa wacce take daya daga cikin krista da za'a harbe amma sai zakara ya bata sa'a, ta roki Claudia ta boyeta.**

Jin tsoro ya hana Claudia. Ta rufe kofarta ta bar matar a waje, Fiyeda shekaru hamsin Claudia tayi fama domin fuskar wannan mata ya fice daga tunaninta. Amma akasin fama da Claudia take yi na wannan lokaci yan ikkisiyar majami'a ta Romania suna da salama a zukatan su domin taimakawa da suke yi wa sojojin Jamus wadanda suka tsere akan hanyar su ta tafiya kurkuku. Sun nemi mafaka a cikin majami'ar Pasto Richard Wurmbrand, A karshen yakin duniya na biyu gwamnatin Nazi ta Jamus mai zafin mulki ita ce ta mallaki Romania. A lokacin da Jamusawa suka fara gazawa a yaki sai sojojin Russia suka mamaye kasar Romania suka fara kama sojojin Jamus a zaman fursonin yaki. Boyewa ko kuma taimakawa Jamusawa a wannan lokaci laifi ne kuma horon kisa ne akan irin wannan laifin.

Sojojin Jamus kuwa a wannan lokacin kamasu babu wuya domin suna saye da fufafin sojoji irin na amince da su taimakesu domin kuwa ba hakinsu ne su shar'anta su ba amma su taimaki kowane irin mutum da suka ga cewa yana cikin hadari. Sun koma mika hannunsu na taimako zuwa ga yayen Jamusawa a wannan lokaci, suna yi ne sanin cewa sune abin da Kristi zai yi a madadinsu.

***Galibi Krista suna da zabi tsakanin abin naunaya ga jikunansu da abin naunaya ga ruhinyarsu. Wannan shine banbanci tsakanin abin naunaya na duniya da madawamin bakinciki a sama.***

***Kristoci na gaske sukan yi rayuwa da yasha banban da na duniya a wani lokaci ma yakan yi wuya a ruwaita. Galibi al'amuransu sun cika tsanani. Ko a cikin al'amuranmu, muna iya fuskantar shawarwari da ke bukatar karfin zuciya kafin a yi su. Me zamu zaba samun tsaro na duniya tabbata ta har abada? Lokacinda ka fuskanci al'amarinda ke bukatar karfin zuciyar da tafi gaban iyawarka, ka roki taimako daga Allah. Zai baka basirar da kake bukatar, a lokacin da ya dace domin ka tsaida shawarar da ta dace.***

***Gama an bayar a gareshi a madadin Kristi ba wai kadai ku ɓada gaskiya a gareshi ba, amma kuma don ku sha wahala dominsa***

***Filibbiyawa 1:29***

## BULAGURO MATSANANTU

### Kasar Sin: Bob Fu

RANA TA 126

***Parfeso bob Fu dan kasar Sin tare da matarsa sukan koyarda Littafi Mai Tsarki a cikin kauyuka. Marmarin jin maganar Allah a wajen kauyawan a kullum mamaki ya ke bashi.***

*Ina jin kishinka ya Allah, ya Allah mai Rai yaushe zan tafi inyi sujada a gabanka?*

*Zabura 42:2*

Wata tafiya da ba'a mantawa ta fara ne da hawan wata motar safa, ta tafiyar sa'oi goma sha biyu wanda a cikine wani shugaban majami'a yake tsaye a gaban wata fasashiyar taga na tsawan lokaci yana tare ruwan sama don dai Fu ya sami hutawa dare na biyu, suka tuka karamar motas akan hanya mai gargadan gaske, da kuma shiga wuri mai tabo har motar ta kafe, daga nan sai suka tuka Tan-Tan na tsawon lokaci a cikin ruwan sama har saida Tan-Tan ta kafe. Daganan fa sai suka yi tattaki cikin dukan dare karkashin farin wata, tsantsi na kwasar su suna faduwa suna tashi a cikin tabo.

Sun sauka a kauyen washi gari kuma an yi musu maraba sosai. Kauyawa suka fara taruwa a majami'a domin suyi addu'a na sao'i biyu kafin a fara sujada. Wasu sun yi tafiyar mil hamsin da kafa don kawai su zo su yi maganar Allah. Babu kujeru a gidan, saboda haka mambobi suka zauna akan duwatsu da gumaguman itatuwa. Suna samun albarka a wannan yankin. Mawuyacin abu ne yan sanda su biyo su. Sun sami yancin sujada na yan kwanaki ba tare da tsangwamna ba.

Ko wannansu yaci nasara da matsanancin bulaguro domin su yi sujada, babu wani cikinsu da ya maida wannan wahala wani abu. Kawai su dai suna da bukata kamar Dauda, wanda yakan yi sujada da dukan karfin jijiyar jikinsa.

***Ga wandanda suke kasashe marasa yancin, zuwa majami'a ba zabi bane dole ya zama, akasin haka a kasashe masu yanci mutane dayawa sukan yi shawara ko suje majami'a, Kosuna da lokaci? Ko ana ruwan sama? Wai menene ma kan maganar wa'azin? Ko kunya babu mu kan yi tunani ma wai lallene ma na tafi sujadar Lahadi. Ga Dauda da wasu sujada ga Allah tilas ne. Alhalima bazasu bar kome ba ya shiga tsakaninsu da sujada ba. Yaushe ka taba rokon Allah ya baka marmarin yin sujada haka? Ka roke shi yau, kuma kayi shirin zuwa majami'a a wannan makon kayi wa Allah sujada.***

# MATSANANCIN MAWALLAFA

## Russia: Nicolaie Moldovae

RANA TA 127

***Bugaggun masu tsaro yan Russia suka shiga dakin kurkuku da rana tsaka a lokacin hunturun kankara. Wani fursuna Nicolaie Maldovae, mawaki kuma mawallafi. Mai bi kuma shugaban kungiyar bishara ta majami'ar Orthodox. An bashi daurin shekaru biyar a cikin mugun kurkukun Russia domin laifin yin aikin bishara.***

*Ku kasa kunnenku yaku sarakuna, ku lura yaku hakimai, zan raira waka inyi kida ga Ubangiji Allah na isra'ila.*

*Alkalawa 5:3*

"Kayi rub-da-ciki, wani mai tsaro yayiwa Nicolac tsawa, saye da guntuwar riga kuma fale-fale da ita da kuma gajeren wando, sai ya kwanta akan dabė mai sanyin daskerawa, sai masu tsaron nan suka hau gadon bayansa da takalman kan- kura har na tsawon sa'a guda.

Bayan da suka fita, sauran fursonin suka durkursa a gefensa su ga irin tsananin raunin da ya ji.

Sai suka yi mamakin jin abin da ya fada masu, cewa ya wallafa wata waka a lokacin da suke tattake shi. Sai ya jera waka. Maganata ba ta samaniyar gaba kadai ba amma bari na sami samaniya da buki mai tsarki anan".

Bayan an sallami Nicolaire daga kurkuku, Yan sandan kwaminis sun binciki gidansa kuma suka kwace wani muhimmin litaffi na rubutun hannu wanda Nicolaire yayi shekaru yana aiki akai. Ayyuka darubuce-rubuce da ya dauke daruruwa sa'oi yana yi. Bayan wannan sai nicolac ya sake wallafa wata waka,"Ina yi maka sujadaada da godiya domin dukan baye bayenka a gareni, amma kuma domin dukkan kaunatattun abubuwa da ka dauke daga gareni. Ka kanyi dukkan abubuwanka a daidai, kuma zan amince da kai. A yau ana moriyar wakokin Nicolac Moldovac ko'ina a kasarsa.

***Masu iya magana sukace "Kashi goma cikin dari na rayuwa na gudanar abubuwane, kashi tasa'in kuwa na maida murtani ne ga abubuwa da suka gudana". Sabili da haka, ainihin al'amuran rayuwa basu zama wajibi kamar halin mutum game da su ba.***

***Wadansu halaye da ake shiga sunfi karfin ikon mutum. Amma hali ko maida murtani zabi ne. Rayuwa yana iya zuwa a hargitse amma da taimakon Allah zamu iya zabin mu yi natsuwa domin shirya rayuwa da ya zo a hargitse. Kaka zaka yi bayanin irin halinda rayuwarka ke ciki? Me kake ciki game da matsayinka? Me kake so kayi don canja muryar ka?***

# MATSANANCIN TA'ADDANCI

## *Alexandria: John Mark*

RANA TA 128

*Gama kokuwarmu ba da nama da jini ta ke ba, amma da mulkoki, da ikoki da mahukumantan wannan zamani mai dufu, da rundunai masu ruhaniya na mugunta chikin sammai.*

*Ephesians 6:12*

**Bayan rubuta Bishara daga hannun Markus, Yohana Markus yayi tafiya ta watsa bisharar bangaskiya a cikin kasashen Africa harma da Misra, a karshe sai yayi matsuguninsa kuma ya tare a Alexandria ya kafa majami'a a wurin.**

A ranar 21 ga watan Afrilu na shekara ta 64 A.D. Markus yayi wa'azin bishara akan tunawa da azaba da kuma mutuwar Kristi wanda a yau muna kiran wannan (Easter Sunday). Ya sami rashin jituwa da fristocin duhu na wannan kewaye, sai suka yi anfani da wannan rana domin zuga jama'a su tasan masa.

Yan tawayen suka tasamma majami'ar kuma suka cabke Yohana Markus. Suka jawoshi daga cikin taron jama'a ta wurin yin amfani da kugiya da igiya zuwa titi suka kaishi bayan birni. Akan turbar da aka ja shi kuwa ga alamun jini da kuma inda duwatsu suka kakkarta naman jikinsa a yayin da ake jansa da igiyar kusa dukan ko ina a jikinsa ya raunana, taron yan iska kuwa sai ba'a suke yi masa. Da furucinsa na karshe, ya mika ransa ga mai cetonsa ya mutu.

Ko da shike markus ya riga ya mutu amma yan iskan basu koshi da muguwar aniyar su ba, sai firistocin suka ba da umarni a kona gawar maimakon binnewa. Ba tare da zato ba kuwa sai ga gugawa ta taso ta tarwatar dukan mutane ko ina gawar Markus kuwa aka barta anan wurin da ya mutu. Sai wasu Krista suka zo suka yi mata jana'iza bisa kai dai.

***Yesu bai taba shugabanta sojojin zuwa yaki ba, bai taba anfani da kalmomin yaki ba bai taba zuga don ayi tawaye ba kuma dai bai taba anfani da kalmomin yaki ba , amma duk da haka mabiyansa kullum a cikin kai musu hari ake don tsananin kiyayya da gaba. Sakon Yesu, sakone na kauna salama da sulhu, duk da haka jama'a da ma'aikatan gwamnati suna hana yin bishara tamfar wani shirin yaki ne. A halin gaskiya ma dai muna cikin yaki ne-watau Mai cetonmu gaba da Shaidan ne ake wannan yaki na ruhaniya. Shi mugun zaiyi dukkan kokari na watsi da mulkin sama ta wur kawo mummunan karshe ga Kristanci. A karshen wann yaki shin a wana gefe za'a taras da kai?***

## ALHERI MATSANANCI
## Romania: Bayahudiya Mai Son Gafartawa

RANA TA 129

**Wani pasto dan Romania tare da matarsa sun boye sojojin Soviet a zamanin da Nazi suka mamaye kasarsu.**

**A yanzu kuwa su sojojin Nazi ke da bukatar mafaka.**

*Ko kuyi hidimarku da zuciya daya kamar kuna bauta wa ubanjigi ba mutane ba.*

*Afisawa 6:7*

Hafsosin soja guda uku ne suka boye a cikin wani karamin gini a bayan gidansu. Matar pasto takan saci jiki takai musu abinci kuma ta tsabtace mazubin sharar su da dare. A zaman ta na bayahudiya tana yin kiyayya da ayyukansu  sun kashe daukan iyalinta. Amma a zamanta na Krista, ta san lallene ta taimaki yan gudun hijira ta basu taimako na jiki da jini dakuma na ruhaniya.

Nuna irin wannan alheri mai yawa yasa kaftin din da ke cikinsu ya shiga yin mamaki kuma yana neman sanin asalin yin abubuwan kirkin nan yace, "Ina mamakin dalilin da zai sa Bayahudiya tayi kasadar rayuwarta domin soja dan Jamus? Ni bana kaunar yahudawa kuma bana tsoron Allah.

"Ina gaya maki cewa a lokacinda rundunar Jamus ta sake kwace Bucharest, wanda kuma lalle ne zai faru, bazan taba yarda na maida maki wannan alheri da kika yi ba.

Wannan daskararren zuciya tasa bai sa matar Pasto ta karai ba. Ta cigaba dayi masa bishara, "Har laifuka mafiya muni ma ana gafartasu tare da bangasiya a cikin Yesu Kristi. Ni bani da ikon gafartawa, amma Yesu yana dashi, idan ka tuba".

Hafsan ya amsa mata yace, "Bazan iya cewa na fahimceki ba. Amma watakila idan mutane suna da irin wannan baiwa ta rama mugunta da alheri, to kisan rayuka zai yi sauki".

Ba da jimawa ba wadannan hafsoshi suka sami tserewa zuwa Jamus, har a wannan lokacin ba tare da sun tuba ba. Amma da pasto da matarsa sun yi musu aiki ta wajen nuna musu ainihin ma'anar kristanci.

***Yesu hayi misali da wani manomi da ya shuka irin gona mai kasa dabam dabam. A wannan labarin irin yana nufin maganar Allah. Kamar tsuntsayen da suka cinye irin da suka zube a gefen gona, irin Shaidan yana so ya dauke maganar Allah daga wadanda suka ji. Akasin haka kuwa wadanda suka zama misalin kasa mai kyau sune wadanda suka bi maganar Allah kuma suka karba. A duk lokacinda mu ke yin bishara ga wasu, bama iya sanin ko wace irin kasace ke a cikin zuciyar su ba.***

***Ba mu ke da hakin irin amsar da zasu bayar ba, ko da I ne ko a'a. ka sami damuwa ne don wani bai amsa maka ba. ka rigaya ka yi naka aiki. Bari Allah kuma yayi nasa.***

# WA'AZI MATSANANCI

## *Romania: Pasto Richard Wurmbrand*

RANA TA 130

*A nufinku mugunta ce kuka yi mini, amma Allah ya maishe ta alheri, don a rayar da jama'a masu yawa wadanda suke da rai a yanzu*

*Farawa 50:20*

**A shekarar 1991 Gwamnatin Romania ta kwaminisanci ta sauya sabuwar fuska. Bisa tsoron tawaye daga yan kasar da suke kiyayya daga ayyukansu. Sai suka roki pastocin Romania Suyi wa'azin su ba tare da tsangwama ba, ko da wurare ne na hukuma. Amma fa sun umurci pastocin da suyi wa'azi akan wani takamammen sako-kayi kaunar makiyin ka wayon ke nan wai don mutane su gafarta musu ta'asa da suka yi wa jama'a Gwamnati na zaton zasu iya anfani da bisharar Kristi ta hanyar wayo don cinma burinsu.**

Krista kuwa sukayi maraba da haka suka shiga yin bishara haikan, ko da shike sun sani cewa wannan shawara ta Gwamnati dabara ce domin kokarin tsare kanta. Amma wadanda sukayi tunani. "Me zai sa mu koya wa wadanda ake kuntatawa su kaunachi masu kuntata musu?" Sai suka lura wannan sako na gafartawa zai karfafa Gwamnatin.

Ana cikin wannan yanayi ne Pasto Richard Wurmbrand ya dawo Romania bayan gudun hijira na shekaru ashirin da biyar. Aka gayyaceshi yayi wa'azi a gidan talabijin na Romania, inda ya jaddada sakon "Kaunar makiya". Majami'a ta daure kanta da wannan kalma kauna, Domin kawai itace kauna sai ta bada kanta ga dukan kasada-harma kasadar yiwuwa ayi anfani da ita ta hanyar mugunta domin a sha kan kowa. Ba zamu taba dakartada koyarda kaunar makiya ba, ko da dan lokaci ne, Allah yana kiyayya da cin ribar ta cutar da mu. Mun gaskanta cewa maganar ita ce Allah kuma a karshe wannan kalma zata sauya zukata harda na wadanda suke kiyayya da Allah".

***Littafi Mai Tsarki na cike da labaru da suke karewa da bam mamaki... har zuwa karshen sura a lokacin da ake gani kamar mugune kecin galaba kuma sauran al'amuran ka ga kamar suna gaba da wadanda suke tsayayyu. Sai Allah ya kawo tsayayyu ga nasara. Sa'ar abin shine Allah ne mahalacin mu maibi da rayuarmu kuma.***

***Mai yiwuwa muyi kamar ba'a isasshen anfani da mu domin aikin Allah. Muna iya jin cewa kokarin bishara da mukeyi ma. Wadansu suna batawa. Amma mu aikin mu shine muyi amincin yin bishararsa, mu bar masa kalubale da akeyi mana garin yin bishara. Akullum Allah yananan yana bada labarin bishara ta wurinmu kuma a kullum mafi alheri yake bamu.***

# MATSANANCI TUNI

## Tibet: William Simpson

RANA TA 131

"An kashe danka"

*Na kan yi wa Allah na godiya a duk lokacin da na tuna da kai*

*Filib 1:3*

Mallam Simpson ya sami wannan sakon a ranan nan. Dansa mai wa'azi William, ya gina wata karamar makaranta a bakin iyakar Kasar Tibet inda yake koyawa yara maganar Allah. Mahaifin William yana da zama kusa da wurin, nan da nan kuwa ya ruga zuwa wurin da jin labarin abinda ya faru. Da ya duba kewaye da wurin sai mambobin kungiyarsa suka fado masa a rai.

William yayi tafiyar Mil dubu hudu akan doki domin yazo ya shaida bishara ga mutanen Tibet. Musulmi masu taurin ra'ayi sun kashe mutane dubu hamsin a birnin Tibet, amma duk da haka wannan bai tsoratar da dansa ba.

William ya rubuta. "Dukkan jarabobi, kadaici, damuwa, ciwo, sanyi da gajiya na wannan dogon hanya, Karfafawa da dukan bakinciki, jarabta da gwadawa basu isa a kwatanta su da daraja da farinciki na shaidar bisharar Allah mai farinciki.

Mahaifin william yayi tattaki ya wuce ta inda aka rusa makarantar har ya taras da gawan yaronsa kacakaca a kasa. Daga baya ya samu labarin cewa wasu sojojin musulmi ne suka yi aika aikar ga nuna rashin tausayi ga mai makarantar. A zaman bishara shi kansa Mallam Simpson yana alfahri da misali irin na Yesu da William ya zama ga sauran jama'a. A karkashin gawar dansa akwai wata yar takarda jike da jininsa ya zaro ta a hankali ya karanta abin da ke ciki "Domin tunawa dani".

***Alamu na tunawa da mutane suna nan ko'ina a duniya kowanne ya nufin tunawa da wata bajinta gwaninta da saudaukar da kai da shiga jarabobi.***

***Mutane daga kowane kar nuna tarihi sun kafa ko gina abin tunawada wasu. Haka rayuwa ya take. Bama so mu manta da wadanda suka sadakarda rayukan su garin tsare manufofin mu da yancinmu na dan adam da kauna da adalchi da sauransu.***

***Zukatanmu cike suke da tunawa da shahidan Krista wadanda suka mutu sabili da Kristi da, bisharasa kuma. Ba a bada girma ko daukaka irin ta soja a wajen jana'izarsu, babu batun gina mutum-mutumi domin su. Amma duk da haka muna karanta labarinsu kuma mu rike ba tare da mun manta ba. Dauki lokaci domin tunawa da su yau, Kuma ya yabi Allah da ya basu karfin zuciyar yin haka.***

***Idan zaku iya nuna mana cewa kune majami'ar Kristi ta gaskiya, zamu juyo zuwa gefenku da gaggawa domin bukatarmu ita ce mu wanzu tare da Kristi. Amma baku zo da hujja ta tabattar da gaskiya ba. Kun jefa mu a kurkuku, kuna iya daukan rayukanmu amma ba bangaskiyar mu ba.***

**Bishop John Balan- Ya maida murtani ba shugaban Yan kwaminis wadanda sukayi kokarin su rinjaye shi yayi mubaya'a ga (orthodox) majami'a mai tsaurin ra'ayi ta Romania.**

## MATSANANCIYAR ALAMA

### *Cuba: Tom White*

RANA TA 133

**Ga wadanda suka sha wahala a kurkuku a dalilin bangaskiyarsu cikin Kristi. Ci da shan jibin Ubangiji al'adace mai daraja; amma ba kasafai ake rabuwa a idanun masu tsaro ba.**

*Sai ya dauki gurasa yayi godiya ga Allah, ya gutsuttsura, ya basu yace, wannan jiki na ne da za'a bayar domin ku, ku rika yin haka domin tunawa dani.*

*Luka 22:19*

Tom White da wani mutukin jirgin sama mai suna Mel suna ratsa sararin samaniyar kasar kwaminis ta Cuba a cikin karamin jirgin sama, suna zubo dubban takardun bishara zuwa ga mutane, dake cikin tsanin mulkin malaka ta Fidel Castro. A cikin yin haka suka shiga cikin mummunan yanayi da ya tilatsa su yin saukar gaggawa. Ko da shike ba'a ji wa Tom da Mel rauni ba, amma sun sauka a cikin kasar Cuba, kuma masu tsaro na kwaminis suna yi lodin bindigarsu suna jira. Da Tom da Mel sun samu daurin shekaru ashirin da hudu a kurkuku.

An baiwa Tom dama matarsa ta ziyarce shi sau biyu, Ofelia wacce take da wata niyya ta kanta. Ta shigo da wani karamin pakiti na hodar lemu da ake sha in an zuba ruwa a boye a cikin wani leda daure da igiyar roba. Tom ya kai cikin dakin kurkuku suyi anfani dashi don cin jibi tare da sauran Krista da suke kurkuku a lokacin da masu tsaro ba zasu sani ba.

Da Tom da Ofelia matarsa sun fahimci abu guda. Tunawa da Yesu Kristi da zubar da jini da yayi akan giciye wanda shine alama mafi iko da yake rike da aurensu da kuma manufar su ta yada bishara babu sausauci, Da Tom da Mel sun sami saki bayan shekara daya da rabi. A yau Tom da Olefia sun cigaba da yada bishara ta bada kai da Yesu yayi domin su a Oklahoma, inda Tom yake shugaban da kungiyar Muryar Shahidai.

***Kristi ya umurci almajiransa da suyi bukin al'adun guda biyu, Baptisma da Cin-Jibi. Su alamu ne na sujada a gareshi Tuni ne na mutuwarsa da tashinsa. Ko da shike dukansu al'adu ne na Krista amma bai kamata su zama al'adu kurum ba. Mai yiwuwa ba zamu iya ganewa masu bi da suke daukar kasadar rayuwarsu domin tunawa da cin jibin Ubanjinmu ba domin wannan al'ada bata zama abin kasada a al'adun mu na gargajiya ba. Amma su da ake azabtasu domin immaninsu suna shirya matsayinsu bisa ga yadda suka sami kansu, alamun nan suka zama da daraja. Me alamun baptisma da na Cin- Jibi yake nufi a gareka? Takaka zaka yi ka kawata nuna farincikin ka a game da baptisma da kuma hada kai wajen cin jibi?.***

## Romania:

RANA TA 134

**A cikin kurkukun Geria, ta Romania akan dauki sunayen fursunoni da suke karya dokoki, kuma akan yi musu bulala ashirin da biyar. Akan kebe rana ta musamman domin yin wannan horo.**

**A wannan ranar hafsan zai bi daki daki yana tara wadanda za'a yiwa horon.**

*Ba wanda ya ke da kamna wadda ta fi gaban wannan, mutum shi bada ransa domin abokansa.*

*Yahaya 15:13*

Tunda gandurobi sukan canja lokaci akai akai kuma fursunoni sun yi yawa, yana da wuya asan dukan fursunoni acikin saukin sanin sunaye.

Sai wani fursunan Krista ya fito yace, "Nine shi dukan lokacinda mai tsaro ya biyo dakinsa, sai ayi ta dukansa akai akai a maimakon sauran fursunoni.

A karshe a lokacin da wannan Krista ya kusa mutuwa don shan duka, sai sauran fursoni suka kokarin karfafa shi suka che masa "Danuwa kada ka damu, ka kusa hutawa zaka tafi sama, Jim kadan ba zaka kara jin zafi ba, sai farinciki".

Sai ya juya ya dube su da kauna yace, bari Allah yayi mani yadda yake so amma idan da zai tambaye ni, zan ce kada ka kai ni aljanna zan fi son a barni a nan cikin kurkuku. Gama na sani cewa a aljanna akwai farinciki mara misaltuwa, amma akwai abinda aka rasa a sama, "Bada kai don wani".

***A irin wannan duniya tamu ta yanzu inda aka fi ba hoarding daraja maimaka taimakon juna akan ga ka'idar bada kai irin ta Littaffi Mai Tsarki tamfar sabon tunani ne". Ka mallaki iya abin da zaka iya mallaka, kuma cikin gaggawa," shine ake yayi idan an zo batun abubuwan duniya. Littafi Mai Tsarki na koya mana wata hanya ta cin nasara. Ana kiranta sadakar da kai- watau yin kasadar rayuwarka domin wani. Wannan irin hada kai ba kasai ake yinshi ba. Ba abu ne mai armishin da za'ayi marmari ba. Amma da zarar mun kokarta sai ya zama hanyar rayuwa. Ruhun Allah mai tsarki dake cikin mu na taimakon mu mu tagaza wa wasu. Alhali ma dai ruhunsa yana taimakon kara mana son yin haka. Kana shirye ka ga cewa an biya bukatun wasu kafin naka?***

# MATSANANCIAR ALMARA

## Isra'ila Labarin Gorun

RANA TA 135

**A cikin wata tsohuwar al'mara. Yesu ya ce wa wani mai binsa da ake kira Gorum "Ka tafi ka kafa tanti akan Dutsen Carmel, kuma ya dakata a can domin yin sujada da addua. "Gorun yayi biyayya da umarnin Yesu.**

***Ku kula da kanku kada zuciyar ku ta zama da yawan shaye-shaye da buguwa, da kuma taraddadin wannan duniya har ba shiri rana mamaye ku kamar tarko***

***Luka 21:34***

Wata rana Gorum ya tafi wani kauye mafi kusa da su ya tambaya, "Ina rokon a bani bargo. Beraye sun cinye nawa, kuma ga shi bana iya barci. "Kauyawan suka bashi bargo da farinciki, amma Gorun yayi ta dawowa akai akai yana neman bargo don kamar da beraye sun tautaune bargon. A karshe wani ya bada shawara, zamu baka kyanwa domin a magance damuwar gaba daya.

Bayan yan kwanaki kuwa sai ga Gorun ya dawo. "Ko zaku iya bani madara domin kyanwata? "Da yake sun gane wannan damuwar ma zata matsa masu, sai mutanen kauyen suka yi shawarar ba shi saniya.

Gorun ya sake dawowa yace, "Ina bukatar abin da zan ba wa saniya taci. Suka bashi fuloti. Gorun ya tambaye su ma'aikata da kuma kayan aiki domin ginawa ma'aikatan gidaje da sauransu.

Bayan wasu shekaru, Yesu ya koma domin ya ga kaunataccen almajirinsa. Wani mutum mai kiba ya gaisheshi kuma ya tambaya, "Aikin me ya kawo ka nan? Me kake so ka saya"? Gorun yanzu dan kasuwa mai arziki, bai ma iya ganewa da maigidansa yake magana ba.

Krista sukan bada irin wadannan labaru a kasashe marasa yanci inda hukumomiin gwamnati sukan jarabci Krista ta hanyar jan hankali domin su yi musun imaninsu da kuma ayukan bishara wai don a ba su ayyuka masu daraja da biya mai tsoka.

***Wani lokaci mukan bukaci yin anfani da labari domin mu ga hasken abin da muke nufi, domin yayi mana tunin abin da yake muhimmi kuma ya falkad da mu ga sanin alkiblar mu. Ba lalle ne a bamu kyanwa ko saniyaba, amma makiyan mu sukan jarabcemu ta wasu hanyoyi domin mu kauche daga hanya. Yakan bamu tsaro a cikin kasashenmu don kada mu yarda da zuwa bishara a wasu kasashe. Zai iya anfani da albarkatun da Allah yake yi mana domin jan hankalinmu- aboki iyaii ko aiki kullum babu lokaci domin bishara. Menene wannen labari ya nuna a rayuwarka game da ja da da baya daga Maicetonka? Aikin duniya yayi maka yawa ne har yasa ka watsar da manufarka ta ruhaniya?***

# LOKACI MAI TSANANI

RANA TA 136

*Ka koya mana mu sani ran muna dan lokaci ne domin mu zama masu hikima.*

*Zabura 90:12*

***Wani mutum ya kama hanyar tafiya zuwa wani gari mai dan tazara a cikin dare sai yayi tuntube da wani abu a kan hanyarsa. Ya sunkuya ya dauki dan karamin jaka cike da duwatsu. Ya waiga kowane gefe cikin duhun dare, wai ko zai hangi wani don ya bar abin da ya daukan da tunanin ko wanine ya ajiye. Da yake baiga kowa ba sai yaci gaba da tafiyarsa da jakar kan dogon hanyar sa a cikin duhu ko farin wata ma babu.***

Domin samun abin yi, sai ya fara jefa duwatsun a ruwa cikin wani kogi da ya bi gefen hanya sai kaji tsundum... tsundum ... karar nutsewar duwatsun na bashi sha'awa, kuma yin haka yana rage masa jin doguwar tafiya. A lokacinda ya isa masaukinsa duwatsun sun rage guda biyu kacal a cikin jakar. Yana shiga gari sai ya matsa kusa da fitila kusa da dandali, rike da su a tafin hannunsa, ya duba walkiya ya kara dubawa kurkusa sai mamaki ya kwache ya razana, domin aske duwatsun lu'u lu'u ne!

Wani fursuna pasto mai hikima wanda yayi aiki tukuru na kawo fursuna da yawa ga Kristi shine ya bada wannan labari. Ya koya ta wurin shan wahala cewa ana iya anfani da kowane minti domin ciyarda mulkin Allah gaba gaba kome wuyar yin haka. Galibi yakan yi mana gargadi.

Kana iya sake samun kudin da ka rasa amma baka iya maida lokaci da ka bata baka yo anfani da shi ba. kayo anfani da lokacin ka cikin hikima domin aikin Allah".

***Akwai dakika miliyan dari da talatin da biyu a cikin kowane shekara, kuma kowane dakika da muka yi a cikin rayuwarmu kyauta ce mai tamani daga Allah domin muyi anfani da shi don cika nufinsa. Idan muka barnatadda su a banza, zasu koma ga Allah, amma bazasu koma wurinmu ba. sun tafi kenen har'abada, kamar wadannan lu'u da aka jefar cikin kogi. Yesu har a lokacinda ake giciye shi, ya bada ceto har a lokacinda yake bakin mutuwa ga dan fashi kuma yana yin kalmomin gafartawa. Kayi tunanin irin darajar da wannan lokaci yake ga wannan barawon wanda yake tare da Yesu a sama a wannan ranar. Shin kana anfani da lokacin ka mai daraja da manufar mai kyau? Ka roki Allah ya nuna maka yadda zaka fanshi lokacinka ba ka bata a banza ba.***

# MATSANANTUN KASADA

## *Kasar Sin: Maginan Majami'a Guda Biyu*

RANA TA 137

**Matannan guda biyu sukan yi tafiya mako bayan mako domin yin sujada a boye. Rashin kafa majami'a a kauyensu ya dame su ya dame su kuma sun gaji da tafiya wani guri domin yin sujada a boye.**

***Labudda duk masu ni'yyar zama na tsakarka suna na Almasihu Yesu za su sha tsanani***

***2 Timoti 3:12***

Bayan sun dauki wattani suna yin addua domin a sami kafa majami'a a kewayensu, sai daya daga cikin matan tace, "Watakila Allah yana jira ne mu gina majami'a in ko haka ne don me zai saurari kukan mu idan bamu da niyar yin wani abu akai da kanmu".

Saboda haka sai suka yi shawarar daukar kasada. Matan nan biyu da mazansu suka gina majami'a a karamin kauyensu na lardin Anhui ta kasar Sin. Nan da nan gwamnati tayi barazanar rushe ginin sai dai in sun shiga da neman izini na sa sunansu a cikin ma'ikatar lura da addinai. Sun bi wannan umarni kuma suka yi sa'a cewa ba a cika binciken lardinsu kamar yadda ake yi'wa manyan manyan majami'un birni ba. Har sukan yi kuru su gayyato wasu pastoci-daga kananan majami'u suzo suyi bishara ba tare da neman izini ba,

Mata sukan yi bishara ta wurin ziyartar asibitoci su nemi marasa lafiya da ke da alamar rashin begen farfadawa daga ciwonsu. Sai su yi addu'a su roki Allah ya warkar da su. A cikin shekara gu da wannan majami'a ta girma har mambobi sun kai guda dari biyu.

Daya daga cikin matan tace, "Munyi addua domin wani mutum na kwana ashirin a mike, kuma bai samu warkewa ba har zuwa karshe. Iyalan sa kuwa suka fara barazana suna tsorata mu, suna cewa muna fusatarda allolinsu. Lalle ne mu dauki kasada domin aikin Allah.

***Bisharar Yesu Kristi sassauka a kuma saurari. Me ya sa kuwa ibilis ya kebe Kristanci a zaman addini na farko a kasashe marasa yanci.***

***Masana masu tsokaci na zamani basa jin tsoro na rayuwansu a kasashe masu tsanantawa. Karfin iko bisa makiyi da Kristanci ya ke da shi a duniya shi ya kawo kyashi da kiyyaya ga addinin. Shaidan baya bata lokacin sa a kan addinai na karya. Shin ruhaniyarka imaninka yana razana shi? Idan haka, ne kada kayi mamaki da ake yi maku kiyyaya. Amma kayi murna don kana gefen gaskiya.***

## MATSANANTUN KAUNA

### Romania: Krista Yahudawa

RANA TA 138

***A karshen yakin duniya na biyu, sojojin Jamus sun sani cewar yan Soviet zasu kaisu sansanin bauta a Siberia kuma yawacin su zasu mutu a can. Sojojin Soviet ba su jima da kwace birnin daga hannun Nazi ba, saboda haka a lokacin da sojojin nan guda biyu suka sami dama, sai suka gudu daga sauran. Suka yi ta tafiya a tsorace cikin duhun titunan Bucharest ta Romania.***

*Amma ku yi kamnar magabtan ku yi masu nagarta, ku bada ramche, kada ku fidda zuciya dadai; ladarku kwa mai-girma che, za ku zama yayan madaukaki, gama shi mai alheri ne ga marasa godiya da miyagu.*

*Luka 6:35*

A lokacinda suka hangi majami'ar Lutherari suka dimauta, domin yan Lutheran na Romania galibinsu zuriyar Jamusawa ne. Amma a yayinda suka gane cewa mutanen ciki yahudawa ne, sai suka kara tsorata.

Nan da nan Paston ya kwantadda hankalinsu "Mu yahudawane amma kuma Krista ne, ba zamu bashe ku da kuke nemen mafaka ba, ba ma bada mutane a hannun makiyansu ba".

A wannan lokaci, idan aka kama wani dan Romania yana boye da ba-Jamuse za'a kashesu nan take. Amma ga wannan pasto mai tausayi, Jamusawan nan da ke saye da kayan sojojin Nazi rayuka ne batattu da ke neman mai ceto. Zai taimakesu kamar yadda ya taimaki yahudawa da suke tsanani.

Ya fadi masu mun wahala kwarai da gaske a karkashin mulkin mallaka ta Jamus. Ko da naka laifin a cikin ko babu, mu ba masu sharanta ku bane. Muna marantar ku a gidan mu, kuma muna mika muku farin kaya domin ku sami damar tafiya Jamus. Muna yin haka don mu nuna muku kaunar Allah da jinkansa a gareku. Shi kadai ne zai iya yantar daku daga laifofinku".

***Kauna takan sa mutane suyi abubuwan mamaki. Mace da namiji da suke cikin kaunar juna suna iya jure abubuwa da yawa don su nuna wa juna soyayya ta aihini haka kuma uwa ke kaunar da fiye da kome a duniya. Fiye da haka kaunar da ke tsakanin Kristi da maibinsa ba wai kawai a tsakaninsu kadai take ba, ita ce kauna mafi ban mamaki, domin ba ta rayuwa cikin kadaici. Alhalima ita ce kauna mai dagantaka da ke girma da habaka ta wurin wanzuwa da wasu dole ne mu kaunaci wasu da kauna irin ta Kristi domin mu iya kaunar wadand basu iya kaunar mu ba. Wanene Allah yake tambayar ka cewa ka kaunace shi a yau?***

*Allah ba zai shar'anta mu bisa ga irin yawan juriyar da muke yi ba, amma da irin yawan kauna da muke dashi Masu bi da suka sha azaba domin imanin su a cikin kurkuku sun nuna kauna.*

*Ni shaida ne cewa sun kaunaci Allah da mutane kuma.*

*Paston majami'ar karkashin kasa na da wanda aka tsare don ban-gaskiyarsa.*

## MATSANANTUN JARUMI

### *Russia: Vania Moiseev*

RANA TA 140

***A zaman sa na sojan Soviet, Vania Moiseev ya kan sami gargadi akai akai domin yada bisharar ta imaninsa. Mutane da yawa na rundunarsa sun karbi Kristi ta wurin shaidarsa. A lokacin da kwamandansa ya umurce shi da yayi shiri game da imaninsa sai yace, "Me tsuntsuwar kanari zata yi idan aka umurceta da ta daina waka? Ba zata iya ba, haka nima".***

*Kada ku daina yi wa baki alheri, gama ta haka ne wadansu suka sauki mala'iku ba da sani ba*

*Ibran 13:12*

Duk wanda ya san Vania yace bangaskiyar sa kamar maganadisu take. Ba da jimawa ba kuwa aka tsare shi aka shiga azabtaddashi. Sai ya rubuta wa uwarsa cewa "Na sani mai yi'wuwa ba zamu sake ganin juna kuma ba, amma kada kiyi kuka domina. Mala'ika yana nuna mani Urshalima ta samaniya, tana ko da kyau da gaske. Ina rokonki kiyi iya kokarinki uwata domin ma sadu a can".

Yaci gaba da tabbatar mata cewa Allah yana karfafa shi ta wurin aiko mala'iku zuwa inda yake. Yayi bayanin irin wannan saduwa da yayi da mala'iku.

Mala'iku kamar madubin taga suke, idan daya na tsaye a gabanka kuma da mutum a bayansa idanunka zasu iya zarcewa ta jikinsa ka ga abinda ke bayansa, nafi ganinsa sosai ma idan aka yi haka din.

Idan ka sami damar gani ta jikin mala'ika nanne ma zaka fi fahimta har ka gamsar ma da mai azabtarwa.

A karshe dai sai aka kashe Vania don bangaskiyarsa yana dan shekaru ashirin da daya. Shi wani saurayin shahidi ne wanda karfin zucitarsa ta rayuwa ta taimake shi zama jarumi sananne a cikin dukan kasashen gabashin Turai.

***Malai'ku suna ko'ina. Kamanninsu yana cikin litattafai, akan siffar ta su a jikin madaukin kandir, ana rataya a gidaje a zaman kayan ado na Krismeti da makamantan su.***

***Mutane da yawa suna bakin cikin cewa ba su taba ganin mala'ika ba-Jaruman yan aike na Allah. Duk da haka ba ma yin la'akkari da mala'iku. Mai yiwuwa wani dan taliki da ke da bukatar karbuwa a garemu ya zama mala'ika ne. Mai yiwuwa abokin gaba da yake horon mu shine mala'ikan nan da muke marmarin gani. Ko ma da an gane cewa wannan dan adam ne zahiri, kaunar da muka nuna wa mutumin zai zama mataki ne na alheri. Kamar damuka nunawa mutumin zai zama mataki ne na alheri. Kamar Vania shin kana duban rayuwarka ta wurin samaniya? Kana neman wurinda da mala'ikun da in da da ka ga magabcin ka kawai? Ko ka nemi wanda za ka kaunache shi tamfar mala'ika a yau.***

# KALACHI MASU TSANANI

## *Gabashin Turai: Mai Jin Yunwa*

RANA TA 141

***Krista da aka tsare a kurkuku yana jin yunwa da zafin rai. Karamin hafsa ya sake zuwa domin ya yi masa tambayoyi. Sai yayi tunanai "Me zai sa akullum ni ake yi wa tambayoyi?"***

*Albarka ta tabbata a gareku sa'ad damutane suka kiku, suka kuma wareku, suka yi kyamar sannanku saboda Dan Mutum.*

*Luka 6:22*

Sai ya jejjefi karamin hafsan nan da tambayoyi, "Ka bada gaskiya ga Allah? Mai zai faru da kai bayan ka mutu? Ta haka aka halicci wannan kyakkyawar duniya? "Sannua a hankali kuwa ya sami damar shaida masa cikakkiyar bisharar ceto. Abin mamaki ga fursunan kuwa shine wannan karamin hafsan ya bada ransa ga Kristi nan da nan.

Shi wannan hafsan kuwa sai ya bawa fursuna mai jin yinwa abincin sa na rana. Wannan Krista yayi murna cewa Allah zai ciyar da shi kuma yayi anfani dashi koda shike yana cikin radadin zafin zuciya.

A wannan lokacin kuwa, shi wannan hafsa ya shiga halin da aka yi masa tsaro na daga-kai-sai-kai, kuma ya shiga halin jin yinwa ainun. Sai ya tuna da kalmomin Yesu domin akwai albarka. Nan danan sai ya tashi ya shiga yin yabon Allah yana rawa a cikin karamin dakinsa na kurkuku. Wannan farin ciki da yakeyi kuwa sai ya jawo hankalin mai tsaron kurkukun.

A lokacinda mai tsaron ya isa gurinsa, sai kawai ya dauka wannan Krista ya haukace. Akwai umarni cewa masu tsaro su kula da wadanda suka haukace sosai, saboda haka sai ya kawo wa Kristan cuku da burodi.

Gashi kuma, Allah ya sake tanardarwa tunani ya fadowa fursunan Kristan nan "Gara in zama wawa a cikin Kristi da in zama mai hikima wanda yake wawancin Fushi akan abubuwan da ba a iya sauya su".

***Mutane da yawa sukan shirya ka'idar bi da rayuwar su har yawuce misali-watau su da suke son kebe zaman duniya kullum suka kayyade. Akwai abubuwan da suka fi karfin mu yi ikon kayyade su shine asirin cin nasara. Misali, ba za mu iya hana mutane fadar albarkacin bakin su ba, amma muna iya zabin mu yi addu'a domin wadanda suke zagin mu. Damuwa akan abin da yafi ikon mu, damuwa irin ta yan Adam. Abinda da bamu da ikon dakatarwa mukanyi kokarin fassarashi domin ya gamsar da mu da yadda mukeso. Amma Allah ya ce mu dena juya al'amura mu gaskanta shi. Kamar dai wannan fursunan. Allah yana mana tuni cewa mu aikata abinada ya fadi ta wurin yi masa biyyaya, shi kuma zai yi sauran.***

# KARIN MATSANANTUN WASIKU (NA DAYA)
## Rome: Pliny



**Wannan wasika ce daga wani gwamna da ake kira Pliny zuwa Sarkin Rome akan batun yaduwar addini Krista kasa da shekaru dari daya bayan giciye Kristi:**

*Da ace mun manta da sunan Allahnmu, ko kwa mun mika hannuwanmu ga wani bako; Allah ba ya tone wannan ba? gama ya san asiran zuchiya.*

*Zabura 44:20-21*

Ban taba halartar shari'a da ake yi wa Kristoci ba, kuma banida labarin salo da iyakar bincike da azaba da ake aiwatar wa ba.

Ko mukanyi la'akari da shekaru ko fanni? Idan Krista ya janye daga addininsa akan yafe masa ko kuma duk da haka sai ya sha horo?

A yanzu ga yadda nake yi-Na kanyi masu tambayoyi akan addininsu; idan suka furta cewa su Krista ne, nakan maimaita tambayoyin, da karin tsoratar da su da hukumcin kisa. Amma idan suka nace, sai na bada izinin kashesu. Ban yarda taurin kansu ya tafi haka ba tare da horo ba.

Nayi wa wasu Krista tambayoyi kwanaki wanda suka yi musun imaninsu bayan tambayoyin. Daga wannan faruwar ina iya ganin muhimmancin zare ainihin gaskiyan taurin yin anfani da azabtarwa daga wasu mata guda biyu. Amma bani iya gano kome ba sai gurbatacciyar koyarwa ta tsananin canfi.

Saboda haka na ga ya kamata na waiwaya kafin naci gaba da wadanan al'amura. Ya dai dace a waiwayeka akan wannan al'amari, musamman idan akayi lura da yawan mutanen dake cikin wannan al'amari, musamman idan aka yi lura da yawan mutanen da ke cikin wannan hadari. Wannan kan fi mai yaduwa ba wai a cikin birane kawai ya tsaya ba, amma ya watsu a cikin kauyuka.

Duk da haka akwai alamar yiwuwar warkadda ita.

***Shin wai warkar da Krista ab une mai sauki? Idan har turi ya zama bangajewa, yawacin masu bi zasu rike bangaskiyarsu ga Kristi ko kuwa kawai suna yi dan zazzabine? Tsakanin ko azaba hanya ce kwarai ta sanin gaskiyar al'amari. Allah kadai ne yasan zuciyar mutum. Amma tsanani yana gabatar damu da gaskiyar kowanene muke, kuma yana taimakawa wajen tabatar da sanin ko zamu juyawa Kristi baya ko zamu tsaya tuttur. Idan har da gaske mun bada kanmu ga Kristi, to sa'anan ne zai bamu halin iya jurewa da muke bukata don tsayawa dominsa. Idan kuma mun bada kanmune ga wata manufa mai makon Yesu da kansa, to zamu sami kanmu muna tuntube a lokacin da muka shiga matsi.***

***Kai al'amar ne da Kristi wanda baya magantuwa, ko kuma abin da kai mai gawurtachen canfi a a maimako?***

# KARIN MATSANANTUN WASIKU (NA DAYA)

## Rome: Masun Bi na Farko

RANA TA 143

*"Jinin Krista da kuke zubarwa iri ne kuke shukawa, Zai tsiro daga kasa ya yadu kuma".*

*Hakika ina gaya maka, ku bude idanunku ku duba gonaki kan isa girbi*

*Yahaya 4:35*

Krista na majami'un farko sun rayu a tsakiyar tsanantawa daga maketan hukumomin gwamnati. Yan'uwansu maza da mata sun azabtu, sun gurguntu, sun konu kuma an kashe su domin Kristi. Kowane shahidun mai bada gaskiya ya baiwa sauran masu bada gaskiya karfafawa. Sukan hangi abinda ke gaba da tsaron rayuwarsu su gano alherin da ke tattare a gaba kamar yadda Yesu yayi bayanin wadanda suke shirye da su karbi Kristi. Sun bada irin wadannan amsoshi ga alkalai da hukumomin da ke shugabantar tsantawa.

Yanzu kuma zaku alkalai kuci gaba da aldacin ku, zaku zama adalai a ra'ayin mutane a duka yayain da kuka hallakar da Krista.

Ku giciye, ku azbatar, ka yanke mana hukuncin kisa, ku nika mu mu zama gari, Rashin adalcin ku shine mashahurin abin shaida na tabbatar vva da rashin laifinmu, gama tabbatan da wannan shine cewa nufin Allah ne musha wahala.

Amma kayi duk iya muguntar da kuka iya, kuci gaba da kirkiro mugayen hanyoyin azabtarwa akan Krista, ba zai tabaka ba. Ku sami ma dai cewa kuna kara jawo hankalin duniya su zama masu kaunar bangaskiyar mu. Kara hallaka mu da kuke yi kara gagganta yaduwarmu ne. Jinin Krista da kuke zubarwa shine irin da kuke shukawawa, tana tsirowa daga kasa ta yadu kuma.

***Ko da shike an rubuta wadannan kalamu shekaru daruruwa da suka shige, har yanzu wannan sako na aiki a yau. Fiye da kasashe arb'ain a duniya na cikin tsananin addu'a a yanzu haka. Ko da shike maJami'a tana habaka a kowani lokaci a cikin yawancin wadanan kasashe a kowane lokaci da kuma karin karfin zuciya daga mambobin. Tsanantawa Krista bata kai ma cinma burinta na rage yawan masu bi ba.***

***Alhali ma dai takan taimaka wajen karuwar masubi da suke bada kansu. A zaman mu na masu bin Kristi, muna duban magabta da suke sintiri a wuraren rayuka na jiran karbar Kristi a zaman wasu kattan mutane da suke so su cinye mu. ku kama mu kalli yan hamayyan tamfar muna kallon mutum- mutumine da aka kafawa tsuntsaye a gona- alamun kankamo ne kawai na bada tsaro. Zaka shiga gonar kayi aikin girbi domin Kristi?***

## MATSANANCIYAR YAHUDAWA

### *Kasar Sin: Gidajen Sujada*

RANA TA 144

***Wakokin yabo sun cika iska. "Karfe hudu na asuba. Daga ina suke zuwa?" wani mutum ya kusa yin dariya yana mamaki.***

*Wannan bishara tana bada iri a duniya kuma tana labaka.*

*Kol 1:16*

Girbin yana da yawa abokina. Da alamar zamu jima yau, amma jimawar mai albarka ce, "Inji pasto yana murmushi. "Bari mu ci gaba da aiki"

Taron masu bi a bakin kogi yana da yawan gaske. Pasto yayi magata juyayi a yayin da yake yi musu baptisma, ko wanne da yake yi musu baptisma, ko wanne da hannaye a dage sama domin sabuwar rayuwa cikin Kristi. Da shi da mataimakan sa suka yiwa mutum dubu daya da dari daya baptisma wadanda suke sababbin tuba ne a rannan.

Allah yana shigowa kasar Sin ta kakkarfan hanya. A kullum ana rubanya masu tuba. A wani birni dake shanxi ta arewa shekaru shida da suka wuce daruruwar Krista sun halarci gidajen sujada. A yanzu yawansu ya karu zuwa dubu saba'in. a wani birni mai yawan dubu hamsin, akwai mummunan tsanani, duk da haka akwai tsayayyun masu bi dubu uku dake taruwa a kowane mako a majami'un karkashin kasa.

Wani pasto yayi furuci kamar mai hange, "Mu masu bi mun fi da karfi. Karin son su nan jawo tutar Kristi a kasa, shine kuma karin tashin tutar. An yi shekaru da dama majami'ar Kasar Sin tana shan tsanani akai akai.

Gwamnatin ta kirkiro wani shiri wai shi, "Nuna da karfi duk don hana yaduwar Krista. Yawan ikklisiya a majami'ar karkashin kasa a yau yana da yawan gaske fiye da yawan mambobin kungiyar siyasar kwaminis ta kasar sin.

***Girma ko yaduwa alama ce ta kashin lafiya. Majami'u masu lafiya suna girma kamar dai yadda shuka mai koshin lafiya take girma.***

***Taki, haske, ruwa da kasa maikyau duka bukata ne domin shuka mai koshin lafiya. Haka kuma, majami'u ma suna bukata wasu sinadari domin girma cikin koshin lafiya. Daya daga cikin sinadarai da kanzo bazata domin habakar majami'a cikin koshin lafiya yana iya zama wani dan tsanani. Tsanantawa ya kan tace ya tsabtace masu bi kuma ya sa su gamsu da darajar imaninsu. Kamar yadda wannan pasto ya nuna, karin tsanantuwa majami'a karin yawan mambobinsu a zaman shaidar karfin yawan mambobinsu a zaman shaidar karfin hali irin na Yesu. Shin kana bakinciki ne ko kuwa na kara gamsuwa ta dalilin tsanani? Kana anfani da karuwar da yaduwar mulkin Kristi?.***

# MATSANANCIN MALA'KA

## Romania: Angela Cazaku

RANA TA 145

*Saboda haka a zamanku na zababbun gaske na kaunatattu ku sutarda kan ku da ta agabi jinkai kaskanci da hakuri.*

*Kol 3:12*

**Angela Cazacu yar talika ce mai zama a Romania a lokacin yakin duniya na biyu da Nazi suka yi mamaya. Ba tare da bata lokaci ba rayuwar yahudawa da Krista ta sauya ta zama ta fargaba. Angela ta shiga aikin satan yayan yahudawa daga unguwannin marasa galihu, kuma tana fasa-kwaurin abinci da tafafi zuwa matan fursunoni dake Krista a kurkukun da suke kewaye birninta.**

Daga baya da aka kori Nazi daga kasar ta sojojin Soviet kuma suka mamaye, Angela tana nan tana aikinta ta na yada bisharar kaunar Allah ta wurin raba Littafi Mai Tsarki a harshen Russia da sabon Alkari a tashosin jiragen kasa inda sojojin Russia suke birjik.

A lokacinda Pasto Richard Wurmbrand yake fursuna a kurkukun Tirgul-Ocna a Lokacin sanyin kankara ta 1951, yana fama da rashin lafiya kwarai. Ramamman jikinsa sai karkarwa ya ke yi daga sanyin kankara mafi tsanani a tarihi. An yardarwa kowane fursuna anfani da bargo daya kawai, abinci kuma yana wuya domin babu mai iya tafiya inda kurkukun yake don tsananin kankara.

A wannan lokaci mai sanyin gaske Pasto Wurmbrand ya sami wani kunshi dauke da abinci da kuma tufafin sanyi wanda ya raba da wasu fursunoni. Wannana kunshi da yake zabon ma ko wani mala'ika ne ya kawo yana ganin ma kamar shi ya ceci ransa.

A nan ma kuma yar'uwa Angela ma'anar Malaika a Romania tana famada aikin ubanta. Talika ce? Watakila. Amma Allah yana farincikin. Anfani da mutane kamar mala'ikunsa masu jinkai.

***Wasu shekaru na baya, domin mai da murtani ga karuwar samun labaru game da harehare da hargitsi da ake nunawa a wurare suka fara fitowa wanda yake nuna kamar taimako ne daga mutane. Taimako da tausayawa ga wanda baka sani ba yana iya ganuwa kamar bai taka kara ya karya ba. Amma Allah yana iya anfani da kai ya sauya abin daka raina din nan ya zama awani abu muhimmi na alheri a rayuwar wani. Ka roki Allah ya taimakeka kayi irin wannan bayeswa ta tausayawa a cikin sunansa yau. Mai yiwuwa ba zaka iya sami ba, amma sai ta dauro ka zama mala'ikan wani a yau.***

***Kamar dai yadda aske gashin damisa ba zai hana zanesa ba, haka kuwa har yanzu ni Krista ne har yanzu muna taro. Da farko sau biyar kawai muke taro a gidana; yanzu muna taro fiye da sau goma sha biyu.***

Malama Vo Thi Manh wata kaka ce da aka sa a Fursuna don bangaskiyarta.

# MATSANANCIYAR ISA

## Nigeria: Rose

RANA TA 147

**"Yi sauri, shiga cikin kabad. Shiru ban da motsi sai kin ji muryata. Kun gane? Rose taji kananan muryoyi na yaranta da basu isa shiga makaranta ba tukuna, "I mama", sa'anana ta fita ta nufi makarantar da diyarta take, tana fatar ba ta makara ba.**

*Amma ya fada mani Alherina kadai ya ishe ka*

*2 Korint 12:9*

A lokacinda aka kaddamtarda shari'a ta Islama a wasu yankunan Nigeria, an yi tarzoma a wasu wurare gaba da Krista domin sunki su amince da dokokin. Babbar diyar Rose tana makaranta a ranar da aka yi tarzomar. Rose kuwa tana jin cewa diyarta tana cikin hadari. A lokacin da ta isa makarantar an rigaya ankai diyar a barikin soja don dalilan tsaro, a hankali kuwa Rose ta same ta kuma suka dawo gida inda kannenta suke jiran dawowarsu.

Washegari lokacinda mijinta ya tafi wani taron Krista, ganin karshe ke nan da rai da ta yiwa mijinta. A kalla majami'u guda dari biyu da sittin ne aka kona a tarzoman kuma an kashe Krista dari hudu da sittin.

A cikin watanni nan tun da ake kashe mijinta, Rose takan ta'azartadda daga littafin Ayyukan Manzanni. Ta ce, Allah nan da ya bari aka jejjefi Istifanus, shine kuma ya bar Bitrus ya fita daga Kurkuku. Allah mai adalci ne kuma alherinsa gamsasshe ne. "Yau Rose tana ci gaba da yin aiki a majamiy'ar da mijinta shahidi yayi aikin pasto, kuma tana nan tana kula da yayanta guda uku.

***Akan fadi cewa Allah ba zai taba kaimu wurinda babu Alherinsa ba. lalle ne mu fahimta cewa wasu lokuta ba lalle ne shirinsa ya hada da warkaswa ta al'ajibi ba daga rashin lafiya, mutuwa, ko tsanantawa. Duk da bai yaske mu ba, lalle mu gaskanta cewa Allah ba zai kaimu wurin yin bishara ko aiki ba sai tare da wadataccen shiri na alherinsa da zai tagaza mana.***

***Wasu lokuta shirinsa ya kan kunshi karfafa mu domin jurewa irin mayuwatan halayen da suka sami kanmu a ciki har karshe, ınaimakon kawar da abin daga gare mu. Ko ka isa ga matakin da zaka dogara a gareshi dungurmgum? Mai yiwuwa ba zaka taba cewa alherin Allah kadai kake bukata ba, har sai alherinsa kadai kake dashi.***

# MATSANANCIN YAHAYI

## *Indonesia: Dominggus*

RANA TA 148

**Dan makarantan tauhidi mai shekaru ashirin da haifuwa yana barchi a lokacin da ihun kira "Allah-u-Akbar! "(Allah da girma yake) Tsagerun Islama suka shiga dakinsa suka yi masa dukar-kawo-wuka. A yayin da Dominggus yake kokarin ficewa ya tsare, aka sarkafa masa wani lauje a bayan wuyansa da ya kusan yanke masa kai. Maharan nan suka barshi jina jina da tsammani zai mutu.**

*Ubangiji shine haske na da cetona kuma tsoron wa zanji?*

*Zab 27:1*

Dominggo yace ruhunsa ya rabu da gangar jikinsa, mala'ikun ne suka dauka suka kai sama, kuma yaga tasa gawar a kasa babu motsi. Babu sauran tsoro ko jin zafin ciwo tareda shi sai jin salama a yayin da yake jiran sabuwar rayuwar sa tare da Kristi. Lokacinka na bauta mani anan bai yi ba".

Muryoyina biye da Dominggo yaji na ma'aikatan gaggawa ta hukuwar lafiyar Indonesia ne. Tunda ba shi sani ba ko shi Krista ne ko Musulmi, suna shawarar ma ya kamata su kai gawarsa.

Dominggus yayi addu'a ga Allah domin ya bashi karfin iya jin magana. A karshe kalmomin "Ni Kristane" suka fito daga bakinsa. Abin sai wanda ya gani, mamaki ya rufe su ga "mataccen" dalibi ya amsa masu.
Yau Dominggus ya warke sarai. Tabbunan raunuka sunan a jikinsa, amma ruhunsa ya sami sabun tacciyar bangaskiya da sakon gafartawa. Dominggus yace yanzu yafi zama kusa da Allah kuma yanzu ya tashi haikan wajen yin addu'oi domin makwabtabsa da ke masallata- kai har da wadansu su ka kai masa hari.

***A cikin irin wannan duniya mai hargitsi da rashin tabbas. Ana umurtar Krista su fuskanci gaba ba tare da tsoro ba. Tsoro ya kan kara zurfafa al'amarin da yana riga ya kwabe ba tare da ya kawo saukin abin ba.***

***Muna iya fuskantar da al'amarun da ba su da tabbas da karfin zuciya a nan duniya domin mun sani cewar inda muka nufa watau masaukinmu na rayuwa har'abada a tsare yake domin mu. Mun sani makomar mu ita ce dawwama tare da Kristi, kamar yadda aka nuna wa Dominggo a fili. Fiye da haka ganin wannan jiki na duniya da makiyan Kristi suke gani kuma suke iya yiwa rauni har ma su kashe, to mun wuce nan. Ranka zai tafi da nisa bayan ma an hallaka gangan jikinka. Gaskiyar makomarka ita ce abin da zai faru dakai bayan mutuwarka. Ba abin da ke faruwa a nan duniya ba. Wane tsoro ka ke da shi game da gobenka? Kana iya mika su ga Allah domin ka fuskanci gobenka ba tare da tsoro ba?***

## MATSANANCIYAR WAKA

### *Korea Ta Arewa: Soon Ok Lee*

RANA TA 149

**"Ban taba sanin ma'anar wakokin da fursonin suke yi ba sai dana zama Krista".**

*Na sami karfafawa da gaske;*
*duka damuwar mu,*
*farinciki na bashi da iyaka.*

*2 Korint 7:14*

Soon Ok Lee fursuna ce a Korea ta Arewa daga 1987 zuwa 1992 ba ta zama Krista, ba sai da ta tsare zuwa Korea ta kudu. A lokacinda ta tara karbar Kristi tunanin abin da ta gani kuma taji a kurkuku ya mamaye ta.

Abubuwa masu sauki, kamar Krista da suke waka a yayinda za'ayi musu hukumcin kisa. A wannan lokacin ba ta gane ba sai tunani take wai suna haukane. Ba'a bata damar magana ba a wannan lokaci, saboda haka bata sami damar yin magana da wani Krista ba. Amma ta kan tuna wannan kalma na "Amin".

A lokacinda nake can ban taba gannin Krista da yayi musun imaninsa ba, ko daya.

A lokacin da Krista suka yi shiru, sai masu tsaro su fusata su dinga shurarsu da kafafu. A wannan lokaci ban gane da dalilin da yasa suke sadauka-da rayukansu ba, tun da zasu iya cewa ban gaskanta ba kammar yadda masu tsaron suke so. Har ma na ga wadanan suke kara hikimar wakar yayinda shuri da buge buge ke tsananta.

Sai masu tsaron su su ce su mahaukata ne sai su kaisu dakin da ake azabtawa da wutan lantarki. Ban taba ganin wanda ya fito da rai ba.
Watakila wakokin wadannan waliyai ne ya shuka iri a cikin ruhaniyar ta wanda kuma sannu a hankali ya kawo ta ga Kristi.

***Kamar dai yan leken asiri, su wadanda suka damu da yaduwar Kristanci suke leka domin sanin minzanin gaskiyar da kansu. Sukan yi lura, su kan yi gadi ko maida hankali, su kan naddace ayukan mu. Duk yayinda Krista suka yi fama da jarabobi su irin wadannan magabta suna zuba ido domin suga lalle masu bi sun fadi, abubuwa ke nan da suke gamsar da su cewa ai krista ma kamar kowa su ke. Amma a yayin da Krista suke yi murmushi a lokacin da suke tsanani su kanji haushi, lokacinda masu bi suka yi tafi maimakon kuka abin yakan basu mamaki. A lokacin da masu bin yesu sukayi waka a lokacin bakinciki su kan sami sabunta ta hanyar da ba'a iya bayyanawa. Idan kana cikin wani jarrabawa a yanzu haka, kana da dama mai tarin yawa na shaidar Kristi. Kayi addu'a domin misalin ka mai farinciki ya tabi wasu.***

## HALIN JUREWA MAFI TSANANI
## *Turkmenistan: Shageldy Atokov*

RANA TA 150

***"Ko ka sashi karayar zuci ko ka hallaka shi! "Masu mulkin Turkmenistan ba su da saura jimirin hakuri da wannan mai wa'azi titi-titi.***

*Bama fasa tunawa da aikinku na ban gaskiya a gaban Almasihu ubanmu da faman da kuke yi domin in kuma sa zuciyarku mara gushewa ga Yesu Almasihu.*

*1 Tassalonikawa 1:3*

Shageldy Atakov ya sami saki a karkashin mulkin shugaban kasa Saparmurat Nivasov a wata dama da ta samu ta bukinchikar fursuna da aka yi ranar 23 ga watan disamba 2000. Amma fa idan zai yi rantsuwa ta biyyaya ga shugaban kasa kuma ya furta kalmatu-shahada. Shageldy yaki amincewa da irin wannan saki.

An tsoratar da Shageldy wurin ma'aikatan gwamnati cewa ya daina wa'azi. A watan Disamba 1998 aka kama shi. Aka kuma daure shi shekara biyu a kurkuku, amma sai suka daukaka kara cewa hukumcin ya fi te rangwame. Sai aka kara masa wani shekara biyu a bisa na farko a kurkuku. Shageldu yana cikin radadin zafin dukan da yake sha da har kai ga fadawa yayansa kada su taba shi.

A watan Fabrairu 2000 an dauke matarsa da yayansa guda biyar da kayi aka kaisu wani kauye kaakhka inda aka yi musu daurin talala a kauyen.
A lokacinda iyalinsa suka ziyarce shi a Fabrairu 2001, Shageldy yayi bankwana da su. Matarsa ta lura cewa a lokacin ziyarar anyi masa azaba, har ga raunana kodarsa da hantarsa, kuma yana fama da ciwon shawara, da kyar yake iya yin tafiya, kuma ya kan suma lokaci lokaci. Ba ya zaton zai rayu zuwa wani dogon lokaci.

Duk da wannan Shageldy bai karaya ba, ba zai bada kai ba, kuma koda shike yana iya zabar a sake shi, ba zai yi na'am da shikar ba in dai har sai yayi watsi da biyayyar sa ga Kristi.

***Yan adam suna iya rayuwa har tsawon makonni ba tareda cin abinci ba, amma ba za mu iya rayuwa kwanaki da yawa ba idan babu ruwa. Ta haka kuma ruhunmu na bukatar abincin ruhaniya. Zamu iya yin kwanaki da dama, watanni harma shekaru ba tare da aboki ba-ruhunmu na iya rayuwa ko da akwai kadaici. Muna iya yi ko babu zaman lafiya, ko muna rashin lafiya, ko da ciwo da ya ki tafiya- ruhunmu ko da shike da damuwa a cikin sa, zai iya rayuwa. Idan muka yi kokarin yin jimiri mai tsawo ba tare da begen Kristi ba to ruhun mu zai yi sanyi. Ba zamu iya rayuwa ba sai da bege, kyauta mai daraja daga Allah zuwa ga bayinsa. Idan kanajin kamar ba za ka iya kaiwa ba, ka roki Allah ya Karfafa ka ya ba ku zari. Zaka jimre wa dukan abu da bege mai karfin aikin Kristi.***

# MATSANANCIYAR BIYAYYA

## Laos: Hezekiah

RANA TA 151

*In bamu da aminci shi kam ya tabbata mai aminci*

*2Timoti 2:13*

***Jim kadan bayan ya zama Krista a 1997, Hezekiah ya tafi wurinda aka sani da sunan, "Mafaka" domin karbar almajiranci na aikin wa'azi. Sa'annan ya koma gidan mahaifin sa, nan da nan kuwa dangin sa guda talatin da biyar suka kewaye shi tare da mutanen kauyen suna tuhumarsa dalilin da ya sa ya zama Krista. Sai ya fadi masu yace "Yesu shine kadai hanya da zan iya samun ceto daga zanubaina domin in sami rai na har abada".***

Taron ya fara fusata, Hezekiah yayi kokarin yayi masu bayani. A karshe suka cabke shi ta gashin ka, suna fara dukansa a fuska har sai da ya fadi ya sumamme.

Wani abokin Hezekiah ya dauke shi zuwa gidansa inda yayi jinya ta kwana hudu. Hezekiah bai taba iya dawowa gidan ubansa ba, amma yaci gaba da tafiye tafiye wasu kauyuka na Laos dauke da bisharar ceto.

Tan faruwar duka da aka yi masa a kauyen, Hezekiah ya sha duka kamar sau goma a wurare dabam dabam, wani lokaci ya kan gwammaci mutuwa a maimakon shan duka akai akai. Ya shaida yace,"Kamar yadda na ginu a cikin tafiya ta da Kristi, Ina da karin bangaskiya na iya jurewa da wadannan wahalu. Jarabobin da na shiga sun taimaka wajen karfafa bangaskiyata, kuma na ga hannun Allah wajen yantar dani. Na gode wa Allah da ya bani ikon kawo mutane talatin zuwa ga sanin ceton Yesu.

***Alkawarin Allah zuwa ga yayansa ba na bani-manda-in-baka-gishiri ba ne. Idan da hakane da tuni an yi watsi damu. Maimakon haka, Allah yana sane da rashin karfin mu amma ya zabi ya kaunace mu a yadda muke. Dolene mu maida hankali a yayin da muke karanta labarun shaidan Krista, bisa ga alkawarin Allah zuwa ga yayansa. Shahidai sune na farko da ya kamata su yi mana tuni cewa labarunsu ba a kan su bane, akan Allah ne! ko da shike mun karanta labaru da yawa akan masu bi wadanda suka zabi su sha tsanani maimakon juya wa Yesu baya, bayanin karshe mai ban mamaki shine ba wai matsananciyar biyayya ta mutum bane amma matsanancin adilcin Allah mai daraja. Kana iya tuntube a cikin bangaskiyarka, amma adalcinsu gareka bashi da iyaka. Dauki lokacin domin godewa Allah da adalcinsa yau.***

## MATSANANCIN MAKWABTA
## *Romania: Sabina Wurmbrand*

RANA TA 152

**Watau matashiyar bayahude yana cikin damuwa. Wani dare Sabina Wurmbrand tayi kokari ta kwantar masa da hankali: Allah ya yi wa Ibrahim alkawari cewa yahudawa zasu sami kyakkyawan rayuwa. Zasu yi yawa kamar yashin dbakin teku da da kuma taurarin da ke bakin teku**

Likitan ta dubi sama da hawaye a idanunta ta ce, "Kammar yadda na fada a bakin gaci, yan kwaminis din nan suna tattakemu. Kada ki kara yi mani magana game da Allahn ki."

Bayan yan kwanaki sai Sabin ta yi rashi lafiya ainun. A yayin da ta kusan mutuwa a gadon asibiti na kurkuku, sai shugaban kurkukun yazo. Yace, mu kwaminis muna da magani da asibitoci, kuma munfi Allahn ku karfi. A wannan asibiti bamu yarda ko amabaci sunan Allah ba. "Sabina ce kadai tayi kuru tayi magana akan cewa akwai Allah. Sauran matan sun razana cewa wani ya bosarewa shugaban asibiti.

Washe gari kuwa sai aka tilatsawa sabina ta koma bakin aiki. Allah mai al'ajibi ya warkar da ita sarai. Labarin ya bazu a kurkuku, har kunnen matshiyar likita. Sai ta tinkiri sabina a wannan daren tace, "Idan Allahn ki zai warkar da ke haka harya baki salama a cikin wannan rami , to lalle ne na yarda Allahn ki gaskiya ne. babu wani iko da zai yi wannan. Ta kaka zan sami tsira?

***Duk lokacin da muka ji karamar rayuwar mu na cikin rami, mu tabattar mutane suna nan suna lura suga yadda zamu yi mu fice daga ciki. Akwai alamar kristanci ya na jawo hankalin yan kallo musamman lokacin da muke cikin gwagwarmaya. Mutane sukan kusta kansu suzo kurkusa domin kokarin menene zancen mu da mukayi akan Allah. Sukan zuba mana idanu a duk lokacin da muke da damuwa. Idan muka dogara da bangaskiyar mu a lokacin jaraba, to fa mutane ba zasu yi musun shaidar da suka gani a irin rayuwar da kake yi? Menene mutane suke koyai da shi daga yadda kake shirya al'amuran rayuwarka tayi duhu, ka tuna cewa mutane suna lura da suga yadda zaka sarrafa shi.***

***Duk da tuna baya da nakeyi, bani da lokacin yin bakinciki. Rayuwata tana cike da farinciki, da kaunatuttun mutane masoya, bazan bada kaina cutar ciwon kiyayya ta galabaitadda ni. Ina farinciki. Ina dariya. Ina buki domin na sani cewa Allah na shine Sarkin Sarakuna, mafifici gaba da dukan ikokin shaidan da dukan barna da ya taba kirkirowa. Kuma mafi mafifici a cikina.***

Pasto Noble Alexander wanda aka sa a kurkuku a kasar cuba na tsawon shekaru a shirin da biyu-zan mutu cikin yanci

# MATSANANCIN SAYARWA

## Sin: Zhang Rongliang

RANA TA 154

*Ubangiji yana kaunar abin da ke na adalci da gaskiya madawamiyar kaunarsa ta cika duniya*

*Zab. 33:5*

***Zhang Rongliang shine shugaban kungiyar dakunan addu'a mafi girma a kasan Sin wanda yake da akalla yan kasar Sin miliyan goma duka masu bi da suke halartan sujada duk mako. A shekarar 1998, da Zhang da wasu shugabanin wadanda su ke wakiltar mabiya miliyan gomasha biyar na karkashin kasa sun sa hannu a wata takarda mai kan magana haka, "Ikirarin Bangaskiya ta majama'ar gida" wanda ya fito filin yayi kira ga gwamnatin kwaminis da su daina damun majami'un gida wadanda basu bada sunayen su ga hukumar ba.***

Bayan yan watanni da fitarda wannan takarda ga jama'a, da Zhang da sauran wadanda suka rattaba hannu akai, suka shiga hannun hukuma aka kuma daure su. Daga baya aka saki Zhang amma da sharadin cewa ya shiga taitayin sa na shekaru bakwai. A yanzu Zhang yakan yi bishara ga mabiya. Tun da baya ya bin umarni kamar yadda gwamnati su ke so ba, Zhan baya kwana a gado guda fiye da yan kwanaki a jere.

A lokacin da Bulus ya rubuta a Romawa 13 cewa muyi biyayya da gwamnatin mu, shi fiye da kowa ya san kasadar. Amma da shike Romawa sun nuna masa tsanani, amma ai ta wurin daukaka kara game da dokokin sune ya dauki bishara zuwa Rome.

Rokon sa na a yi masa shari'a a zamansa na mutumin Rome ya taimake shi wajen ciyar da bisharar gaba zuwa Rome, ko da shike wannan ya zama tafitarsa ta karshe.

Kamar Bulus, Zhang yayi kasada mai tsanani lokacin da ya yayi wannan roko. Sakamakon daukar kasadarsa, yasa dayawa suna sami sanin Kristi.

***Kamar Bulus, shugabannin majami'a a kasar Sin sun sani cewa Allah shi ke nada gwamnatoci. Amma kuma sun sani cewa Allah ba zai kyale rashin adalin mugayen hukumomi ba. Al'ada ta nuna cewa Romawa sune tabbas suka fille kan Bulus. Haka kuma, masu bi na kasar Sin sun wahala. Idan sadaukar da rayuwarsu domin kawo adalci ga Kristi ya zama dole, to pastoci kamar wadannan a shirye suke su mutu. Yaya karfin bukatar mu na son ganin an yi adalci yake? Wace irin daraja muke baiwa yancin yin wa'azin maganar Allah? Yi addu'a domin masu bi a kasar Sin yau wadanda suke karfafamu domin mu nemi adalcin Allah domin masu kuntata masu. Ka roki Allah ya nuna maka hanyoyi da zaka taimakawa cikin su domin ciyarda aikin Allah gaba.***

# ANNABCI MAI TSANANI
## Rome: Bitrus

RANA TA 155

***Sau uku kenan, Kristi ya tambayi Bitrus, Simon, dan Janas, kana kaunata?"***

*Muka kuma aiki Timoti danuwanmu, bawan Allah kuma na al'amarin bisharar damasiku ya kafafa ku a nan al'amuran bangaskiya*

*1 Tassal. 3: 2*

Bitrus yayi bakinciki. Yayin musun Kristi sau uku, gashi kuma Yesu ya sake tambayarsa ko yana kaunar sa har sau uku. A wannan karon ya amsa a hankąli sai kace ko yana auna muhimmancin kalmomin da ke fitowa daga zciyar sa, "Ubangiji ka san duka kome, ka san cewa ina kaunarka". "Ka kula da tumaki na" Yesu ya maimaita sau uku. Sai dai a wannan karon ya kara, "A lokacinda kake yaro ka suturta kanka kuma kakan tafi duk inda ka keso, amma lokacin daka tsufa wanene zai suturtaka kuma ya kai ka wurinda ba ka son zuwa. "Sa'anan Yesu ya ce ka biyo ni Yoh 21:15-19

Nero ya azabtad Bitrus a lokacinda yake da shekaru saba'in na haifuwa. Bisa ga alamara, abokan Bitrus da sauran masu bi sun matsa masa da ya ki, amma daga baya sun matsa masa da ya gudu daga birnin Rome. Da farko ya ki, amma daga baya suka rinjaye shi da ya tsere. A lokacin da ya tinkari kofar birni domin ya fice, sai ya ga alama ta Yesu yana takowa da kafa zuwa cikin birnin. Sai ya rusuna a gwiwoyin sa yana yi masa sujada, "Ubangiji ina zaka tafi? "Na zone domin a sake giciye ni ka biyo ni".

Bitrus ya juya, kuma ya bishi zuwa inda baya son ya tafi, ya koma ya fuskanci Nero. A lokacinda aka tsareshi ya roke su da su giciyeshi a juye kafafu a sama kai a kasa gama ni bani da martabar da ta isa ni a giciye ni a tsaye kamar da aka yi wa Ubangijina.

***Manufar wannan almara ba wai a nuna cewa an giciye Yesu sau biyu bane. Yesu ya mutu kuma an tashe shi sau dayan nan babu kari.***

***Manufar wannan almara shine domin ya tunashemu cewa Yesu yana sane da irin wahala ko azaba da muke ciki tamfar ma kamar shi ke cikin wannan wahala da kansa. A batun Bitrus kuwa Littafi Mai Tsarki yace, annabcin da Yesu yayi can baya yana nufin giciyewar Bitrus ne. Wanene kuwa in ba Yesu ba da zai iya bayanin abin da zai faru da Bitrus game da azabtarwa? Yesu masanine game da batun shan wahala. Yesu ya san kome akai shi yasa ya bi tare damu. Idan akwai ciwo ko damuwa a rayuwarka, Yesu yana sane. Idan raunan ka akeyi Yesu yananan kuma. Bari ya karbi kayan nauyin ka da bakincikin ka ta wurin addu'oinka yau.***

## MATAR PASTO MATSANANCIYA

## Romania: Sabina Wurmbrand

RANA TA 156

***Akwai fitaccen banbanci tsakanin karkarar Romania da azabatar da Krista da Yahudawa suke sha a hannun yan Nazi da kwaminis masu mamaya. Game da Sabina Wurmbrand kuwa damuwarta sun kashi uku: ita Krista ce Kuma Bayahudiya ga ta kuma matar wannan pasto.***

*Ya fadi wannan ne yana kwatanta irin mutuwar da bitrus zai yi ya daukakakaAllah. Bayanya fadi haka ya bi ni.*

*Yahaya 21:19*

Watarana ta sami labari cewa uwarta, ubanta, kannenta mata guda uku da kaninta dan shekaru tara da haifuwa an hadasu duka anyi musu kissan gilla a sansanin azabtarwa. A wannan rana ne bangaskiyarta ya tabbata rayayye.

Cike da alherin Allah, Sabrina tace,"Bazan nuna murtukakkiyar fuska ba. Na dukam ma kaina alkawarin zama mai bada gaskiya ga Allah tareda farinciki, ga majami'a kuwa zama misali ne karfin zuciya kuma ga mijina kuwa mace mai canjin hali".

Sabina bata taba bari alamuranta na damuwa ko bakinciki su hana ta karfafa wadanda suke kewaye da ita ba. A zuciyarta ba ta da zabi. Da mutuwa da shan wahala musamman ma a tsakanin mambobin majami'ar karkashin kasa ya zama ruwan dare. A zamanta na matar Pasto sukan zuba mata idanu. Idan ta karaya ai mabiya wane karfafawa zasu samu? Daga baya Sabina ta yi shekaru uku a kurkuku da tsananin bauta. Inda mata suka fuskanci duka da cin mutumci harma a kurkukun. An santa da sunan kawar kowa, kuma a kullun tana anfani da kalmomi masu tausasa zuciya.

Kafin ta bar Romania, Allah ya ba Sabina ladarta Ita da mijinta Richard daga baya suka janyo makashin iyalen su zuwa ga Kristi.

***Aikin pasto aikine na hadin kai tsakanin pastoci da abokan zamansu. Babu wanda zai zama cikakke ba tare da bishara da kuma karfafawa abokin zama ba. Allah baya kiran Krista domin yayi aikin kadaici- yana kira zuwa ga jama'a. Muna bukatar sauraran Krista su wanzu tare damu a majami'un mu domin samun hikima da karfafawa daga lokaci zuwa lokaci. Ba a tsammacemu da mu yi aiki mu kadai ba-ko kuma mu jaraba yin abokin bishara, wanene kake hulda da shi a cikin aikin bishara? Wa ke addu'a domin ka zama shaida sosai a wurin aikuna, gida ko makaranta? Ka roki Allah yayi maka jagora zuwa ga abokin aiki Krista wanda zai karfafa ka a lokacinda kake da bukatar haka din.***

RANA TA 157

*A kullum ka zama da shiri domin amsawa dukan wanda ya tambayeku dalilin begen ku da ku ke dashi*

*1 Bitrus 3:15*

# MATSANANCIN KARFI

## *Indonesia: Fritz*

***Fritz yana jin zafin kowane naushi da ake kawo masa a ka kuma sai addu'ar samun karfin jurewa dukan ya ke ta yi. Masallata da suka kawo masa hari suka kewaye shi suna ka masa naushi a fuska bi da bi. Daya daga cikinsu ya zar doguwar wuka da tunanin wannan zai gama da paston Krist din nan. Sukar farko da aka yi masa da wukar sai Fritz ya kwala ihu don zafin yace "Yesu, an sossoke shi akai akai kuma a kowace suke sai ya kwala ihu yace "Yesu!" Maharan sa suka ji haushi wai yaki mutuwa!***

Tsagerun yan islama suka wuce gaba suka fara zaro bencuna akan bagadi na cikin majami'a suka sa musu wuta biyu daga cikin masallatan suka soki Fritz kuma suka jefa shi cikin wutar. Daga ganin sun gamsu da ta'asarda sukayi sai suka gudu daga wurin. Fritz bai iya tuna abin da ya faru ba bayan wannan amma ya san abu guda. Ko gashin kansa guda daya bai babbaka ba.

Bayan wannan harin, an kawo Fritz a asibitin mafi girma a wannan yanki na Indonesia amma aka ki karbansa da suka ji cewa shi Krista ne. Sai aka kai shi wani asibiti amma likitan da ke bakin aiki yace in har ya rayu zuwa gobe zai sami ta'adin a cikin kwakwalwarsa.

Bayan jinya mai tsawo, Fritz ya sake komawa yin bishara a wata sabuwar majami'a. Abin da ya bashi mamakin shine, daya cikin musulmin da suka kai masa hari ya fara nema inda Fritz yake, kawai don yayi masa tambaya guda daya; "Wanene wannan Yesu din".

***Wanene ba zai jidadin cewa ana zaton shine gwani? Tana iya zama makankai, kafinta masu zane ko yan guje-guje kowa ma naiya zama gwani a kalla unguwa guda. Mukan so mu yi tambaya akai wasu al'amura da muka saba dasu. Amma inda mutum zai yi tambaya "Wanene wannan Yesu din?" zamu iya zama a ashirye kamar wani gwani da yake da shiri? Ba kowane Krista ne mai bishara ba, amma kowa Krista zai iya shaida bishara ta wurin tattauna maganar shirin ceto a yana yin da damaryin haka ta samu. Idon wani abokinka ka marabi yayi maka wannan tambaya ta kaka zaka bashi amsa? Idan kana shakkan kayi magana da wani wanda ya sani.***

# MATSANANCIN KUNGIYAR MATASA
## *Russia: Pasto Serebrennikov*

RANA TA 158

***Jaridun gida sun yi bayanin wurin cewa an yi rashin mutunci, ba wuri ne na kisa ba, ba wuri ne na kadarin mota ba; Makaranta ce ta tauhid.***

*Kune hasken duniya ai birni da aka gina bisa tudu ba shi boyuwa. Ba a kunna fitila a rufeta da masaki sai dai a daurata akan madorinta sa'an na ta ba duk mutanen gida haske*

*Mat 5:14-15*

Wannan labari an buga shi ne a cikin jaridar kwaminis ta Russia wajen 1960. Inda aka ce, "Samari da yan'mata sunyi wakokin ruhania. Sun karbi al'adannan ta baptisma da kuma rikon mugun, koyaswar su munafunci wai kauna zuwa gama kiyi. Labarin mai gigitarwa ya cigaba da bayyana cewa a zahiri ma yawancin matasa da ke cikin kungiyar matasa kwaminis Kristoci ne a boye. Dole ne mu gaskanta mai cetonmu kamar yadda Krista na farko suka yi. Pasto Serebrennikov ya fadawa kungiyar matasan. A garemu babban doka shine Littafi Mai Tsarki. Bamu amince da wani abu dabam ba. Mu hamzarta mu ceci mutanen daga zanubansu, musamman matasa".

An jefa paston a kurkuku don an gano wata wasika da wata sabuwar tuba ta rubuta. Matashiyar ta rubuta "Ina aika maka albarku daga Ubangijinmu makaunaci. Yana kaunata sosai!" Yan jaridu sun yi mamakin yadda daliban kwaminis suka yadda su bi Krista suka kuma baiwa makarantun kwaminis laifin zama marasa karfi kuma wadanda basu san haske ba. Su nce Krista na iya kwace almajiran ta daga hannun malaman ta masu halin ko in kula".

Ba halin ko in kula bane ga malaman, Kira ce ta kaunar Kristi kamar yadda pasto Serebrennikov tare da kungiyar samari-Krista sun bar haskensu ya haska a cikin kasa mai duhu.

***Wannan karamar fitila tawa, Zan barta ta haskaka... "Wannan sananiyar waka ta yarinta tana da karin waka mai sauki ga kuma saukin yawan kalmomi domin a iya haddaceta-tana zama a zuci bayan an rairata. Kananan yara suna iya koyon ta ciki sauki, amma tafi wuya wajen bin abinda take fadi, musamman idan muka kara girma. Sau nawa muka sani zamu iya barin fitilarmu ta haskaka ta girmama Allah? Sau daya ko biyu? Goma? Ashirin? Ba kirgen ko yawan ne magana ba, maganar ita ce amsar da bayarwa ga abubuwanda muke fuskanta kullum. Wa ya sani? Hasken ka yana iya zama abinda wani yake bukata domin ya gane hanya.***

# MATSANANCIN SAYARWA

## *Romania: Sabina Wurmbrand*

RANA TA 159

***Maimaitawa yana tada mata hankali kamar ta fashe don haushi, amma hafosan bai fasa ba. "Muna da hanyoyin da zamu sa ki. Kiyi magana wanda ba zaki so ba, kada ki yi kokarin nuna mana iyawa, yana bata mana lokaci".***

*Da tamani aka saye ku; kada ku zama bayin kowane mutane*

*1 cor. 7:23*

Tambayoyin su na kokarin su sa ta ta fadi sunayen wasu Krista-wadanda ta lura dasu cikin bangaskiya kuma ta karfafa su, su zama da dagewa idan aka fuskanci tsanani. Yanzu kuwa ita ce ya kamata ta yi karfin hali amma a yadda takeyi kamar ma ba zata iya jure wani zagaye na tambayoyi kuma ba.

Zagaye na gaba su nyi anfani da hankali da wayo. Shi mai yin tambayoyin shi, "Malami kadai ne kuma yana murmushi, ke yammata shekarunki talatin da shidda ne kawai ga rayuwarki a gabanki. Kurum ki bamu sunayen masu cin amanar kasa". Sabina tayi shiru. Yaci gaba "Bari muyi magana, a zahirance, kowa na da nasa farashi, to me yasa ba zaki fadi naki ba? Ki dai gaya mana abinda ki ke so. Walwala a gareki da mijinki? Gida mai kyau da majami'a? Zamu kula da iyalin ku sosai.

Sabina ta amsa masu da zafin imani. "Na gode maka, amma na rigaya na sayar da kaina".

"Kin siyar? Mai tambayoyi yayi mata katsalandan "A nawa kuma ga wanene?" An azabtar da Dan Allah kuma ya bada ransa domina. Ta wurin zan shiga aljannah shin zaka iya biyan farashin da yafi wannan?

***Muna sa rai cewa matasa su bi ta nan. Kuma cewa hanya ce dawajibi a bi. Duk da haka mukan yi tunanin cewa abin zai ci gaba da addabar mu har zuwa lokacinda mu har zuwa lokacinda muka zama mutanen kanmu. Matsi irin na aboka sa'anni- ya kan sa mu yi kamar wani abu ne dabam inda muka kauche wa yarda da abubuwan da muke gani zasu kaucewa akidodin mu, wannan jin sai ya zama kamar an zage a matsayin wawaye. Sai muyi kamar gwanjon mu akayi, domin mun tozarta kanmu a matsayin wawaye. Amma Kristi ya biya farashi mafi tamani domin ya jawo soyayyar mu. Idan kowa na da farashin, tun farko. Saye da yayi da jininsa ya bamu damar wanzuwa a gareshi. An rigaya an saye ka an biya saboda haka kada kayi rahusa da kanka. Ka tunatarda kanka game da wannan yau.***

# *Majami'ar da bata tunawa da azabtattun yan'uwanta ba majami'a bace dadai.*

***Wani pasto na Lutheran wanda ya jimre matukar azaba domin ya kare yan majami'arsa ta karkashin kasa.***

# MATSANCIN KAYAN AIKI

## *Kasar Amirka*



*Amma kaka zamuyi addu'a ga wanda ba su gaskanta da shi ba, takaka zasu gaskanta mai wa'azi?*

*Rom 10:14*

**Hayaki da yake tashi daga cikin taragu na jirgin kasa da yayi hadari yana da yawan gaske ga kukan zafin ciwo da yake fitowa daga fasinjojin da hadarin ya riske su a ciki wadansu rauninsu na zubar da jini wadansu kuma sun karairaye kuma suna cikin mokadaddun tarago. A cikin masu rauni da wadanda ke bakin mutuwa sai ga wani likitan fida yana tafiya, bai sami rauni a hadarin ba. Amma ya rasa kayansa, sai cewa yake "kayan aikina! Kayan aikina! Ina ma da na sami kayan aikina!"**

Da da kayan aikinsa na likita da ya ceci rayuka da yawa. Da hannu wofi kuwa bashi iya taimako sai dai yakalli mutum yana mutuwa. Majami'ar yau da ke cikin tsanani ba ta sha bambam da abinda wannan likita yake ciki ba. Suna da sani da niyyar ceton rayuka da yawa da ke makale a cikin taragun hadari na kwaminis ko kuma Islama da babu Kristi. Abin da suka rasa shine kayan aiki.

"Ku saurari kukan yan'uwanku maza da mata a cikin kasashe marasa yanci!" inji pasto Richard Wurmbrand a lokacin da yazo Amirka da farko.

Ba neman su tsere sukeyi ba, kadai kayan aiki suke nema domin dakatar da gurbata matsanancinya da akeyi wa-manyan gobe-da koyarwar rashin yarda da Allah. Suna neman Littafi Mai Tsarki. Ta kaka zasu yada bishara idan basu da Littafi Mai Tsarki?"

Krista da suke kasashe marasa yanci ba zasu iya samo wadannan kayan aiki don kansu ba. Suna dogara ga Krista da suke zama a yantattun kasashe domin su taimaka. "Ku bamu kayan aiki da muke bukata"Wani Krista ya fada mana, mu kuma zamu dau nauyin yin anfani da su."

***Alli domin malami, allura domin mai aikin jinya, hakuri domin iyaye kuma tantan domin manomi, ko wace sana'a tana da kayan aiki. A zaman Krista munsa kayan aikin mu na ruhaniya domin muna karanta su a cikin maganar Allah amma me zamu ce akan wadanda basu karanta ba akan kayan aiki na misalin-gafartawa, kauna, taimakon juna da dukan baiwa da Allah yayi mana? Bai kamata ka bar wannan baiwa ta ruhinaya ga kanka kadai ba, kana boye ta kamar yadda mai tsananin tattali yake boye zinariya. Ka yi anfani da kayan aikinka tare da sauran jama'a da kecikin bukata.***

# MATSANANCIN BULAGURO

## Vitnam



***Jijigar da jirgin kasar keyi garin tafiya shi yasa wannan Krista yar Vietnam mai karamin jiki mara karfi ita ma take jijjiga akan kujerar katako tana jin zafi. Amma ta fito tafiyan nan ne da manufa.***

*Ka yi kwazo cikin wadannan al'amura; ka bada kanka garesu sosai; domin chingabanka ya bayanu ga kowa*

Tana bukatar abincin ruhaniya domin Krista da take ciyarwa a Vietnam ta arewa. Taro kashi uku na mutane suna addu'a cewa shugaban su ta sami nasarar kawo Littafi Masu Tsarki.

Ayyuka da take yi a can gida masu gajiyarwa ne, ita kadai ce Krista da ta ginu a wannan yankin, kuma ta kafa majami'u guda uku da kokarin kanta, tana samun masu tuba daya bayan daya sannu a hankali ta wurin bishara da takeyi. Bata da mota ko basukur. Takanyi tafiya da kafa ko kuma tayi anfani da wata yar kwale kwale zuwa taron majami'a.

Ta sha fuskantar tsoratarwa daga Yan Sanda da kuma iyayenta domin bangaskiyarta. Yanzu kuma ga ta a cikin jirgin kasa tana yin tafiyar mil dari takwas wanda zai dauke ta kwanaki uku da zuciya cewa zata yi kicibis da wani mai bi da zai iya taimakawa. A karshe ta isa birnin Ho Chi Minh.

A canar da ta hadu da Krista da suka zo ziyara daga Turai su suka bata Littafi Masu Tsarki domin masu bi na arewa. Kuma suka bata basukur domin ya taimaka mata gudanar da ayyukan majami'u da ikklisiyar ta. Kafin ta tafi sun yi addu'a tare, sun rokon Allah ya albarkace ta bisa ga doguwar tafiya dake gabanta da kuma aikin ta na bishara.

Wani cikinsu ya tamabye ta ko shekarunta nawane? A lokacin da ta tashi tafiya. Matar ta kware gashin kanta daga fuskarta sai ta rada, "Shekaruna ashirin da biyu ne."

***Mubazzaran yara suna da baiwa ta musamman na kwazon da yafi karfin shekarun su. Mai yiuwa ma musan wani da ya kamalla karatun sa na koleji tun yana dan shekaru goma sha biyar da haifuwa, ko kuma wanda ya wallafa waka kafin ma ya chika shekaru gomasha biyu da haifuwa, kuma wanda gwanace a wasan guje-guje da tsalle-tsalle yana dan shekara goma sha shida. Galibi mukanji kyashi, mukan yi fatar cewa ina ma da mune muka yi wani abu gagarumi a lokacin kuruciyar mu domin mu sami karbuwa. Ita wannan mata yar Vietnam kuma Krista fa abin da tayi kenan, amma mai yiwuwa ba ta da wani kwarewa na musamman fiye da na sa'anninta. Amma tana da muradin bin Yesu domin ta kawo Yesu ga mutanen kasarta. Krista na yi maka kira da ka zama mai himma da kwazo domin shaida kaunar Allah mai sauki da ba lalle ne a bukaci gwaninta ta musamman ba-kawai ka bada zarafinka.***

# MATSANANCIN UMARNI

## *France: Da Revennasa da Martin Guillabert*

RANA TA 164

**Da zarar kinji an yanke muku hukumcin kisa, ku dauke shi tamfar gayyata ce daga Sarki Mai Daraja, wanda ya gayyace ku zuwa bukin angoncinsa."**

*Gama na sani cewa babu mutuwa ko rai babu mala'iku ko iskoki ko na yanzu ko na gaba ko ma wani iko a can sama ko a karkarshin kasa babu wani abu kuma a cikin haliya da zai iya raba mu da kaunar Allah ta wurin Yesu Kristi Ubangijin mu.*

*Rom 8:38-39*

Ko da shike umarnin na da wuya amma a bayyane yake. Marubatan nan yan Faranshi watau Franz Ravennas da Martin Guillabert sun rubuta wata takarda ta bi da Krista ga yadda ya kamanta su Fuskanci irin barazanar da akeyi musu ta hanyar kashe su. Madaba'ar su ta wallafa shine dakinsa na kurkuku a zamanin juyin-juya-hali da aka yi a kasar Faransa. Sun maida dakinsu na kurkuku "karamin daki da ke zaman matakala zuwa Aljannah."

"A lokacin da suka karanta hukumcin da zasu yi maku" wannan takardan taci gaba. "Zaku fada kamar shaidai da yawa da suka shige kafin ku. Mun gode wa Allah. Kuyi wakokin farinciki. A lokacin da suke daure hannunku. Kuyi anfani da kalmomin Bulus. Ni bawai kawai a shirye nake a daure ni ba amma ashirye nake na mutu domin sunan Yesu Kristi. "Akan hanyar tafiya inda za'a harbeku, kuyi wa masu tsaron bisahara ku nuna masu farincikinku na shan wahala da kuma mutuwa domin Kristi. Wanene zai raba mu da kaunar Kristi (Rom 8:35)

A lokacin da kuka yi fuska da fuska da mai zartas da kisa ku tuna da kalmomin gagarumin shahidin nan Ignatius. A yaushe wannan ranar farinciki zata iso a yayin da za'a dauke raina a dalilin Mai Cetona. Har yaushe zan jira? Ku tuna kuma cewa lalle ne kuyi addu'a domin masu azabartawa.

A fille kawunan Raveennas da Guillabert. Kalmomin su da ban mamaki ga yawan cin Krista da ke kasashe masu yancin, amma a kasashe marasa yancin kam har yanzu ana anfani da su.

***A zaman mu na rayuwa a kowace rana takan zo da irin gargadinta. A kula hatsari na iya faruwa babu zato. Ko a cikin mota ko a kafa, ko a aiki, hatsari na iya zuwa, ko cuta ko tarzo ma ta yan ganganci. Sanin cewa ba ma iya zama da alkawarin da Allah ya bamu. Babu abin da zai raba mu da kaunar da muke da ita ga Yesu. Ko da shike ba lalle ne ka mutu domin bangaskiyar ka ba, kana iya fuskantar kiyayya da kuma tsanantawa. Nufin Allah zai bi da kai kuma ya taimake ka fuskantar dukan abubuwa da suka tunkaro ka yau.***

# KARIN KAYAN AIKI MATSANANTA

## Kasar Parisa

RANA TA 165

**"Mune yumbu, shine kuma maganin".**

*Duk da haka ya Ubangiji kaine Ubanmu. Mune yunbu kaine magini dukanmu cikin hannunka.*

*Ishaya 64:8*

Wani Krista ya tsaya ta taga, yana lura da alamar motsi a cikin duhun titi-titi ko da za'a ga lokacin da Yan Sanda zasu samamo domin tsare masu sujada. Krista suna taronsu ne na boye a kudancin Parisa. Bako daga kasar waje da yake tare da baki daga waje.

Ba a jima ba da sakin wani Krista daga tsaron Yan Sanda kuma kukkujewa da ke jikin sa yayi bayanin irin abinda yafaru dashi a can. Ko da shike Yan sanda suna ido akansa, kuma sun sani irin aiki da yake yi na Krista, yaci gaba da aikin sa kamar yadda zai iya duk lokacin da ba ya tsare.

Yayi magana da karfin so na kwarai yana iza taron masubui suyi girma cikin rayuwa irin ta Kristi, kome wuyar yin haka. Dukan su sun sani sakamakon yin haka mai daci ne, amma dukansu sun sani Krista da aka taba tsarewa, aka doddoke su ko kuma aka karkarshe. Wasu ma bace wasu ka yi ba'a san yaya akayi da su ba.

Wannan taron sujada yayi dadi yayi bakon mamaki daga kasashen waje ya tamabayi mai maganar game da abubuwan da ya gani a zamansa na kurkuku da irin wahalun da ya jure. Ya tambaye shi cewa, "Takaka kake rike da ruhaniya mai bege da kuma farinciki a tsakiyar irin wannan hali da ka sami kanka a ciki"

Sai maibi Ba-Parishe ya amsa yace, "Wadanan Jarabobin kayan aiki a hannun Allah."

"Wanene ni da zan ga abin kayan aiki da Allah yake anfani da shi wajen kara tsarkake ni?

***Dan Adam ya jarabta da son sanin abin dake zuwa a gaba. Misali muna da masu duba, da wasu da ke nuna suna iya duba ga abinda ke zuwa, an rubuta Littaffai, an shirya majigin iri iri game da tafiya zuwa abinda bai iso ba tukuna ( timetravel) mukanso musun me ke tafe akan rayuwarmu ta duniya, kamar dai yadda yumbu bashi iya cewa magini gina abu kaza da ni, haka kuma ba zamu iya tambayar Mahalicin mu abin da zamu zama ba. Amma mu gaskanta cewa Allah zai hallici wani abu maikyau kuma mai tsarki da rayuwarmu. Mun sani ta wurin bangaskiya cewa mu halittace daga Allah. Ta wace hanya bukatar gaskanta Allah. Mai ikon gina ka ga aiki mai Fasaha.***

# MATSANANCI YAR KAUNER GICIYE

## Rome: Andrew

RANA TA 166

**Idan baka yi musun Yesun nan ba, zaka mutu a kan giciye gwamna Aegaeas ya fusuta. Wannan Krista ya kawo masa rudewa a idanun jama'ar Rome ta wurin yada bisharar addinin Krista a ko ina cikin yankin Girka na mulkinsa kai hai ma ga matar gwamnan.**

*Muna zuba ido ga Yesu shugaban ban gaskiyar mu da mai cikanta shi wanda ya jimrre da giciye domin farin zuciya da ake sa gabansa yana rena kumya, ya kwa zamn a hannun dama na al'arshen Allah.*

*Ibraniyawa 12:2*

"Da ina jin tsoron mutuwa a kan giciye. Da banyi bisharar mulki da darajar giciyen Kristi ba. "Andrew ya amsa. To ya zama haka din! A giciye shi"

A lokacin da andrew ya nufi inda aka kafa giciyen, sai ya shaida cikin farinciki. Ya makaunaciyar giciye! Ina murnar gananki a kafe a nan. Na zo gareki cikin salamar zuciya tare da fara'a da bukatar cewa ni da nike Almajirin shi wanda aka kafa akan giciye shi sami giciyarwa. Dukan kusato giciye da nakeyi kusatar Allah nakeyi."

Andrew ya zauna a rataye a kan giciye har kwana uku, yana bishara yana fadakar da jama'a da ke gabansa. Ku tsaye a cikin maganar Allah da kuma dokokinsa da kuka karba, kuna yi wa juna gargadi domin ku zama na Allah har matuka, domin kuma ku sami rabonku na alkawarinsa.

Andrew ya shaida ya Ubangiji Yesu kristi! Kada ka bar bawan ka wanda yake rataye akan iytace a dalilinka ya sami saki ya zamma tare da mutane kuma. Ka karbeni zuwa malinka". Sa'anan bayan ya gama rokonsa sai ya bada ransa ga Allah.

***Tangaran azurfa, zinariya. Kai har Jauhari akanyi adon zane na giciye da alamu na ado iri iri a yanzu. Kayan ado na zinari ko azurfa. Kayan ado na ratayawa a bango harma madubin duba baya ta mota. Wannan abu da akekira giciye da ta bazu a koina. Da dukan tsananin sani da aka yi mata, Krista guda nawa ne suka tsaya suka yi zurfin tunani game da ma'anar rataya alamar giciye? Na daya dai, giciye ma na nuna alamar azabtarwa-kayi tunani kaka zaka ji idan aka rataya a bango ko aka ajiye a daki alamar maratayi irin wanda ake kashe mutum da shi a kurkuku ko kuma kujerar lantarki ta kashe mutane a kurkukun? Giciye na mana tunin irin mutuwar azaba da Kristi ya sha fiye da haka giciye a zaman gada ta hawa kai doron zunubi wanda ya shiga tsakanin Allah da mutanen sa. Yesu ya dawo damu wurin Allah ta wurin giciye. Yanzu haka kayi tunani abin da giciye yake da shi dominka.***

# MATSANANCIN CETARWA

## The Netherlands: Dirk Willems

RANA TA 167

***A cikin kasar Netherlands ta karni na gomasha shida an rada wa Dirk Willems suna "Anabaptist" a zaman mulkin Katolikan mutanen kasar Spain kuma aka daure shi yanzu kuma gashi yana kokarin tserewa daga kurkukun don ceton ransa.***

*Ka dogara ga Ubangiji ga dukan zuciyarka da ka jingina ga naka fahimi.*

*Misalai 3:5*

Ya tsere ta wata karamar taga ya zura kansa ta anfani da igiyar da akayi da tsun mokara. Ya sauka a kan daskarren tafki da ya bi ta bayan shingen kurkukun, yana sanda a hankali akan daskarriyar kankara, yana tsoron ko zai nutse. Amma tsananin yunwa da ya jimre a kurkuku gashi ya zama abin taimako. Nauyinsa bai wuce laba dari ba.

Kafin ya ketare zuwa daya gefen tafkin, sa yaji kara. Ka tsaya nan inda kake! "Mai tsoron kurkuku ne ke magana ta tagar da Drik yana dap da yanci. Sai yaci gaba da tafiya.

Maitsaron kurkukun ya sake kira da ya tsaya a yayin da shima ya fara taka kankaran tafkin, sai ya fara saun domin ya cinma Dirk, amma taku na uku akwai inda kankarar ta tsage. Sai gashi tsundum ya fada cikin ruwa ya nutse a cikin sanyin kankara. Fadarda yake na Drik ya tsaya sai, ya koma ya zama kuka yana cewa wayyo a ceceni: ina rokonka ka cece ni"

Dirk ya dakata ya dubi hanya gashi ya kusa tserawa ya juyo kuma nan da nan ya dawo wannan tafkin kurkuku yayi rub-da-ciki ya mika hannunsa domin ya ceci wannan mai tsaro daga daskararren tafki. Domin muna godiya irin ta gatse sai mai tsaron ya cafke hannun Drik ya umurceshi da maza ya koma kurkuku.

Duk da irin bajintar da Dirk yayi kona shi aka yi a daure a jikin itace da aka kafe domin bangaskiyarsa,

***Krista da suka bada kansu basa yin rayuwar yau da kullum irin na duniya ba, Su kanyi abubuwan ba zata da sanin cewa ana iya samun sakamako mara dadi. Sukan fuskanci yin abin da ake zato baya yiuwa kamar wani abu mai sauki a garesu. Masu bi sukanyi rayuwa bisa ga umarnin ruhaniya. Ayyukan su da hanyar su ta maida murtani sunsha bambam da na duniya ainun shi yasa wasu lokuta ba a fahimtarsu. Ga wasu cetar da mai tsoro da Drik yayi wani zabi ne dake bana mutumtaka ba. Ko kuma ma watakila wauta ce. Drik kuwa ya gaskanta cewa yana bin asali na Littafi Mai Tsarki. Ya aza bukatar wani gaba da nasa. A lokacin da da muka ba da kanmu, mai yiwuwa wannan ba da kai ba zaiyi ma'ana ga mutanen duniya ba, amma mun sani muna samun ginuwa daga ikon Ruhu Mai Tsarki. Kana rayuwarka yau da kullum irin na duniya ne? ko kuma shin kana bin umarnin Allah ko ta halin kaka?***

RANA TA 168

***Ina kiyayya da hanyar yan kwaminis,***
***amma ina kaunarsu.***
***Ina kiyayya da hanyoyin yan kwaminis,***
***amma ina kaunar mai zunubi:***
***Ina kaunar mutanen kwaminis da dukan***
***zuciyata. Kwaminisawa suna iya kashe krista,***
***amma ba zasu iya kashe kaunarsu da suke***
***da ita har ga masu kashe su ba,***
***Barni da bacin rai ko haushi kome***
***kankantarsa gaba da kwaminisawa***
***ko ma wadanda suka azabtaddani.***

*WANI TSOHON FURSUMAN BANGASKIYA A*
*KARKASHIN MULKIN KWAMINISANCI*

# MATSANANCIN TSARO

## *Kasar Misra: Ahmed*

RANA TA 169

***Me yasa kake sa yaranka a cikin irin wannan hadari? Inji daya daga cikin hafsoshin kasar misra guda uku.***

An sha tsare Ahmed sau dayawa domin yada bishara ta bangakiyar sa da kuma raba takardun bishara. Amma shi a gareshi duk lokacin da ake yi masa tambayoyi dama ce ya samu ta yin shaidar Kristi.

*Ku yafe dukan makami na Allah, domin ku sami ikon da zaka yi tsayayya da dabarun Shaidan.*

*Afisawa 6:11*

Tsaron lafiyar ya yana ba daga gareni yake zuwa ba. "ya shaida wa hafsoshin nan a cikin ruwan sanyi "Daga Allah ne.

"Me yasa baka da niyyar biyayya ga gwamnati? In ji shugaban hafsoshin "Ba zan iya dakatar da yin bishara akan Kristi ba, domin shine hanyar gaskiya. "Inji Ahmed. "Yesu ya sauya zuciyata".

Hafsoshin suka tambaye shi game da takardun Kristi da aka yi dab'ia boye. Sun kuma yi tambaya akan wasu Kristoci da ayyukansu. Ahmed bai amsa wadannan tambayoyi biyu ba.

Daga baya yayi bayani yace, "Ban fada masu kome ba". Ba zan iya zama mai cin amanar rukanin Jikin Kristi ba," da aka ce ya rinka kawo rahoto ga yan sanda yace musu. "Wannan ba aikina bane"

A wani lokacin kuma, an sake kama Ahmed a kasar. Turkiya dauke da wata jaka da take cike da takardun Krista. Suka ce "Idan baka taimake mu ba, zamuyi cajinka da haddasa rudami ga gwamnatoci, "Ahmed ya amsa. "Yana so mu shaida kaunarsa da gafartawar sa.

***Yantsokana, sune yaran da ba sa daina yin surutu a cikin aji. Sune masu cin zali a makaranta da kuma kwacen kudin abincin yara. Sune yan tsegumi a wurin aiki suna bata wasu kuma suna yada jita-jita kamar cuta. Ba a kirawo Krista domin su zama masu tsokana ba Alhali ma dai Yesu yana kira garemu da mu zama masu sada zumunta. Wannan doka tana da mafita guda daya. Watau kin neman sada zumunta da Shaidan mu cakune shi mukishi har da hanyoyin sa duka. Kada muyi tunanin ko Shaidan zai kyale mu a zaman wadanda ba zasu iya yin wani abu ba. Addua ita ce muhimmiyar kayan yakin mu watau makamin mu. Shin addu'oin ka suna damawa Shaidan shirin sa? Shiga aiki tukuru yau ta wurin yin addu'a a cikin sunan Yesu gaba da shirin makiyin ka.***

# MATSANANCIYAR BIYAYYA

## Kasar Sin: Wani Pasto da Mahaifiyarsa

RANA TA 170

**An yiwa wannan pasto tambaya kuma ya sha duka akai akai, amma yau mai tsaron ya kai shi wani daki domin yayi magana. Ya ce, "Ina da doki akan addininka shi yasa nake so ka karanta mani dokokin Ubangijin mu guda goma din nan."**

*Amma da shike kuna tarayya cikin azabai na Kristi sai ku yi murna; domin akan bayanuwar darajar sa kuma ku yi murna; 1*

*Bitrus 4:13*

Abin ya baiwa pasto mamaki sai ya fara zana su, a lokacin da ya kai "Ka girmama Uwarka da Ubanka" sai hafsan ya tsaida shi. Tsaya a nan. Ku Krista kungaskanta cewa Allah ya zabi "ka girmama Uwarka da Ubanka a zaman doka ta musamman. Ka dubi gefen can, pasto ya juya sai ya ga wata tsohuwa da ke daure jikinta a kukkuje a karkashin wasu tsummokara. Ita ce mahaifiyar wannan Pasto. Mai tsaron hanya yace dubi dai yadda mahaifarka ta wahala, idan ba ka bude mana asirin abin da kukeyi ba zai nuna cewa ka kasa bin umarnin dokokin Ubangiji kenen na ka girmama uwarka da ubanka, idan ko ka kyale jininta na kanka.

Pasto ya juya wajen uwarsa wacce take farfadowa daga suma da tayi. Ya mahaifiyata me ya kamata nayi? Cike da kauna kuwa sai ta amsa masa. Tun lokacin da kake yaro karami na koya maka cewa ka kaunaci Kristi da majami'arsa. Kada ka yarda ka juya wa Allah baya. Ashriye nake na mutu adalilin sunannan Mai Tsarki. Pasto ya dubi mai tsaro da karin karfin zuciya ya ce, "Ka fadi daidai kaftin. Na farko lalle ne mutum yayi biyayya da uwarsa".

***Ko menene ya sa akwai wahalu a duniya? Masu shakka da rashin yarda sukan so su bata Kristanci. Ba su iya rabawa kaka Allah da yake mai kauna ne kuma yaya aka yi yana bari bayinsa masu binsa kuma marasa laifi su wahala. Alhali ma suna iya rinjayar Krista wadanda suke shan azaba cewa jarabar da suke shiga yana nuna cewa shirin Allah ya kauce. Wai shin shan wahala yana cikin shirin Allah ne da gaske? Wajen amsa wannan tambayar, duba a cikin rayuwar Yesu a duniya. Wahalar da yasha akan giciye shine tushen shiri na Allah, kana tafiya a inda Yesu yayi tafiya, zuwa giciye, zuwa kabari kuma a karshezuwa sama. Zaka gaskanta cewa Allah yasan abin da yakeyi koda a cikin zafi ko radadi da kake ciki.***

## MISALAI MASU TSANANI
### *Amirka: Uwar Sophia*

RANA TA 171

***A Shekarar 1996 diyarmu Sophia ta sami rashin lafiya da ya yi wa kwakwalwarta lahani, ta wahala da gaske na tsawon watanni, ta kanyi kuka don zafin ciwo na tsawon kwanaki uku a jere wani lokacin. A wasu lokuta ma ba ta iya shaida mutum.***

*Bayyanamu ne ku wasikar Kristi, abin hidimar mu, rubutatacciya ba da tadawa ba amma da ruhun Allah Mai Rai; ba cikin alluna na dutse ba amma cikin alluna da ked zukata na nama.*

*2 Kor 3:3*

Wata mai aikin jinya tace ita bata gane ko wadanne irin mutane ne mu ba muka ki muyi fushi da Allah wanda ya bar irin wannan abu ya faru damu. Nayi kokarin na taimake ta wajen gane cewa mufa bayin sa ne kuma ba zamu iya musun gagarumar kyauta da Allah ya bamu ta wurin dansa.

Watanni hudu bayan faruwar wannan rashin lafiya Sophia ta rasu. A ranar da ta mutu, naga wani hoto a cikin mujallar Muryar shahidai na wata yar'uwa yar Kasar Sudan wacce aka yanke mata nonon ta duka biyu a zaune, kusa da jaririnta. Masu tsananta mata sun azabta ta ta wurin irin wannan mugun abu na tilasta mata ta zauna haka ta yi kallon yadda danta zai mutu da yunwa. Ko da shike tsakanin mu akwai nisan mil dubunai. Na san irin zafin da take ji, kuma nayi kuka, ina tunanain bai kamata in zauna haka kawai ba na jin tausayi.

"Wannan matar da wasu kamarta basu da zarafi na samun kula da lafiyar su ta wurin maganin asibiti, haka kamar yadda mu muke da shi. Duk da haka sun shayin juriya mai yawa ni kuma ta wurin alherin Allah zan iya jurewa.

Ina da bukatar wadannan horarrun kalmomi na Ubangiji Yesu Kristi domin fahimtar cewa Yesu yana da rai kuma wannan duniya ba wurin zama bane

***A yayin da Allah yake tare damu a kalla ta wurin Ruhu Mai Tsarki muna da bukatar karfafawar masu jini a jika domin tagaza mana a cikin bangaskiyarmu, watau Shahidai da sauran masu bangaskiya daruruwan shekaru, su mutane ne na kwarai, wadanda misalan su na ainihi yana karfafa mu kuma yana iza mu gaskanta cewa watakila mu iya maida murtani kamar yadda suka iya yi. A yayinda ba lalle ne mu shiga halin da suka shiga ba, amma muna iya daukar salon dagewarsu da bajintarsu domin ta wani labari na matsanancin bangaskiya, ka na shaida wa wasu. Wasu ma su karu. A koya wa wasu domin su sami karfafawa daga wadanda suka rigaye mu, kuma suka bar misali da zasuyi mana koyi.***

# KI MAI TSANANI

## Russia: Serghey Mechen

RANA TA 172

***"Kristanci ba koyaswa ne da mutum zai samu daga littafi ko gargadi ba" inji Serghey Mechen a wa'azinsa, Serghey Mechen shine shugaban majami'ar unguwar Maroseyka ta birnin Moscow.***

*Allah kuwa na alheri duka, wanda ya kiraye ku zuwa cikin madawamiyar dora fatasa cikin Kristi bayan da kun sha wuya yan kwanaki, da kansa za ya kamala ku, shi kafa ku shi karfafa ku kuma.*

*1Bitrus 5:10*

A shekarar 1923, wata sabuwar gwamnatin kwaminis ta Russia suka kaddamar da abin da suke kira "Majami'a Mai Rai". Wacce ba kome bane illa gurguzanci amma a rufe da sunnan Kristanci Pasto Serghey ya fito keke da keke ya ki ya karanta rubuttatun addu'oin su kuma yayi wa'azin irin Allahn da kwaminis suka yurda a ambata. Sai yaci gaba da wa'azinsa na gaske ga mabiya, da sanin cewa mai yiwuwa ya sha wahala domin ki da yayi.

An tsare Serghey na tsawon shekaru biyar kuma an rufe majami'ar sa. Amma ina zaman bishara. Daga sake shi kuwa sai ya hada kai da majami'ar karkashin kasa yana bishara na tsawon lokaci ko wace rana har sai da tsohon paston sa da ya juya wa Allah baya ya tona asirinsa. Gwamnati kuwa ta biya shi da aiikin parfeso a zaman ladarsa.

Serghey yakan karanta kalmomin Yesu cewa "makiyayi mai kyau yakan bada ransa domin tumakin sa. "Ya tsaida shawara cewa bazai taba tone asirin yan'uwan sa ba a dalilin tsayawa tutur ga aikin Kristi, aka kashe Serghey ta hanyar harbewa da bindiga a shekarar 1941. Ransa ya tafi amma shaidarsa tana nan. Gaskiya bata sakewa domin biyan bukatar wani.

***Allah ba mai zuwa a takure bane, yakan zo ne a cikin cikakken ikonsa, in ko ba haka bane to wannan zuwan ba na Allah bane sam sam. Wani mutane sukan yi gaggawar fada cewa ba sa yin gaba da aikin Allah, idan fa Allahn da suke so a yi wa'azinsa ne sai kace suna cikin dakin da aka sayar da ruhaniya, sai su zabi wanda suke so kuma suke jin dadin sa akan bayi na Allah, sai su watsar da abubuwan da basa so. Halayen Allah ba sa sakewa. Muna iya misalta Allah ta wasu haniyoyi, amma babu shakka a karshe ba zamu ci nasara ba. Kada ka yarda da dukan wanda yake kamanta halayen Allah ta hanyar son zuciya. Zaka iya gane jita-jita in an fade ta?***

## SHIRU MAI TSANANI

### Romania:

RANA TA 173

**Da Pasto da matarsa tare da kannan yaransu guda shida sun karanta Zabura ta 23 a lokacin da suke karya kumallo. kwatsam sai ga yan sanda sun shigo musu gida domin su yi bincike kuma su kama shi,**

*Zaka rike shi cikin cikakkiyar salama, shi wannda yana kafe bisa gare ka, saboda yana dogara gare ka*

*Ishaya 26:3*

Yan sandan sun tambaye shi. Shin baká da abin fada ne? Baka da damuwa ko kuma kayi da-na-sani? "Sai Pasto ya fada musu a hankali, "Kune amsar addu'ar da muka yi a zabura 23, cewa Allah ya shiga tebur domin mu a gaban makiyan mu. Muna da tebur amma ba bu makiya. Yanzu kuwa gashi kun iso. Idan kuna bukatar wani abu daga kayan da ke kan teburin, zan so rabawa tare da ku. Allah ne ya kawo ku.

Ta kaka zaka yi irin wannan maganganun banza? Zamu kai ka kurkuku, kuma a can zaka mutu. Ba zaka sake ganin yayanka ba kuma, cikin natsuwa kuwa Paston yace, wannan ma munyi karatu a kansa yau, ko da na ratsa ta ramin inuwar mutuwa, ba zanji tsoro ba.

Hafsan nan kuwa, sai yayi ihu, kowa na tsorom mutuwa na sani domin nakan gani a fuskokin su.

Inuwar kare bata cizo, haka kuma inuwar mutuwa bata kisa. Kana iya kashe mu ko kasa a kurkuku, amma babu mugun abu da zai faru da mu.

Muna aikin Kristi kuma idan muka mutu zai kaimu zuwa duniyar sa.

***Lada da daraja na karuwa tamfar jari na tattalin arzikin zamani na rashin kwanciyar hankali da tarzoma. Amma abu mai dadi shi ne cewa dukan masu bi suna da hannun jari a cikin kyautar Allah ta wurin Yesu Kristi.***

***Amma mutane da yawa sun rasa wannan salamar, wadansu suna yin kokarin neman salama ta hanyar da ba na Allah ba kuma ko wane irin jin dadin su ba zai dore ba, sai a dawo cikin damuwa kamar da. Akasin haka salama ta Allah takan taimake mu wajen cin nasarar shan wahalar mu, babu wata jaraba da zata iya kawar da imaninka a gareshi. Kamar dai wannan kamilin pasto, ko da shike damuwa na iya zuwa cikin bazata sami zama a shinye tare da kyakkyawar salama ta Allah.***

# TUNANI MAI TSANANI

## *Russia: Dan Sarki Vladmir*

RANA TA 174

***Motsa shi! Inji mai tsaron yana duniya, ya cafke hannun saurayin yana cewa bari mugani ko zaka sa sabon muhalinka. Masu tsaron suka ingiza kayar dan sarki Vladmir daga gidansa na sarauta ta Ghica zuwa cikin kurkuku. A gefe guda ya ga, fursuna suna diban tufafi da bayanna daga cikin wani mattacen fursuna. a can baya kuwa yana jin kukan radadi na fursunan da ake azabtawa.***

***Salama kuwa ta Allah, wadda tafi gaban ganewa duka zata tsare zukatan ku da tunaninku cikin Kristi Yesu.***

***Filibbiyawa 4:7***

Wannan wuri ya sha bam bam ainun da, rayuwa ta jin dadi da ya saba da shi a gida. Duk da haka Dan Sarki Vladmir ya haye irin kaskancin da ake yiwa rayuwar dan adam a kurkuku ta wurin mannewa bangaskiyarsa a cikin Kristi wanda ya sanyaya masa zuciya kuma ya bi dashi. Abokin dakin kurkuku, tare da Vladmir ya taba cewa. Babu inda na taba jin addu'a masu tsarki da tunani masu daraja irin ta ruhaniya sai a kurkukun kwaminsawa.

A wallafa irin wadannan tunani na Vladmir masu koyarwa a littafi. Ya rubuta. Masu albarka ne su wadanda yake faruwa a lokacin da suke cikin shan wahala. Shi wanda waki kansa a dalilin taimakon wani, yana sutura kansa da Kristi. Ka nemi agazawa wanda bai tunkare ba. Kayi bayaswa ga wanda bai tambaye ka ba. Ka kaunaci wanda yake guje maka. Ina roko kada farinciki na ya zo ta wurin shan wahalan wani ko wasu. Ina roko shan wahala na ya kawo farincikin wasu.

Wanene zai taba mafarkin cewa irin wadannan addu'oi da tunani masu daraja zasu iya samuwa da saukakken Dan sarki wanda ya haye azabtar kurkukun kwaminis.

***Tunani mara kyau in ya yawaita yana iya yiwa mutum lahani. Idan muka aza zukatanmu ga wahalan da muke sha, zamu zama masu dacin zuciya Idan kuwa muka zabi yin tunani masu kyau koda muna cikin wahala ko damuwa, sa'anan zamu samu cin nasara cin al'amuran mu. Ba wai kadai zamu fitar da kanmu daga karyar zuciya da yanke kauna ba amma kuma zamu iya taimakon wasu. Vladmir ya yi farinciki a yayin da yake shan wahala. A yayin da kake cikin jaraba ko damuwa yaya tunanin ka yake? Kakan yi tunanin kila abubuwa marasa kyau ne zasu faru da kai? Ka tuna, ba ka da ikon juya akalar abubuwan da ke tafiyar da rayuwa. Amma kana iya wa naka hali. Ka guje wa mugun tunani ka roki Allah ya baka tunani mai kyau yayin da kake cikin damuwa kuma ka bude idanunka don taimakon wasu.***

***Zuciya bata da kwanciyar hankali har sai ta kai ga hutawa a gareka.***

**ST. AUGUSTINE**

# MATSANANCIN WALIYYI

## Russia: Dan Sarki Vladmir

RANA TA 176

***"Kada kayi", Nicholas yayi ihu a yayin da ya ga mai gayawa-jini-na-wuce ya daga takobin sa don ya fille kan wani fursuna. Baiyi laifin da yakai ga irin wannan hukumci ba," Ana, dab da hallaka wannan mutum ne domin bangaskiyar sa a cikin Yesu Kristi. Nicholas yayi bajintar cabke takobin daga hannun mai aikata aikin kisa a kurkukun kafin takobin ya kai taba jikin fursunan.***

*Kayi kamar Ubangijin ku ya tsarkakansa duka. Ubangiji yana kiyayya da masu aminci.*

*Zabura 31:23*

"Ka yi yadda kake so Nicholas... Ina da wasu mutane da yawa dazan kashe su a yau," mai aikin kisan nan ya tsarta miyau a yayinda ya juya baya ya kama hanyar tafiya don yaci gaba da aikin sa a wani gurin.

Nicholas yayi maganan domin Kristi a fili ba tare da fargaba ba a mayuwacin lokaci na tarihi. A shekaru 303 Sarki Diocletian ya fara daya daga cikin mugun tsanantawa Krista. An kashe Krista masu yawa har yakai ga ajiyarda, masu kisar domin kuwa har karba-karba sukayi da juna wajen kashe mutane.

An sawa Nicholas lamba da jar wuta ta katfe. Ya sha duka sau dayawa a hannun masu tsaron amma ya tsira bai mutu ba kuma ya jimre wa azabu masu yawa-karum domin yaki ya yi musun Yesu Dan Allah ne. Ta kaka zai yi musun abinda yake zahiri ne a gareshi? Nicholas ya tsaya a dage da bangaskiyarsa a tsakiyar rashin adalci mai tsanani.

Bayan an sake shi daga kurkuku yayi dukan rayuwarsa wajen kafa gidajen marayu kuma yana taimakawa yara. Ya badakansa ya ciyar da bisharar Kristi gaba ta hanyoyin masu azanci. Har ya taba jefo kudi a kunshe cikin safa ta tagar gidan wadansu yan mata guda biyu kuma matalauta ainun domin kada a sayar da su ga gidan karuwai.

***Shekaru da dama bayan mutuwar sa aka rada masa mukami na zama Waliyyi watau ya zama Waliyyi Nicholas. Ga yana da yawa, ranar jajibirin Krisimeti ita ce rana mafi inganci a garesu domin ita ce ranar da yara ke jiran isowar Santa Claus wannan kuwa kirkira ce ta St. Nicholas. Ainun labarin rayuwa game da St. Nicholas yana da jarumtaka da nuna kauna fiye da yadda yara suka yi tsamani. Kayi tunani akan naka labarin rayuwa. Ko mutane sun san gaskiyar game da gaskiyan bangaskiya a cikin Kristi? Ko da shike Santa Claus ba zahiri yake ba. St.Nicholas zahiri ne, kuma kaima, haka, ka iya jin kamar waliyi kake amma duniya tana bukatar tsayayyun masu bi. Me zaka yi yau domin nuna bangaskiyarka ta zahiri.***

# MATSANANCIYAR YARDA

## *Baitalami: Maryamu Uwar Yesu*

RANA TA 177

***"Ba ta haka na hangi yadda za mu fara samun dan mu na farko ba: in ji budurwa da ke kan gwiwa. "Ta tambayi saurayin da ke tashinta watau Yusuf.***

*Maryamu ta ce, gani baiwar Ubangiji, bisa ga fadin kashi zama haka*

*Luka I:38*

Ban sani ba, masoyiyata, in ji shi cike da damuwa, "Amma abin da muke da shi kenan, na sani Allah zai kiyaye wannan jariri. Babu shakka Allah ya na da shirinsa domin mu shi yasa ya nufi da a haifi wannan yaron annan.

A lokacin da ta sake jin zafin yunkurin nakuda, saurayin ta ya bada shawara ta yi kokari ta nufasa da karfi." Ya fada mata haka kuma yana share mata fuska da jikakken kyalle. "Ki kara jimrewa ... ba da jimaya ba zaki sauka."

Da cizon hakora ta amasa, naso na haifu a gida na, na so da uwata tana wurin dominta taimake ni". Ai gani, ina nan ne domin na taimake ki, in ji Yusufu, saboda haka sai muci gaba don kan mu. Kuma dukanmu mun sani "Allah yana nan tare damu. "Sai yayi mata dan wasa in har muna da bukatan karin taimako ai ga shanu da tumaki kusa da mu.

Nakuda ta wuce, kuma, Maryamu ta dubi saurayin ta tayi murmushi. A zagayowar wata nakudar. Maryamu ta fara nunfasawa tana turawa. Jim kadan kuwa danta ya fito duniya. Suka sa masa suna Yesu kamar yadda mala'ika ya bada umarni. Wasu lokuta mukan manta da irin wahalu da maryamu da Yusufu suka sha kuma suka jimre wajen haifuwar Sarkin Sarakuna, barga ne dakin haifuwa, gudun hijira zuwa Kasar Masar, talauci da tsegumi.
Duk da haka sun jimrewa komi da yardar rai domin kaunar Allah da ke cikinsu.

***A yayin da muke karanta Littafi Mai Tsarki muna iya saurari cewa gaskanta allakawarin Allah zasu fi saukin yi idan ya shirya su da wasu tabbattun alamu, kamar dan aikan mala'ika. Duk da haka ko maryamu ma wacce ta sami irin wannan alama, ta yi irin wannan shakka. A lokacin da mala'ika.***

***Jibra'ilu ya shaida wa Maryamu cewa zata haifi Dan Allah, watakila labarin ya razanata cewa wannan ba abin da za'a tunanin yiwuwar su bane. Ta tambaye mala'ika ta kaka wannan zai yiiwu, tunda ya ke ni budurwa ce? "Duk da damuwar da ta nuna, Maryamu ta zabi ta gaskanta alkawarin Allah, kuma ta yi biyayya da haka din. Yardar ta ya kawo cika shirin Allah na kawo ceto ga dukan duniya ko Allah yana kira gareka duk da shakka kakeyi? Kamar maryamu yardar ka tare da biyayya yana iya kawo cin gaba madauwami ga mulkin Allah.***

# MALLAFA MATSANANCIYA
## *Romania: Dumitru Bach*

RANA TA 178

***Dumitru Bacu wani Krista ne da ya yi fursuna a shekarun 1950 da 1960. Kamar da wasu da yawa, laifin sa shine zama Krista, Dumitru yayi anfani da zaman kurkuku na shekaru ashirin wajen walllafa wakoki na kauna ga Allah. Ya rubuta baitocin a hankali cike da lura a jikin sabulu yakan kusa ko kuma ta wata alama ta musamman na kwanakwasa da sake zuwa zuwa daki har sai dukansu sun koya.***

*Gama na rigaya na koya, zaman danika cikin ka dukà, raina ya kwanta da shi.*

*Filibbiyawa 4:11*

Zafin ciwo da ke raunan jikunan mu kuma ya gajiyar da mu ba sa iya iko da zukatan mu," Haka bacu ya fadi bayanan sallamme shi daga kurkuku. Maimakon kiyayya, mun girbi kauna, fahimta da hikima."

Ga daya daga cikin wallafarsa wacce ya shirya a dakin kurkukun daga-kai-sai-kai inda yake cike da beraye, kudin cizo da kwarkwata.

Yesu ya kayyana a dakin kurkuku jiya da dare, yana da tsawo; ya nuna bacin rai, amma haske ne shi Hasken nuna dake shigo mai ta kafofin ramuka sun dishe ga firgita ga farin ciki, sai na dube shi ya zo ya tsaya a gefen tabarma ta a tsanake ya nuna mani irin azabar da ya sha tabbunan sunanan duka, a hannayen sa duk kafafun sa da wanitabon a gefensa, inda zuciyar sa ke bugawa yayi murmushi, kana ya tafi sai na fadi akan dutse Ni kuwa nayi kira a gareshi. "Ya Yesu kadaka barni ni kadai. Da yake ina rike da karfafan kurkuku harsun huda tafin hannayensa. Bayarwa mai albarka, tabbuna masu albarka.

***Halin zama a kazamin dakin kurkuku da rashin yanci ba yanayi ne maikyau da zai baiwa mawallafi damar yin tunani mai kyau da zai sashi iya kirkiro baituna masu azanci ba. Amma Dimitru ya juya wannan yanayin na wahala da azaba ya maida shi wata dama na yabon Allah da kuma kosarda rayuwar wasu domin Kristi. Wahala da yake sha suka zama kamar ba kome bane idan ya kwatanata da azabu da Yesu ya sha a madadin sa. Jin irin abubuwan da Dumitru ya fuskanta, masu bi da yawa zasu dauka cin kaskan yadda su maimakon su zama masu koyi da kuma samun karfafawa. Wasu ma su yi shukka suce shin Allah yana kula damu kuwa!***

***Wallafa wakoki baiti baiti na yabon Allah abu ne da ya kamata ya nisanci tunanin mutane a cikin irin wanan mayuwancin hali. Amma duk da haka Dumitru ya juya dadaita al'amuransa ga Kristi mai makon sa tunanin sa ga kazamin dakin kurkuku da yake ciki, saboda haka kuwa sai ya cika da yabo. A lokacin da wahala ko damuwa kaka kake yi? Shin zaka ga wannan a zaman dama ce ta yin yabo da bauta ga Allah.***

# MASHAWARCI MATSANANCI

## *Romania: Anutza Moise*

RANA TA 179

***Bayan da kwaminisawan Soviet suka kwace mulki a Romania anyi farautar Jamusawa domin sun tausayawa Nazi. Anutza Moise yayi shawarar ta boye mutanen nan dai da suka nuna mata kiyayya domin ita bayahudiya ce kuma Krista. A lokacin da ta bada kanta ga taimako wajen boye wadannan mutane daga kwaminisawan, sunyi shakka ko aniyar ta na ainihi ne.***

*Ku kaunaci makiyan ku, ku yi alheri ga wadanda suka ki ku.*

*Luka 6:27*

*Filibbiyawa 4:11*

"Baki iya tunawa bane cewa mudinnan mune muka aika ki a kurkuku? Daya daga cikinsu yayi wannan funci.

"Kwarai kuwa na tuna" in ji Anutzai "Amma ni Krista ce, kuma Allah bai bani damar riko ko hikidu ba. Na gafarta maku, kuma gashi na sami wata dama na taimaka muku. Yesu yana kaunarku, ni ma ina kaunar ku.

Wannanm irin kauna nata ya basu mamaki har da yawa a cikinsu suka karbi Kristi ta wurinm ayyukanta.

Ita kuwa tare da Richard da Sabina Wurmbrand da kuma wasu, sun debi kananan yara wadanda suka hallakar da iyayensu a sansanin azabtarwa wai don su yahudawa ne kuma aka rene su sosai. A karshe Anutza ta kaura zuwa kasan Norway inda tayi aiki tare da Kungiyar Yahudawa masu Bangaskiya. A cikin wanan aikin ne ta shugabanci gwagwarma yar tara zunzurutun kudi har $10,000 (Dala dubu goma) domin biyan kudin fansat fito da paston ta Richard Wurmbrand daga kurkukun da ma Romania gabaki daya. Anutza da kanta ne kuma ta dauki dawai niyar shirya tafiye tafiyan sa da shi da matarsa da kuma dansu Mihai zuwa karsahen Turai. Idan da ba tare da kauna da tsayawa da Anutza ta yi a madadainsa ba, da mai yiwuwa da sanannen pasto kuma wanda ya kafa kungiyar manufar Shahidai ya mutu a kurkukun kwaminmis.

***A lokacin da Allah ya kiramu cewa mu bishi kuma muka amsa, to ma'anar wannan shine binsa koina kuma muyi dukan komi kuma kome kasadar yin haka. Haka kuwa Anutza ta karbi wannan kira da gaske, kuma tayi aiki cikin kauna da gafartawa ga makiyanta. Aikin baiwa makiyin ta zabi nuna kauna maimakon dacin rai da tunanin yin ramaki kuma ta bi misalin Kristi na nuna kauna. Me Allah yace maka kayi? Kada ka kuskuri yin hasarar anfani da dukan damar da ka samu na yin***

## TUNINI MATSANANCI
## *Iran: Wani Pasto da ya sha Tsanani*

RANA TA 180

*Gama kuncin mu mai sauki, wan dake na lokaci kadan. Yana aika domin mu nauyin daraja ma da wani gaba gaba kwarai*

*2 Kor. 4:17*

***"Wasu lokuta na kanyi tunani kamar jiya ta dawo yau watau zamanin shan tsanani!***

Wadannan kalmomi sun fito ne daga bakin wani pasto dan Iran (Kasar farisa). Wanda ya tare zuwa kasar turai.

A kasar Farisa kamu da dama hankalin masu bi ya zama jikin harma ya rasa gidansa da kuma aikinsa a dalilin bangaskiyarsa. Yanzu kuwa gashi ya sami yancin rayuwa da kuma yin sujada a duk lokacin da yake so. Ta kaka kuwa zai yi tunani ko duba baya galokacin tsanantawa.

"Wasu lokuta na kanji kamar jiya ta dawo yau," in ji shi domin a lokacin a tsaye nake daram, a kulluma a wannan lokaci naknji lalle Yesu yana tare dani."

Wannan pasto ya kafa majami'a a kasa da bakin daga na yakin Iran da Iraq. Yana sana'ar tuka motar hanya (Taxi) kuma ya tada majami'ar ta wurin ta wurin yiwa fasinjojon sa bishara a cikin shekaru biyu ya sami masu tuba daga harsuna guda tara. Sojojin yawa suna sujada tare da shi a kowane mako, kuma yayi wa musulmi goma sha biyar da suka tuba baptisma.

Wannan pasto tare da matarsa sun yi dogaro ga Allah game da dukan abubuwan da suka yi. A yayin da bom na yaki da akeyi kewaye dasu ya fadi kusa dasu ya fashe sukan yi addua domin tsaro daga Allah a lokacin da basu da isashen kudi sukan yi addu'a domin Allah ya basu kuma kuma a kowace rana Allah yana huwace musu.

Sun sami ladar aikinsu na bisahara goma daga cikin mambobinsa su zama yabanya daga lokacin bishararsa ta bakin daga.

***Idan baka taba yin sujada ta kauna ba, ba zaka taba gane ma'anar makaunaci ya juya maka baya ba. Idan ba ka taba rasa makaunaci ba, da wuya ka fahimci abin da mai rashi yake ciki. Ba zaka iya gane. Ba zaka iya fahimtar wata fatar jiya ta dawo yau irin na dabon. Ba wai suna fatar sake shiga tsanani bane amma suna fatar samun hada kai da zumunta da tsananin ya kawo musu a wannan lokacin, ba dokin azabtar suke yi ba amma suna dokin ribarda azabar su koya musu. Sakamakon alheri da aka samu a karshe ya ribanya azabar da aka sha. Idan kana so kayi tafiya mafi zurfi da Yesu, lalle ne ka zama mai bada kanaka kuma mai sadauda domin sa, wannan irin shan wahala ne domin su.***

# FURTAWA MAI TSANANI

## Russia: Peter Siemens

RANA TA 181

*Magana akan kari. Tana kama da tunawa na zinariya cikin kwanduna na a zurfa.*

**Misalai 25:11**

**Pasto Siemens yana kwance akan daben kasa a dakin kurkuku na Russia bayan doguwar suma na kwana uku. An tsare shi ne domin yayi bishara ga kananan yara. Abokan dakin sa na fursuna sun yi masa dukar-kawo-wuka wai don masu tsaro sunyi musu alkawarin shika in har suka yi haka din.**

**A yayin da suka kai masa hari kuwa Peter bai ce musu uffan ba.**

Da suka ga ya farfado daya daga cikin fursunonin ya tambaye shi, "Meyasa baka yi kuka ko ihbu ba a yayin da muke dukan ka?" Mamaki nakeyi ko dan radin kanku kuke yi mani duka, ba tare da izinin mai tsaro ba, Peter ya bashi amsa da lebuna a farke jina jina. Idan haka ne, kuma da nayi ihu da za'ayi muku horfo domin karya dokar kurkuku, bana son kusha wahala, domin Yesu yana kaunarku haka ni ma.

Wannan furfici da Peter yayi ya rinjayi zukatan wadanda daga rarun masuu laifi da ke tare dashi a kurkuku. Sai suka aika da sako ta hanyoyin su na yin haka a kurkuku cewa kada kowa ya tabashi. Koda wani kurkuku aka kai shi ko kuma wane irin alkawari na kyauta aka yi musu.

Wasu fursunoni da aka yanke wa shari'ar kisa, kuma suna jiran a kashe su a kurkuku suka sami labarin Peter sai suka aika masa cewa suna bukatar taimakon sa. Peter ya amsa, kuma ta hanyar wasu masu tsaron kirki, ya shaida musu bisharar kaunar Kristi watakila ma wasu daga cikinsu sun karbi kristi kafin a zartas musu da hukumcin su na kisa a dalilin bisharar da Peter yayi musu.

Zaman sa na yin misali da kauna Kristi ya kawo muhimmiyar dama ga wasu, Su wadanda da ba don wannan ba, ba zasu taba jin labarin bishara ba.

***Furta magana yana zama abu mai iko kwarai kalmar shawara da akayi anfani da ita akan kari, kauna ko karfafawa takan tafi da nisa a yayin da wani yana aikin bukata. Amma yaya batun lokacin da mutum yana cikin bukatar ruhaniya? Kamar da Pasto yake da ita ga Kristi ita ta iza shi yayi amfani da wadannan kalmomi da ya mora. Wannan kamar ita ta bashi karfafawa yin shaidar kauna Kristi ga makiyansa adaidai lokacin da ya kamata su saurari maganar. Peter kuma yayi amfani da kalmomin peter domin ya juyo da abokan kurkukn sa zuwa ga manufa madawwami domin kawo ka ga Yesu? Idan Allah ya kira ka da ka shaida wa wani akan Yesu, zaka yi biyayya da shi a lokacin? Kayi la'akari da bam bamci madawwami da kalmominka da misalin da za'a yi koyi da shi daga halayen ka zasu iya yi.***

***Tsanani baya iya dauke mu daga gidan mu, tsanani yana taimaka wa wajen bi damu bisa turba ta tafiya zuwa "gidanmu" na ainihi.***

***Pastor J, Colaw***

## SABAWA MATSANANCI

### Gabashin Rurai: Shahararren Mai Bishara

RANA TA 183

*Dole mu yi ayyukan wanda ya aiko ni tun da sauran ran dare yana zuwa in da ba mai iya aiki ba.*

*Yoh. 9: 4*

***Shahararren mai bisharanan ya yi magana ta bayan karafan kurkuku. Gogaggen mai wa'azi, fitacce ne kuma koina a Gabashin Turai, yana bayanin yadda ya kasa samun salama. Wannan mutumin ya kawo dubunan salama. Wannan mutumin ya kawo dubanan mutane ga Kristi, saboda haka su dau yan Krista wanda suke fursuna ne suka kasa gane abin da yake sa shi jin cewa ya gaza.***

"Na yi bishara a wani taro na Krista, nayi bayani na fadi abin da ke zuciya ta kuma, kuma a karshe mutum dan biyu sun fito gaba sun karbi Kristi. Zuciya ta ta motsu don tsananin jin dadi amma kuma gashi na gaji tikis. A lokacin da nake barin wurin wani saurayi yazo guna, "Pasto, ina so in yi magana da kai, in jishi, sai na ce masa na gaji kwarai, ko zai iya dawowa da safe. Bai sake dawowa ba. Daga baya kuwa yankwaminis suka kama ni a wannan yamancin. Aka ta yi mani tambayoyi babu saurarawa, dare da rana har kwanaki biyar. Na amsa dukan tambayoyin su. Na amsa domin ina taron azantarwa da duka da zan sha idan ban basu amsa ba. don tsananin tsoron kwaminis, na iya in magana har na kwana ki biyar dare da rana babu tsagaitawa.

Amma ta wurin kauna ga Allah, na kasa saurawa inji magana ta minti biyar ga wannan saurayi wanda yake neman hanyar tsira. Wace irin tsayawa zanyi a gaban Allah nayi lisafin kawo mutum dari biyu kawai ga Krista a wannan ranar don kuwa da don biyu daya zasu zama.

***Muna iya zabin rena dama da Allah ya bamu ne na yadda bisharar Kristi ga wasu, da tumnanin cewa ai zamu iya yi daga baya, kokuma mu yi tunanin cewa zamu samu lokacin da yafi dacxewa. Amma tana iya daurdowa ba zamu taba samun wata dama ba. Lokacin da mukeyi muyi amfani da zarafin da Allah ya bamu. Mu ma kamar wannan mai wa'azin ba zamu ankara ba sai muga lokaci ya sullube mana watau wata dama da ba kasafai take samuwa ba. Abin tausayi ma shine yana iya zama ma wannan shine lokaci kadai da mutumin yake dashi da zai sami damar jin maganar Allah takyautar rai na har abada ta wurin Yesu. A sama maiyi wuwa Allah ya tambaye ka ko menene dalilin ka na rashin yiwa wani bishara bayan kuwa ka sami damar yin haka? Wace irin amsa zaka bayar?***

# KYAUTA MATSANANCIYA

## *Kasar Sin: Wata Diya Matsananciya*



*Yan'uwa kadan jarabobi sun same ke, ku maishe shi abin farinciki sarai*

*Yakub 1:2*

***"Ina so nayi magana da ke akan wata kyauta da ta fita dabam, "In ji wani wani mahaifi dan kasar sin yana fadawa diyarsa kyakkyawa mai bakin gashi. Tayi murmushi da nuna dokokin ji. Ta kanyi dadi sosai duk lokacin da mahaifi ta mutum mai hikima ya tattauna batun maganar Allah tare da su. Yana kaunar Kristi kuma duk wanda ya san shi yajanyi sa'awar tausayi dajinkansa.***

Ya bude wani tshon kodadden Littafi Mai Tsarki ya fara, "Wannan kyauta ana samunta ta Filibbiyawa 1:29 tana cewa. Gama an kudurta a garfeku a madadin Kristi ba wai kadai a bada gaskiya a gareshi ba, amma kuma a sha wahala domin sa. Duk wani abu da aka ce ya bayar ya ya zama kyautar. Kyauta guda biyu a wannan aya sune bangaskiya da shan wahala. Shan wahala wanda yake tasowa daga bangaskiyar mu ga Allah kyauta ce musamman wanda sai a sama ne zamu fahimci darajarta.

Diyarsa tayi murmushi tace na gode baba, kuma na gane. Wannan yarinyar tayi girma har ta zo ta zama matar pasto Li Dexian wanda ya sha kamu fiye da sau goma ya sha duka kuma har kusan ya mutu domin bangaskiyarsa. Takan yi aiki tare da shi cike da jimirin domin ta koya tun tana karama cewa shan wahala domin Allah bangaskiya ce. Pasto Li da matarsa sun kawo rayuka da yawa ga Kristi a Kasar Sin ta kwaminisanci, kuma suna gaba da aiki a tsakiyar tsoratawa ne tare da su kullum.

***Baiwa ta gaskiya, da baiwa ta shan wahala shine na sukutum, da suke tafiya tare. Babu alamar a rabasu domin kowace baiwa ta kan karfafa yar uwarta. Idan baiwar mu ta vada gaskiya ga Kristi ne, to lalle zamu bi Kristi. Bin Kristi yanha nufin daukar kasada, yin gaba da wadansu sanan nan al'adu, ka sa gane manufarmu, kai har jimrewa ciwo na jiki da lamiri. Galibi bangaskiya ya kan kai mutun ga shan wahala. A yayin da muka dandana shan wahala kama irin na Yesu, wannan yakan kawo ga karin sanion Yesu kwarai. Shan wahala yana karfafa bangaskiyar mu. Kada ka zaci za ka iya tace shan wahala daga rayuwarka ba tare da rage karfin bangaskiyar ka ga Kristi ba.***

# MATSANANCIN MARUBCI

## India: William Carey

RANA TA 185

***"Sam basu iya yin wannan ba "inji 'William. "Baka ganin rashin daidaitar yin haka?"***

"Duba yawancin mutanen garin nan suna tunanin cewa dai ya kamata ayi", in ji kidimammen jamiai'ar gwamnatin. "Abin ya shafi addinin su: William ya yi tambaya. Ta kaka daure mace mai rai a jikin gawar mijinta kuma a kone tare zai zama abu ne da ya dace a yi?"

*Yesu kuwa ya zo wurinsa ya yi zance da su, yace, dukan hukumci a cikin sama da kasa an bayar gare ni. Ku tafi fa ku a:!majirantar da dukan al'ummai, kuna yi musu baptisma zuwa cikin sunan Uba, da na Ruhu Mai Tsarki.*

*Matta 28:18-19*

Da jin wannan, jami'un gwamnatin nan ya mika hannu, yace "William, ya amsa mutum kadai zai iya sauya wannan al'ada ba, ka hakura kawai ka koma wajen kula da garken ka?

Tun da darikar sa ta ce "Allah shi kadai zai juya mutanen da ke cikin duhu a kasashen da basu yarda da Allah ba. William ya yi burus da su ya tasam ma daya daga cikin tafiya mafi nasara ta aikin bishara a tarihin majami'a. Bugu da kari ka koyi magana cikin harsuna da dama kuma ya wallafa littafi da ya zama tushe, na sannin tubar masu yin bishara na zamani. Kuma ya fassara da sabon alkawali zuwa harsuna talatin da hudu (34) tsofon alkawali kuma zuwa harsuna takwas (8).

William Carey yayi aiki na shekaru da dama gaba da wannan muhimman al'ada na kona mata da ransu tare da gawar mazan su. Sannu a hankali, duk da kiyayyar gwamnatin kasar Indai, yaci nasara da smun gwamnati ta haramta wannan al'ada.

Carey yayi anfani da rayuwarsa a zaman makikiri domin Kristi. Tare da fuskantar mayuwantar halaya domin ya kawo bambanci mai ma'ana. Kuma an san shi da karfafa ja'ama da su sa rai ga abubuwa masu kyau ga Allah, ya tunkari manyan abubuwa domin Allah (bisaga Ishaya 54:2-3) haka kuwa William Carey ya yi.

***Mutane sun kasu kashi-kashi a yayin da aka shiga yin batun bangaskiya, masu tafiya sosai masu tafiya a hankalai da marasa tafiya. A yayin da Yesu ya kira masu bi da su shiga cikin duniya su almajirantar, wasu sun amsa da marmari kwarai. Kama, William Carey, sukan tafi kuma su kara tafiya domiin bishara. Haryanzu wasu suka amsa, amma rabi da rabi, suna amaja ga ka shekaru na karuwa ko kuma kawo hujja da da batun aiki yayi yawa babu lokaci. Abin damuwa shine masu bi da yawa suna cikin wannan rukuni na Krista masu amaja. Sun saurari umarni amma sai su ji wannene ya kamata ya cika wannan umarni ba su ba. a wani rukuni kake na amsa kiran Yesu zuwa bishara? Ka roki Allah ya sabuntar da bukatar ka ta shaida ban gaskiya ga wasu. Idan kana sa rai ga manyan abubuwa daga ansara, to ka zama da shirin fuskantar manyan abubuwa a cikin surransa.***

# MATSANANCIN SAHIDAI NA DA
## *Rome: Chyrsanthrs*

RANA TA 186

**"Dana, ka san wannan abu cewa, Yesu tabbattcce ne, "Inji mahaifin Chyrsantheas.**

*Amma kai, ya Ubangiji ka ṭabbatar har abada; ma tuninka kuma har tsararaki duka.*

*Zabura 102:12*

"Gaskiyane nasan da haka baba, inji Chyrsanthes. Na bada gaskiya cewa Yesu ya zo cikin duniya domin ceton masu zunubi ramar ni da kai. Shine hasken duniya. Babu bege ga gumakai dakake wa sujada".

Ubansa kuwa don jin haushin abinda ya fadi sai ya kule shi a dakin kasa mai duhu a zaman horo na kwanaki, amma duk da haka sai yayi ta jin yaron yana wakoki yabo ga Allah. Wajen kokarin juya bangaskiyar Chyrsanthes, babansa yayi kokarin kewaye shi da kayan alatu, da yan mata, amma Chyrsanthes ya dage. Sai uban ya kawo Doris wata mata mai bautar gumaka kuma ga ta da tsananin kyau a cikin gidansa domin ta sa shi ya manta da Kristi. A maimakon haka Chyrsanthes ya kawota ga Kristi, kuma aka yi mata baptisma.

Daga baya Chyrsanthes da Doris suka yi aure kuma suka ji dadin yin bishara tare suna kawo masu tuba ga Kristi: Duk yayin da masu tsaro na Rome suka yi kokarin su daure shi sai igiyar ta zabar daga hannunsu. Gwama ta umurci sojojin da su daure Chyrsanthes a jikin magodarar gini suyi masa duka da sandar karfe amma dukar ba ta wata abu ma a jikinsa ba sakamakon haka ya sa shi gwamman da masu tsaron suka fadi a gabansa furta laifofinsu ga ikon Allah.

A kasar da ake bautar gumaka Chyrsanthes ya yi fice domin ya gaskanta Allah mai rai, ba duwatsu ko sassaka ba. a dalilin jimrewarsa marasa yarda yanda da Allah da yawa sun bada gaskiya.

***Bisharar Kristi ba sabon ɗabu bane. Ta dade tana rayadda mutanen a shekaru aru-aru, kuma zata ci gaba da yin haka har dawowar Yesu zuwa duniya. Labarun da sune na yanzu. Shahidan Krista da suka sa tufafin da aka dinka da hannu kuma suka yi amfani da takalmin fada zukatansu ba su bambamta da na Shaidan, zamani ba ya iya bambamta wadanda suka bar wasiya ta bangaskiya a da da wadanda suke dauke da ṇasara yau. A wane matsayi kake a cikin wannan labari? A shirye kake ka kamata shaidar ka da ta Wiliyyan da? Ka ma yi cikakken ẓaman rayuwa irin da Kristi yayi yadda zaka bar wasiya domin na baya. Kana iya taimakawa ga sauya rayuwar iyali, ko ma'aikata ko yan unguwa, ko kuma ma kasa gabadaya domin Kristi.***

# ALMAJIRCI MATSANANCI
## Urshalima: Yakub Dan Zabadi

RANA TA 187

*Zan nuna maka bangaskiya ta ta wurin ayyuka na*

*Yakub 2:18*

***Tarihi ya koya mana cewa mutumin da aka umarce shi da zartas da hukumcin kisa akan Yakub ya ki yin haka din. Sarki Hiridas ya fille kuwunan su su biyu watau da wanda aka zartar masa da hukumcin, watakilama yaki aikata hukumcin. Watakila ma ga yadda abin ya faru:***

An shirya zartas da wannan hukumcin kisa, a rana ta musamman, watau ranar juma'a Idin Paska, misalin shekaru goma sha hudu bayan giciye Yesu an kai Yakub. Dan zabadi dakin da ake ajiye sojoji da dama. Fitilai

A-ci-bal-bal da ke dakin ya haskake wurin ga alamun jini akan daben dakin. Masu bin Yesu Kristi guda nawa ne suka rikgaya suka tafi ta wannan hanyar kafin shi a wannan dan dakin?

Yakub ya dubi idanun mai tsaronsa amma mai tsaron sa ya kauda fuskar sa, zuciyarsa kuwa cike da damuwa. Yakub ya sha yi masa bisharar Yesu ta karamar taga na kurkuku mai bishara ta shige shi. Yanzu kuma sai gashi abokinsa ya zama mai zartar da wanan hukumci na fille kansa da Yakub.kuma ba tare da kunya ba ya durkusa. Lokacin da aka daga takobin sama sai takobin ta girgiza ta kanyar bazata, kubce ta fado kasa kusa da Yakub, ba tare da fama shi "Ba ba zan iya ba" shi mai aiwatar da kisan ya fada da karfi. Ba zan kashe shi ba! Abin da yake fadi akan Yesu gaskiya ne bazan iya kashe bawansa Yakub ba.

Da ganin haka sai sarki Hiridus ya sa a hada har da shi, sojoji kuwa suka kabke shi suka daure hannuwan sa ta baya. Suka danne shi zuwa ka dabe inda Yakub yake a durkushe, kuma aka fille musu kawuna.

***Bada shawara sannannen batu ne ko a sha'anin rayuwar duniya ko na ruhaniya. Da alama ana tara jama'a suna lura da babban amfani da hulda ta tsakanin mutum da mutum da mutum ta taimakawa. Daya yana da abin da zai boyar ta hanyar koyarwa. Yin la'akari da wani wanda yake bin Kristi sau da kafa kuma ayi koyi da haka shine ma'anar karbar shawara ta ruhaniya. Wani Krista ya nuna wa wabi yadda zai yi ratuwa ta ruhaniya akaice. Wanene zaka ambata a zama Uba-nabada shawara a ruhaniyance a ga rayuwarka? Wane hali na kamanta Kristi ka gani a rayuwarsa ko rayuwarta da kake so ka bi.***

# MATSANANCIN MA'ANA TA ADDU'A

RANA TA 188

***Wannan wasika mai ban sha'wa anyi fasa-kwaurin ta ne daga cikin Kasar-Sin.***

*Domin wannan ko wane ne mai tsoron Allah shi yi addu'a gareka*

*Zabura 32:6*

Ni baligi ne kuma soja na bataliyar Red Guard. Ba na bada gaskiya ga kowane irin Allah, ko jahannama, ko wani Mai Ceto, ko ma ko menene sam sam. Watarana garin murde murden neman tashoshin rediyo sai na kicinisa da tashar ku ta rediyo na. Da farko sai na yi kamar na kashe rediyo na. Kwaminis na ainihi ba su yarda da Allah ba. Amma darashin da ake gabatarwa ya ja hankali na sabo da haka sai na ci gaba da kama tashan daga lokaci zuwa lokaci. A yanzu kuwa na gaskanta Kristi amma ina da tambayoyi guda biyu.

Na farko: Ko Allah yana karbar koma da wanene ne daga Kasar Sin ta kwaminsanci? A cikin darasinku ku kan kara yin magana akan majami'a, amma ni ina Kasar Sin, wurin da kusan ma babu majami'u. Ko Allah zai karbi wanda bashi da majami'a

Wannan matashin soka bai san akwai majami'u da suka gudana a boye a kasar Sin ba, sai yayi tambayar sa ta biyu. Ko za'a iya koya mani yadda zan yi addu'a? Kukan fara kowane darasin bisharku ta rediyo addua kuma kukan nufi ne addu'a. Ina so in yi addu'a amma ban san yadda zan yi ba. Wannan saja bai taba shiga majami'a ba, amma yan iya kwatanta abin da ake nufi, "Watau a wuni ana magana domin bayan ka fadi abinda kake son fada sai ka kara kalmar "Amin"

***Addua ba abu ne na halin mutum ba. Alhali ma bata zuwa ga mutum ta hanyar mutumtaka. Domin ita akan ji ta ne ta hanyar ruhaniya. Allah yakan bamu bukata irin ta ruhaniya domin mu sami sadawa da shi ta hanyar yin addu'a kamar dai lissafin Kimiyya ko batu na harshe, addu'a fasaha ce da ake koyo. Idan muka saba yin addu'a a kullum fashar mu ta yi haka zata kasu kuma mu gwanance. Wannan matsayin mai bi ya fassara al'amuran rayuwa saboda haka kuwa sai ya maida rayuwa kacokan a zaman addu'a ga Allah. Kaka iyawarka ta yin addu'a take habaka? Ka yi sanyi ne wajen yin addu'a a kullum farawa daga yau ka roki Allah ya baka bukata ta ruhaniya domin ka iya yin magana da shi ya baka ikon maita yin addu'a ya zama. Bari jiki a gareka a kullim. Toka dara jarrabawa rayuwarka ta zama addu'a.***

# *Kafin shiga kurkuku muka sami bisharar Allah. Amma a cikin kurkuku muka sami isasshen sanin Allah.*

***Wani shugaban gidan addu'a a Kasar Sin wanda aka sa a kurkuku a dalilin ban gaskiyarsa, ya sha tsananin yunwa, ciwo da bala'in fashewar nakiya a ramin tonar ma'adinai in da aka tilatsata masa yin aiki amma allah ya ceci ransa.***

# MATSANANCIN HAUKA
## Russia: Anna Chertocova

RANA TA 190

***Rigar karfe ta kikam da aka sanya wa Anna Chertokova yana azabtawa. Ta ki jinin a rufe mata hannuwa kuma a daure su dab da jikinta. Ga masu sarrafa abubuwan nan a gareta babu wani bambamci a tskaninta da dabba, ba taci ma a saurara mata ba.***

*Gama na rigaya na koya zaman da nake ciki duka raina ya kwanta da shi.*

*Filib 4:11*

Anna tayi shekaru goma a cikin gidan da ake tsare mahaukata a Russia. Ita kuwa ba ta da ko alama na ciwon hauka. Wani alkali ne ya aikata a can domin kawai ita Krisata ce. Kin yardar da tayi na musun Kristi, ga wannan alkalin, hauka ne.

A keweye da masu ciwon hauka, amma da kanta wasu lokuta takan tambayi kanta anya ita ma kuwa lafiya take? A cikin dare sai tayi kuka tana kira ga Allah a cikin lamirin zuciyarta, kamar dai yadda su na keweye da ita sukanyi kuka cikin fushin su kokuma cikin barazanar su ta hauka. Duk da haka bata taba muna fushi ba. Wannan imani da taki yin musun sa a dakin shari'a, haka kuma taki musunsa a gidan mahaukata, ga wadanda suka fahimta. Anna tayi kokarin shaida misalun kaunar Kristi.

Ina gaishe ku tare da kauna a cikin Ubangiji Yesu Kristi. "Amma ta rubuta daga gidan mahaukata, "Ina addu'a ga Allah da yasa mu zama abin sha'awa kuma tsayayyu a cikin Kristi. Kuma ya shugabanci cikan al'amuran mu. Ina bada tabbacin cewa Allah da ya halicci zuciyhar kowa da kowa kuma wanda yake gwada dukan al'amarunan dukan mahaluki zai shar'anta rashin yardar ta da matsafa na rashin yarda da Allah kuma zai aiwatar da shari'ar sa da adalci".

***A wasu lokuta Krista na iya samun kansu a mahaukacin matsayi da zai jarabci irin jimin da suke yi ya kuma gwada halinsu. Kamar tsarin mayuwancin rayuwa, siyasar wurin aiki, da mai mugun hali. Shin zamuci gaba da dogaro ga Allah kome wuyar al'amuran mu? Zamu iya idan muka san sirrin iya yin tawakkali. Littafi Mai Tsarki na koya man cewa tawokkali da ke cikin lamirin zuciyar mu lalle ne yayi mulki a yayin da muke fuskantar al'amuran waje. Halayen mu na daukar majarin su ne daga Allah amma ba daya abubuwan da muke bane. In ko da daga kanmu ne da abubuwan sun gamshe kome wuyar al'amuranka.***

# Romania: Dr. Karlo

RANA TA 191

***Cin gaba da binciken takardar nema yayi tsawo da kuma gajiyarwa. Binciken ya fadada, har ma an kusa a barar da batu takardar nema ta Dr. Karlo domin jita-jita da akeyi na cewa wai yana da dangantakar da "Krista".·Amma Dr. Karlo ya haye wannan bincike mai tsananin har an bashi mukamin Likitan Yan Sandan Asiri. Bai yarda ya gaya musu cewa shi Krista ne ba.***

*Na zama dukan abu ga dukan mutane domin ko da kaka in ceci wadansu.*

*1 Kor. 9:22*

Iyalin Dr. Karlo da kansu sun juya masa baya domin suna tsammanin ya zama dan kwaminis. Daya bayan daya iyalin sa na majami'a da duk wadanda suke makusanta a gareshi sun juya masa baya. Babu wani a cikin su da ya san manufar sa na zuwa neman pasto.

A matsayinsa na zama Likitan Yan Sandan Asiri, yana iya shiga da fita a kowane daki a kurkuku sabo-da-haka ya gano inda aka kulle pasto. Karlo ya aika ga labarin ga jama'ar Krista, wadanda kuma suka aika da labarin ga duniyar Turai. An gaya musu wai ya mutu, amma yanzu suna da tabbacin cewa Pasto Richard Wurmbrand yana raye. A wani tsakanin Krushev da Eisenhower a shekarar 1956, Kristoci ko ina a duniya sun yi hargowa akan neman a saki Wurmbrand. Sannu a hankali kuwa ya samuy saki ta fansar. $10,000.

Idan da ba domin wannan Likita ba, "Wurmbrand ya rubuta daga baya wanda ya shiga aikin Dan Sandan Asiri musamman domin ya neme ni, da ban taba samun a sake ni ba, da zanci gaba da zama a kurkuku-ko kuma a makabartar kurkuku".

***Wakilan asiri sune taurari, ayyukan da suke yi wa kasa ya shafi kuru da kasada iri iri wajen aiwatar da ayyukanswu don cika umarnin hukuma. Ta haka kuma matsanantan masu bangaskiya na kasashe marasa yanci su na da rayuwa mai kasada ko kuru, labarinsu na kayo bambanci mai kyau ga mutaneda yawa. Kada su kuskura su tallatar da manufar su, amma kullum a shirye suke su yi amfani da dukan damar da suka samu domin shaida kaunar Kristi. Ba tare da la'akari da kasa ko matsayin rayuwa ba, Allah yana kiran kowanen mu ya zama wakilin sa na ruhaniya yana kai rahoton sa zuwa samaniya. Muna cikin aikin yin bisharar kaunar Allah a kullum, Allah ba ya bada alkawarin cewa lafiyara ka ba zata tabu ba a yayin da kake aikin sa, amma yayi alkawarfin madauwamin lada.***

# MATSANANCIN SHEDANCI

## *Rome: Polycarp*

RANA TA 192

*Dole ne mu bada gaskiya ga Allah kullayaumin sabili da ku yanuwa, abinda ya kamata kenen da shike bangaskiyar ku tana yin girma kwarai.*

2 Tass. 1:3

***Polycarp almajiri ne na Yohana, amma yan cikin gudun tsarewa a zamanin da ya rigaya ya mayanta. A lokacin da yake cikin bulaguro wani yaro ya gane shi kuma ya gaya wa sojoji. A yayin da suka same shi yana cikin cin abinci tare da sojojin da suka zo kama shi.***

Bayan sunci abincin tare. Polycarp ya roke su su bashi sa'a guda domin yayi addu'a, sojojin sun yarda amma daga baya sunyi da-na-sanin shawarrsu. Polycarp yayi addu'a da tsnani har ya kai ga sojoijin da suka gane da laifofinsu na zunubi.

Sannu a hankali kuwa aka kai Ploycarp a gaban gwamna wanda yanke masa hukumacin kisa ta kone shi a bakin kasuwa. Wannan ya bashi damar ya ceci ransa idan yayi musun Kristi. Polycarp ya ki yana cewa. "Na yi shekara tamanin da shida (86) ina bautamasa. Me zai sa nayi sabon sarki na wanda ya ceci ni?'

Aka daure Polycarp a jikin itace aka kuma kunnawa itatuwan da aka jera kewaye da su wuta. Wuta ta kama kewaye da mai ban gaskiyan nan kuma mai karfin zuciya amma-abin mamaki-ba ta kona ko gashin sa ba. Gwamna kuwa ya fusata ya umurci wani soja da ya soke hakarkarinsa da mashi. Ta haka suka cinasara da kashe Polycarp, amma basu iya kashe bangaskiyar sa ba da kuma ruhaniyarsa mai nasara.

Rubutacciyar addu'ar Polycarp ta kashe ita ce: ina yi maka yabo domin ka sani a zama na kirki kuma karbabba ga zama daya daga cikin shahidai a yau kuma a wannan rana kuma a wannan sa'a domin na samu daga modar Kristi. Domin tayar da ruhuna.

***Polycarp ya kirkiro sabuwar ma'ana ga wannan sashen magana "Mai kuzari cikin marabus" gawurtaccen waliyyi a cikin shekarunsa na Tamaniya, Polycarp yayi tsawon rayuwar da bai ma damu da yadda makiyan sa suka ji akan bangaskiyarsa ga Kristi. Ta daya gefen kuma galibi samari masu aniya sukan fuskanci magabci ba tare da sun sani ba. Yawancin masu bi sukan samu a tsakanin biyun. Yan lokacin da muke matasa muka rasa anniyar mu ta sa kai duk da haka ba muyi tsawon rayuwar da har zai hana wasu su fadi albarkacin bakin su game da bangaskiyar mu ba. Abin godiya shine Yesu ya karbe mu a yadda muke kuma kamar yadda ya kamata mu zama. Ka dage bashin dukan dama na ba da kanka da zaka iya yi domin ya rayad da kai zuwa mafificiyar bangaskiya a gobe.***

## MATSANANCIN MAI HIDIMA

### Pakistan: Zeba

***"Maimaita wadannan ayoyi!" Aka umurci Zeba.***

*Amma wanda ya ke so shi zama babba a cikin ku, baran ku zaya zama*

*Matt. 20:26*

"Ba zan maimaita ayoyin ba. Ni Krista ce. Kuma zan cigaba da zama Krista a kullum".

Da yake daga iyali masu talauci ne ta fito, sai ta zama dole Zeba ta yi aiki a mukamin yar aiki a gidan wani attajirin Musulmi. A yayin da take aiki, shi mai gidan yayi kokarin ya koya mata game da Islama kuma kuma sai yake rinjiyarta ta ta haddace wasu ayoyi daga cikin Kur'ani Sau uku a lokuta dabam dabam Zeba ta ki yarda, tana cewa "Ni Krista ce". Kuma akan yi mata duka a duk lokacin da ta ki.

Masu gida da Zeba take yiwa aiki kuwa suka sa aka kama Zeba, da hanyar wai ta yi musu sata. Baya ta sami fitar da diyar ta. Uwar Zeba ta ziyarci wannan iyalin Musulmin domin ta kare diyarta. Amma ba a yi mata maraba ba.

Daya daga cikin iyalin ta fada da karfi, "Ke kafira ce! Da ke da diyarki duk kafirai ne bai ma kamata ki rayu ba, "Sai suka watsa wa uwar Zeba fetur a jikin ta kuma kyatsa ashana.

**Zebe ba ta sake ganin uwarta ba kuma. Amma duk da wannan bala'i Zeba ta ci gaba da tafiyar ta a cikin Kristi kuma anyi mata baptisma.**

Yau a Pakistan an kafa makarantar koyon dinki domin matasan yan matan Krista kamar Zeba su daina neman aiki na wanke wanke da sauransu a gidajen masallata. Duk da ciwon rashin uwarta da tsanani kuma Zeba ba tayi gunguni ko jin haushi kuma ga wasu a kasarta. Tana so ta zama malama mai koyar da Littafi Mai Tsarki.

***Mulkin Allah yana tsayawa a daidai ne a lokacin da kake tsaye kai bisa kafa ga jerin sa na muhimmancin al'amura, idan aka kwatanta da yadda duniya take shirya matsayi na al'umma za a ga bambamci. Maimakon a ga gwani kyakkyawa ko attajiri shine na farko sai ka ga cewa Allah yana anfani da kaskantuttun talakawa su zaman su ne akan gaba wajen aikin ruhaniya a gaban Allah, watau zaman duniya "Kashin-dandali-ne" a sama kuwa akasin haka. Zeba ba kowa ba ce a idanun duniya, amma duk da haka tana yin gagarfumin aikin mulkin Allah. Ba lalle ne mai aikin gida ya zama gwani ba, amma dai akwai mai aikin gida "Yaron gida" yana da muhimmanci ga aikin Allah. Ka yi shirin kaskantar da kanka don zama yaron gida ko bawa don aikin Allah? Kyakkyawan labari?.***

# JUYOWA MATSANANCI

## *Kasar Sin: Chang Shen*

RANA TA 194

***Kafin juyowar sa, Cheng Shen shahararren dan caca ne, ma neman mata kuma barawo ne. A lokacin da ya makance a yayin da yake cikin matsakantan shekarun sa na rayuwa; makwabta sun ce ai horo ne daga alldi na danyen ayyukan su.***

*Ku tube ga zancen irin zaman ku na da tsofon mutum wanda yana kara dacewa bisa ga sha'awan yin yaudara; ku sabonta kuma cikin ruhun azancin ku kuyafa sabon mutum wanda wanda an hallice shi bisa ga Allah cikin adalci da tsarkin gaskiya.*

*Afisawa 4:22-24*

A cikin shekara ta 1886 chang yayi tafiya mai nisan gaske zuwa wani asibitin Mishan inda ake yi wa mutane aikin ido. Ya sami sa;ar warkewa kuma ya fara gani kadan kadan, kuwa a nan ne ya fara jin labarin Kristi. Na farko a rayuwarsa. Bamu taba samun wani majinyaci da ya karbi bishara ba da farin ciki irin sa ba, "in ji likitan".

A lokacin da Cheng ya nemi wani a yi masa baptisma. Sai shi baturen Mishan James Webster ya zo ya sami masu bi da turin yawa. Ya yi wa wannan sabon mai bishara baptisma da farinciki mai yawa.

Daya daga cikin kazamin boka ya cuci Cheng ta wajen, lallata masa dan sauran gani da yakeyi, amma Cheng ya cigaba da tafiyan sa zuwa kauyuka, dabam dabam. Ko da shike wasu sukan tofa masa miyau wasu kuma su ki karbar sa duk da haka ya kara samun daruruwan masu zuwa Kristi.

A zamanin da tawayen dambe ya faru, Krista suka kai Chong wani kogo na cikin duwatsu domin kariyar lafiyar sa. Yan damben suka yi wa Krista hamsin kafar rago domin a zartas musu da hukumcin kisa kusa ga wani gani amma suka yi alkawarin barin su duka idan har Cheng ya fito wurinsu. A lokacin da labarin ya isa ga Cheng, ya ce "Zan yi farincikin mutuwa domin su".

Bayan kwana uku kuwa aka fille wa Cheng kai, kuma aka saki dukanin Kristoci.

***Wannan gagarumin musaya shine gagarumin abin bisharan Yesu, ya bada dama mu yi musayar tsofuwar rayuwa da wata sabuwar rayuwar. Duk yadda ya sauya chang daga wani mai rayuwar duniya zuwa wani wanda ya sadaukar da kansa gaba daya ga Kristi. Koda wace irin barna muka yi a tsofuwar rayuwar mu, ana iya yi mana garbawul zuwa ga daidaita da iya aikata nufin Allah. Shine ya sa shaidar mu tana da karfi wajen yin bishara. Rayuwar da ya sauya ya juyo da Allah yakan zama shaida kwakkwara domin tabattar ceto, ba zamu ci gaba da maganganu barkatai kamar ta da bai wa kake ganin ya kamata yasan irin bambamci da Yesu ya kawo a rayhuwar ka?***

# MATSANANCIN NAUYI

## Columbia: Juan

RANA TA 195

***Babu abin da zai hana yaduwar bishara a Columbia, ko da hadarin iblis ne ko kuma na yaki.***

*Gama karkiya ta mai sauki ce, kayana kuma mara nauyi*

*Matt. 11:30*

Juan tare da matarsa Maria masu aikin bishara a cikin mutanen kabilar yankin arewacin Cali ta kasar Columbia. Yankin Cali na kasashen mulkin Sojojin Juyin-Juya-hali na Columbia. (FARC), wata kungiya ta Yan-Sari-Ka-Noke. Masu aikin Bishara na Columbia da dama sun fuskanci kiyayya daga FARC, har ya kai ga sa su barin yankin. A lokacin da Juan ya gamu da wani gungu na yan sari ka noke guda hamsin shekaru uku da suka shige, ashirin daga cikinsu sun karbi Kristi. Kamar yadda yakan fadi, "Mukanyi musayar bindiga da bishara."

Yanzu kuwa, sojojin yanci na kasa suna kawowa majami'un Krista hari a wannan yanki. Can ba da dadewa ba an rufe majami'u fiye da ashirin, kuma pastoci da yawa sun gudu domin tsira da rayukan su galibi. Yan sari ka noke sukan zo ne don su kwashe dukan baiko da zakka ko kuma dan su dauki ran pasto. A yanzu kuwa Juan ne kadai pasto da ya rage a wannan yankin, kuma ba ya samun taimako daga waje. Duk da haka Juan da matarsa suka yi shawarar zama da kuma cin gaba da yi wa mutanen bishara. Suna cewa, "Idan zamu mutu don wa'azin maganar Allah, to mun gwammaci mutuwar maimako barin majami'ar.

Juian bai la'anci wadanda suka tashi ba kuma bai yi maganar irin wahala da suka fuskanta ba. Ya gwammaci ya shaida abinda Allah yake yi da kuma nauyin da ke kansa domin bishara. Ko da shike akwai damuwa na makiya amma ba wannan ne ke tayar masa hankali ba a'a hankalinsa yana kan kokarin isarda bisharar Kristi ga mutanen Columbia.

***Yesu yayi misali da dabba da ke dauke da kaya. Dabbar bata yin kokawa da mauyin kayan, gama da wuya ta ji nauyin. Dauka nauyin bisahar bai zama daya da fama da nayin al'amuran duniya ba. Ma'anar nauyin bishara shine cewa a farga da bukatar wasu ta ruhaniya. Juan yana dauke da kayan nauyi. Amma nauyin bai tsananta ba. Bin misalun Kristi shine mu dauki nauyin kawo battatun mutane.***

***Wannan kayan nauyin sa babu yawa domin muna ragewa ta hanyar bayarwa. Bai kamta mu rike bisharar don kanmu kawai ba. An taba kin karbar ka a yayin da kake yin bishara? Watakila ka yi shawarar janye wa domin akwai kiyayya. Bari irin nauyin kaya da Yesu ya dauka akan giciye ya iza ka domin ka kara yin juriya.***

RANA TA 196

***Idan mu krista ba mu ci gaba da yada bishara ba muna ture mahassada, to hassada zata far mana. Idan muka ci gaba da rufe bakunan mu wajen shaida bishara, to bishara ba zata wanzu ba idan haka ne kuwa Kristanci zai shude a Amirka***

***Ray Thorne-Baturen Mishan mai duba majami'u da ke cikin tsanani***

# MATSANANCIN MAI BISHARA
## Kasar Sin: Pasto Li Dexian

RANA TA 197

*Idan dai kun lizima cikin bangaskiya a kafe, masu tsayawa kuma ba masu giruwa ba daga bege na bishara*

*Koloss. 1:23*

***"Zan yi ta wa'azi har sai na mutu".***

Bayan mintoci kalilan da karasa, wa'azin sa, sai hafsoshin Ma'aikatar Tsaro suka shigo gidan Pasto Li Dexian. Suka ja pasto zuwa waje suka yi masa duka da shi da sauran masu ibada yan Kasar Sin.

An kuma sake yi masa duka a yayin da suka isa Caji Ofis, har sai da yayi aman jini. Hafoshin sunyi ta dukar fuskarsa da Littafi Mai Tsarki, sun barshi jina jina kusan ma kamar somamme akan daben dakin da ake kulle masu laifi.

Bayan misalin awa bakwai kuwa sai aka sallameshi, shi kuwa me zai yi in ba yaci gaba da bisharsa ba. Karo na gaba kuwa da ya sake yin bishara a wannan majam'a Hafsoshin Yan Sanda guda bakwai suka shigo suna tuhumar mai bisaharar. A lokacin da suka ga bakin turawa daga turai tare da shi, sai suka fice, amma bayan minti goma sha biyar sai suka sake dawo da karin yawan yan sanda. Hafsoshin nan suka ja shi zuwa waje suka fara dukansa suna bugawa a jikin bangon ginin dutse. "Me yasa kake dukansa? Inji bakin da murya mai karfi "Ina yancin addini da kuka ce kuna dashi a Kasar Sin?"

Hafsoshin nan suka kai bakin turawanan a Caji Ofis tare da matar da ta mallaki gidan inda aka yi taron. Danta ne yakai rahoto ga yan sanda game da batun taron.

Tun daga wannan kai harin irin yawan mutane da ake samu a taron ya tsaya amma majami'ar ba ta tsaya ba. Yanzu sukan yi kananan taruka a wurare fiye da arba'in, kuma sababbin tuba suna zuwa ga Kristu a kowane mako.

***Tafiyar dige digen zaiba, a lokacin da makiya suka yi kokarin hana majami'a yaduwa, kawai raba kansu zuwa kannan taruke. Majami'u dake kasashe marasa yanci da wuya su gina manya manyan wuraren sujada kamar na kasashen turai, amma duk da hak yawansu na karuwa. Alhali ma wata majami'ar Krista a Korea tana da girman da yafi na wasu majami'u a turai. Haka kuwa, kamar irin dabarun yan Kasar Sin, taro masu sujada na korea sun rarrabu ne guri guri, da mambobi kadan kadan amma gobjen addu'ar sunfi dubu. Wasu abubuwa da zasu zo mana a zaman hana yin bishara sukan juya su zama alheri a faskance. Idan ku samu cikas, hakan ba da kaine nan da nan? Ko kana iya dagewa ka kirkiro wata hanyar da bishara za ta sami gaba?***

## MATSANANCIYAR TILASTAWA
### *Bangladesh: Idris Miah*

RANA TA 198

***"Idan Abu yana so ya zama Krista; to sai dai yayi haka din a wani wuri. Mun kewaye gidansa da shirin mu fitar da shi karfi da yaji kuma mu kone gidan.***

*Ya Allah na adalci na, ka amsa mani a lokacin da nayi kira lokacin da ina cikin kunchi ka yalwata ni.*

**Zab. 4:1**

Da muka matsa masa sai muka ji shi yana magana. Shin ya tarawasu ne don su taimake shi? Muna mamaki sa'anan muka gane addu'a yake yi domin ilahirin kauyen kuma yana rokon Yesu ya gafarta mana domin shirin ta'asar da muke yi! Wannan kuwa har ya kara fusata mu, sabo da haka mutane ashirin da biyar daga cikin mu suka tasama gidan domin kama shi. Amma akwai wani iko da ba'a iya gani da ya hana kowa iya shiga gidan, abin kuwa ya tsoratar da mu muka bar wurin.

Lokacin da na isa gida kuwa na kasa yin barci. Nayi ta tunanin addu'an Abu. A karshe kuwa misalin karfe uku na asuba, sai na koma gidan Abu, na tambaye shi ya fada mani labarin Yesu. Bayan tattauanawa na sa'oi uku da Abu. Na roki Yesu ya gafarta mani, kuma na bada rayuwata gareshi. Nayi maza na tafi gida na shaidawa matata abin da ya faru da ni, ita ma ta zama Krista, tare da yayana".

Cikin yan kwanaki kuwa wannan mai bada gaskiya dan Bangladesh wanda ya bada wannan labari, ya fuskanci jarrabawa. An kore shi daga makaranta. Amma duk da haka yace ya na da Yesu a zuciyarsa.

***Galibi bamu da zabi na iko da rayuwarmu, amma muna iya zabin irin hali da maida murtani ma dauwa. A kullum muna iya yin zabi kome wuyan al'amura. Haka kuwa kamar Abu da yake tsaye a bakin wata maisifa, shin zamu zabi yin addu'a, da maida murtani irin ta kaman ta Kristi ko zuwa zamu razana ko mu kidime? Ba abu ne mai yiuwa ba ga wasu kome kokarinsu. Su iya fusata mu ko gajiyadda mu. Mukanyi zabin da kanmu. Haka kuma, mun iya zabin mu kamanta Yesu ta kwaikwayar sa wajen maida murtani ga yan hammaya. Wa yasa abin da zai auku? Ka nemi taimako daga Allah yau domin ka iya zaben amsa da tafi dacewa a kowane matsayi mawuyaci da ka sami kanka.***

# MATSANANCIN BAWA

## Virgin Islands: Leonard Dober

RANA TA 199

***Leonard Dober ya yi mamakin wai ko Yesu yayi tunani game da giciye kwarai; daga nan sai ya tuna da addu'ar Yesu a cikin gona tare da cewar: - Ba zabi na ba, amma naka Uba. "Da alamar aikin da ke gaban Leonard mawuyaci ne, amma nufin Allah yake so ba nasa ba.***

*Bamako ba mu cikin hankali ba, ga Allah ne; ko muna cikin hankali a gareku*

*2 Kor. 5:13*

Leonard Dober ya Kudura cewa kiran da Allah yayi masa na ya isar da sako ne ga bayi a wannan tsibiri da ake kira, Virgin Islands. Yayi shirin isa ga wadannan maza da mata ta wurin sayar da kansa a zaman bawa kuma yana aiki tare da su kowace rana a yayin da yake shaida musu batun kaunar Allah. Tunanin zama bawa yakan tsorata shi ya dameshi. Ya ki jinin keta hadinsa da akeyi. Amma Kristi ya yarda ya mutu domin na akan giciye" ya yi tunani. "Babu wata wuya da zata yi yawa a gare ni wajen bauta masa.

Ba iyayengijin bayin ne suka fi tsanantawa dokar ba, amma wasu yan'uwa Krista ne. suna tambaya ne game da kira da yace anyi masa na yiwa bayi bishara, suna kuma yi masa ba'a cewa yayi wawanci wajen wannan shirin nasa. Amma wannan bai takawa Dober birki ba. Ya isa wannan tsibirin a karshen shekarar 1730.

A lokacin da ya zama yaron gida a cikin gidan gwamna, ya tsorata da cewa, wannan matsayi da aka bashi ya nisanta daga bayi wadanda a dalilin su ne ya zo yin bishara. Sabo da haka ya bar gidan gwamna zuwa dakunan da aka gina da tabo inda zai iya yin aiki tare da bayi.

***A cikin shekaru uku rak, Dober yayi bishara da ta kawo mutane fiye da dubu goma sha uku ga tuba. Masu kaunar Kristi sau-da kafa-mutum mai zaman yanci wanda ya zabi yayi zaman bauta domin ya samu daman kawo bayi ga Kristi. Ana shirye da ya yi dukan abin da zai iya domin kawo masu tuba ga Kristi. Ga doka wannan yana nufi tabbatacen shiri da yake da ma'ana a gareshi ba ga kowa ba. Shinn an taba fidda rai game da kai da irin bin Yesu da kake yi sau-da-kafa? Idan Allah ya kira ka da ka je shugaban a sauyi domin sa a cikin iyalinka, ko a majami'a ko cikin jama'a, dole ne ka yi biyayya. Ko da wasu zasu kira ka mahaukaci to bari Yesu ya sameka sa zaman mai ba da kai kuma mahimmaci.***

## MATSANANCIYAR SUJADA
## *Kasar Babila ta Da: Daniel*

RANA TA 200

***Ya ji yekuwa da ake yi ta shelar kafa wata doka daga tagarsa: daga yanzu kuwa kwanaki talatin duk wanda yayi addu'a ga wani wanda ba shine Sarkin Babila ba ne, za'a jefa shi a ramin zakuna".***

*Amma sarki yayi magana da Daniel yace, Allahn ka wanda kake bauta masa kullum, shi zaya cece ka.*

*Daniel 6:16*

Daniel ya tura kyamare ga a bude dukan tagunansa. A kowace baga kuwa sai ya lura akwai masu zuba masa idanu. Daga nan sai ya kona tsakiyar dakin. In da kowa ma zai iya ganinsa, ya durkusa ya fara yiwa Allah sujada.

Sarki yayi bakinciki a lokacin da aka kawo Daniel a gabansa. An yi wa sarki dabara. Dokar kuma da aka kafa da hatimin Sarki ba ta janyuwa. Har ya yi famar neman hanyar fitar da Daniel dukan wuri domin ya san daniel mutumin Kirki ne. ku tafi da shi, Sarki Dari ne ya umurci masu tsaro. Sa'anan ya dubi Daniel a idanu ya ce, "Bari Allahn Ka da kake bautawa a dukan lokaci ya cece ka" ( Daniel 6:16)

Sojojin kuwa suka kai Daniel a raminm zakuna, Sarki kuwa na binsu a baya. Daniel bai ce uffan ba, amma sai yayi wa Sarki gaisuwa, sai ya shigo cikin zakuna, kofar shiga kuwa aka taushe da katon dutse.

Daniel ya tafi tsakiyar makwancin zaki nan ya durkusa, ya fara yi wa Allah sujada.

***Matsananciyar sujada ba abu ne na yabo ba, ita ba wata kayyaddaddiyar hanya ce ko kuma wata al'ada ce ta musamman ba. Alhali ma dai dangantakar ta da yadda muke yabon Allah ba yawa. Matsananciyar sujada takan sami bayyana ne ga lokaci da kuma wuri inda mukan yi sujada. A lokacin da ta dauro mu shiga yin sujada a lokacin da muke cikin matsanacin matsi na damuwa, anan ne muke shiga yin matsananciyar sujada. Kamar Daniel kada mu yarda mu ba al'amaren mu su aza mana sharadi na yaushe da kuma ina ya kamata mu bauta wa Allah. Lalle ne mu zama da shirin yin bautar bangaskiya ko da a ina ne kuma ko da yaushe ne. a shirye kake ka bauta wa Allah a cikin matsananciyar sujada a yau?***

# MATSANCIN KI
## *Korea ta Arewa*

RANA TA 201

***"Sun roke ni sun kuma kara roko na, amma bazan iya basu ba, "Inji mutumin. Na sani Krista masu bayarwa ne, amma ni bazan iya eabuwa da wannan ba. "Cikin damuwa kuwa ya mika hannun sa domin ya nuna wa wanda yake yi wa bayani mallakarsa mai daraja.***

***Gama ina farinciki da umarnin ka domin ina kaunar su.***

***Zabura 119:47***

A zahiri naso, amma na kasa yin haka. Ka gani mutane a Korea ta Arewa sun fada mani cewa sun yi shekaru hamsin, suna addu'oi don su samu, kuma ban jima da samu ba daga wani pasto a Korea ta Kudu".

Sai yayi ajiyar zuci a yayin da tunaninsa ya karkata zuwa wurin masu bi da ke cikin bukata a Korea ta Arewa suna addu'a a dukurshe domin samun Littafi Mai Tsarki guda daya tak. Ya rungumi Littafin sa Mai Tsarki a kirjinsa. Ya tsare daga kurkukun kwaminis a yanzu kuwa yana zaman yanci a Korea ta Kudu.

Ba safai ake ganin Littafi Mai Tsarki a Korea ta Arewa ba. A dalilin hamayya daga kwaminis, masu bi suna baiwa Littafi Mai Tsarki darajar da tafi ta zinariya. Akwaiwani mutum da aka lakaba wa duka da karfe har sai da ya mutu akan iyakar Kasar Sin a lokacin da aka kama shi yana shigowa da Littafi Masu Tsarki zuwa cikin Korea ta Arewa wannan suna faruwa akai akai.

"Bana iya mantaa da wadannan mutane," ya fadi haka da ajiyar zuci. Ba zan iya mutuwa da ganin kyashi da ke fuskokinsu ba a likacin da na nuna masu Littafi Mai Tsarki. Ina damuwa domin su".

***Ko da shike wannan Littafi ya ci gaba da zama gaba gaba wajen sayarwa daga shekara zuwa shekara amma da alamar ba a karatun sa yadda ya kamata. Wannan littafi shine Littafi Mai Tsarki a wajen wadannan wurare inda aka fi sanin darajar wannan littafi sarai. Da a ce muma munyi shekara ashirin muna addu'a kafin mu samu, da wane irin riko zamu yi wa littafin mu Mai Tsarki?***

***Me zaka yi domin ka farfado da matsananciyar kwadaituwa ta ciyarda aikin Allah mai daraja gaba.***

# MATSANCIN GARI

## Russia: Liuba Ganevskaya

RANA TA 202

***Liuba Ganevskaya ta sha duka sau dayawa a kurkukur Russia. Amma idan ta dubi mai azabtar da ita na rike da bulala, sai ta yi murmushi.***

*Ni Ubangiji na kira ka cukin daukaka domin bude idanu da ke makance*

*Ishaya 42:6-7*

"Me yasa kike murmushi? Ya tambaye ta da mamaki. "Ba na iya duban ka kamar yadda ka ke iya nuna kanka yanzu", in ji Liuba ina yi maka duban yadda ya kamata ka zama-kyakkyawa kuma kamar jariri mara aibi. Kanmu daya da kai, mu sa'annin juna ne mai yiwuwa ma munyi wasan yarinta tare".

Allah ya bude idanun Liuba domin tayi masa gani na dabam. Ta lura da irin gajuyar da ke tare dashi, yayi mata duka har ya gaj kamar yadda ita ma ta gaji da shan gukar. Ya fusata cewar ya kasa ya sa ta bayyana ayyukan suna masu bi.

Shi ma kamar ke yake', Allah yana furta wa Liuba a zuciyarta Dukanku biyu kun sami kanku a cikin al'amuran rayuwa. Da ke da masu azabtar da ke dukanku kuna bi ta matsayi na danuwa" Ganin mutumin ta idanun ruhaniya, halin Liuba ya sauya. Tac gaba da yi masa magana. "Ina yi maka wani gani wadda ina fata haka dinne zaka zama. Wani mai tsaron kwarai fiye da yadda ka taba yi a rayuwarka-Saul na Tarsus-kuma yazo ya zama ma bishara kuma waliyyi". Ta tambayoyi mutum da bai yi masa wan hani ko rauni ko laifi ba.

Ta wurin nuna damuwarta tare da kauna. Liuba ta yi sanadin kawo mai azabtadda ita ga mulkin Kristi.

***Anfani da idanun mu na gani a duniya yakan zama garara t wurin cututtuka dabam dabam, kasa gani daga nesa glaucoma, da sauransu. Kamar dai yadda idanun mu sukar sami taimakawa daga madubin idanu, idanun zukatan mu zasu ci ribar karuwa daga ikon ruhaniya. Ga irin nam iyawa, mukanyi gani ne amma na mugayen abubuwa ga wasu amma ba masu kyau ba. Amma Allah yana bada tafarkin samaniya. Zamu iya fara ganin shugaba mara hakuri, ko kuma da yake bukata a nuna masa kauna. Kana y masu gani da idanun samaniya? Wane bambamci idanur ruhaniya zasu kawo a rayuwarka?***

# *Na gwammace a rataye ni da in ci amanar Ubangiji na*

***Sateema- Yar shekara goma sha tara a pakistan wanda aka yi wa tsanani ainun a dalilim bangaskiyarta***

## MATSANCIYAR DAUKAKA

### *Romania: Valeriu Gafencu*

RANA TA 204

***Valeriu Gafencu tare da iyalinsa sun yi rashin mahaifin su, kuma sun sha wahala kwarai a hannun masu azabtarwa kwaminis. Duk da haka bashi da wata bakar magana game da yan kwaminis wadanda suka kawo wahala ga iyalinsa. T kaka zai shiga irin wadannan wahalu kuma ya ki yin magana gaba da masu azabtar da shi?***

***Kada ku zartas, ku kuma baza azartas muku ba: kada ku kayas, ku kuwa ba za a kashe ku ba; ku kwance za a kwance ku kuma.***

***Luke 6:37***

Ya amsa, "A lokacin da Sarki Dawuda yake cikin hakin aiki da damuwa, shi ya jefe shi da tsingaro, ya la'anta shi kuma ya dora masa laifin da baiyi ba (Sama'ila 16) Daya daga cikin sojojin Dawuda yayi shirin karshe Shimei amma Dawuda ya hana. Ya bar Shimei ya yi la'anarsa, gama Ubangiji ya Umurce shi. Dawuda yana da cewar bai yi waddanan laifuffukan ba amma ya sani cewa akwai wasu laiffufuka da yayi wanda Shinei bai san kome akai ba!

Kwaminisawa na kiran mu yan fashi kuma magabtan jama'a, wanda ba haka ba. Amma dukan mu laifin rashin waliyi ta girfma wajen kamanta Kristi. Maida murtanin mu ga wannan abubuwan wanda kwaminis suka yi bai kamata ya zama kiyayya ba, amma ya sabunta lamirin mu.

Tsakiyar haske na tsarkaka zai bulbulo daga garemu ya hallaka mugu. Kalmar Girka ta sunan Allah (Theo) asalin ta daga wata kalma ne da ake fassaranta da bulbula! Shaidar Gafencu a kurkuku ya kawo mutane da tawa ga Kristi, kuma haryanzu ranar da ya mutu, ya ki yayi anfani da kalma daya mara dadi gaba da wadanda suka azabta shi.

***Shin ya kamata a baiwa abokin gaba daukaka? Zai yi wuya ayi tunanin yin haka. Amma duk da haka muna iya koyo daga majami'u da suka sha tsanani cewa Allah na iya amfani da magabtan mu ma domin ya kawo mu kusa gareshi. Ta wannan hali muna iya daukaka magabtan mu domin abubuwan da suka sa ya faru da rayuwar mu, idan kana fama da la'anta magubtan ka domin irin wulakanta ka da suke yi, tsaya kayi tunani ko me yasa Allah ya bari haka ya faru da rayuwarka. Wai shin kana kara saukakawa ne ko kuma kana taurare hanyar sa? Allah zai koya maka wani abu ta wurin wannan? Idan haka ne kuwa zaka sake fuskantar wannan har sai ka koya?***

# MATSANCIN JITA JITA
## Kasar Sin: Masu Bi na Kasar Sin

RANA TA 205

***"Mun ji jita jita cewa mutane a kasashen turai sunji cewa babu azabta Krista a Kasar Sin". Haka wata wasika ta fara daga wata kungiyar masu bi na Kasar Sin.***

***Ku tuna da wadanda ke cikin sarka kaman kuna damre tare da su; wadanda ake wulakanta kuma, da shije kuma cikin jiki da kanku.***

*Ibran. 13:3*

"Fiye da yan'uwa Krista guda dari aka tsare a nan, kuma Krista da yawa da ke kasa da shekaru goma sha takwas suna cikin mugun matsi daga yan sanda. Wadansu ma jefa su ake yi a cikin ramin zaki, wadansu kuma ana dukan su da wata na'ura mai aiki da lantarki, wadansu kuwa ba su iya tashi sai rarrafe don tsananin duka.

Wasu kalilan ma sun kasa jurewa wannan. "Sun tona asirin masu bi ta bada sunaye da adireshi-na abokan aikinsu ga yan'anda. An yi musu hukumci, amma wadanda suka ki yin magana an sake su daga baya, domin rashin cikakken tabbaci.

Tsanantawa ya zama jiki a garemu. A lokuta da dama akan sake mu bayan anyi mana tambayoyi. Sa'anan sai mu koma wuraren namu muci gaba da bishara. Wadansu matasa suka so su bada kansu ga Allah domin aikin Kristi na cikakken lokaci. Sun fito daga gidajen su, da shirin yin amfani da dukan rayuwar su a cikin wannan aikin bishara mai hadari na kaiwa da kawowa na yada bishara a zaman masu yin bisahara. Mun fuskanci haka cikin tsoro da makyarkyata, tsoron cewa bayan yin bishara ana iya korare mu.

"Bishara ta kafu ta hanya mawuyaci an zubar da jini, jibi kai har hawaye mai yawa, an sadaukar da rayuka masu yawa, kuma an yi bajintar shiga iska da guguwa da ma ruwan sama".

***Jita jitar cewa a daina yiwa Krista tsanani a Kasar Sin sun tabbata karya ne. Alhali ma, wadannan jita jita na iya zama dabaru ne ga magabta suke anfani da su wajen danne addu'oi da taimako da masu shan tsananin ke bukata. Galibi mukanyi kamar idan muka fada wa kanmu cewa abukaza fa ba haka yake ba, to watakila kuwa ba haka yake ba, idan muka kare kanmu da lissafta batun tsanani da labarun masu bi da suka shiga tsananin da suka haye amma da kyar, sa'an nan zamu fara gaskantawa babu tsanani. Ba zamu iya boyewa ko kuma musun gaskiya da tunani a gaba zata sauya ba. Tabbasa yan uwan mu maza da mata na cikin tsanani a yau a cikin kasashe marasa yanci. Saninn haka, me zaka ce? Za ka yi addua? Zaka yi aiki? Zaka bayar? Ka dauki lokaci ka yi tunani da addu'a akan irin amsa da ya kamata ka bayar.***

# MATSANCIN TAMBAYA

## *Rome: Ptolemaeus*

RANA TA 206

***"Kai Krista ne?" Sau uku ana masa tambayar sau uku kuma yana amsawa, "I". An shahidantar da Krista guda uku. Mai mulkin Kasar Rome a lokacin watau Sarki Urbicus makiyin Krista ne kwarai a shekaran A.D 150.***

*Kune gishirin duniya. Amma idan gishiri ya rasa dandanon sa ta kaka zata sake gyaruwa.*

*Matta 5:13*

Ptolemaeus ya sami zargin cewa yana koyaswa cewa ceto yana samuwa ne ta wurin bangaskiya ga Yesu Kristi kadai. Ya ki jijnin irin rudi da rashin halin Allahntakar wannan zamani. Sabo da haka lokacin da Urbicus ya tambaye shi ko shi Krista ne, ba zai iya karya ba. Lalle ne ya tsaya wa gaskiya ya amsa da Karfin zuciya, "I". A dalilin haka kuwa aka daddaure shi da sarka aka doddoke shi sau da dama.

Aka sake kaishi gaban Urbicus, aka sake yi masa tambaya daya kawai kai Krista ne?"

Radadi da azaba basu iya sauya tabbataccen abu "I" Ptolemaeus ya sake amsawa.

Dajin kama shi da aka yi, wani dattijo mai nisan shekaru ya roki Urbicus da kada ya kashe shi. Me zai sa ka ka kashe wannan irin kyakkyawan malami? Ribar me zaka samu daga kai har Sarki? Bai karya wata doka ba.

Abin da yayi kawai shine ya shaida cewa shi Krista ne. Da jin irin kariyar da dattijo ya kawo, sai ya yi masa tambaya guda daya kawai. "Kaima Krista ne?" Dattijo ya yi karfin hali ya dage "I, ni Krista ne".

"Idan haka ne kana iya haduwa da malamin". Idan wannan bai isa ba, wani mutum ya fito da kin abinda suke so suyi. Bugu da kari aka sake wannan tambayar, "Kai Krista ne?" su Krista ne hukuma ta bada izini aka kashe su.

***Wannan tambaya ce mai sauki,"Kai Krista ne?" tambaya ce mikakkiya, tambaya ce na mutum da kansa. Amsar ita ce I ko A'a. Idan haka ne menene wuyar bada amsa? Ba ana nufi ko Kriksta basu san yadda zasu amsa bane. Abin da ke kawo damuwa shine wasu ba sa yi mana wannan tambaya akai akai. Ba wai muna zama a cikin wata rayuwa dabam ba, da kowa zai yi tunanin cewa tambayar ta fita dabam daga rayuwar mu. Dole ne mu yarda cewa mutanen da ke irin wannan tambaya da aka yi wa Ptolemaeus kalilan ne. wannan dhine aihinin abin dubawa. Tun yaushe rabonka da nuna halin rayuwa da ya iya jawo hankalin abokin aiki, mawaki, ko abokin kut da kut su yi sha'awa har su nemi sanin shin wane addini ne kake bi? Ka san amsar-yanzu kuwa ka yi rayuwar da zai sa wani yayi tambatar.***

## MURMUSHI MATSANANCI

## *Romania: Milan Halmovici*

RANA TA 207

***Wannan dakin kurkuku mai sanyi da kuma duhu yana cike da Krista yan Romania wanda suka dage da nufin kawo hasken Yesu zuwa cikin wannan duhun. Daya daga cikin fursonin masu bi din bayahuda ne mai suna Milan Haimovici***

*Kuna murna cikin bege, kuna hakuri cikin kunci, kuna lizima a cikin addu'a*

*Rom. 12:12*

Watarana Milan ya fara yin magana da wani abokin dakin sa wanda yake mashahurin mai ilmin kimiyya ne kuma farfeso amma mara sanin Allah. Milan bai kai wannan matsayi a ilmance ba, amma ya bashi labarin Yesu. Farfesannan ya karyata shi. "Kai makaryaci ne, Yesu ya yi rawuwarsa shekaru dubu biyu da suka shige. Ta kaka zaka ce kunyi tafiya tare har kuna zanta da shi?"Milan ya amsa, "Gaskiya ne cewa ya mutu shekaru dubu biyu da suka shige amma kuma ai ya tashi daga mattatu kuma yana raye a yanzu haka.

Daga nan sai farfeso ya yi wa Milan takala, "To kace ya kanyi magana da kai, "Wane irin alama kakan gani a fuskarsa?"

Milan ya amsa, "Wasu lokuta yakan yi mani murmushi"."Irin wannan karya", farfeso yayi dariya. "Nuna mini yadda yake yin murmushi. "Milan kuwa cike da alheri ya amince. An yanke masa gashi kuma ga shi sai fatar jiki da kasusuwa, da kuma idanunsa da dan duhu duhu kewaye da su. Wassu hakoransa sun zube kuma yana saye da rigar fursuna, amma murmushi mai ban sha'awa ya fito daga lebuna sa. Fuskar mara tsabta ta haskaka. Gashi cike da salama, da gamsuwa, da Farinciki mai yawa a fuskar sa. Farfeson nan mara sannin Allah ya sunkuyad da kansa ya yarda, "Yallabai, ka ga Yesu".

***Murmushi al'ada ce da dan adam yake anfani da ita wajen nuna gamsuwa, amincewa ko yarda. Yin murmushi a lokacin da mutum yake jin zafi ko ciwo ko ma cikin azaba yana iya bada shaidar cewa ikon Allah ne ke aiki. Idan Yesu Kristi dan Allah yana cikin zukatan mu da gaske, to lalle ya kamata wasunmu su zama da bukatar mu shaida wa fuskokim mu wannan kyakkawan labari! Wasu lokuta mukan yi wakoki a majami'a sai kace wadanda aka yi wa mutuwa-tunanin mu sukanyi nisan miloli daga kalmomin bakunan mu. Me fusjarka ta ke bayyanawa game da dangartakar da Yesu? Kai mai shaida ne ga wadanda hanya ya hadaku? Kana shaidar gamsuwar Kristi a zuciyar ka? Ko roki Allah ya taimake ka wajen fahimtar sakon zuci kuma ya cika ka da farin cikin sa.***

## KALUBALE MATSANANCI

### *Judea: J. Oswald Smith*



***Ubangiji Yesu Kristi yayi amfani da dabara ta musamman a lokacin da ya ciyar da mutane dubu biyar wadanda suka bi shi da kafa daga garuruwan kewaye. Dare ya kusan yi, sai almajiran suka zo wurinsa, suna rokon Yesu ya sallami jama'a domin dare na kawo kai. Yesu kuwa yana da nashi shirin dabam. Ya sa mutane suka zauna layi layi bisa ciyawa. Bayan Yesu ya dauki abincin yayi godiya, almajiran suka fara rabo daga layin gaba har zuwa karshe suna baiwa kowa taimako.***

*Gama Allah yayi kamnar duniya har ya bada dansa haifafe shi kadai domin dukan wanda yana bada gaskiya gareshi kada ya lallace amma ya sami rai na har abada.*

*Yoh. 3:16*

J. Oswald Smith mai wa'azi ne kuma marubci, ya yi wata tambaya da ba a saba yin ta ba a wannan karo. Ko almajiran sun sake zagaye na biyu cewa su sake dauka?

"A'a! Idan da sunyi haka da wadanda suke layin baya sun tashi sun nuna kiyayya da yin haka. Da zasu ce, ku dawo nan. Ku kara mana. Domin me ne ne su da ke layin gaba zasu samu sau biyu kafin mu sami na farko?" Da kuma sune za a baiwa gaskiya. Muna yin maganar dawowar Yesu na biyu. Da yawa basu sami labarin zuwan sa na farko ba tukuna. Don me wasu zasu sami bishar sau biyu bayan wasu basuji na farko ba? Babu mahaluki guda daya a cikin mutanen nan dubu biyar ya sami zagaye na biyu sai da kowa da kowa ya samu a zagaye na farko".

***Krista da yawa na tsoronzuwa inda wani mai bishara bai taba takawa ba. abu mafi sauki shine a zauna a wuraren da aka fi sabawa. Duk da haka Yesu ya Umurci masu bi da su tafi cikin dukan duniya domin samun sababbin wurare inda ba a taba shaida sunan Yesu ba. Fassanar Smith ta ciyarda mutane dubu biyar yana kalunalantar dabarun mu game da watsa bishar. A dalilin menene mutane suna bada taimako zuwa ga mutane da suka rigaya suka ji bisharar kawai? Gaskiyar ita ce da yawa daga wadannan kasashe suna cikin hadarin cika da majami'u, a yayin da wasu wurare suke cikin rashin mallakkar ko da Littafi Mai Tsarki guda daya da aka fassara da harshen su. Ko taimakon zai tagaza ya daidaita nauyin ma'aunin? Ko rayuwar ka zai iya kawo bam bamci ga kokarin yin bishara a gobe?***

## Ingila: Bill da John

RANA TA 209

***Bill da John suna kusa da tashar jiragen ruwa a kudancin Ingila a lokacin da suka ga tutar Kasar Romania a kafe a kan wani Jirgin ruwa. Wannan lokaci kuwa shine yaÿin da Romania ta ke karkashin bakin mulkin kwaminisanci.***

*Galibi ban gaskiya ta kan zo daga jin bishara. Kuma akan ji bishara ta wurin maganar Kristi.*

***Rom 10:17***

Ba tare da dogon jawabi ba, sun gane fagen yin bishara da ke gabansu, suka kwance akwutunan Litattafansu Masu Tsarki, suka hau cikin Jirgin. Suka shiga dakin shakatawa inda dukanin ma'aikatan Jirgin mutane talatin da biyar suka taru. Bill da John suka yi bayanin dalilin zuwan su, sai suka fara zaro Litattafai Masu Tsarki da aka buga da harshen Romania. Ma'aikatan jirgin suka natsu don sauraren mutanen nan guda biyu. Yawancin su basu taba samun labari akan Allah da dansa Yesu ba.

A lokacin da Bill da John suka farga da cewar basu da isassun Littafi Mai Tsarki cikin harshen Romania. Wadansu masu kasumba suka cabke Bill a hannu da karfi kuwa suka aza shi akan kujera. Suka yi bayani tare da ban-hakuri a cikin turancin da basu kware akai ba cewa Bill zai zauna anan har sai John ya dawo da Litattfai isassu don kowa.

John bai san ta yi ba, yayi dariya ne ko yayi kuka, amma wannan shine kadai hanyar da yan Romanian zasu iya tabbatar da dawowar John.

A cikin kasar Kwaminis da ke cike da karya alkawura, basu yarda da kowa ba. John yayi maza ya tafi ofis ya debo Litattafai cike a cikin akwati.

Cikin sa'a guda kuwa sai gashi ya dawo, ma'aikatan jirgin kuwa suka karbi Litattafai Amsu Tsarki da godiya suka kuma saki Bill.

***Ku isar da kalmar. Allah da Yesu ya fada game da bisharar sa ta kowace iyawa, ta dukan inda bisharar sa ta bi ta kowace iyawa, ta dukan inda muka tafi, ta ko ma me muka yi, lalle ne muyi aikin bisharar Kristi. Ba da kamnu zai iya kaimu cikin tashar jiragen ruwa ko ma ga makwabtan mu da basu san Yesu ba. ko ta kaka lalle ne mu zama da shirin shaida maganar Allah ga wadanda suke cikin rashin ruhaniya. Kana samun karfafuwa domin isar da bisharar Kristi? Ko kana sane da cewar tana iya yiwuwa lokacin da kake da shi na isar da kalmar Allah takaitaccene? Kada ka yi naka cikin aikin, me zaka iya yi yau domin yada bisharar Kristi.***

***Muna yin addu'a domin gwamnatin Sudan, kuma muna yin godiya ga Allah domin irin wannan gwamnatin. Muna godiya domin irfin manufofinta da kuma yadda takeyi gaba da Krista-razanarwa, tsoratarwa da dauri a majami'a ta yadu. Dubi abin da Allah yayi a tsakiyar dukan wadannan tsanani! Dubbaine yawan mutanen da ke juyowa zuwa ga Kristi***

*Wani Ba Sudane Krista*

## WATA MATSANANCIYAR MAI BUGA TAKARDU

### *Kasar Sin: Kati Li*

RANA TA 211

***Bakin sun sauka a cikin sirri kuma a boye suka isa gidan wata dattijuwa yar Kasar Sin. Aka raka su ta bayan labule sa'annan suka yi rarrafe na fiye da tsawon takun kafa 1200 ta wata hanya da aka gina karkashin kasa doguwa kuma cike da duhu wanda ya kare a wasu kananan dakuna guda biyu masu kama da kogo.***

*Da yake an amince da haka cewa shi wanda ya fara aiki mai kyau a cikin ka zai kai aiki ga kamala har zuwa rananar Kristi Yesu.*

*Fil. 1:6*

A cikin daya daga dakunan Kati Li yar shekaru gomasha tara da haifuwa tana gudanar da buga takardu da wata na'urar irin na tsofon zamani. Kati ta kanyi wattani a cikin wannan daki mai kamar kogo tana buga takardun da gwamnati bata bada izinin a yi ba watau na Krista. Idan aka kane kuwa, ba zata iya kara kanta a fili ba.

Amma a yayin da madaba'ar boye take cin gaba da buga takardun sai Ma'aikatar tsaro ta fara yin zargi ta shiga yi wa mutanen kauyen da kewaye tambayoyi. Wadanda suka san da madab'ar suka yi alkawarin bada kai.

A karshe suka fusata domin rashin samun hadin kan kauyawan, sai yan tsaro suka fara anfani da nakiya suna tarwatsa gidaje a kauwen har sai da suka iso gidan tsohuwar. Sun gano kogon kuma sun kwace na'urar dab'i. Ma'aikatan madaba'a sun rigaya sun tsare tuni ba tare da samun wani rauni ba.

Har wa yau, da Kati Li da sauran ma'aikatan suna cikin buya. Idan ko aka kama su to za'a daure su a kurkuku ba tare da bata lokaci ba, kuma ma ana iya yi musu hukumcin kisa. Ba zasu sake ganin abokansu ko iyalinsu kuma ba. Amma aikin da Kati ta yi ta wurin littafai da mujallu da ta buga. Da ke Krista suna karanta wadannan takardu nata.

***Ana iya katsewa, ana iya juyi, ana ma iya dakatarwa na wani lokaci. Amma mulkin Allah a kullum gaba gaba yakeyi. Ba za'a taba iya tsayarwa ba. Kristi iza wannan mulki ga cin gaba a lokacin da ya ba mafificin umarni ga almajiran sa. Tun daga wannan ranar kuwa, wadanda ake karawa ga wannan mulki sai cin gaba da karuwa suke yi da karfi kuma baicin biyayya magabta. Lalle ne da yawa sunyi kokarin tsayar da bashara? Kana da damuwar cewa abokinka ya kare a dalilin wasu al'amura da baka zata ba? Ka tuna Allah bai gama da kai ba tukuna. Kokarin ka na yada bishara zai shafi wadansu muddin kaci gaba da rike bangaskiyar ka a gareshi.***

# MATSANANCIN ARZIKI

## Kudu-Maso-Gabashin Asiya: Kristocin Hmong

***Sun soki wani Krista da wata doguwar wuka ta bakinsa kuma suka zuba wa wani ruwan zafi ta makogwaro wanda aka kama shi wai don an same shi dauke da Littafi Mai Tsarki. Akwai ma iya sukutum da aka nutsar a kogi.***

*Da nufin a iske auruwar bangaskiyar ku- abin a yafi zinariya daraja, wadda takan lallace ko da an gwada ta da wuta-ta kai zuwa yabo da daraja da girma a kan bayyanuwar Yesu Kristi.*

*1 Bitrus 1:7*

Masu bi na kabilar Hmong ta kudancin Asiya sun amince da su bada shaidar su a dauke a cikin majigin video. Suna so su karfafa Krista da suke Turai. Wani Krista na kabilar Hmong ya shaida: Hukomin kwaminis sun tsorata domin mutanen Hmong da yawa sun zama Krista. Sukan yi wa Krista duka domin suna kokarin tilatsa masu da su juyo ga baita wa mugayen ruhu".

Yan sandan kasar sun haramta mana zama Krista. Suna tsoratar da mu cewa za a jefa mu a kurkuku, ko kuma a kashe mu". Wata mata ta kara da cewa. "Amma in lalle mu mutu domin Kristi to a shirye muke.
Wadannan masu bi a shirye suke su shiga kowane Irin hadari, domin duniya ta sani a tsaye suke daram domin fuskantar tsanani.

Kabilai Hmong ita a mafi girma a Kudu-Maso-gabashin Asiya, kuma suna cikin yin yaduwar Kristanci mafi girma. Ita ce kuma kabilar da tafi shan tsanani.

Wata matar ma tace, "Na godewa Allah da yake nuna aikin karfin mu. Na bada gaskiya cewa tsanani na jarrabawa ce ta bangaskiyar mu ga Kristi. Tana zabulo arzikin mu na gaske. Addu'a cewa zamu iya manne wa bangaskiyar nu har Karshe.

***Ana karfafa karfe ta wurin aiki da wuta a nakera-a kanyi anfani da ziga-zugi a zafafa wutar ta yi tsanani, sa'anan a fito da shi bayan yayi jawur ayi ta duka da guduma a sa.rafa shi zuwa yadda ake so bayan an fitar da datti da sauran su sa'anan a barshi yayi sanyi domin karfen ya taurara. Sarrafawa mai kamar haka yana karfafa bangaskiyar mu. A lokacin da aka gasa mu da zuga-zugin kiyayya daga wasu, aka yi mana duka da gudumar azaba, sa'anan mu sami sanyayawa daga Allah, dukan dattin mu zasu bace bangaskiyar mu kuma ta karfafa. Ko ka lura da sarrafawa da ke faruwa da rayuwarka? Kada ja cije wa, kop wannenta. Ka koya daga yan'uwan ka maza da mata na kabilan Hmong. Magabtan ka basu sami ashe sakamakon kiyayyar su zai kar karfafaka ne.***

# KARIN MATSANANCIN DAN FASA KWAURI

## *Gabashin Turai: Mihai*

RANA TA 213

***Motar Volkswagen ta Mihai tana karatowa a hankali zuwa iyakar kasa inda ake binciken motoci kafin a baye. Sai ya yi gajerwuwar addu'a, "Ya Yesu, ina rokonka ka tsare maganar ka kada masu tsaro da ke bincike su gano kuma a kwace.***

*Amma muna da wannan kaya mai-daraja cikin tukwane na kasa domin ta ci girman iko ya kasance na Allah ba daga wurin mu da kanmu ba.*

*2 Kor. 4:7*

Masu tsaron iyaka suka umurce shi ya ya sauka daga maotar sa daga nana kuwa suka fara yi masa tambayoyi. "Me yake kawoka kasar mu? Zaka ziyarci wani ne a cikin Kasar mu? Idan haka ne to wanene shi? Kana dauke da bindigogi?"

A hankali kuwa mishau ya amsa kowace tambaya, amma zuciyarsa tana tana cike da dimauta, domin a yayin da ake masa tambayoyi wasu suna binciken cikin motar kuma ya gani ta gefe, idanun wani mai tsaro yana duba karkashin kujerun motar. Mihai ya fara gajiya da tsagewa na dogon lokaci haka. Bayan sun gamsu da amsoshin da ya bayar, masu tsaron iyaka suka bashi damar shiga kasasu, hajjar sai mai tunani kuwa ta sami nasarar wucewa ba tare da sun gani ba. Wannan saurayi mai karfin zuciya yayi shekaru goma yana sjigar da Littafan Krista zuwa cikin kasashen kwaminis na gabashin turai, kuma ba'a taba gano hajjar sa ta boye ba. Muhai mutum ne kamar kowa wanda yake da baiwa ta hangen nesa fioye da misali kuma kokarin da yake yi abu ne da ya kamata ya kalunalance mu. Bashi da kafafu-an yanke su har zuwa chinya-amma ya dage ya ki yardar wannan larura ta hana shi yin abinda yakeyi.

Kamar mai bishara Bulus. Mihai ya sani cewa ikon Yesu Kristi zai sami kammalawa a cikin laruran da yake da ita ta jiki. Bayan da aka yi masa kafafu na karfe sai aka yi masa karfafa na karfe, sai ya cusa takardun bishara a cikin ramukan kafafunsa na karfe da doki kuma sai ya ci gaaba da bulagonsa.

***Idan aka zo batun aikin Ubangiji, to shi mai bada dama ne dai dai ga kowa. Mihai ya ga cewa larura da yake da ita domin aikin Allah. Kowace irin bishara tana iya zama wata dama na bauta wa Allah. Misali, wadanda suka shiga cikin hatsarin ambaliyan teku ko kogi, irin wannan lyali zasu taimaka wa wasu da suka shiga irin wannan hali domin su dandana irin wannan bala'in a baya. Me kake jin yan saka ja-da-baya wajen zama da anfani ga aikin Allah. Ka mika su ga Allah ka ga yadda zai yi anfani da su wajen daukaka sunansa da kuma ribar da, kai zaka samu.***

# MATSANANCIN DUKIYA

## Tajikaistan: Taron Majami'ar Grace Sonmin

***A ranar lahadi ne lokacin da majami'ar Grace Sonmin ta e yin taron sujada ne kowane mako a garin Dushanbe a kasar Tajikistan, kuma ko da shike a yanzu Kasar tana da yanci daga tsananin Kwaminis, yan tsagerun Islama haryanzu suna yiwa majami'u kiyayya a fili. Tsanantawa Krista bai kare ba hannu kawai ya canza daga wani dan sunkuru.***

*Kullum a cikin jiki muna dauke da mataswar Yesu domin ran Yesu kuma shi bayana a cikin jikinmu. Gama mu da muke da rai, tuttur ana bashe mu ga mutuwa saboda Yesu domin Yesu kuma shi bayana cikin jikin mu mai mutuwa.*

*2 Kor. 4:10-11*

A daidai lokacin da bakon pasto mai zaiyara ya kamala jawabin sa sai aka ji karar fashewa wani abu can bayan majami'ar kuma ya rushe ginin. Bom ne. A cikin kyaftar ido juwa masau sujada suka dimauta suka fara gudu domin tserewa da rayukan su. Suka yi kokarin fitiowa, amma sai wani bom din ya sake fashewa a kan hanyar da suka biyo garin fita. Gawawwaki a ko ina a warwatse a cikin majami'ar da aka sani da zama mafaka".

Wata tsofuwa tana kwance akan dabe ba ta iya ko motsi. Littafi Mai Tsarki da ta ke anfani da shi nan baya ba da jimawa ba ya fadi a gefen ta da jininta a jikin Littafin. Kuma Littafin na bude zuwa wani shafi inda ta zagaya wasu ayoyi guda uku da alkalami wani lokaci kafin ranar kawo wannan hari a majami'ar ta. "Amma munada wannan a cikin tunkuyar yumbu domin ya nuna wannan iko-mafi karfi daga Allah ya ke ba daga gareku ba. A takure muke ta kowace hanya, amma ba a ruguje ko a rude ba ba wai mun fidda rai ba ko kuma azabtu amma kuma ba a yashe mu, ko kaimu kasa ba, ba a kuma hallaka mu ba. (2 Cor. 4:7-9)

***Tsagerun musulmi sun dauki cewar mutane marasa laifi abin kashewa ne don ciwa burin manufar su. Amma mutuwar masu bangaskiya ya haskaka kuam yana kyalli kamar jauhari a zaman shaidar amincewa ta Allah. Ta yiwu magabta suin raunana tsuhuwan nan a jiki-"Tunkuyar ta yumbu"-amma dukiyar ta ta can ciki ta fito fili a yayin da ruhunta ya tafi aljannah yan kwanaki bayan kai harin. Muna sane fiye da da cewa 'mutuwa na iya zuwa ba tare da zato ba ta hannun maganta. Amma da ma kwarai makiyio zai iya yi shine ya kashe wannan jikin. Wannan jikin ba shine ainihin ka ba. "Ka zama da kwanciyar rai yau tunda ka sani cewa dukiyar ruhun***

## MAFARI MATSANANCI

## *Amrika: Richard da Sabina Wurmbrand*

RANA TA 215

***Kayi tafiya cikin hikima wajen wadanda ke waje.***

***Kolosiyawa 4:5***

***Watarana a shekarar 1967 da bazara wannan iyali suka zauna a gaban tsofon kekken rubutun su da ke ajiye a kan tebur a cikin sabon gidan su-cikin Kasar Amirka. Ba a dade kwarai ba da Pasto Richard Wurmbrand ya sha zama a dakin kurkuku mai sanyin gaske da duhu na gaske a Kasar Romania domin yin aikinsa na majami'ar karkashin kasa. Matarsa Sabina, ta mai hukumcin bautar gwale gwale a sansanin kurkuku.***

Iyalin nan suka shiga zurfin tunanin wannan sako da Allah ya basu. Suna so su sahida labarun jarrabawa, da nasaru da fuskantar Krista da ke cikin tsanani a kasashen kwaminis don duk duniya ta ji kuma ta sani. An tsoratar da wannan iyali a Romania ta bakin Yan Sandan Asiri cewa kada su fadi wata maganar batanci akan kwaminasaci, amma tsoratuwar bai shaitse su ba. A garesu tilas ne su tada fadar wahalar da jikin Kristi ya ke sha-muryar da a kyale kuma duniyar da ke da yanci ta manta. Kalmomin su tsaru daga shafi zuwa shafi, kafin a yi nisa kuwa mujarlar su ta farko da ake kira "Muryar Shahidar" ta wallafu. Sun fara da jarin dala dari ($100) kacal da sunaye da adreshin wasu Krfistoci da suke da sha'awar taimakawa alkibilar da aka hanga kuma aka haifar a cikin dakin kurkuku na daga kai-sai-kai yanzu ya habke zuwa wata gagarumar kungiya da ke ko ina a cikin duniya inda bata da kai domin yi hidama ga azabtattu domin Kristi. An raba milyoyin mujallu da kasidau na Muryar Shahidai a ko ina a cikin duniya wadanda aka fassara zuwa harsuna fiye da goma sha biyu.

***A fara ta wani wuri. Ta hakane shawarwari masu kyau na yin hidimar Ubangiji suke farawa. Da wuya sukan yi amaja wajen anfani da wani tunani mai kyau da yazo musu, maimako su fara ta wani wuri. Muna fadawa kanmu zamu bautawa Kristi, a lokacin da yara ke girma su zama mutanen kansu; a lokacin da muka biya basusukan mu, har da zakka. A kowane lokaci mukan ce zamu fara bauta wa Kristi, bayan wasu abubuwan sun kammala, to mun kuskuri ainihin kira da akayi man kenen. Me Allah yake kiran ka da kazo kayi? Me kake yi yanzu domin cika umarnin kira da yake yi maka?***

# DA MATSANANCI

## *Kasar Girka: Timothy*

RANA TA 216

***Ko da shike Thimothy yaro ne, Bulus ya karfafa shi da ya zama abinn misali ga kowa. Timothy kuwa ya nuna cewa shi da ne***

*Amma ka lizima kai a ayyukan da, ka koyo wadanda ka tabbata da su kuma, ka sani wurin ko wadannan ne ka koyo su.*

*2 Timoti 3:14*

Timoty ya fito daga garin Lystra, daya daga cikin birane da Bulus ya ziyarta a tafiyar sa ta farko ta bisharar. Mahaifin Timothy mutunmin Kasar Girka ne, amma mahaifiyarsa da akarsa Yahudawa ne masu bi wadanda suka renwe shi ya tashi da al'adar uwayen sa. Alhali ma dai Littafi Mai Tsarki ya nuna misalin bangaskiyar Timothy ne. Babu shakka Bulus ya hangi cewa Timothy zai zama kakkarjan mai bangaskiya. A lokacin da Bulus ya zagayo tafiyasrsa ta biyu tare da Silas da Luka. Timothy ya tafi tare da su zuwa Maikidoniya.

Bulus ya dauki Timothy a zaman dansa a cikin bangaskiya. Lokacin da majami'ar Afisawa ta bukaci Pasto. Bulus ya ajiye Timothy a wurin domin yayi koyi da rawar Bulus. Da alamar ma yana tare da Bulus a ranar da aka fille kansa a Rome domin Bulus ya aika masa cewa ya zo domin yin ziyara ta karshe.

Bayan mutuwar Bulus, Timothy ya koma Afisawa domin ya shugabanci majami'ar.

Ya ci gaba da la'anta bauitar bautar gumaka wanda shine asalin yin arzikin mutanen Afisawa da yawa. A lokacin da Domitian ya ba da izinin tsananta wa Krista karo na biyu a Rome sai matsafan suka sami karfin zuciya. Aka jejjefi Timothy da duwatsu har ya mutu a shakarar AD 98. ya dagawa ban gaskiya har karshe kamar yadda Bulus ya koya masa.

***Ba a tsammaci wani ko a karfafa wani cewa yayi rayuwa ta Kristanci shi kadai ba. Alhali ma dai babu damar yin haka. Kamar dai yadda Bulus ya shugabanci Timothy, muna bukatar wani wanda zai nuna mana hanya kuma ya amince da hangedn irin kokari da zamu kawo ga hidimar bishara. Mukanyi girma a wurin koyi da kyawawan misalai na shugabannin mu cikin majami'un mu, ko na unguwar mu, ko na iyalinmu, ko na makarantun mu. A yayin da muka fara zama mutanen kanmu, to muma zamu zama abin kallo ga na bayan mu.***

***Wanene abin koyi ga bangaskiyarka? Wanene ke da alhalin koya maka yadda kake yin rayuwa ta ruhaniya. Mai yiwuwa wani dan'uwane, aboki, ko pasto. Ka gode Allah da ka sami koyi ta wurin su.***

***Yanzu na gaskanta cewa Allah cikin hikimar sa yana a sami shahidai a kowane karni domin, idan ba tare da su ba, ta hakika mutuwar Kristi zata ci gaba da dishashewa… A yayin da muke duba [shahidai] hazon da wani lokaci yakan yi mana inuwa Golgotha ta karni na farko ya kan kone sarai, sa'annan zanu ga Ubangiji a manne da kusoshi a kangiciye.***

***Mark Galli***

## Romania: Wani Pasto da yayi Fursuna

RANA TA 218

*Zakayi murna kuma babu wanda zai iya kwace muku farincikin ku.*

*Yoh. 16:22*

***Abin da'ban mamaki yadda kake ganin Yesu a fuskar masu bi. Fuskokinsu na walkiya, kuma wannan wata nasara ga daukakar Allah ta haskaka a fuskar Krista a cikin kurkukun kwamnins. Ba mu yi wanki ba-ni banyi wanka ba har tsawon shekaru uku-amma daukakar Allah ta haskaka har ma bayan irin dattin da yake tare da ni. Kuma a kullum fuskokinsu na dauke tare da murmushi irin na cin nasara," wsani fursunan pasto ne ya rubuta wannan.***

Nasan da wasu Krista da aka saki daga kurkukun Kwaminis, kamai dai nawa. Kamar su, an sha tsayadda ni akan titi watau masu wucewa suna tambaya? Yallabai, menene ka tsare dakai? Muna yi maka ganin mutumin da ke cike da farinciki. Menene asalin farincikin ka? "Na gaya masu asalin daga zaman kurkuku ne na shakaru da yawa a kasashen kwaminis ina shan azaba a madadin Mai Cetona.

"Basu iya fahimtar haka ba domin bazasu iya tunani su hange gaba da tunani suyi hange gaba da wahalau na rayuwansu ba. Basu koyi bin tafarkin Ruhu Mai Tsarki ba domin su ji kuma su karu da bayanar Allah tare da su. Da yawa zasu yi tunani. Ina ma da kusan irin rayuwana da nake da ita-mijin da ke dukan matarsa-matar da ta cika yin gunaguni, yaya da ke bautawa iyayensu rai, akwai al'amura ma su wuya da yawa. Amma yaya batunsu yake? Yaya suke ma da za'a kwatanta su da farincikin sanin Yesu?

***Abin da Yesu ya bayar, babu wanda ya isa yakwace. Yakan bamu farinciki da tarayyar Ruhu Mai Tsarki a cikin mu. Kuma ko da shike al'amuran mu sukanyi dubu, amma farincikin mu yana haskakawa. Harma datti shekaru uku a cikin kurkukun kwaminis ba ya iya boye farinciki irin na Krista. Ba lalle ne mu yi farinciki da azabar da muke sha ba. Babu mai yin murna da abin bakinciki. Duk da haka mukan lizima cikin farinciki a dalilin kusantar da Kristi ya kan zo mana a lokacin bakincikin mu. Ko kana cikin rashin farinciki? Ko ka gane babu mai iya kwace maka farincikin ka? Idan har kana aikin wannan rashin a rayuwarka, ashe don ka bada ita ne da son ranka. Ka roki Allah ya sabunta farincikin ka a gareshi yau.***

## MATSANANCIN WARKASWA
### *Pakistan: Asif*

RANA TA 219

*K'innuwa na sunji labarin ka yanzu kuwa idanu na sun gan ka.*

*Ayuba 42:5*

***Kafar Asif ya sami karaya a lokacin da motar ta buge shi a kan titti a Pakistan. Cikin tsakiyar zafin ciwo, sai yaji an sa hannu a kafar. Da ya daga kansa sai ya ga wata mace tana addua domin Yesu ya warkadda shi. Asif ya fara fusata domin shi musulmi ne a lokacin kuwa sai wani irin karfi na bam mamaki ya fara shigo masa a jiki. Kafarsa ta mike, kashin kuwa ya koma gurbin sa. A hankali kuwa ya tashi ya taka da kafarsa zuwa gida daga lokacin.***

Kwadayin son kara jin labarin irin al'ajiban warkawa na cikin Littafi Mai Tsarki wacce matar ta bashi. Asif ya tafi wajen limaninsa da tambayoyi a masallacinsu. "Me ya sa kake magana akan Yesu? "Limanin ya tambaye gastsine. "Me zai hana in nuna sha'awa a gareshi? "Asif ya tambaya, "Ya warkadda ni".

Limanin tare da wadansu kulle Asif a wani daki suka tilatsa shi ya sha dafi, da tsananin cewa idan ya mutu kafin ya karbi Yesu, zai tafi Aljanah. Duk da haka Asif ya farfado kuma sai dakin nan mai kura ya cika da haske Asif kuwa yayi shaida da bakinsa yace, rayuwa ta taka ce. Muddin ma duniya. Zan yi aiki dominka"

Tun wannan lokacin, iyalin Asifsun ki shi, kuma an she yi masa duka domin ya ki ya daina shaidawa mutane labarin sabon aboki da yayi watau Yesu Kristi.

***Wasu lokuta sai mun dandana ikon Allah kafin mu gaskanta. Alhali ma dai marasa bi da yawa sukan fi son yin muhawara akan addi'ni daga nesa maimakon fuskantar muhawara akan addi'ni daga nesa maimakon fuskantar muhawara ta ruhaniya mutum da mutum. Babu wanda za musunci abin da mutum ya yi ko ya gani. Shi wanda ya gani ai shine ganau. Kusantar Allah shine samun damar jin ikonsa da jin kusantar sa. Littafi Mai Tsarki na cike da misalai masu yawa na marasa bi da suka dandana ikon Allah. Wasu sunyi na'am da sujada. Wasu sun kangare kuma sun shiga azabtar yin taurin kai. Ko da ta wane hali ne mutum ba ya zama kamar yadda yake bayan saduwa da ikon Allah. Abin kamar ma Allah ya na yin magana ne da zuciyar da ta kangara, ni hakika nake. Kayi biyayya. Ta wane hanya Allah ya nuna maka hakikansa? Da wanene zaka tattauna abin da ka sani game da Ubangiji?***

# MATSANANTAN BALAN BALAN
## Koriya ta Arewa: Muryar Shahidai

RANA TA 220

*Kowane nassi hurarre ne daga wurin Allah. Mai anfani ne ga koyaswa ga tausayawa ga kwabewa ga faro kuma da ke cikin adilci.*

*2 Tim. 3:16-17*

***"Kaka, dubi abinda na samu!" yarinya yar Koriya tana murna, tana rike da wani abu da bata taba gani ba. Kakarta ta duba amma da yake idanun tsufa ner ba ta gane ko menene abin. Saboda haka sai ta kira uwar yarinyar. Zo nan ki duba kuima ki gaya mani menene wannan abu da yarinya ta samu".***

Diyar tsohuwar ta shiga daki ta karbi abin daga hannun uwarta. Diyarta ta fara karanta kalmomin da aka buga (rubutu ) a jikin balan balan na roba. "Ubangiji Yesu yana kaunar ka. Yan uwanku maza da mata basu manta da ku ba. Gama Allah yayi kaunar duniya yar ya bada dansa haifaffe shi kadai".

Sai tsofuwar ta fada da karfi ta ce, wannan maganar Allah ne aka rubuta! Sun aiko mana da ayoyin Littafi Mai Tsarki a jikin balan balan! Ki ci gaba da karantawa". Wannan balan balan yana dauke da kalmomin karfafawa domin dukansu uku da bakin zamani uku watau kaka, Ya' da jika. Yana dauke da sako daga Kristocin Turai kuma akwai ayoyin Littafi Mai Tsarki fiye da guda dari shida, yana bi da mai karantawa daga lokacin halita har zuwa lokacin giciye, har ma zuwa dawowan Yesu na Biyu. A cikin shekaru goma baya, fiye da balan balan irin wannan guda dubu dari aka zubo a kan Koriya ta Arewa.

Kungiyar Muryar Shahidai ta sami wani hanya na musamman don isar da maganar Allah zuwa ga mutanen Koriya ta Arewa da ke cikin rashin yanci.

A zabura 19:1 an rubuta "Sammai suna shaida daukakar Allah, gajimarai kuma suna shelar aikin hannun sa".

***Kamar dai balan balan na cikin wannan labari, Allah yana son ya zubo mana maganar sa a cikin zukatanmu a dai dai lokacin da muke cikin bukatar haka din. Amma mu sani ba zai kawo wa tunanin mu kalmomin da ba bu su ba tun farko.***

***Akasin haka kuwa shine, ko da shike muna walwala a, a kasashe masu yanci, galibi mukan yi alamuran mu kamar muna kasashe marasa yanci irin su Koriya ta Arewa da basu da damar isa ga maganar Allah. Binciken mu na Littafi Mai Tsarki kullum muke sai kace ba mu mallaki littafi ba sam sam. Watakila lokaci yayi da zamu roki Allah ya zubo mana kalmominsa su ketere-kan iyakar dodadden lamirin mu. Kirkir lokaci domin binciken Littafi Mai Tsarki kowace rana kuma ka roke shi ya sabuntar da bukatar ka ta maganar sa.***

# MATSANANCIN GASKIYA

## Pakistan: Nadia naira Masih

RANA TA 221

***In hakanan ne Allahn mu wanda muke bauta masa, yana da iko ya ce mu daga hannuka ya sarki. Amma idan ba haka bane, an sanashe ka ya sarki; ba za mu bautawa Allahn ka ba, ba kwa zamu yi sujada da gumki na zinariya banda ka kafa ba.***

*Daniel 3:17-18*

***Nadia Naira Masih yar shekaru goma sha biyar Krista ce tsayayya. Abin da take yi a kullum a lokacin da take gida shine tayi addu'a ta karanta Littafin ta Mai Tsarki a kowace safiya. Ko da shike iyalin ta basu ganta ba tun watan Febrairu 2001. Sun dauka tana cin gaba da yin haka a gidan mai kamata.***

Wani musulmi mai suna Maqsood Ahmed ya suce Nadia. Uwar Maqsood a wannan lokacin kawa ce ta iyalin Nadia ita ta taimakata ta jan hankalin Nadia daga cikin gida, inda aka tilasta mata shiga wata mota tare da Maqsood da yan'uwansa maza guda biyu da kuma wani abokinsu dauke da makamai masu sarrafa kansu.

Ba a sake ganin ta ba tun lokacin. A Pakistan ba kasafai ake jin labarin satan yan'mata ba, amma sanannen abu ne ga kowa cewa Yan Sandan Pakistan sukan kau da kansu duk lokacin da aka karya dokar kasa idan dai Krista ne aka cuta, musamman ma idan aka basu cin-hanci. Haka kuma ake jin ya faru a batun satar Nadiya. Yan sandan unguwan sai amaja suke yi wajen bincike. An kawo takardr shaida gidan Nadia da cewar tayi bayani, ta wurin auren ta, Nadia ta zama musulma bisa ga dokokin su ita ba Krista kuma ba. Nadia yar shekaru kalilan ne, iyayen Nadia suna jin bacin rai da jin rashi, iyayen Nadia basu ce kome ba ga game da Masqood ba. maimakon haka suna bada gaskiy Allah mai iko ne da zai yi abinda ake bukata domin Nadia ta dawo gida.

***Aminci wani abu ne da ba za a ia fahimta sosai ba sai dai idan ta dauro baka da sauran wani abu sai ita. Iyayen Nadia sun san yaya amincewa yake. Ba lalle su amince watarana Nadia zata dawo ba, maimakon haka suna da amincewa cewa Allah yana da ikon da zai sata ta dawo lafiya. Akwai gagarumin bambamci. Idan suka ce zasu amincewa wani takamammen sakamako, amincin suna iya samun gargada idan haka di bai samu ba. Amma sunyi zabin su amince da ikon Allah da yafi kowane iko. Idan Allah cikin hikimansa bai bada izinin dawowarta ba, zasu amince masa duk da haka. Kana amincewa da Allah, bisa ga sakamako? Ko kuwa ka amince dashi ko da wane irin sakamako ne ya zo?***

# HAKIKANCI MATSANANCI

## *Rome: Justin*

RANA TA 222

***"Idan aka fille maka kai a zaman mai laifi, ka gaskanta cewa duk da haka din zaka tafi aljannah?" inji Rusticus jami'in birni.***

*Kuma kada ku ji tsoron wadannan da suke kir jiki, ba su kwa da ikon kashe rai, duk da jiki cikin jahannama.*

*Matt 10:28*

"Na ba da gaskiya idan har na jure wa dukan abubuwa zan sami dukan abubuwan da Yesu ya alkawarta mani". Inji Justin. "Gama na sani kyautar sa ta na nan daram tare da dukan wadanda suka manne a gareshi har karshen duniya." "To kana tunani kenan cewa zaka samu lada a can?" Rusticus kishingide ga rashin hakuri. "Lalle ne ka yarda ka yi hadaya ga allolin".

Justin ya tsaya ba tareda motsi ba. "Babu wani mai cikakken tunani da zai yarda yayi wa sa da dangatakarsa da Allah. Rusticus fa abin ya ishe shi. "Sai fa ayi maka hukumcin kisa". Na sani idan na mutu a dalilin shaidarsa, bani da bukatar jin tsoro. Ina lissafin mutuwa domin wannan dalili ya zama samun cetona da amincewa a gabab Kristi, "Justin ya amsa masa. Saura da ke tsaye tare da Justin suka ce, kuma bama yin hadaya ga gumakai."

Rusticus ya zartas da hukumci akan Kristocin da suka ki bin umarninsa, "Wadannan mutane da duka ki suyi hadaya ga Allolin mu kuma suka ki biyayya da dokokin sarki za'a fille musu kawuna kamar yadda doka ta tsara."

***A lokacin da Justin ya fadawa mai aikata kisan "Kana iya kashemu, amma ba zaka iya yi mana wani labarin zahiri ba, "Wadannan kalmomi mahaukaci ne? A rude yake ko kuwa yana cikin zurfin yin tunani ne na tabbacin mutuwar sa? A'a ya hakikace da abu guda, watau kyautar rai na har abada daga Yesu Kristi. A yayin da yake cikin zurfin tunanin karshen rayuwar sa ta duniya. Kusam ma sai kace Justin ya na hangen mazaunin sa na samaniya. Ka fi jin tsoron rasa ranka ne fiye da tabbacin da kake da shi rayuwa har abada a samaniya? Mutuwa ba shine lokaci na yin shakka ba. ka daidaita al'amuranka tun kana da rai kuma da lafiyar ka. Karbi kyautar Allah na rai na har abada ta wurin dangantaka mai ceturwa tare da Yesu Kristi.***

# MATSANANCIN MARUBUCI

## Ingila: John Foxe

RANA TA 223

*Gama dai anyi mana wa'azin bishara, kamar yadda aka yi masu kuma: amma maganar kunne ba ta anfanensu ba, domin ban gaskiya ba ta hada ta da wadanda sukaji ba.*

*Ibran. 4:2*

***John Foxe, wani matashin malami ne da yake koyarwa a Kolejin Magdalene, yayi roko a cikin addu'a, "Suna ƙiran kansu firis naka da kuma masu hidimar ka, amma suna bautawa kansu da ikonsu na siyasa. Ka taimaka masu su gane cewa babu wani bukatar wani mai shiga tsakani zuwa ga Allah daga mutum sai Yesu Kristi kadai da kalmar sa".***

Wani ya saurari John nan da nan kuwa ya kai kararsa zuwa hukumar Kolejin. Suka bashi wani lefin rikon wani kowaswa da yake tamdar yin tawaye da Gwamnati da kuma Majami'ar kasa. A lokacin da yaki ya janye wannan batu sai majalisa ta sallame shi daga Kolejin.

A dalilin haka, John Ya shiga wani hali na wuyar samin aikin malanta. Watarana cike da gajiya da kuma yunwa, ya zauna yana addu'a a cikin wata majami'a. wani mutum wanda bai taba ganinsa ba ya zo inda yake ya bashi kudi a kunshe a hannunsa. "Kayi fara'a". Inji shi, nan da yan makonni zaka sami aiki "Bayan yan kwanaki kuwa aka bashi aikin koyarwa.

A karkashin mulkin Henry na takwas akwai hakuri da Krista irin su John. A lokacin da Mary ta daya ta hau gadon mulki, takan yanke hukumcin kisa ga duk wanda ya ki bin dokokin addini na kasa. Mutane dari uku ne suka mutu a zamanin mulkin tana shekaru biyar John da matarsa da ke da juna biyu suka gudu suka bar ingila zuwa kasar Belgium da kyar ya tsere domin kadan ya rage a kama shi.

Domin kariyar wadanda suka mutu a dalilin bangaskyarsu ne John ya rubuta litafi da ake kira Littafin Foxe akan shahidai [Foxe's Book of Martyrs]

***Ana iya karanta labarin masu bi da suka sha tsanani, amma kuma shiga tsananin da kansa wani abune mahimmi. Haka kuma, mutane da yawa sukan karanta labarun masu bi da suke ba da kansu har ayi sha'awar karfin zuciyarsu da suka yi. ba sa iya danganta shi da tushan sa wanda yake kusanta da kuma danganta da Yesu Kristi ne. sun iya karanta sakon bishara, duk da haka ba sa yin amsa ba bangaskiya. Shahidai sun, yi rayuwa kuma sun mutu suna kiran saura har ma da masu gaba dasu zuwa ga bangaskiya cikin Kristi. Wannan kira kai ma agareshi take a yayin da kake karanta wannan littafi. Kada ka yabe su kawai a lokacin da ake gayyace ka don ka dan dana abinda suka.***

## RANA TA 224

***Dauri a kurkuku bazai taba zama hani ga rayuwa mai amfani ta Krista ba.***

***Pasto Richard Wurmbrand***

## HORO MATSANANCI

## *Ingila: John Wycliffe*

RANA TA 225

***A cikin sanyin safiya irin ta Ingila a shekarar 1428, mutane suna kaiwa wa suna kawowa a cikin magabarta ba tare da gajiya a cikin magakarta. Daya daga cikinsu wanda yake saye da kyakkyawar doguwar rigar Frius, ya ce, "Gawurin nan. Toneshi. Gara mu gama da wannan batu".***

*Amma muyi farinciki kuma cikin kuncin mu: muna sane kunci yana faradda hakuri, hakuri kuma gwadawa kuma bege.*

*Rom. 5:3-4*

A lokacin da ceburin haka ya bugi wani abu mai tauri, mutumin nan da ke saye da kyawawan tufafi yana tsaye yana kallo sai ya ce "Bude shi". "Amma yallabai shekarun sa hamsin kenan a cikin nan! "Inji daya daga cikin masu hakar.

"Raguwar abinda ke ciki ba zai yi yawa kuma ba. Malamin addinin nan ya girgiza ya kada kafada. In haka ne ka juyo abin gaba daya. Zamu kona su duka". "Me ya sa mutumin nan ya fusata da abin haka? Me ya kawo tona kabarin mutumin da ya mutu shekaru hamsin baya domin ayi bidi'ar kone shi a zaman zindikanci?

A wajen shekarar 1976 John Wycliffe ya wallafa tauhidin mulki kamar yadda aka kafa a cikin alheri. "Wannan sako mai tsanani jayayya kadai ne ta isa ayi mulkin rayuwar Krista da ita a ko'ina".

Wycliffe kuma ya riga ya fara yin fassarar Littafi Mai Tsarki juyin Vulgate ta harshen Latin zuwa turanci kuma yana rabarwa a asirace a zaman kasidu da Litattafai. Yaci gaba da yin wannan aiki har mutuwarsa a shekarar 1384 shekaru dari daya da talatin da uku kafin zamanin Tajadidin Krista.

"Watsa tokar a cikin kogi, mutumin ya dokace su a lokacin da wutar ta yi sanyi. "Wannan shine lokaci ne a karshe da aka ji labarin John Wycliffe da irin koyawa ta sa". Wadansu shekaru dari suka wuce daga lokacin kafin a sami izinin karanta Littafi Mai Tsarki a cikin harshen turanci (Ingilish) .

***Shugabannin addini sunyi iyakar kokarin su su batar da aikin John Wycliffe. A maimakon haka da alamar tokar gawarsa da aka kona ya kirkiro sabon kishirwar maganar Allah a cikin Kasar Turai. Kokarin hanawa ya fadi, ainihi ma dai sun taimakawa aikin Kristi. Haka kuma mu na iya ganin magabcin mu, Shaidan yana daukar iya ganin matakin da zai iya ya hana Kristanci duk da haka kokarinsa yakan koma kansa. Allah yakan bari mu shiga tsanani domin mu karu da karfafawa zuwa cin ma nasara ta bada kai. Ko kana barin al'amuranka ganin cewa kiyayyar mai tsananta maka da yakeyi yana kawo maka albarka daga Allah.***

# MATSANANCIN SHAHIDANCI-NA DAYA
## Rome: Carpus

RANA TA 226

***"Na farko kuma zababben sunana shina Krista. A nan duniya kuwa ana kira na Carpus."***

*Gama maganar giciye wauta ce ga wadanda suke lallacewa; amma ga mu da ake ceton mu ikon Allah ne.*

*1 Kor. 1:18*

"Ka san dokokin da sarki ya tsara "inji mutumin, "Lalle ne ka bauta wa allolin Rome masu cikakken iko. Sabo da haka ina baka shawara ka zo gaba kayi musu hadaya."

Ni Krista ne, ina daukaka Kristi, dan Allah, wanda ya zo bada jimawa ba can baya domin ya cece mu, kuma ya fanshe mu daga hautar Shaidan. Ni ba zan yiwa gumaka hadaya ba.
"Dole ka yi hadaya, Kaisar ne ya bada wannan doka".
"Masu rai basa yin hadaya ga mattatu".
"Ka gaskanta allolin mattatu ne?"
"Su basu taba zama mutane ba, basu kuma taba rayuwa ba balle su mutu

"Su wadanda suke bauta masu sun sami kansu a cikin tsaka mai wuya", "Na kyale ka kayi maganganun banza da yawa kuma yanzu ka yi wa allolin da shi sarki kansa sabo. Lalle ne ka daina haka ko kuma ka makara. Zakayi hadaya ko zaka mutu! "Ba zan iya yin hadaya ba. ban taba yin hadaya ga gunki ba ko kuma ba zan fara yanzu ba".

Wakilin Kasar ya sa ska rataye a sama ya bada dokar a fede fatarsa yana ji yana gani da kayan aikin azabtarwa, shi kuwa da yaji zafi sai yayi ta kira da karfi, "Ni Krista ne! Ni Krista ne! Ni Krista ne".

***Kamar dai wannan Wakilin Kasar a wannan labarin, sakon bishara na giciye wauta ne ga waddanda basu gane ba? sukan ji cewa yakamata ayi kiyayya da shi. Watakila suna tsoron abin da basu iya ganewa ba. Watakila girman kansu yake hana su kaskantar da kansu, su karbi bisharar Allah ta bangaskiya. Koma menen dalili sun gwammaci su halaka da su amince da sakon giciye. Lalle ne mu gane cewa su wadanda suke masu gaba da Kristanci galibi suna yi ne domin ba zasu iya karbar gaskiya ta wurin bangaskiya ba. kara yin addu'a domin wadanda ke gaba da bishara? A yayin da kake addu'a domin su da suke yi wa wadansu tsanani, ka roki Ruhu Mai Tsarki ya taimake su, su dami fahimtar sako na giciye.***

# MATSANANCIN SHAHIDANCI-NA BIYU
## *Rome: Papilus*

RANA TA 227

*...i ma yan- uwa lokacin da ...a zo muku ba da gwanintar zance na zo ba, ko da hikima, in yi maku shelar asirin Allah.*

*1 Kor. 2:1*

***Wakilin Kaisar ya juya hankalinsa zuwa wurin Papilus, babu nisa daga inda Carpus yake rataye jini na zuba. "Kana da yaya? Wakilin ya tambaya.***

"I, mana, ta wurin Allah ina da ya'ya da yawa". Wani daga cikin taron da ya kewaye su yayi magana da karfi, "Yana nufin cewa yana da ya'ya ta wurin bangaskiyarsa ta Krista".

Dajin haka sai Wakilin Kaisar ya kara fusata. "Me yasa kake yi mani karya, cewa kana da ya'ya?" yayi kara.

Ina fada maka gaskiya. A kowane yanki da birni ina da ya'ya a cikin sunan Allah". Fusata da Wakilin Kaisar ya yi bata sanyaya ba. ko ka yi hadaya ko ka sha wuya irin na Corpus! Me kace yanzu? Papulus ya amsa ba tare da jin tsoro ba, "Na bautawa Allah tun ina karami, ban taba yiwa gumaka hadaya ba. Ni Krista ne. Babu abin da zan fadi wadda tafi girma ko tafi ba da mamaki fiye da cewar ni Krista ne.

Wakilin Kaisar ya bada umarni a rataye shi a gefe kusa da Carpus a fede shi da kayan azabtarwa. Papulus bai ce uffan ba, anna kamar namijin yaki yayi matukar juriya.

A lokacin da Wakilin Kaisar ya ga irin tsayayyen dagewarsu, sai yasa aka kone su duka biyu da ransu. Dukansu biyu sun sauka kuma sun shiga dakin taro, tare da gamsuwa cewar ba da jimawa ba zasu sami yncin barin wannan duniya. An kafa itae inda aka kafe Papylusa da kusoshi. A lokacin da wutar ta tashi sosai yayi addu'a kafin rai yayi halinsa.

***Galibi Krista sukan sami damuwa a yayin da aka kira su domin su kare bangaskiyar su. A lokacin da dama ta samu, mukan tsokani kanmu kamar yan makaranta muna gwajin tambayoyi kamar zamu dauki jarrabawan tsakiyar shekara. Yaya kenan idan suka tambaye ni matsayin(Trinity) watau "Uku cikin-Daya. Me zan fada idan suka tamabaye ni cewa kaka makomar wadanda ba su ji bishara ba take?" Ta kaka zan iya kare haifuwa da budurwa tayi? "A zahiri, ba zamu iya samun wata shaida da ta wuce tamu shaidar bangaskiya a cikin Kristi da muka rigaya muka yi ba. "Babu wani abu da zan fadi wanda zai fi girma ko ban mamaki fiyé da cewar ni Krista ne". Duk jarraba tambayoyi da zaka yi ba zasu rinjayi mara-bangaskiya ba fiye da shirinka na nuna kaunar ka domin Kristi.***

## MATSANANCIN SHAHIDANCI-NA UKU

### Rome: Agathonica

RANA TA 228

*Da haka ba za nu juya ga barinka ba; ka rayadda mu, mu kuma mu a kira bisa sunanaka.*

*Zab. 80:18*

***An kafe Carpus a jikin itace da kusoshi a yayinda wutar ta dau zafi, cikin farinciki yayi addu'a, "Yabo ya tabbata a gareka, ya Ubangiji, Yesu Kristi, Dan Allah, da kai ka dauke ni, ni mai zunubi, ka bani damar mutuwa a zaman shahidi" daganan sai ya kwanta dama ya bada ransa zuwa samaniya.***

A yayin da Carpus yake yin addu'a, Agathonica ta darajar Allah ta iso wurinsa, sama ta buda ta nuna bukin anganci na Dan Rago na Allah. Da kayan alatu shinfide a kan teburori a gaban ta ga Yesu da kansa yana tsaye a kanta. Ta firgita ta tashi firgigi, sai ta gane wannan kira daga sama ne.

Sai ta mike a tsaye tayi kira da karfi, "Wannan abinci nimma an shirya domina. Lalle ne nima na karbi abincin daukaka". Anji kuka daga masu kallo. "Tausaya wa jaririnki.

"Allah zai kula da shi". Agathonica ta amsa gama Allah shine mai baiwa kowa kuma mai kula da kowa. Nikam zan tafi in zamna tare da shi". Ta yi tsalle ta shiga dakin taron ta cire rigarta waje da farinciki kuwa ta mika kanta a kafa mata kusoshi.

Mutanen da suke tsaye suka fashe da kuka. "Sunyi kuka, wannan hukumci akwai rashin tausayi da rashin adalci". A cikin wutar tayi kira, Ubangiji Ubangiji, ka taimake ni gama gani nan zuwa gareka!" Daga nan sai ta mutu ta sadu da Ubangijin ta, wannan ya faru ne a shekarar AD 165.

***Faruwa daya bayan daya, shine faruwa na ba-zatata da wani rayuwa ke da shafar wani kaman wani shiri na ba-zata wanda ba'a yi shiri dominsa ba. Abin ya fara daga Carpus, wanda ya nuna hanyar yin karfin zuciya ta jarumtaka ga Papylus, ga yadda aka azabta su, dauka biyu domin bangaskiyar su, sai kuma wata da take kallon abin da ke faruwa taga irin jarumtalar zama shahidai, sai ta jefo kanta zuwa ga bangaskiya da son kanta cewa ta mutu a kafe. Yau mune na biye wajen tsare bangaskiya a majami'un mu, a ma karantaun mu. Mu kan gani a kauyuka, a garuruwa da unwanni a kasashe masu yawa inda rayuwar wani ta kan tsaburi na wani. Har ma kuma na wata zuwa ga gagarumin bada kai. Tun yaushe rahama da samun Tsabura ne bada kai a majami'ar ka ko a unguwar ku? Yi Addua domin sabuntarwa ta fara da kai-mahadi mafi daraja na jikin sarkar.***

# MATSANANCIN DAN GUDUN HIJIRA

## *Kasar Sin: Lo Lieu*



***A hankali cikin tsanaki Lo Lieu ta yi tattaki a kan titti a Kasar Sin, tana ta waigawa domin ta tabbatar cewa babu wanda ya biyo ta ko ya shaida ta. Ta wuce kusa da wata takarda da aka kafe akan allo ana neman ta kuma akwai ladan kusan $600 ga duk wanda yayi sanadin kama ta.***

*Kowane dayanmu fa ya kawo lissafin kansa ga Allah.*

*Rom. 14:12*

A lokacin da Lieu take yar shekara goma sha bakwai kacal, tas bar gida domin yin aikin Allah. Ta kafa wata kungiya da ta taimaka aka kafa majami'u da basa cikin wadanda gwamnati ta san da su-watau marasa izini haramttatu kenan ga hukuma ta gwamanatin kwaminis. Aikin ta ya kai da tayi ma'amala da Krista daga kasashen waje wadanda suke yin fasa-kwaurin Littafai Masu Tsarki zuwa cikin kasar.

Kusan shekaru goma Lieu tana wannan aikin sai yan sanda suka kamata, ta jure wa tambayoyi masu tsanani. Wani lokacin ma anyi mata duka kwarai ba ya kaita ga suma na dogon lokaci. Amma Lieu ta ki ta basu wani labari da suke so game da masu bi da take aiki tare dasu da kuma ayyukan da suke yi.

An sake ta bayan yan wattanni ba tare da gaya mata kome ba game da aikinta, amma suna zuba mata ido. Bayan yan shekaru, aka sake kamata da ita da wasu mutane biyar, kuma aka kwace dukan abinda ta mallaka. A wannan karo dai an daure ta shekaru uku a sananin bauta.

An sallami Lieu daga kurkuku bayan ta cika shekarun ta na fursuna, amma haryanzu yan sanda na zuba mata ido. Amma duk da razanar kamu, Lieu ta ci gaba da rayuwa irin ta dan gudun hijira a dalilin Kristi, ta zama mai laifi don tana kaunar Kristi kuma tana shaida wannan kauna ga wasu.

***Kayi tunani akan wannan. Da ace takardar kotu ta bada izini a kama dukan Krista masu bada kai, wa zai mika kai ga hukuma? Irin gaisuwa ta alheri da kake yi wa jama'a duk mako a yayin da ka tafi sayayya a kanti zai sa mai kantin nan da kuka saba ya tona asirin ka? Ma-kwabta zasu yi maka ganin cewa kai mai bada kai ne ga Almasihu kuma ya kamata a kama ka? Abokan aiki fa zasu yi maka ganin Krista ne na gaske don su sa a kama ka? Ko kuma zasu gamsu da cewa take taken ka bai kai na Kristan gaske ba? me kake tunani? Me ya kamata ka yi?***

# MATSANANCIN ANFANI
## Pakistan: Safeena

RANA TA 230

***Safeena kykkyawar yarinya ce, kuma bata magana shiru shiru take. Girma a kasar Pakistan, ta koya cewa a zaman ta mace kuma Krista, ci gaban ta na rayuwa zai zama takaitacce kuma kadan***

*Bisa ga ya'yansu za ku sansanche su. Daga wurin kaya ana chiro anab, ko kuwa baure daga wurin zakami. Hakanan kuma kowane itachen kirki, ya kan fitarda yayan kirki; amma batachen itache ya kan fitarda munannan yaya.*

*Matta. 7:16-17*

A lokacin da ta sami aikin dafa abinci da wanke wanke a gidan wani attajiri kuma Musulmi, tayi farinciki cewa zata tara yan kudi domin ta taimaki iyalin ta da ke matalauta ne.

Sannu a hankali kyaun Safeena da hankalinta ya ja hankalin dan mai-gidan. Sai ya sami iyayyensa game da daukar yarinyar ta zama matarsa, ta amma Safeena Krista ce. Suka matsa mata ta shiga Musulunci, amma Safeena tayi karfin zuciya taki. Bayan matsi na makonni sai ta so barin aikin, amma ta san cewa iyalin ta na cikin bukatar kudi.

A karshe saurayi ya hakura, ya daina kokarin rinjayar ta ta zama matarsa sai yayi wata matsananciyar shawara. Yayi mata mugun ja zuwa cikin daki dakunan yayi mata fade.

Wannan abu ya rugurguza lamirin ta nan da nan kuwa ta bar aikin, amma kafin ta kai kara, iyayen suka juya a kanta suka gaya wa yan sanda cewa tana sata. Nantake kuwa aka tsare Safeena, ta kuma kara shan wulakanci a kurkuku.

Safeena ba ta yin da-na-sani domin matsayinda ta dauka na Kristi, sai dai tana nan tana jin kunya da abin da ya faru a gareta. Tananan da karfin halin mannewa alkawarin Allah domin samun warkaswa na jiki da na lamirin ta a yayin da ta ke fama da kokarin gafartawa wanda ya dauki alhakinta.

***Mukan koyi abubuwa da yawa akan addini ta wurin gwajin sakamako na rayuwar masu bi. Wannan labari ne na wani iyali da suka bi bataccen hanya. Addinin wannan iyali yana matsa masu sarrafa karya, rashin adalci da fasikanci. Akasin haka Allahn da Safeena ke wa ibada Allah mai kauna, ya bi da ita ta zama mai kwazo da bada kai kuma tsayayya. Watarana Allah zai taimaki Safeena tazo ga gafartawa wadanda suka cuce ta.***

***Ka maida hankali a duk lokacin da kaji ana cewa duk addinai daya ne. an kira mu domin mu zama masu zaben anfani- a hankali muna gwada anfanin rayuwar mutane domin bankado manufar su. Kada ka sami yaudara ta wurin karanta labarun wasu addinai. Ka zauna ka dubi irin rayuwar da masu addi'nin suke yi ka yi aiki da sakamakon da ka samu.***

# *Karin zafin kawo hari na Shaidan karin samun jindadin cin nasara da shi ne yazo din ya gani*

***Wani Krista a Kasar sudan***

# MATSANANCIYAR MAFAKA
## Bangladesh: Andrew

RANA TA 232

***Hidimar bishara da Andrew yake yi ya kawo musulmi guda 749 ga tuba da baptisma. Buguda kari sun yi rabon Littafi Masu Tsarki da linjila guda dubu uku (3,000) da kuma kasidu fiye da 137,000.***

*Sa'annan ce ma almajiran sa, girbi hakika yana da yawa, amma ma'aikata kadan ne. ku yi addu'a fa ga Ubangijin girbi shi aike ma'aikata cikin girbin sa.*

*Matta. 9:37-38*

Amma Andrew ya hangi akwai hadari ga musulmi da suka tuba sai ya gina mafaka inda zasu sami zaman lafiya. Iyalin Kristoci ko kuma mutane dai dai daga ko ina a cikin kasar sukan iso wannan mafaka, amma ba domin hutawa ko fakewa ba. Sababbin tuba na samun horo na almajirci da zama masu bishara daga safiya har dare.

Bayan kammala horon su, akan kai wasu kauyakan da ba a sansu a wurin ba. wannan kuma sai ya zama sabuwar tashar su ta aiki. Kristocin nan sukan zo mafakar ne don su tsira daga hadari, daga baya kuwa sai su shiga wani hadarin ma da ya fi wanda ya koro su. Amma sun sani ba su kadai suke ba, daruruwan yan uwansui maza da mata sun rigaya sun fita kafin su domin isar da Yesu Kristi ga dukan kasar Bangladesh.

Aikin Andrew fa akwai Hadari, an kama shi sau da yawa kuma yan sanda da ma tsagerun Islama sun sha yi masa duka su da suke tsoron irin kwazon da yake da shi, iyalinsa da gidansa ma, ansha tsoratar da su.

Aikin Andrew shine baiwa Musulmi da suke tuba mafaka, amma aikinsa na cikin hadari, hadari a kullum ga iyalinsa da su wadanda ke aiki tare da shi, amma ai dalibansa suna da rai madawwami kuma sukan kware suzo suma su baiwa wasu damar samu.

***Kayi tunanin manomi da yake so yayi girbin babban gona shi kadai, ko da wane irin kokarin iya yin aiki gareshi shi kadai, ba zai samui damar isasshen lokaci ba na gama wannan aikin. Yesu yayi kwatance dabatattun mutane a gonar rayuka da suka isa girbi. Wannan yana bukatar aiki mai yawa da mutum daya zai fuskanta. Sabo da haka ne akeyi mana kira da muyi anfani da dabarar Andrew a kasar Bangladesh. Lalle mu koya wasu yadda suma zasu shaida wa wasui bisharar Kristi. Kawo masu tuba ga Kristi bai isa ba. dole mu Almajirantar. Kai kamar mai gonar nan kake kana fama kai kadai. Ko kana wa wasu yadda zasu yi aiki a gona.***

## MATSANANCIN JIMREWA
## *Azerbaijan: Pasto Roman Abramov*

RANA TA 233

*Kuma bari hankuri shi chika aikinsa, domin ku kamilta, ku chika kuma, ba ragaggu na chikin komi ba.*

*Yakub 1:4*

***Pasto Roman Abramov da matarsa sunyi aiki wurjamjam na tsawon shekaru uku domin su kafa majami'a a garin Ismailly, ta Kasar Azerbaijan, amma cikin shekara daya da kaura zuwa kauyen, hukuma ta tsare su da nufin a tilasta musu barin garin.***

Mambobi goma ne a majami'ar, yawacin makoni, amma suka ci gaba da yin bisharar Kristi. Don tsananin matsi daga hukuma ga masu gidaje, basu iya samun gidan haya ba. Sai suka yi kokari suka yi gini inda zasu zauna su kuma yi taronsu a ciki ba tare da ketara doka ba.

A lokacin da Abramov suka fara yin taro a sabon gininsu sai mambobi suka fara karuwa a hankali. Sai shugabannin Musulmi suka zo wurin su suka ce musu basu da izinin yin sujada, irin ta Krista a nan.

Pasto Abramov ya kare majami'ar sa, ya gayyece su zuwa ma sujada. Daya yayi na'am da gayyatar kuma har ya dawo. Dayan kuwa sai yace wai wani Krista ya taka warka guda ta kur'ani da kafa saboda haka suna neman gwamnati ta rufe majami'ar. Jami'an gwamnati suka fara ziyartar mambobi a gidajensu ana tsoratar da su ana yi musu tambayoyi ana basu daurin kwanaki goma a kurkuku.

Duk da tsananai da kuma tsoratar da mambobi Pasto Roman yana bada gaskiya cewa tare da addu'a za'a sabuntar wannan ikklisiya. Gidansa a bude yake ga kowa da zai iya zuwa taro.

***Da so samu ne akwai abubuwa da zamu so mu kauce musu a rayuwarmu. Jarabobi na daya daga cikinsu. Me yasa rayuwa abune inda ana fita daga wata damuwa sai a sake shiga wata damuwa? Littafi Mai Tsarki na koya mana cewa rayuwa ba ya iya zama babu damuwa. A zaman yara mukan hakura idan wani almajiri ya yi mana tsokana. Mukan hakura mu bari idan wuya tazo. Amma yayin da muka girma muka zama mutane mukan koyi yin jimiri-mu dage da ganin cewa abin ya yiwu. Haka kuma, a yayin da muke kara rike a bangaskiyar mu, mu kan koyi sanin darajar yin jimiri. Haryanzu ba ka rika ba, kana samun gazawa ta fitar da rai? Ka shaida wa Allah cewa a shirye kake ka girma.***

# MATSANANCIN ASKI

## *Amirka: Park Gillespie*

**Galibi mutane suna da sha'awar bayarwa sosai domin taimakon yan'uwansu maza da mata da ke cikin tsanani a ko ina cikin duniya. Wani malamin koyarda ilimin kimiyya mai suna Park Gillespie, yana iya zama na farko da ya ba da gashinsa!**

*A lokacin da ya ga taron sai ya yi tausayin su.*

*Mat. 9:36*

Bayan da yayi ma'aikatan Krista sun yi wa almajira a jinsa bayani akan Sudan, almajiransa suka yi hangen taimakawa yan gudun hijira wandanda ake wa tsanani a dalilin bangaskiyarsu. Tausayin da almajiran suke yi ya wuce na malaman su.

Abin da ya fara da yan aji bakwai suna nemen taimako na garguna don su cika wa yan Sudan da ake cikin tsanani cikin karamin lokaci ya watsu a cikin makarantar gabadaya, a hankali kuma ungwar ma ta dauka. Gillespie yayi magana da tashar Talabijin na WBTV a garin Charlotte ta Carolina ta arewa ya shaida musu abin da yara suke shiryâwa domin taimaka wa masu tsanani a Sudan. Barguna suka fara cika ajujuwa, kuma gashi tunanin cewa akwai fa kudin sufurin jirgin ruwa domin isar da kayan ga masu bukata bai ma taso ba tukuna a lokacin dan jaridar WBTV ya iso domin daukar labarin Gillespie yace zai aske kansa kwal kwali idan za a taimaka da kudin sufuri, jim kadan bayan ana watsa labarin sai aka fara aiko da kudade.

Ta haka wurin nuna kaunarsa ga mutanen da taba gani ba, Gillespie ya aske kansa. Makarantar gabadaya ta taru wajen askin dan jaridar daga WBTV kuwa ya dauki hoton wannan aski. Galibi Amoikawa sukan ji kamar suna iya yikn kalilan domin taimakawa Krista da ke shan tsanani a wassu kasashe, Gillespie ya nunawa Amirkawa na yin fiye da haka.

***Park Gillespie da dalibai su koya mana yadda tausayi ya ke rikida ya zama hanyar Kirkirar yin taimako. Park da dalibansa sun nuna murna domin sun samu iya biyan surufi-ko da shike har ya bada gashin kansa! Tausayin hali ne na mutumtaka ta dan adam wajen maida murtani da ganin wani yana cikin azaba. Lalle ne mu ci gaba da tausayawa kuma mu kirkiro hanyoyin magance damujwar mu. Gaba lalle ne mu ga cewa mun bada kanmu. A wane matsayi kake .,an? Kana anfani da Tausayinka yayi aiki da tauayin kirkiro dabaru? Ka bada kanka don taimako da zai kawo banbanci a rayuwar wasu?***

# HORO MAFI MATSANANI

## Paskistan: Ayub Masih

RANA TA 235

***"Wannan tsare ni da aka yi a kurkuku ba zai hanna cin gabada kaunar Ubangiji na, Yesu Kristi ba", in ji Ayub Masih. Yanzu yayi fiye da shekaru biyar a kurkuku domin an yi masa shaidar zur.***

*Gama hakin zunubi mutuwa ne, amma kyautar Allah rai na har abada ne cikin Kristi Yesu.*

*Rom. 6:23*

Galibi Kristoci a Pakistan sukan sami kansu a cikin tashin hankali domin ana basu laifin da basu yi ba kamar ba cewa sunyi sabo game da Mohammed, wanda ya kafa addinin Islama. Bisa ga dokokin musulmi, yin sabo laifi ne da yake dauke da hukumcin kisa. Ayub yana hira da wani abokinsa musulmi wanda sula yi tadi tare daga lokaci zuwa lokaci suna wasa da juna akan wasu al'amura, hikrar ta kai ga ambata Littafi Mai Tsarki da ake kira "Ayoyin Shaidanci" (The Satanic Verses) wani littafi da ya kawo jayayya game da addinin Islama. Wandansu sun ji su suna maganar, kuma ta wurin matsi da wasunsu, abokin Ayub ya kai shi kara.

Aka kama ayuba aka yi masa hukumcin kisa wai don yayi sabon Mohammed. Jim kadan bayan wannan sai aka kaiwa kauyen su bari, kuma dukan iyalin Krista guda gomasha biyu sa suke da zama a can aka kore su daga gidajensu. Ayub ya roki kotu a kanshi bai aikata laifin ba, kuma ya daukaka kara zuwa gaba. Yayi jira na shekaru biyar tare da lizima ga yin addu'oi a kurkuku yana ta jiran samun amsa daga Kristi.

A yanzu haka ana tsare da shi ne a babban kurkukun Sahiwal a garin Multan ta kasar Pakistan. Yana sane da cewar, ko da ya sami saki, rayuwarsa zata ci gaba da zama a cikinhadari, kuma zai kawo hadari ga wasu daga cikin iyalansa ko ma unguwarsa. Cikin farkon shekarar 1998, an taba kai masa hari, kuma wani shugaban Islama ya taba yin alkawarin biyan $10,000 ga duk wanda ya kashe Ayub.

***A kasashen musulmi a yau, yin wadda ake jin tana gaba da islama yana iya kawo kisa. Littafi Mai Tsarki yana koya mana cewa horon zunubi shine mutuwar ruhaniya. Banda Yesu Kristi ya biya mana horon mutuwa watau ga duk wanda ya bada gaskiya, har Musulmi. Yesu Kristi ya dauki matsayin mu a hanun mai-kisa ta wurin rataya shi akan giciye. Mutuwarsa ta bamu iyawar samun rai na har abada tare da Allah a samaniya. Ka godewa Allah saboda an kawas hukumcin kashewa kuma an gafartaka maka. Kuma kayi addua sabili da wadanda suke kasashen Musulmi wadanda ke iya kashe Krista a duniya, amma idan basu da Kristi zasu fuskanci mutuwarsu ta har abada.***

# MATSANANCI AZANCI

## Sudan:



***"Raira wannan waka (kalmar shahada ta Islama) ko ka mutu", in ji wannan soja dan Arewacin Sudan. Shi wannan kamammen Krista ya iya ganin kiyayya wurjamjam a idanun mutumin nan kuma yana tunanin cewa yasan yawan rayukan da ya kashe. Sojan nan kuwa ya danna wuka a daidai makogwaron shi Krista din.***

*An gicìye ni tare da Kristi, kuma ba ni da sauran rayuwa, amma Kristi ne ke rayuwa a cikina.*

*Gal. 2:20*

Sai azanci ya zo masa a zuci Raira! Allah ya sani cewar tursasa ka akeyi. Me ya sa zaka kasa fadar wani abu kada ka bada kanka haka kawai da kasa fadar ya kalmomi akan abin da baka yarda da shi ba?"

Ta wani fannin kuma, ya sani Littaffi Mai Tsarki yana koyar cewa kalmomin mutum suna da iko. Ya tuna cewa yin ikirari a gaban Kristi abu ne mai ikon gaske.

Shin yin ikirari na sabo zai zama cike da iko? Yana tunani, "Idan ma banyi da niyyar na karba ba? Tambayoyin fa sai cin karo da Juna suke yi a zuciyar sa. Azancin sa na karo da kaunar Kristi da yake da ita. Krista a sudan sukan fuskaci irin wannan zabi, kuma sun ga abokan su da yawa da iyalansu da aka kashe domin gaskanta Kristi. Shahidan sunki su raira kalmar shahada, domin ba sa so su gurbata ruhaniyarsu da wakokin sabo da gudun kada su yiwa Allah rashin aminci.

Kariyar su ita ce wai Kristi da yake cikin su masu bi bai iya yin wakar ba shi ya sa suke kasa yi. Sabo da haka dole ne su fuskanci sakamakon kin yin haka. Wannan Kristi da yake zamne a cikin su wanda baya wakar, kuma baya tsoron mutuwa. Masu bada gaskiyan nan sun rigaya sun maida kansu mattatu a cikin Kristi-Krista da ke cikin su ba a iya fama shi.

***A kowane lokaci muka dauko batun game da azanci da kuma bangaskiya. Sai mu ga azanci yana iza mu mu karba haka. Bangaskiya kuwa tana gaba da farinjini na duniya, a yayin da muka saurari azanci, tana iya daurowa mu ajiye amincewar mu a gefe domin mu biya wa wani bukatar sa. Sau nawa kake raira wakar wani domin gujema hukuma? Watakila aiki ne da yake bukatar a yi anfani da rudi. Azanci na gaya maka kada ka fadawa kowa don kada aikin ka ya baci. Idan har ka gane cewa ka saurari muryar azanci na dogon lokaci, ka roki Allah ya taimake ka da ka juyo hankalinka a gareshi. Ka roke shi ya baka bangaskiya a gareshi. Ka roke shi ya baka bangaskiya da kake bukata domin ka sami hikimar magana akan kari a lokacin da ya dace.***

# KARIN MATSANANCI DAN FASA KWAURI

## *Ukraine: Kristocin Karkashin Kasa*

RANA TA 237

*Ga shi, na aike ku kamar tumaki cikin tsakiyar kerketai: ku zama masu-azanci fa kamar machizai, marasa- barna kamar kurchiyoyi.*

*Matt. 10:16*

***Mai tsaron iyaka da Russia yuana sintiri irin na yau da kullum a bakin aiki. Da yake a lokacin karshen yakin duniya na biyu ne, ana tsaron iyakokin kasa don hana ayukan da ba a yarda da su ba a cikin abin da suke tsoron zai faru abubuwa biyu ne gaba da kome: yan kasar Soviet masu kokarin tserewa daga kasar sa Yan Fasakwauri da ke kokarin shigar da harmattun kaya kamar su Littafi Masu Tsarki.***

Wannan mai tsaron yana aiki ne a iyakar da ke tsakanin Jami'iyar soviet da Romania. Yayi tafiya a hankali a cikin snyin kankara. Alamun takun sawu! Alamun takun sawu ya nufi Romania! Ya dauki usur dinsa ya sa a lebunansa yayi wata doguwar busa.

Ba da jimawa ba kuwa sauran masu tsaro suka kewaye shi. "Ku biyo nan! Ku biyo nan! "Yayi tsalle yayi ihu, yana nuna alamun takun sawa na mutane guda hudu. "Ban ce sunyi nisa ba! Watakila zamu iya kama su kafin su shiga Romania! "Taron masu tsaron suka sa kai nan da nan suka bi dare.

Da jin karar, wadansu Krista bayan Romania suka yi tsit a cikin duhu, suna sauraron su, a yayin da surutunsu da magana da sukaji da karfi sai kara nisantarsu takeyi. Sai suka juya suka kalli juna suna murmushi. Shugaban su na kada kai kuwa sai sukaci gaba da tafiyarsu, suna tafiya a hankali ta baya baya zuwa cikin Ukraine, dauke da hajjarsu mai daraja Littafai Masu Tsarki zuwa ga yan'uwansu maza da mata ma majami'un karkashin kasa.

***Littafi Mai Tsarki ya fada cewa abokan gabar ruhaniyar mu sukan yi anfani da wayo ko makirci garin yin yunkurin ruguza Kristanci. Akasin haka kuwa shine mu da muke dauke da bisharar salama an yi mana ganin marasa laifi abin koton kyarkeci. Yesu ya umurcemu da mu zama masu gane hadarin zama tunkiya a tsakiyar kyarketai. Lalle ne mu yi anfani da dabaru masu ma'ana da azanci mai fasha domin mu sha kansu mu ci nasara da makiya. Shaidan yana da iko, amma Allah shine mafi-iko dauke zai baka damar cin nasara da bisa kan makiya. Aikin ka shine ka roki hikima da karfin zuciya domin tabbatar da nasara da Allah ya shirya. Kana da wan takamakon na al'amari ne da ya buwaye ka? Ko kayi addu ka roki Allah ya baka hikima, a yayin da kake shirin kan gaba? Ka amince da shi cewa zai sha kan makiyan ka-kullum Ubangiji na cikin yin haka sabili da mu.***

***Tun da mun sani Kristi ba ya nan duniya kuma, yana so jikinsa, watau majami'a ta yi shaidar wahalun sa da yasha ta wurin shan wahalunta. Tunda mune jikinsa, shan wahalun mu shan wahalunsa ne.***

***John Piper-Kwadaitu da Allah***

# JIGILI MATSANANCI

## Vietnam: Linh Dao

***A yayin da Linh Dao da uwarta uka kusanci kurkuku, ta rigaya ta san abin yi. amma zata yi shi don a gane kamar ma wata yarinya ce karama sosuwar rai ya sha mata kai.***

*Ya Ubangiji, ka koya mani tafarkin ka; ni kuwa in yi tafiya cikin gaskiyar ka, ka daidaita zuciya ta ta jin tsoron sunanka.*

*Zab. 86:11*

Mahaifin Linh Pasto ne na majami'ar karkashi kasa a Vietnan. Shekara daya baya, a lokacin da take da shekaru goma da haifuwa, yan sanda guda hudu suka shiga musu a gida suka binciki gidan, suna neman Littafi Mai Tsarki da ta boye a cikin jakanta na zuwa makaranta. Aka kama mahaifinta aka yi masa hukumcisake-ilimintarwa da horon aikin kodago mai tsaanani.

A lokacin da suka iasa mahadar katanga wanda ya raba tsakanin su da mahaifin Linh, Linh ta hango wata dama. Sai tayi maza jikin katangar, ta tafi a sukwance taa rungumi shi da karfi. Masu tsaro suna kallon ta. Bayan haka ma wace barna kamar karamar yarinya zata yi.

Iyalin Linh suka sami damar shigar da alkalami a kurkukun don uban ya sami damar yin rubutu da kuma yin wa'azi a jikin kwalin taba sigari. Wa'azin da yake rubutawa a jikin kwalin sigari ana zagayawa dasu daga daki zuwa daki a kurkuku kuma ya kawo fursuna da dama ga Kristi. Yanzu dai Linh Dao ta zama budurwa mai gajin hakuri, wacce ba ta damu da kasada da take dauka ba kafin ta yi abin da yake daidai. Sha'awarta shine ta bi sawun mahaifin ta a kasar domin ta zama mai wa'azin bishara. Ta a kasar Vietnam ta kwaminis kuma ta cigab da zama jigilalliya wajen biyayya da Kristi maimakon biyayya da dan adam.

***Daya daga cikin dalilan da masu bi ba sa kuma yin jigili a shaidarsu ta Kristi shine sukan ji muryoyi guda biyu maimakon su ji guda daya kawai. Jigilliliyar biyayya ba zata taba tasowa daga zuciyar da hankalinta ya rabu biyu ba. mukanji muryar Allah a kukatan mu wadannan yana gaya mana abin da ya kamata mu yi a lokacin wasu al'amura, "Fade shi yanzu, shaida bangaskiyar ka", Duk da haka a lokaci guda sai muce muryanmu muke ji yana kawo mana dalilai barkatai. "Ba yanzu ba, daga baya zanyi. Me kake yi?" Allah ya bamu zuciya daya wanda yake saurarawa muryarsa kadai. A yayin da muka kintsu a cikin bangaskiyar mu. Muna iya cewa biyayya na zuwa bisa ga halin mutumtakar mu-cike da jigili kamar kyafarwa. Ga wace murya zaka saurara a yau?***

# MATSANANCIN IKO

## Bangladesh: Abdullah

RANA TA 240

***Tun farko da Abdullah ya karbi Yesu, iyalinsa sun yi kokarin gaske su sa shi ya sake shawara. Baysn fs mahaifan sa mutum ne da ake girmamawa a kauyen su da kuma kasar bangladesh ga baki daya, da yake ya gina masallaci kusa da gidajen su.***

*Amma zaku karbi iko a lokacin da Ruhu Mai Tsarki ya zo maku.*

*Ay. Manz. 1:8*

A lokaxin da suka ga bada baki bai rinjayi Abdullah ya dawo addi'nin Islama ba, sai suga shiga yi masa duka. A lokacin da duk bata anfana ba, sai suka kira wasu da suzo su taya su dukan sa. Duka dai basu yi aiki ba. Abdullah ya rike bangaskiyarsa daram a cikin Kristi. A karshe cikin redawa uwar ta daina bashi abinci. Abdullah yayi addua samun karfi daga Allah kuma ya tsaya tuttur.

A shawarsu ta karshe iyalin suna kira shugaban addi'ni na Islama, ya zo yayi addu'a irin tasu wai don a fitar da Shaidan daga jikin yaro. Malamin ya zo gidansu ya karanta addu'oin Islama akan yaro. Yayi waka, ya fitar da hannu akan yaro. Yayi rawa, yayi ihu. Ruhun da ke cikin Abdullah yana nan daram. Bayan sa'oi biyar malamin ya hakuri gashi a gajiye. Ruhun da ke cikin abdullah ya fi nawa ruhu karfi, ya gaya wa uban yaron a yayin da ya tashi tafiya. Ba za a iya juya Abdullah ba, kuma ba za a iya tsaida shi ba daga shaidar wannan ruhu nasa ga wasu. A cikin yan wattani kuwa abdullah ya kawo Musulmi guda 27 ga Kristi yana jika su sarai da ruhun Kristi.

***A cikin yin kokarin maganta alamar tababababarewa gudanar da makamashi, injiyoyin zamani sun yankura ga tsara motsi da zasu iya yin aiki da batura kawai ba tare da shan fetur ba. tangardar ita ce dole motocin su ta sami mahadi inda za a iya yi wa batrin caji. A yanzu dai wannan tunanin saon abu ne domin tashahin da za a yi cajin batura kadan ne kuma nesa da juna. Idan ba tare da tashar cajin batir ba motar ba ta da katabus. A haka kuma Krista da ke yankurin shaidun gaske ba tare da ikon Ruhun Mai Tsarki domin samun hikima, kariya da kuma iko domin shaidarmu. Kana yin abubuwa bisa karfin ka ne. domin Yesu maimakon ka baiwa iko da damar gudana a cikinka.***

# Ingila: Wata Bara Karama

RANA TA 241

***A karni na goma sha shida, sarki Philip na biyu ya dauki tsauraran matakai gaba da wadanda kẹ fassara linjila domin kansu. Dukan wanda aka samu yana nazarin Littafi Mai Tsarki a wannan lokaci akan rataye shi a kona shi sarkafe jikin itace, a nutsar a yayyage shi ko kuma abizne shi da ransa.***

*Ka bude mani idanu na domin in sami ganin abubuwan mamaki na dokokin ka.*
*Zab. 119:18*

An aiko masu bincike daga wurin sarki su duba gidan Magajin Garin Brugge su ga ko ana binciken Littafi Mai Tsarki a can. A cikin binciken su kuwa sai suka gano Littafi Mai Tsarki. Dukan su da suke wurin suka yi musun sanin wani abu akai. Daganan sai karamar yarinya barar gidan ta shigo. Da aka tambaye ta game da Littafin nan Mai Tsarki sai ta shaida cewa 'ina karantawa'. Shi Magajin garin ya nemi ya kare ta cewa "A'a bata iya karatu ba".

Amma itạ barar ba ta da bukatar yin anfani da karya domin a kareta. "Gaskiya ne, wannan littafi nawane. Ina nazari ciki, kuma tafi komi daraja a gareni!" An yanke mata hukuncin kisa ta hanyar kware ta, a cusa ta a dabe acikin garun birnin. Kafin zartas da hukumcin wani jami'in ya tambaye ta, "gaki yarinya ga ki kuma kyakkyawa amma kuma za'a kashe ki?" Sai ta amsa, "mai cetona ya mutu domina. Ni ma kuwa zan mutu dominsa. "A lokacin da ya rage tubali guda daya kawai a hada katangar, sai aka sake gaya mata. "Ki tuba! Ki ambaci kalma guda kawai na tuba!" Maimakon haka sai ta furta bukatar ta guda daya shine ta tafi wurin Yesu sai ta kara da cewa "Ya Ubangiji ka gafartawa masu kasheni!"

***Ga wasu littafi ne kawai-mai farin jinin kasuwa na tsawon shekaru aru-aru. Ga wadansu kuwa tamfar ibada ce ta iyali-ana kyauta da shi a bukin aure, haifuwa harma da na jana'iza. Har yanzu ma ga wasu tsattsarka kuma hurarriyar maganar Allah ce. Wadannan masu bi sun mannewa maganar Allah tamfar wasiku ne daga makaunaci, da ake zuba musu akai-akai. Me sukan gani a aikin gaskiya maganar Allah? Me yakan sa su daukar kasadar mutuwa domin karantata? Ka roki Ubangiji domin bada amsa. Idan gaskiyar wannan littafi ya zama maka abin da ya gagara fahimtuwa a gareka, ka roki Allah ya buda idanunka domin ka sami ganin kalmominsa sarai. Idan ba tareda taimakon sa ba, kalmomin zasu zama zane ne kawai a shafuka. Amma Allah yana iya baka damar ganinsu a raye.***

# Korea ta Arewa: Wata Uwa da Danta

**RANA TA 242**

***Me ya faru? "Inji wata mata yar Korea a lokacin da danta ya shigo ta kofar gidan da fuskarsa a murtuke.***

*Da shike an maye haifuwar ku ba daga iri mai rubewa ba, amma mara rubewa ta wurin maganar Allah wadda take rayuwa ta kuma dawama.*
*I Bitrus 1:23*

"Ina tare da abokina yau a lokacinda hafsoshin yan sanda guda biyu suka tsaida mu. Suka buge abokina suka kaishi kasa suka kuma bashi laifin cewa shi Krista ne. Abokina baiyi kokarin kare kansa ba. Harma da nuna masa bindiga da akayi a fuskarsa yacigaba da nuna salama. "Ya zuba musu ido ba tare da cewa uffanba.

Nasan abinda yake fadi. Yanaso nima in gaskanta abin da shi ya gaskanta. Sai kuma yace na sa musu albarka. An kasne shi a gabana domin shi Krista ne. Ni ban ma san komenene ake kira Krista ba ni ban gane da wannan ba. Bayan da ya bada labarinsa, uwarsa ta rike kansa a hannunta tace, "Na gane". Sa'annan ta fara bashi labarin gaskiyar game da Yesu Mai Cetonta Ta koya wa danta game da haifuwar Yesu Mai Ban mamaki, da kuma dama da ya samu na ceto wurin mutuwarsa akan giciye.

Ko da shike taji zafin rashin gayawa danta domin tana da damuwa akan hadarin da ke dauke da yin haka tana godiya domin Allah yana sake basu wata dama. A yayin da harsashin nan ya har zuciyar abokinka, Allah ya shuka iri na bege a naka zuciyar". A yin haka wannan saurayi yana cikin faman shigarda litattafai masu Tsarki cikin Korea ta hanyar fasa-kwauri watau (Simogal) kuma yana kafa gidajen addu'a.

***Ta wurin matannan yaro yazo duniya tunda itace ta haife shi ya shiga wannan iyali. Amma ta mika masa dama da ta samu wajen taimakon sa samun rai na har abada ta wurin maya haifuwarsa. Wannan rayuwa ta duniya mai shudewa ce, amma kyautar Allah ta rai na har abada baya shudewa. A yayin da muka shaida bisharar Allah tare da wadanda muke kauna. Allah ya na basu rai na har abada.***

***Ko ka kasa yin anfani da wata dama da ka samu na shaida bisharar ceto tare da wadanda kake kauna. Ka roki Allah ya sake baka wata dama kamar yadda ya baiwa wannan mata uwar yaro. Kada ka jira sai wani abu mai ban tausayi ya faru kafin kayi anfani da damar da ka samu.***

# Korea ta Arewa: Elizabeth Prentiss

RANA TA 243

***"Ji nake na zama fanko" Elizabeth Prentiss ta yi kuka. Rashin yaya biyu tashin hankli ne, ko da shike ta taba shiga mummunan hali na rashin iya amfani da kafafun ta amma bangaskiyar ta ga Kristi ya bata salama da yakansa ta yi fara'a ta wata hanya ta musamman da ke karfafa wasu.***

*Amma cikin ko wace matsala mu koda kanmu masu hidimar aikin Allah cikin hukunci duk da haka masu farin ciki tuttur*
*II Cor. 6:4, 10*

"Wannan karon abin yayi tsananin da zata iya jurewa, Allah ina rokon ka bi da ruhu na mai rauni". Allah ya amsa adduwata. Wata rana a cikin bakinciki mafi yawa ta rubuta wannan waka mai karfafa zuciya.

*Karin kauna a gareka ya Kristi karin kauna a gareka! Kaji addu'a da nakeyi a durkushe wannan shine karin rokona; a gareka karin kauna ya Kristi. Gareka na taba neman farincikin duniya. Na nemi salama da hutawa yanzu kuwa rai kadai na ke bida... Bani abin da yafi dacewa... Bari damuwa tayi aikinta, na aiko da bakinciki da radadi sakoninka masu dadine, haka kuma jan baitinsu a yayinda suke rairawa tare da ni. Karin kauna a gareka ya Ubangiji.*

Elizabeth ba ta taba sanin irin kwantadda zuciya da wannan waka zata yi wa Kristan wannan zamani ba. A Korea ta Arewa shugaban Kwaminis mai rasuwa kimil sung ya gano Krista talatin da ke zama a karkashin kasa, ya sa an fito dasu domin a kashe su a bainar jama'a. Kalmominsu na karshe a yayin da suke fuskantar mutuwa sune kalmomin wannan waka nata. Karin kauna zuwa gareka.

***Yesu baiyi mana hassadar mu shiga bakinciki ba. Ya sani wani lokaci dole ne bakinciki ya same mu har muyi kuka. Amma da yake yana kaunar mu ainun ba zai barmu a cikin hawayenmu ba. Yakan barmu muyi bakinciki na wani lokaci domin tayi aikinta a rayuwar mu tana kuma taimaka mana ga yin girma. Sa'anan in mun fara kaiwa inda ba zamu iya daurewa ba sai muga rayuwar mu na kara kyau lokaci zai zo da zaka ji karfi. Nauyi kuma zaya sauko kamar dai su Kristocin Korea ta Arewa da kejin shan tsanani. Ba da jimawa ba zamu san ma'anar yin farin ciki ko da muna cikin shan tsanani. Ka taba shiga cikakken bakin ciki? Ya kawo karin kaunar Kristi?***

# Matsanancin Mai Lissafin Sunaye

## KURKUKN KWAMINISAWA: FLORICA

**Rana ta 250**

**Florica tana shakka tana jin dai kamar bata da sauran sa rai ga fita daga kurkuku. Anyi makonni suna ganin ana fitar da mata da ga kurkuku. Babu wanda yasan inda ake kaisu a yayin da ake kiran sunayen mata da suka taru a filin gidan kurkuku. Watakila ma sallamarsu ake yi su tafi gida.**

Da haka kuwa, sai ta sallamarda komai a hannun Allah ko da menene, zai faru a lokacinda aka kira sunan ta. Soja mai mukamin manjo da ke zaunae a bayan teburin sa ya ce, lallai ne kusani cewa nafi Allah iko a wannan wuri. Tunda yake harwayau, Allahn naku bai iya shiga tsakani ba domin ya taimake ku. Amma wai shin kun farga da haka? Abinda nake nufi shine, dole ku farga da cewar babu bukatar Allah a cikin al'umar kwaminis. Saboda haka ku ma baku kamata ku bukaci Allah ba. Idan har kuka sami shika daga nan, zaku ganarwa kanku irin cingaba da muka yi a cikin yan shekarun nan, wannan kuwa mafari ne kawai!"

Florica ta dubi takardun da ke bisa teburin sai tace, "na ga lallai kai mai iko ne. Kuma na tabbata kana da wasu takardu game dani wadanda ni ban taba saninsu ba, kuma wadanda ke iya zama dauke da batun rayuwa ta na ko inyi rai ko inmutu. Amma kasani cewa Allah ma da kansa yana da Lissafin ko wane mahaluki babu wani cikin mu da zai iya rayuwa sa tawurin Allah. Sabili da haka duk inda Allah ya ajiye ni ko anan ne ko kuma a sake, ina gamsuwa da cewar shi ya fi mani alheri." Bayan kwana uku kuwa, sai aka saki Florica.

*...domin bakin kowa shi kwa bu a komo da dukan duniya kalkashin hukurcin Allah. Rom. 3:19*

*A yayin da yara suka shiga makaranta sukan koyi sanin irin iko da allon alli yakeda shi. A fahimtar yaro rubuta sunan yara akan allo da malami yake yi yana nuna cewa su kangararrun dalibai ne a cikin aji . A zaman mu na yara mukan so a rubuta sunayen yara masu haddasa rigima a cikin aji akan allo, domin yin haka zai kawo a hukumtasu nan da nan. Ina amincewar irin wacce muke da ita tun muna yara? Shin bazuwar shaidanu a ko ina a cikin duniya a yau shi ya sha kanmu har muna mantuwa cewarAllah yana lissafin duk abinda mukeyi? Littafi Mai Tsarki yana koyo mana cewa kowa zai amsa abin da yoyi a gaban Allah. Sabo da haka kada ka karai a yayin da kaga mugu na walawa babu hukumci. Allah zai kawo su ga hukumci.*

# Matsaṇantan Yan Juyinfuwya -Hali

**ROME:**

**Rana ta 251**

**Kristocin da can mutane ne masu kaunar zama yan juyin-juya-hali na Ruhaniya. Zama a cikin wata al'umma mai bautar gumaka kuma wadanda suka dauki duk wanda ba ya tare dasu a zaman "Fandararru", Kristocin wannan lokacin masu ji da addininsu ne wanda karfin su na haka din har ya fara tsoratarda rayuwar birnin Rome. Sunci gaba da karo da dokokin kasar 'wanda ya tsoratarda hukuṃar Rome sosai. Wannan ya kawo musu kiyayya ainum, har ya kawo ana kashe su da dinbin yawa kai harma kisan gilla ake yi musu.**

Kristocin yan juyin-juya-hali ne na Ruhaniya wadanda suka yi shelar shari'a ta karshe da kuma samun sakewa dungur ungum mai zuwa na duniya ta wurin dawowar Kristi domin dayawa su sami ceto. Sun tallata Yesu Kristia zaman hukuma mafi daraja fiye da shi sarkin Rome. Sabo da haka sarki ya aika da doka cewa dukan wanda ya ke nuna shi Krista ne a yanke masa hukumcin kisa ba tare da anyi masa shari'a ba. Babu batun bin kadi ga wadannan "yan tawaye wandanda ke Kalubalantar mulkin sarki.

Mulkin masarautar Rome sun jagoranci wasu matsanantan lokuta dabam dabam guda goma na azabtarda Krista, Kuma kowane lokaci da yazo yakanfi na baya zafi.

*Kayi yakin kirki na Imani, ka ribce rai na har abada, wanda aka kira ka zuwa yareshi (1Tim. 6:12)*

Daganan ne aka fara sanin yan-juyin-juya-hali na Ruhaniya da sunan shahidai. An fara karbar haka ne ga shaidu da suka bada shaida a gaban alkabai da sarakuna tare da tsaro sosai na horarrun sojoji. Aka kirasu shahidai ko kuma masu yin ikirari, ko da basu mutu ba wajen tuhuma, sam sam babu abin da yạ sa su su canja ra'ayinsu. Shahidanci yakan nuna zama shaida na bangarkiyar mutumin a cikin Kristi komi hassadar al'amura, kowane mutum mai shaida Kristi dan juyin-juya-halin Ruhaniya ne na zamani.

*Shahidai da ke cikin tarihi, kamar yadda muke sojoji ne na yakin Ruhaniya. Wannan yaki ya farane a lokacinda Yesu ya tumbuke ikon shaidan ta wurin mutuwarsa a kan giciye. A cikin mutuwarsa ya kawas da makamai na Jahannama da ibilisanta, shahidai kuwa sun cigaba da wannan yakin, amma fa yakin ba da kayan yaki irin na duniya ba amma na Ruhaniya. Ikirarinsu shine makaminsu na zuba. Suṇa shiga yankunan magabta kamar kasashe marasa yanci ba tareda tsoro ba kuma suyi, shelar cin nasarar Kristi bisa shaidan. Mallakarsu ba ita ce rayuwarsu ba, amma shaidar su. Shiyasa suke bada rayuwarsu domin tabbatarda imaninsu. Ta ina zaka fara yakin? Ko zaka girgiza makamin ka na bangaskiya?*

# Sautu (Aike)

**Rana ta 252**

*Na Roki Ubangiji Da ya Taimaki Makwabcina*

*Ya kai Bishara Zuwa Kasa she Masu Nisa,*
*Da Kuma Yin jaje Ga Marasa Lafiya,*
*Amma Yace Mani,*
*Idan Kana Kamnata, Ka Zama Hannayena.*

*Na Roki Ubangiji Domin Na Tafi Gurin Masu Macewa,*
*Da Kuma Marayu ............... Akan Titi,*
*Kuma Na Ziyarci Fursuna, Amma Yace Mani,*
*Idan Kana Kamnata, Ka Zama Kafafuna.*

*Na Roki Ubangiji Da Ya Dubi Matalauta,*
*Yau,*
*Da Kuma Zuba Ido Kan Kowane Jariri da Yayi Kuka,*
*DA Kuma Duba Bukatun Kowane Mutum,*
*Amma Yace Mani,*
*Idan Kana Kamnata Kazama Idanuna.*

*Na Shaida wa Ubangiji Cewa Inaso in bauta maka,*
*Amma ban san daga ina zan fara ba,*
*Kamna Itace Amsa, ya shaida mani,*
*Idan kana kamnata, ka zama zuciyata.*

**G.Susan Westfall**

# Matsanancin Kin Yarda

## BATMUSA: YOHANNA MAI BISHARA

**Rana ta 253**

**Kaka zaka yi da mutumin da aka bararraka a cikin mai amma baya mutuwa?**

An fadi cewar sarki Domitian na Rome ya bada umarni a bararraka Yohanna Mai Bishara a cikin mai har sai ya mutu, amma sai Yohanna ya cigaba da yin bishara daga cikin tukunyar mai. A wani lokacin kuma an tilastawa Yohanna da yasha dafi, amma,kamar yadda aka alkawartar a cikin Markus 16:18 dafin baiyi tasiri a kansa ba. Sabo da haka kuwa, aka kori Yohanna shugaban majami'a na Afisawa na wannan lokaci zuwa Batmu sa a cikin shekarar A.D. 97.

Yohanna ya haye dukan wadannan domin Allah bai gama amfani da shi ba tukuna. Da akwai saura domin"wahayi" na tafe.

A lokacin da yake cikin wani kogon dutse akan tsibirin Batmusa, Yohanna ya karbi wahayi. Wannan wahayi shi ya zama littafin Ruya ta Yohanna-Littafin da ya zama ginshikin karfi na yada bishara a zamanin shekarun bishara ta majami'a.

Littafin yayi annabci game da al'amuran da ke kewaye da batun dawowar Kristi. Yohanna ya yi rubutu game da zuwan Kristi na biyu, kuma ya marabci da wowarsa. Harwayau rubuce rubucen sa suna karfafa masu bi da su ka sa begen su ga dowowar Krist mai daraja.

Shekaru biyu bayan korar Yohanna Sarki Domitian ya mutu, Yohanna kuwa sai ya koma Afisawa. Shi Yohanna shine mafi kankancin shekaru a cikin almajiran Yesu, shine kuma acikinsu yayi rayuwa zuwa shekaru mafiya yawa a duniya, ya mutu a Afisawa a cikin salama yana da shekaru tamanin da haifuwa bayan gwagwarmaya ta yin hidima ga majami'ar Kristi na sheharu fiye da hamsin.

*Ni Yohanna, dan'uwanku da abokin tarayya da ku cikin isanani da mulki da hankuri da ke cikin Yesu ina cikin tsibiri da akece dashi Batmusa Ruya ta Yoh. 1:9*

*Ba ta yiwuwa a janye aiki ko ayi murabus daga yin hidima ga Allah. Ka tambayi Yohanna. A lokacin da matsakaicin shekaru na rayuwa a duniya bashi da tsawo, Yohanna ya rayu har tsawon shekaru tamanin, yana hidimar sa da bangaskiya.*

*Watakila kauma kana fama da naka kokari na yin hidimar Allah. Watakila kana jin ka tsufa ainun kuma kana samun kanka cikin tunanin cewa Allah zaiyi amfani da wani mai kanana shekaru a maimakon ka. Ko ma kila kai saurayi ne mara aure kana zaton Alla zaifi son yin amfani da mai aure. Maimakon gujewa Allah yana so ya gina Ruhun dagawa wanda bashi karaya. Ka fara roko yau domin Allah yayi maka budi domin kasan mataki na gaba na yi masa hidima.*

# Rashin Biyayin Matsananciya

## JERICHO: RAHAB

Rana ta 254

**A lokacin da Joshua ya aiki yan -leken-asiri guda biyu su duba kasar Jericho, sun buya a gidan wata karwa da ake kira Rahab. Gidan Rahab an ginashine akan ganuwar garin. Jericho wadda aka gina domin hana magabta shiga birnin. A lokacin da sarki ya sami labarin yan leken asiri daga Isra'ila suna cikin garin, nan da nan ya aika wa Rahab sako. Ya umurce ta da tayi maza ta kawo bakin da suka shiga gidan ta.**

Rahab ta yi rashin biyayya da wannan umarni na sarki ta boye yan leken asirin, har takai ga fadin karya domin ta hana su sanin inda mutanen suke. A wannan daren kuwa ta fitar dasu a asirce ta wurin yin amfani da igiya ta zura su takan ganuwa da igiya ta tagar gidanta suka fice.

Kalilan Rahab ta sani game da Allah na Isra'ila, amma a shirye take ta taimaki mutanensa. Tayi wa hukumar ta mara sanin Allah rashin biyayya, harma tasa rayuwarta a cikin hatsari. Sakamakon yin haka kuwa ya cetar da ranta.

Ana iya samun makamancin irin wannan a cikin Ayyukan Manzami 9:25, Jim Kadan bayan tubar Bulus, yayi kwanaki da dama tare da almajiran a Damascus, yana bishara da kuma koyaswa a haikali. Yahudawa kuwa suka yi ta mamakin wannan sauyi na Bubus har suka yi tunami cewa ya zama magabci. Almajirai kuwa suka fitar dashi ta kan ganuwa suka zura shi kasa da igiya a wajen gari domin tsirar dashi daga Yahudawa da suke kullin kashe shi.

*Sama baba wani iko sai na Allah. Rom. 13:1*

*Wadansu Krista sukan-yarda cewa kin yin biyayya ga dokokin hukuma na kasashe marasa yanci ya isa ayi wa mutane tsanani. Wai shin Krista yan China da suka ki su bada sunayensu a rubuta a littafin majami'ar su ta hukuma sunciayi musu duka kuma a tsananta musu ne? A kasashen Musulmi, masallata da suka tuba suka karbi Yesu sunci a jejjefe su da duwatsu a kashesu ne? Ko da shike akan sami bambamcin farsara a wasu sassa, dukan Krista sun yarda cewa ba zamu bari gwamnatoci su tilasta mana yin rashin biyayya da dokokin Allah ba. Haka kuma wannan bai kamata ya sa Krista sununa rashin da'a ga hukumaiba. Rashin biyayya tana iya zuwa ne a lokacin da ya kuma yin biyayya yakan zo ne a lokacinda ya zama dole ke dauki matsayi tsakanin dokar Allah da dokar huhuma. A wana matsayi kake? Yi nazarin Littafi Mai Tsarki domin kanwa*

## KOREA TA AREWA: WATA TSOHUWA

**Rana ta 255**

**"Wata rana malamar mu ta gaya mana cewa zamuyi wani wasa na musamman. Sai ta rada mana a kunne game da wani muhimmin littafi da iyayenmu suke boyewa, ku nemi wannan littafin, ku kawo mana a asirce a makaranta gobe domin mu baku kyauta ta musamman. Na tafi gida kuma nan da nan na fara neman wannan littafin.**

"Washe gari na zama daya daga cikin yara gomasha - hudu da suka kawo wannan littafi mai bakin rufi, Littafi Mai Tsarki, Zuwa aji. Aka bamu kyautar jajayen dankwali, sauran yan-makaranta kuwa suka yi ta tafi a yayin da malamar mu take nuna mu a aji.

"A ranan nan na tafi gida a guje da rana domin na kosa na nunawa uwata, yadda nayi naci kyautar jan-dankwali, amma da ita da babana babu wanda ya komo gida, sai na fara tsorotchi. Ina jin yinwa ga kuma dare ya fara yi. Sai na fara jin kasala, sai barci ya dauke ni akan kujera.

Washe gari sai yan sanda suka zo suka daukeni suka ce mani wai daga yau ina karkashin kulawar gwamnati. Ban sake ganin iyaye na ba.

Wata tsohuwa daga Korea Ta Arewa ce ta bada wannan labarin. Bata sake taba jin labarin iyayen ta ba kuma, har yanzu kuwa gwagwarmayar neman gafara takeyi. Ita tilo ce daga masu yawa da suka shiga irin wannan jaraba.

*Har shaidan da kansa ya kan mayasda kansa kamar mala'ika na haske, ba wani abu ne fa masu hidimansa suma su mayar da kansu kamar masu hidimar adalci. 2Cor.11:14-15*

*Sabanin sanannen zanen nan da ake yi na hoton Ibilis shaidan ba ya rike da mashi mai kai biyu cikin jajayen tufafi wannan zane ne kawai. A saukake muna iya gane jan hakali zuwa mugunta. Amma kuma kamar wannan yarinya na wannan labarin, wasu lokuta mukan fuskana' mugun ta wasu hanyoyi dabam. Galibi wakilan magabcin sukan zama mutane ne masu jan hankali kuma masu manyan mukamai. Kayi la'akkari da abokin harka mai iya magana. Ko ma kayi tunanin irin iko da parfeso na University yake dashi ta sunan koyarwa. Kamar yadda wannan diya ta gane a karshe, magabaci duk yayin da muka ruske shi ko wakilansa. Kana da saukin shiga hannun magabci? Ko kuwa zai same ka da shirinka?*

# Matsanancin Fursuna

## VIETNAM: TO DINH TRUNG

**Rana ta 256**

**To Dinh Trung yayi tafiya doguwa ta daruwuwan miloli akan basukur dinsa tafiya akan hanya mai gargada da datti domin yakai bishara ga mutanen kabilar KHO. Wannan kabila tana daya daga cikin kabilu sittin na Vietnam wadanda gwamnati ta haramta akai musu bishara. Yana shiga kauyen kenan a watan Afrilu. 1995, yan sanda suka janye shi daga kan basukurinsa suka hau shi da duka. Suka dauki hotonsa da ridiyo suka yi masa ba'a a gaban mutanan kauyen.**

Aka kai shi kurkuku aka rike shi har watanni shida kafin a kaishi wajen shari'a. A lokacin da yayi wata waka da yara suke yi da ake kira "Ka kaunaci Ubangiji" Dare da Rana", Sai ma aka kara rike shi a kurkuku.

Amma da yake kungiyoyin Krista dabam dabam sun matsawa gwamnatin sai aka saki Trung watanni shida Rafin ranar fitarsa daga kurkuku Amma ko da shike yana da mata da ya'ya biyu kanana, mai bisharannan fa ya ce bai yi shirin barin kurkuku ba! A ganinsa wannan wata baiwace daga sama na bashi damar yada bishara ga batattu me zasu iya yi masa?

*Domin wannan ni Bulus damrarre na Kristi Yesu. Sabili• da ku Al'um mai. Afisawa 3:1*

Ta wurin kokarin Trung a kurkuku kusa da Quang Ngai da yawa sunzo ga Kristi. Bayan da yaji labarin cewa Krista da yawa suna ta addu'oi da rubuce rubuce dominsa, ta kaka zai bar irin wannan dama ta wuce inda zai bar misali ta wurin maida ransa ba Kome ba domin Mulkin Allah? Trung dai yaki fita daga kurkuku ya zabi yaci gaba da zama a ciki yana yada bishara.

*Trung ya taba zama fursuna kuma an nuna masa mugunta da azaba, amma a lokacin da ya zabi ya zauna a kurkuku donlkansa, sai ya zama fursunan Yesu Kristi. Hukukuka tayi kokarin karya su amma Yesu ya farfado dashi, Hukuma tayi kokarin rufe bisharar bakinsa amma Yesu yakai bisharar a kowane dakin kurkuku ya riba kwazon Trung fiye da da. Trung yana yi mana tunin yaya dadin walwala cikin yanci yake a karkashin mulkin Yesu koma dayake muna tokare da damuwa na wannan rayuwa. Mai yiwuwa kaji kamar kai fursuna ne game da wasu al'anura. Bari Yesu ya yantar da kai ta wurin bashi damar ya zama Ubangijin rayuwar ka.*

# Matsanancin Pastor

## SUDAN: PASTOR LUKA

Rana ta 257

**Pastor Luka yayi mawuyacin ban-kwana da ya'ya'n sa guda biyar da kuma matarsa kafin ya fita daga sansanin yan-hijira domin ya tafi fagen bishara a kudancin Sudan. Zai kai tsawi on watanni uku kafin ya sake-saduwa da iyalins, domin wurin da yake zuwa yada bishara yana daya daga cikin wuraren da yakin basasa ya fi shafa ga kuma hare-hare da gwamnatin Islama ke kawo masu.**

Taron masubi na Pastor Luka basu da ginanniyar majami'a domin an rusarda gine gine masu yawa a cikin tsawon kusan shekaru ashirin na yakin basasa ta kasar Sudan.

Sukan yi taro a kowane mako a karkashin inuwar wata babbar itaciya wadda aka fafe alamar giciye a jikinta. Mambobi sukan zauna a kar ko kuma su tsaya a tsaye, a lokacin sujada a yayinda Pastor Luka yakan tsaya kusa da inda akai sa alamar giciye yayi wa'azi.

Idan da Pastor Luka zai zauna da iyalinsa to zai sami isasshen lokaci domin su a kullum. Haka kuma masu aikin agaji zasu cigaba da raba abinci ga yan Sudan masu fakewa a sansani, ana lura da biyan bukatunsu. Amma Allah ya kira Pastor Luka domin ya lura da biyan bukatunsu na Ruhaniya. Idan da bai tafi ba wanene zai dauki gurbinsa?

*Wanene zaya iya raba mu da kaunar Kristi? Rom. 8:35*

Luka yana bishara a yankin da da ma can babu majami'a takamaimai. Yana biyayya ne da umarnin Allah domin ya zama gishiri da kuma haske a yankin da ke cikin yaki. Akwai wuya- wani lokacima da tashin hankali wajen barin iyalinsa. Amma gashi Allah ya albarkaci bada kai da yayi ta wurin samun habakar wannan" Majami'a ta karkashin itaciya".

*A wasu lokuta akin Allah yana raba mu da iyalinmu da muke kauna. Yesu da kansa yabar dukan abubawanda ya taba sani a garinsu da kuma iyali a lokacin da ya cika shekaru tsalatin domin ya fara bishararsa. Idan fa zamubi shirin Allah domin rayuwar mu, galibi tumanin mu yakan dauke hankalinmu daga abubuwanda muke yi wa Yesu zuwa wadanda bamu sani ba. A yayin da tafiya na iya rabamu da kaunatattunmu, gidajenmu, Walwarin da tsaron lafiyarmu, ba a taba iya raba mu da kaunar Krist. Kaunar sa ita ce abokin tafiye atuttur, shi yasa a kullum bama tare da kadaici. Karin cikin kadanci domin tunanin. Gida, kyali, abokai? Idan kana da tabbacin jin cewa kana bin shirin Allah domin rayuwar ka, to lallai ne ka dage wa aikin da ke gabanka. Kristi kuwa zai cigaba da zama abokin aiki naka.*

## VIETNAM: DAN'UWA K'BE

**Rana ta 258**

**Da farkon farko da ya'yan dan'uwa K'be suka ganshi a cikin akwatin talbijin sai suka dimauta da farinciki, amma murna ta koma ciki da suka ji mai bada labari yace ubansu mai laifi ne. Suka ce yasha yiwa gwamnatin Vietnam laifuffuka masu yawa.**

Laifuffukan Dar'uwa K'BE. Sune yin bishara a gidajen - addu'oi wadanda gwamnati ta haramta ayi taro a gurin. Gwamnati ta sa notonsa a talbijin wai don ta kunyatar dashi ta kuma gargadar da mutana cewa ga fuskarsa don kamashi a gaba. Kuma sun nuna amsa tambayoyida yan sanda -suka yi masa a talbijin kuma aka watsa ta rediyo mai sauti, amma sai yin haka ya zama kara yada bishara gaba gaba. Wannan ya bashi wani mataki na isa ga mutane dayawa domin Kristi. Wadanda suka ganshi a talbijin suka tambaya wai wane addini yake bi, anan kuwa ya sami damar gaya musu game da Kristi.

Yayi bayani, ya ce, "Sun nuna fuskata talbijin domin mutane su gane ni. Makwabtana suka ce, 'me yasa kabar iyalinka?' Na shaida masu cewa Allah ne zai lura da wannan. Lallai ne na tafi.. Lokacin girbi yayi, amma ma'aikata kuwa basu da yawa?

Ganin cewa wannan nuni na kunyata a K'BE yada bishararsa bata hanashi aiki ba, sai yansanda sukayi masa barazana cewa a gaba idan aka ganshi yana wa'azi za'a tsare shi'. " Matata tana farinciki domin sunayen mu na rubuce a cikin littafin rai kuma fuskata shaida ce a cikin talbijin. Yan sanda suna taimakawa ga yada bishara, suna iya rushe majami'a amma ba shaidar bishara ba.

*Bisa ga bisharata wadda nike shan wuya a cikinta har su demadamra kamar mazambaci; amma ba a daure Allah ba. Maganar Allah ba. 2Tim 2:8-9*

*Ana iya rataye masu bi a buga musu kusa ko a daure su dasarka acikin kurkuku koma a kulle su ba a ganinisu. Masu bi suna ma iya mutuwa. Amma duk da haka bishara fa saidai taci gaba. Ko wurin taro ko kuma wani mai bi tilo ba. Ana iya rufe ginin majami'a. Ana iya barin wurin taro. Ana iya daure mai bi ko ma a kasheshi. Wai shin fahimtarka ga addinin Krista ya ta'allaka nega wani Pastor ko wani girin majami'a ko wata hidima? Shin bangaskiyar ka zata ci gaba idan aka dau ke wadannan? Maganar Allah tananan daram. Kamar yadda K'BE ya dage, kaima kana iya dagewa?*

## Rana ta 259

***Dama Na Zama Mai Hidimar Ubangiji***
***A yalwace Yake A Dukan Lokuta Kuma A Dukan Wurare***
***Bai Kamata Hamayya Ya Kawo Wani Bambamci Ba.***
***A Ruhaniyance Muna Da Shugaba Daya Ne Tak.***
***Shi Yake Umartar Tafiyar Mu.***

Tom White wanda yasha azaba a cikin kurkukun kwaminisawa na Cuba domin jefo mujallun bishara daga cikin karamin jirgin sama da ke firiya ta kan tsibirin.

# Matsananciyar Likita

## ROMANIA: DR. MARGARETTA PESCARU

**Rana ta 260**

**A cikin kasar kwaminisanci ta Romania, akwai likita guda daya wanda yakan zauna tare da masu yiwa fursuna tuhuma su kuma nunawa masu tuhumar (Tuhuma) hanyoyi mafi zafi na azabtarada mutum ba tare da ya mutu ba. Amma wadansu likitocin gaske kuma sunki jinin abin da kwamini sawan suke yi.**

Daya daga cikin irin likitocin kirkin nan ita ce wata kyakkyawar Krista mai suna Margaretta Pescaru. Akan binciki dukan likitocin lafin su shiga cikin kurkuku amma, Dr. Pescaru tana daukar kasada kwarai wajen boye magani ta shiga dashi akai akai; wannan ba da kai nata ya ceci rayuka da dama.

An taba tura ta zuwa wani asibitin kurkuku wanda aka kebe musamman domin masu ciwon tarin-fuka.A wannan lokacin, kwaminisawa sun nada wasu mutane na musamman waisu masu "Sabunta-ilimantarwa" domin suyi amfani da duk abin da ke akwai su rinjayi mutum ya janye daga duk wani imani da yake da shi ya kuma bada kansa ga cikakkiyar biyaya gakwaminisanci.

*Zani wurin sarki ko da shike ba bisa ga shari'a ba ne, idan kuwa na lalace na lalace kenan. Esther 4:16*

Wadannan masu sabunta-ilimantarwa marasa tausayi ne, kuma Kritsta da yawa sun mutu a karkashin azabtarwar su. A lokacin da Dr. Pescaru ta sami labarin cewa sun iso wannan asibitin domin su fara wannan barna da suke yi akan masu ciwon tarin fuka, sai tayi abin da ba a taba yin tsammani ba. Sai ta tafi wajen manyan shugabannin dukan kurkuku da ake tsare mutane, kuma ta yi roko game da dukan fursunonin. Babu wanda yasan yadda tayi haka, amma Dr. Pescaru ta sami tagomashi game da haka a wajen shugabannin.

Saboda haka aka dakatarda irin wannan azabtarwata "Masu-ilimantarwa" a kwaminisancin Romania zuwa wani lokaci, godiya ga irin karfin zuciya da kokarin da tayi.

*Kokari. Shine bambanci tsakanin cigaba da rashinsa. Yin kokari shine abinda Krista sukanyi idan suka sa zuciyarsu akan bisharar Kristi. An Kokarta. Fadincewa an kokarta shine kawai hanyarda masu bi zasu yarda su sadu da rashin nasara. Gaskiyan a babu yadda zamu san abinda zai faru har sai mun kokarta. Watakila mukan yi gajin hakuri yayin da wata shawara maikyau ta zo mana game da ciyarda bishara gaba ko a gida ko a cikin unguwar mu. Mukance kila ma abin bazaiyi aiki ba, mukanji kamar hamayyar zata yi karfi, amma ba zamu sani ba sai mun kokarta ashirye kake kayi biyayya da Kristi ko ta halin kaka? To kafara yau.*

## KOREA: ROBERT J. THOMAS

**Rana ta 261**

**Robert J. Thomas ya tashi zuwa Korea a shekarar 1863 tare da matarsa a zaman baturen mishan ma farko. Bada jimawa ba bayan isarsu sai matarsa ta rasu. A cikin shekarar 1866, da yake yayi bishara na wasu watanni a Korea kuma ya koji yin magana da harshensu sai Thomas ya hau wani jirgin ruwa na Amirka mai suna, The General Sherman, a bokin gabar Kogin Taedong zuwainda yau aka kira babban birnin Korea ta Arewa, amma Jirgin ruwa mai suna Sherman ya kafe akan yashi. Sojojin Korea da ke bakin gaci suna shakkar jirgin kuma suna tsoro, sai suka hau jirgin, suna kada dogayen wukake da ke hannayensu.**

A lokacin da Thomas ya ga lallai kasheshi za a yi, sai ya fito da Littafi Mai Tsarki cikin harshen koriyanci yace musu, "Yesu, Yesu". Aka fille masa kai. Shekaru ashirin da biyar bayan mutuwar Thomas, sai wani ya gano wani masaukin baki a wannan yankin da wani irin adon bango na takarda. Takardar na dauke da wasu harufai irin na Korea a rubuce akai. Shi wannan mai gidan yayi bayani cewa ya nane shafunan wannan Littafi a bango domin tsare rubutun daga kodewa.

Mai gidan da ma baki da ke sauka sukanzo su karanta takardun a nane a bango. Wannan shine Littafi Mai Tsarki da Thomas ya baiwa wadanda suka kashe shi.

Ko da shike kwaminis ne ke mulkin wannan yanki a yau, majami'a ta rayu. Aikin Robert J. Thomas - da ake kira "Mai aikin mishan na wucin gadi" - yana cingaba a Korea ta Arewa, in da yanzu bishara ba a bango kawai take ba, amma a zukatansu.

*Ni na dasa Apollos ya yi ban ruwa; amma Allah ne mai ba da amfani domin wannan fa shi da ya dasa ba wani abu bane, ko shi wanda ya yi ban ruwa kuma, sai Allah wanda ke ba da amfani. (I Kor. 3:6-7)*

*Kwatanta shirya lambu a lokacin bazara, kuma ka kaura a lokacin rani. Dukan lokancinda ka bata kana shuka, kana ciran ciyawa da ban ruwa na irin tumatir, barkono, kankana duk ya zama bata lokaci. Muna iya fadan haka game da wannan mai shaida Kristi. Amma anan muhimmancin ya wuce gaban batun kwandon tumatir. Ba tare da ganin sakamakon aikin mu ba, zai yi wuya mu gaskanta cewa aikin da mukayi tukuru abin karba ne da kuma mutumtawa. Mu tuna Allah shikesa dukan a buya girma. Mu gaskanta cewa Allah zaici gaba da habaka ayyukan da muka fara - ko ma da ya tashe mu zuwa gaba. Wane irin lambu kake so ka barwa wani don yaci gaba da raya shi?*

# *Karfin Hali Matsananci*

Rana ta 262

## MASARAUTAR MULKIN ROME: BLANDINA

**Blandina wata baiwa ce wadda take cike da ikon Allah domin wadanda suke azabtar da ita wanna ya daka ya ba wannan dare da rana amma sai duk su gaji su hakura. Alhalima azabtarda ita sai kara mata imani yake yi. A fili take shaida bangaskiyarta, tana cewa, "Ni Kristace kuma bazamu kunyataba."**

An azabtadda Blaridina a zamanin Sarkin Rome Marcus Aurelius Antoninus (A.D. 161-170). A wancan lokaci ne Krista suka fara kebe lissafin dukan wahalunsu. Suna sa rai zasu karfafa masu bi wadanda zasu zo a baya su karanta labarun gaskiya na karfin hali da akayi a baya. An rataya Blandine a kan ice duk da haka tayi jimiri, domin ta karfafa wadanda suke rallon azabtata da ake yi. Bayan da ta haye wannan al'amari sai aka saka ta a cikin kewayayyen fage da zakuna tare da wani yaro Krista dan shekaru goma sha biyar. Blandina ba ta nuna wani tsoro a gaban dabbobin nan ba' amma tana nuna "farinciki da daukaka game da rabuwa da wannan duniya kamar wadda aka gayyata zuwa wani bukiri cin abinci na aure".

*Zuwa dukan hakuri da jimrewa tare da farinciki kuna ba da godiya ga Uban wanda ya isarda mu mu zama masu tarayya na gidan tsarkaka cikin haske.*
Col. 1:11-12

Sau biyu suna jefa Blandina a gaban zakuna amma ba su iya taba ta ba. Haka kuwa aka dawo da ita cikin kurkuku ba tare da kwarzane ba. Amma daga baya zakuna sunyi mata rauni aka kuma tube ta zindir aka dora ta akan gasasshen kujerar karfe mai rafi ainun. Duk da haka ta rayu kuma tana karfafa na kusa da ita don kada su kauce wa imaninsu. Amma a karshe sai suka soki Blandina da takobi bayan sun kasa canja mata ra'ayi.

*Ko da shike babu nasaba da bisharar Krista. Akwai wasu al'amura da ba zamu iya hana musu ba wadanda ke fama da abokin aiki mai wuyar sha'ani. Yin hakuri da mawuyacin hali na rayuwa. A wasu lokuta mukangama ba zamu iya kara yin dauriya ba sai muji kamar ma gara mu fasa. Koma da wane irin al'amari muke aiki Allah ya na bamu jimiri da kwazo na yin duk abinda ya kira mu muyi. Allah ya baiwa Blandina jimiri. Yana iza mu mu nemi taimako, don kula da iyali, don fuskantar abokin aiki, ko ma mu aikata wani aiki da bamu taba zaton zamu iya ba. Yin amfani da sunan Yesu, zamu iya zama shaidunsa. Allah yana tare damu yana bamu iya yin jimiri da farinci ki, a wane bangare kake da bukatar matsanacin karfin hali?*

# Matsanancin Barawo (Na Daya)

## RUSSIA: NIKOLAI KHAMARA

Rana ta 263

**An kama Nikolai Khamara da laifin fashi, akayi masa daurin shekaru goma a kurkuku. Khamara yakan kalli Krista sai yayi ta mamaki wai wadanne irin mutane ne wadannan. Maza ne su, amma duk da azabarda suke sha suna nuna farinciki kuma sai suyi ta raira wakoki a cikin dufun dare. Idan suka sami guntun burodi, saisu raba da wani wanda bashi da nasa. A yayin da suke magana da wani wanda shi Khamara ba ya iya gani sai fuskokinsu su haskaka.**

Wata rana wasu Kristoci guda biyu suka zauna da Khamara, suka tambaya yadda yazo kurkuku, Khamara ya gaya musu labarinsa mai takaici sai ya karasa da cewa "Ni kam ai batacce ne ni." Da ya daga cikinsu yayi murmushi, ya tambayi Khamara. "Idan waniya batar da zobensa na zineriya, menene tamanin wannan zoban zineriya a lokacin da zoben ya bata?" Wace irin tambayaice wannan! Ai zoben zinariya zoben zinariya ne. Ka batar da shi, amma wanine zai tsince shi."

"Wannan amsa ce kyakkyawa," in ji shi Kristan. "Yanzu gaya mani, menene tamanin mutumin da ya bata? Mutumin da ya bata, ko da barawo ne, ko mazinaci, ko mai kisankai, yana da cikakken tamani na zama mutum. Yana da wannan tamani da Dan Allah yabar samaniya dominsa ya mutu kan giciye domin ya cece shi.

Wannan Krista ya shai'da wa shi mafashin: mai yiwuwa ka bata din, amma kaunar Allah na iya tsamoka." Daga jin haka sai Khamara ya ba da ransa ga Kristi.

*Amma Allah yanashaidar kamna tasa garemu da shike tun muna masu zunubi tukuna Kristi ya mutu sabili da mu Rom. 5:8*

*Yaya ake mizanin tamani domin sanin darajar abu? Galibi ta wurin jarintar lokaci da mutum yake yi, ko ta kudi ko ta wurin abin da akeji. Watau, yadda mutum yake kula da mallakar sa, ayyukansa ko ma ma'ammala da wasu yana nuna irin tamanin da ke akwai kwatanta wannan misali, bambamcin yadda zaka adana sababbin tufafi da tsofaffin tsummokaranka da ka gaji dasu. Ko kuma irin riko da zakayi wa abin shan ruwa da akayi da takarda ke kuma wanda aka yi da dutse mai daraja (Crystal). Kuma idan abu mai tamani ya bata ko masoyi yaji ciwo, akan zubar dahawaye. To yaya tamanin mutane yake--- kai fa? Kamar yadda aka gaya wa Khamara kana da tamani shi yasa Yesu ya bar sama ya zo ya mutu a giciye domin batattun halittunsa masu tawaye. Allah yana kaunarsu sosai. Ana kaunarka, kana da tamani "Yi farinciki ka shaida wa sauran" masoya" na kusa da kai.*

# Hali Matsanancin Barawo (Na Biyu)

## RUSSIA: NIKOLAI KHAMARA

**Rana ta 264**

**Nikolai Khamara ya shiga kurkuku a zaman barawo kuma ya fito a zaman Krista Bayan sallamarsa, sai ya hada kai da majami'ar karkashin kasa ta Russia.**

Bayan wani lokaci sai aka kama paston majami'ar Khamara. Aka azabtadda shi, da sa rai ko zai tona asirin majami'ar, amma baifurta masu Kome ba. Daganan sai aka kama Nikolai Khanara suka kawo shi gaban pastor suka gaya masa, " Idan baka bude asirihku ba zamu azabtadda Khamara a gabanka"

Pastor ya ga ba zai iya jurewa ganin wani yana shan azaba dominsa ba. Amma Khamara yace masa. "Ka rike amanar Kristi kuma kada ka basheshi.!

Shirye nake na sha wahala domin sunan Kristi. "Sai suka kwakule idanun Khamara. Pastor fa ya kasa Jure wannan. Yayi kira ga Khamara, "Ta kaka zanga irin wannan abu? Zaka ci gaba da zama makaho!"

Sai Khamara ya amsa. "Lokacin da aka raba ni da idanuna, zanga abubuwa mafiya na duniya kyau da nake gani da wadannan idanun. Zanga. Mai Ceto, "Lallaine kaci gaba da yin imani ga Kristi har karshe."

A lokacinda masu azabtarsa suka fada wa Pastor zasu yanke wa Khamara harshe, Khamara yace, "Mu yabi Ubangiji Yesu Kristi. Gashi na fadi abu mafi daukaka da zan fada, kuma idan kana so kana iya yanke harshe na." Wannan tsohon barawon ya sace wa wadannan hafsoshi wata dama na kwace masa ban gaskiyarsa. Yayi mutuwar shahidanci.

*Barawo ba yakan zo ba sai domin sata da kisa da hallaka, ni nazo domin su sami sai. Su same shi a yalwace Kuma. Yoh. 10:10*

*Wannan Labari na Khamara darasine mai nuna bambanci tsakanin mulkin Allah da na mulkin shaidan . Littafi Mai Tsarki na koya mana. Yadda zamu gane wadanda ke sata, kisa da rugujewa a zaman mambobin mulkin mugun. Ga batun Khamara kuwa mugun ya dauke masa idanu, ya ruguzar da harshensa har ma ya kai ga kashe shi. Akasin haka, mulkin Yesu bati ne na samun rai-rai har ga matuka. Domin haka Yesu ya biawa Khamara sabuwar rayuwa, Kuma iya kawo baiawo ga fansa. Wadannan mulki guda biyu suna sabani da juna kuma rayukan mu suna sabani da juna kuma rayukan mu sune ganimar.Khamaya "Kaura" Zuwa daya gefen a lokacin da Kristoci biyu suka nuna masa yadda zai shiga mulkin Allah. Me kake yi domin kawo wasu zuwa cikin mulkin Allah?*

# Matsananciyar Fassara (Na Daya)

## INGILA: WATA KRISTA GWAMRUWA

**Rana ta 265**

**An gurfanar da maza gudashida da gwamruwa guda daya a gaban kuliya domin yin wani matsanancin laifi ga majami'ar Ingila. Sun koya wa ya'ya'n su addu"ar Ubangijin mu da kuma dokokin Allah guda goma a cikin harshen Turanci.**

A shekarar 1519 a Ingila ba a yarda a koyarda ko kuma ayi nazarin Littafi Mai Tsarki da wani. Harshe ba sai Latin kadai. Amma talakawan Ingila ba su da wani harshe sai Turaoci. Sai masu bi suka fassare wasu wurare na Littafi Mai Tsarki asirce zuwa Turanci, a hankali kuwa suka raba wa mutane gida gida. Amma yanzu gashi an kama su, kuma za'a daure su a jikin kafaffen itatuwa a kone su a fili. Ahuwar kuliya tazo ga wannan gwamruwa kadai cikin mutanen nan guda bakwai, aka sake ta. Babu wanda yayi sukar yin haka din, ba ta da kowa, kuma akwai yara da take lura dasu a gida.

Wani mai tsaro mai suna Simon Maurton ya bada kansa domin ya raka tsofuwar gida. A yayinda Simon yake rike da hannunta suna tafiya sai yayi wata kara" cas" a cikin hannun rigarta, Sai ya fito da takarda da aka fasaarta da turanci, irin wanda suke koyawa yaransu. Ko da shike yanzun nan ta kubuta daga hukumcin kisa amma taki ta rabu da takardun domin yayanta na da bukatar sanin maganar Allah. Yan zu kam kaddara ta buga hatimi.

*A gareni shari'ar bakin ka tafi dubban zinariya da azurfa Zab. 119:72*

Jim kadan bayan haka, mutanonran guda shida da ita gwamruwa mai karfin hali suka sha dauri tam a jikin itatuwa guda uku kuma aka kone su da ransu.

*Yanzu muna cikin wani zamani na na'urar kararrawa wace take gasa da ci gaba irin na bankuna, abubuwa da muke rikewa da daraja sanannune gidajen mu da mallakarmu suna da tamani a garemu da ba zamu so rusasu ba. Amma ga Krista da suka rayu a karni na goma sha shidda, maganar Allah ita ce mallakarsu mafi tamani. Kamar dai wannan gwamruwa mai taurin kai na wannan labari, sun yarda su ba da ransu a bakin guntayen takardu da ke danke da magarar Allah. A yayinda mun sani lokuta na sauyi mu nuna darajor maganar Allah- ko da shike babu alamar yin haka zai kawo mutuwa a garemu. Ko wasu sun san irin daraja ko rashin daraja da kake ba maganar Allah? Zasu iya fadan irin darajarda maganar Allah ke dashi a cikin rayuwarka?*

**Rana ta 266**

***Lallai Ne A Kawo Rahoton Dukan Masu Aikin Mishan Na Krista Kuma Ayi Fiton su Waje Ba Tare Da Makawa Ba Domin Su Masu Wayon Kyarkyeci Ne Wadanda Suka Zama Kayan Aiki na Mulkin - Mallaka.***

Gargadi na gwamnatin Korea da ta Shelar wa mutanen kasar

# Matsanancuyar Fassara (Na Biyu)

## INGILA: WILLIAM TYNDALE

**Rana ta 267**

**"Amma, maigida Tyndale, Lallaine ka yarda, "Inji masanin likitan tauhidi, "Mutane sunfi dacewa da dokokin majami'a da suke iya fahimta maimakon dokokin Allah na cikin Littafi Mai Tsarki.**

William Tyndale ya bata rai da jin haka. "Ina kangara wa firistoci da dokokinsu! Idan Allah ya ga ya dace ya barni a raye, to kuwa kafin wani lokaci gaba sai naga cewar dukan wani yaro da ke tura garman shanu yasan Maganar Allah fiye da yadda suka sani a yanzu!" Wannan furuci na Tyndale ya jawo hikidu a tsakanin sa da hukumar majami'a. Ba da jimawa ba kuwa sai ya gudu ya bar Ingila zuwa karkara inda ya wallafa nasa Littafin Linjila da harshen Turanci da aka "Haramta" ayi.

Anyi shekaru ana shigarda Litattafan Linjilada Tyndale ya fassara zuwa Ingila ta wurin fasakwaurin cusa su acikin adilolin auduga da ake lodi a jiragen ruwana, James da sauran su, amma sai abokin Tyndale Henry Phillips ya tona sai masa asiri, aka yi masa shari bidi'a. A yayinda Tyndale ya ke kurkuku har na tsawon fiyeda shekara guda yana jiran hukumcin kisa, an sami labarin cewa sai da ya kammala fassarar Attaurat Turanci. Kalmomin sa na karshe kafin a kone shi a kafe ajikin ice a watan Oktoba na 1536 sune, "Ubangiji! Ka bude wa sarki idanu!"

Allah yayi haka din. Bayan shekara daya kacal da shahidancin Tyndale, masaraurtar Ingila ta bada izni a baga Littafi Mai Tsarki na farko da harshen Turanci. Bayan sheharu saba'in da biyar kuma aka buga Littafi Mai Tsarki (King James Authorised Version). Kashi tasa'in cikin dari na fassarar King James Version na yanzu aikin Tyndale ne kalma na bin kalma.

*Gama sabilida ka mai nasha. zargi kunya kuwa ta rufe fuskata. Zab. 69:7*

*Hamayya ba ta taba zama daidai darashin cin nasara ba. Wani lokaci ma akasin haka ne. Abokan mu masu yi mana kyawawan fata ma wani lokaci sukan yi hamayya da irin harka da muke game da yin hidimar bishara. Sukar ra'ayinmu na iya bamu mamaki harma mu fara yin shakkar abin da muka sa a gabai. Duk lokacin da Allah yayi man budi domin bishara, kamar yadda ya baiwa Tyndale, lallaine mu nuna aminci ga wannan aikin ko ta halin kaka. Bai kamata masu sukan ra'ayi su kashe mana jiki ba amma ya zama kalulale na karfafa manufarmu. Ko Allah yayi maka wani budi domin hidimar bangahar kiyar ka? Kamar dai Tyndale, maiyiwuwa ba zaka ga sakamakon aikin ka da wuri ba, in har zaka gani. Mai yiwuwa ma a yanzu ana tsauce maka. Har yanzu, ka dage ga yin aikin. Allah kuwa zaiyi maganin yan hamayya.*

# Kananan Yara Masu Matsanancin Karfin-Hali

## KOREA TA AREWA: CHENG LEE DA HONG JUN

**Rana ta 268**

**Kwaminisawa sukan gayawa kananan yara na Korea ta Arewa cewa idan har suka kuskura aka kama su a China zasu shiga mummunan hali. Amma yaran sun kuma san cewa idan har suka yi sa'ar tsere wa, su nemi gini mai alamar giciye a jiki domin samun taimako. Wadansu yaran Korea ta Arewa guda biyu wadanda suka yi kokari su ketaro zuwa majami'ar ne suka bada wannan labari ga pastor.**

*Sa'anda fa suka ga karfin zuciya na Bitrus da Yohanna, suka gane kuma mutane marasa-karatu ne talakawa, suka yi mamaki. Suka dauki zobe a kansu da suna tare da Yesu. Ay. Manz 4:13*

"Sunana Cheng Lee. Muna ji muna gani da ni da yaru wata iyayen mu suka mudu da yinwa. Kokari muka yi muka taka muka haye kogin Yalu a yayin da yake a daskare. Bayan da muka haye, sai yar tawa tace, 'Ka dakata anan, kamata yayi na kara yin gaba kadan ni ka dai.' Ba ta sake dawowa ba. "Cheng dan shekaru shida ne kacal.

Hong Jun yaro mai shekaru gomasha daya ya ce, "Ina so na koma Korea ta Arewa na basu labarin Kristi" sai ya fashe da kuka yana waka:

Ya Ubangiji, kabamu muryar yin bishara.
Gama Ubangiji yana kaunar yan'uwanmu masoya.
Ina dukan wadannan suka tafi? Ubangiji yana lura da su.
Ya Ubangji, ka aike mu garesu, ga yan'uwanmu yan Korea masoya.
Ya Ubangiji ka aika mu garesu, ga yan'uwanmu yan Korea mosoya.
A duk inda suke, bari suyi huda kamar furanni.

Bayan yan watanni, sai aka sace Hong Jun aka mayar da shi Korea ta Arewa. Watakila yanzu haka yana can yana yiwa wadanda suka kamashi bishara.

*Karfin-hali yana daya daga cikin abubuwanda mutum ba ya sanin yana dashi sai ta dauro. A daidai lokacin da ake bukatar haka din, anan ne za'a saru ko akwai ko babu. Haka ma ya shafi hali-wani irin hali da aka shiga zai nuna ko muna da shi ko babu. Sakamakon haka, hali da karfin hali abubuwa ne guda biya da zai yi wuya a kwaikwaya. Sa'ar mu ita ce Yesu Kristi ya bamu karfin hali na din-din-din da kuma kyawawan halaye na innanaha a duk lokacin da bukatar haka ta taso. Muna iya nuna jarumtaka amma Yesu kadai ke bamu karfafawar, muna iya zama sanannu ga jama'a, amma Yesu ne kadai zai bamu kyawawan halaye. A ina kake ganin karfafawa da kuma kyaun hali na rayuwarka a wajen aiki?*

# Karin Matsanacin Haske

## PAKISTAN: ZAHID

**Rana ta 269**

**Zahid malami ne na Islama, wanda yakan yi wa Kristoci kwanto ya kone masu Littafi Mai Tsarki. Wata rana sai yayi shawarar ajiye guda daya domin yayi nazari ya nuna cewa addinin Krista karya ne.**

"Na karanta Littafi Mai Tsarki, ina neman wurin da zan sami sabani game da addinin Krista. "Zahid yana bayani, "Nan take, wani babban haske ya bayyana a dakina, kuma sai naji wata murya na kiran sunana. Hasken ya haskaka dukan dakin.

"Za hid, me yasa kake yi mani tsanani? Muryar tace. Sai na tambaya, "Ko wanenene kai? "Nine Hanya, Nine Gaskiya, Nine Rai. 'Kwana uku a jere wannan murya da hasken na zuwa. A dare na hudu, na durkusa na karbi Yesu ya zama mai ceto na.

Daga tubar sa ga Kristi, sai aka sare Zahid a kurkuku wai ya ci amanar Islama, aka azabtaddashi a kurkuku har tsawon shekaru biyu, daga nan kuwa akayi masa hukumcin kisa.

A yayin da aka sa masa igiyar rataye shi a wuya, sai Zahid ya shaida wa masu kasheshi cewa Yesu shine Hanya,, shine Gaskiya, Shine Rai. Yay'sha'awar yayi amfani da kalmominsa na karshe domin yin bishara ga mutanensa.

Kwatsam sai ga masu gadi a guje suna cewa an dakatar da zartas da wannan hukumcin kisa, aka kuma saki Zahid. Babu wanda yasan dalili, amma a yau Zahid yananan yana cin gaba da tafiye tafiye na yin bishara a kasar Pankistan.

*Yesu Ya Amsa Ni Ne Hanya Nine Gaskiya Nine Rai, Ba Mai Zuwa Wurin Uba Sai Ta Wurina Yoh. 14:6*

*Mukanen da suka taba shiga wani hali na tsallake-rijiya - da baya akullum sukan fadi abu guda. Sukance Allah ya so su don kila akwai abin da yake so suyi masanan gaba shi yasa basu mutu ba. Ba kasafai zakaji a cewa an koma an dubi rayuwar wani wanda akayi hira dashin talbijin game da abinda ya faru dashi a gani ko haka dinne. Ko sun gano nufin Allah domin rayuwarsu ko babu? Gaskiyar ita a Allah yana da nufi domin rayuwar kowannen mu. Yaneso mu sanshi kuma mu sanar dashi ga wasu. Wadansu kamar Zahid suna iya bi ta wata hanya ta musamman domin isowa ga saninsa. Duk da haka mu sani manufarmu daya ce. Katabajin kamar akwai wani aiki na musamman domin ka? Dalilin shine domin ka sanshi kuma ka sanar da saninsa.*

# Matsanancin Iko

## ROME: VINCENT

**Rana ta 270**

**Igiyar da aka daure a hannayensa da kafafuwan sa sun mike ta wurin jansu da ake yi har sai da Christian Vincent na Roma ya ji kafafunsa na motsi kamar zasu fita daga gabar kafadar, haka kuma yake ji a kwatangwalonsa.**

Decius, maimulkin Rome ya tsaya a gefen rage inda aka daure Vincet. "Zaka mụtu a cikin mawuyacin hali mai zafi," ya fadi wa wannan saurayin Krista. "Ai babu mutuwa mafi daukaka irin ta shahidanci." Vincent ya shaida wa sarki da karfin zuciya." Ina hangan samaniya, kuma naki jinin gwmakanka."

Cikin bacin rai kuwa sarki yi yokina da a azabtarda wannan Krista kari bisa kari. Duk da haka suka kasa tsayar da murmucjida yakeyi. Cikin jin zaji kuwa ya gaya wa sarki, "Jiki nane kawai kake iya rugujewa, wacce dama can ai rubewa zatayi. Akwai wani Vincent dina can cikina, wanda ba ka da iko a kansa. Wancan Vincent din ba a iya daure chi kamar haka kuma ba a iya kashe shi Vincent ya marabci mutuwa da murmushi.

A karshe sokojin Rome suka janyo shi daga jikin ragar, ammafa azaba ba ta kare ba. Suka tuba masa tufafi suka jafa shi a cikin kurkuku, wanda aka farfasa gilasai aka zuba a ko ina a cikin dakin. Dayake bai iya tashi tsaye ba, sai ya kwanta aka farassun gilasai. Aarga irin wannan matsayin Allah yana tare da shi. Daga baya masu tsaro suka gaya wa sarki wai Vincent yana kwance akan gilas kamar yana kan gadon da aka shinfida da furanni".

*Karfafaffu bisa ga dukan iko, bisa ga ikon daukakar sa, zuwa ga dukan hakuri da jinrewa tare da farinciki. Kol. 1:11*

*A zamani irin na yanzu, batun mulki ya twallaka ne ga iko da mu kami. Mulki ya zama na muhimman mutane masu ilmi kuma tatattu. Amma, tarihi iya kaye mane cewa mutane dayawa da ke cikin manyan mukamai ba su iya kamanta daidai idan basu da kwazo a lamirin su . Akasin haka Allah yakan baraci karfin mu na can ciki ta wurin kasancewaqr Ruhu Mai Tsarki. Shan wahala ajinsa ne inda yaka kaya mana yadda zamu zama da karfi. Sai mu iya jure wa abufiya fiyeda kịma. Mai yiwuwa kaji kamar wahalar ka ta gajiyar da kai. Ka tambayi Allah ya nuna maka yadda rasu karfafaka. Ka zage damtsenka, zaka ga cewa karfin ba yafi yadda kaka zato.*

## MASARAUTAR ROME: MUTANE ARBA'IN MASU IMANI

**Rana ta 271**

**Sarki Constantine ya kafa dokar amince wa da addinin Krista a kasar Rome a shekara ta 320. Amma, Licinius, wanda yake mulkin gabashin kasar, ya yanke hulda da Yamma kuma yaci gaba da tozartadda Krista.**

A lokacin da Licinius ya kafa doka cewa dukan sojojin da ke karkashin ikonsa suyi hadaya ga allolin Rome. Kristocin nan guda arba'in na bataliyar da ake kira "Thundering Legion suka ki sai. Hafsan Nafsoshi mai suna Lysiasyasa aka yi musu bulala, aka yayyaga su da kugiya, sa'annan aka sasu a kurkuku daure da sarka. A lokacin da suka ki su rusuna su kuma daina yiwa Allah sujada, sai yasa aka tube su aka dora su akan daskararren kogi wai har sai sun janye.

Akan ba wanda ya janye dama yayi wanka da ruwan dumi. Mutanen sukayi ta addu'a domin kada wani ya ba da kai. Amma ashsha, duhu na karatowa sai wani ya tashi ya gudu wajen yin wanka da ruwan dumi.

*Kwjimre ina wahala tare da mu kamar soja mai inganci na Kristi Yesu. 2 Tim. 2:3*

Daya daga cikin masu tsaro wanda yake kallon su suna wakoki ya ji haushi domin daya ya ba da kai ga Lysias. Haushin sa ya zama juyi zuwa bangaskiya.

Sai ya yaga tufafinsa, ya zo ya shiga cikinsu, wannan ya cika alkawarinsu na zama amintattu arba'in sojojin Kristi masu kurfin zuciya/ "Arba'in din nan suka mutu tare a ranan nan, shima wanda ya gaza yaje wanka da ruwan zafi ya mutu.

*Mabiya dabam dabm masu bada kai sosai ga Kristi sune sukan hadu su zama wata al'umma ta Krista. Ko da taron Kristane na dalibci, ko taron Krista na hidimar bishara, ko majami'a ko iyali hannan yan'uwan taka wani karfi ne wanda ya kamata ayi la'akka yi da shi. A kullum mukan fi karfi idan muka tsaya tare. A cikin dukan gargadin da Allah ya ke yi mana a littafi yana cewa mu tsaya tare a zaman iyalin bangaskiya. Fiye da jadawalin karfi ga mai yawa, ita kunguyar jama'a ta Krista takan karfafa mambobi. Kamar wannan labari, mai karfi yakan agazawa mara karfi. Ko ka gane da kungïyar ka ta yan'uwa Krista? Kana tabbatarda goyon bayanka garsesu ko ta halin kaka?*

# Matsanancin Kyau

## LENINGRAD: AIDA SKRIPNIKOVA

**Rana ta 272**

**"A kurkuku, al'amari mafi wuya shine rayuwa ba tare da Littafi Mai Tsarki ba."**

Aida Skripnikova wata kyakkyawar budurwa ce. A lokacin da take da shekaru ashirin da yankai na haifuwa takan tsaya a gefen titi a Leningrad takan rabar da kasidu na shaidar kaunarta ga Yesu Mai Ceto. Jim kadan kuwa aka kama ta, amma ta nuna cewa ita fa tsayayya ce ga bangarkiyar ta, ko da shike anyi mata hurkukucin dauri na shekara daya a kurkuku.

A lokacin da Aida ta cika shekaru ashirin da bakwai na haifuwa ta fuskaci daurin ta a kurkuku na hudu domin kokarinta na kare bishara. Taci gaba da zama mai fadi a fili, tana cewa" Ba zamu yi shiru game da batun da ya zama cikakken ma'ana na rayuwar mu ba Kristi kenan, a cikin wata takarda da ta rubuta."

Zaman kurkukun ta na hudu ya zama mafi wahala a gareta.

Sukan ja hankalinta domin ta saki bangaskiyata ta wurin zage zage ko kuma suyi alkawari zasu ba ta cakuleti. Amma, abu mafi wuya a gareta shine zama babu maganar Allah. An kwace mata na ta. Daga baya sai ta sami Linjila ta ko rike Littafin tamfar abinda ya fi rai daraja.

Bayan da aka sake ta ba a ko iya gane ta-wannan kyaun nata ya bace, ta zama kamar tsohuwa. Amma kaunar Allah ya haskaka ta wurin murmushirta kaunar Allah ya maye kyaunta na ciki.

*Kada adonku ya zama ado na waje, amma ya zama boyayye na zuciya cikin tufafi da basu lalucewa na ruhu mai ladabi abin da ke da tamani a gaban Allah.*
*I Bitrus 3:3-4*

*A cikin kantunan saida kayan abinci na gwangwan da sauransu man shafawa na adon mata ya fi yawa, zaka ga talla iri iri shafa zaka kara kyan a jiki. Idan da muna fin damuwa da kyaun da ke cikin cikinmu maimakon na waje. Shahidai suna koya mana cewa mufi darajanta sabuntar ainihin ko mu su wanene dagacan cikin ciki. Ni na can ciki. Shi ne mutumin da babu wata azaba da zata karyshi. Wannan shine wanda yake kokarta kamanta Kristi. Kana iya son ka burge mutane bisa ga bin duniya. Amma. Allah yana nuna cewa kai na can ciki mafi jan hankali na. Ta wace hanya kake girma ta can ciki kana kara kyau a yayin da shekarunka suke karuwa?*

*Na Roki A Karfafa Ni*
*Allah Ya Bani Al'amura Masu Wuya*
*Wadanda Za Su Sa Nayi Karfi.*

*Na Roki Hikima-*
*Sai Allah Ya Bani Al'amura Masu Wuya*
*Domin Na Warware*

*Na Roki Wadata-*
*Sai Allah Ya Bani Kwakwalwa*
*Da Kaifin Tunani Na yin Aiki*

*Na Nemi Karfin Zuciya-*
*Sai Allah ya Bani Abin Kawo Hadari*
*Domin Na Kayad Da su.*

*Na Roki Kauna-*
*Sai Allah ya Bani Zarafi*

*Ban Karbi Ko Daya Daga Cikin Abubuwan*
*da nake so ba-*
*amma na karbi kome da kome da nake bukata.*
*An amsa addu'a ta.*

***Daga iyalin Michael Job, dalibin koyon aikin likita***
***a India wanda aka Kashe a Yuni 1999domin***
***ubansa na yin bishara***

# Matsanancin Koyaswa (Na Daya)

## INGILA: DR. ROWLAND TAYLOR

**Rana ta 274**

**Mutanen garin Hadley sunroki Dr. Rowland Taylor kada ya tafi ganin bishop na Winchester da Lord Chancellor. Sun sani cewa shi bishop yana jin haushin irin koyarwar Dr. Taylor.**

An yi wajen shekaru ashirin kenan ana rabar da Littafi Mai Tsarki na turanci da cikakken iznin hukuma ta Ingila. Koyarwa kawai da Dr. Taylor yayi shine ya shaida wa wadanda suke majami'arsa cewa su ci gaba dakaranta Littafi Mai Tsarki kuma subi koyaswar sa. Akasin haka, shugabannin addini a karkashin mugun mulki na sarauniya Mary I suka yi kira ga lallai a dage ga bin al'adu na majami'a.

Bayan yasha zagi a hannun Bishop da dora ma sa laifi, Rowland ya amsa, "Ni Krista ne. Ban yi wani sabo game da majami'a ba. Alhali ma dai; ta wurin wannan caji da kake yi aikai ne mai bidi'a. Kristi ya mutu sau daya domin zunuban dukan mutane. Wannan ya isa. Da ku da al'adunku ba zaku iya kara tsinana komai ba."

*Yesu yace dukan wanda yana kaun ta zai kiyaye ko yaswa ta. Yoh. 14:23*

Dr. Taylor yayi shekara biyu a kurkuku. A lokacin da ya sami labarin za'a daure shi a jikince a kone shi a wajen garin Hadley, sai yayi ta tsalle don farinciki. Bai damu da a binda zai faru dashi ba. Maimakon haka, tunanin zai sake wuce wa ta cikin garin Hadley ya ga yan'uwansa maza da mata cikin bangaskiya shi ya bashi farinciki.

An shahidantadda Dr. Rowland a lokacin hunturu na 1555.

*Akanyi maganar kauna ta harsuna dabam dabam. Mutane sukan so suji suanan kauna a cikin harshensu domin su fahimce ta. Wasu maza sukan baiwa matansu abincin safe tun suna kan gado domin su nuna kaunarsu. Wasu kuma sunli son wata yar kyauta na kauna. Yesu ya ce harshen kauna tasa ita ce biyayya. Ta haka zamu nuna kaunarmu zuwa gareshi. Idan muka yi masa biyayya'mun nuna kauna kenan. An kashe Taylor domin ya koya wa mabiya subi umarnin Kaunar Yesu. Ya koya musu su karanta Littafi suyi biyayya da koyarwar sa. Ka nuna wa Yesu kana kaunarsa Kuma a tuna da Dr. Taylor yau.*

# Matsanancin Koyaswa (Na Biyu)

INGILA: DR. ROWLAND TAYLOR

**Rana ta 275**

**Kafin a kone shi a daure a jikin itace da aka kafa domin laifin koyar da Littafi Mai Tsarki Dr. Rowland Taylor ya rubuta wadannan kalmomi masu ban sha'awa.**

*Ka kiyaye dokoki na ka rayu: koyas wa ta kuma kamar kwaryar ido. Mis. 7:2*

Na shaida wa matata da ya'yana, Ubangiji ne ya bani ku. Kuma Ubangiji ya dauke ni daga gareku: Albarka ya tabbata ga sunan Ubangiji! Ina farinci ki cewa Ubangiji mafi aminci ne kuma mafi tagomashi gaba da kowane miji ko uba. Mu gaskanta da shi ta wurin cancantar makaunaci Mai Cetonmu: Ku gaskanta dashi, ku kaunaceshi, kuma kuyi masa biyayya. Kuyi addu'a zuwa gareshi, gama yayi alkawarin taimakawa. Kada kuyi lissafina a zaman matace, gama zan rayu har abada kuma ba zan taba mutuwa ba. Nayi gaba, kuma zaku taho daga baya, zuwa gidanmu na din - din - din.

"Ina shaida maku abokaina masoya na garin Hadley, da kuma dukan wadanda suka taba sauraren wa'azi na, Ina rabuwa da ku nan tare da kyakkyawan lamiri game da koyaswa ta, wanda addu'a ta ita ce kuna yi wa Allah godiya tare dani. Gama ta wuring amfani da yar baiwa da Allah yayi mani ne na iya shaida wa wasu abubuwanda na samu a cikin Littafin Allah, watau Littafi Mai Tsarki mai albarka. Saboda haka, idan ni, ko wani mala'ika daga sama yayi maku wata bishara dabam da wacce kuka tare de ita, to bari Lalanar Allah ta sauka bisa kan wannan mai bisharar!

"Ina rabuwa da nan tare da tabbataccen bege,kuma ba tare da shakkar samun ceto na harabada ba, Na godewa Allah Uba na sama, ta wurin Yesu Kristi tabbataccen Mai Ceto."

Rowland Taylor

*Kana iya tunawa da malamar ka da kafi tunawa dashi a lokacin da kake kankani ? Watakila irin kamshi turaren da take shafawa. Watakila ma yadda ya ke shafa saikon sa. Wani amma fa, bayan mum yi wayo mukan dubi darajar malamanmu ta wasu dalilai dabam. "Mukan tuna abin da suka koya mana-bama mantawa. Kullum mukam tuna wadanda suka fara koya mana maganar Allah. Ba zamu iya mance al'amuran gaskiya da aka koya mana ba game da kaunar Allah da cetonsa. Idan wani yazo da sunan wayar da kai ko iya boko, gaskiyar Allah zata kare ka ta taimaka maka kare rashin gaskiya. Sunfi gaban abin da za'a tuna. Sune mallakarka mafiya daraja.*

# Matsanancin Iyali

## CAMBODIA: DA HAIM DA IYALINSA

**Rana ta 276**

**A cikin kurmin jeji na Cambodia, aka baiwa Haim da iyalinsa cebura, aka gaya musu su haka kaburburansu. Kungiyar Khmer Rouge ce ta kama su domin su a garesu Krista abokan gaba ne na juyin -juya - hali da suke yi.**

Sojojin suka baiwa Haim da iyalinsa dama suka durkusa, suka rike hannuwansu, suka yi addu'a. Sa'annan Haim ya iza wa sojojin nan yace su tuba su karbi Yesu Kristi ya zama Ubangijinsu da Mai ce tonsu. Sojojin su ka yi mamaki domin sunji muryarsa kamar ma shine ke jin tausayinsu maimakon shi da yake fuskantar kisa.

Yana magana kenan, sai daya daga cikin ya'yansa ya gudu ya shiga cikin itatuwa, sojoji kuwa suka bishi, amma sai Haim ya dakatar da su. Irin kwanciyar hankali da ya nuna ya rinjayi kwaminisawan su jira su ga abin da zaiyi.

A lokacin da iyalin suke durkushe da sojiji suna nunin bindiga a kansu. Sai Haim ya taka zuwa gefen kurmin. Yace "Dana, waishin satar karin yan kwanaki na rayuwa a zaman maguji a cikin wannan dokan kurmi zai kwatantu da hada kanka tare da iyali anan kewaye da kabari, amma ba da jimawa ba zamu yantu kuma mu wanzuce aljanna tare da Kristi? "Bayan wani dan lokaci, sai akaj karar takawa a ciyayi a yayin da dan Haim ya fito yana hawaye sai ya durkusa tare da Ubansa.

*Dukan wanda ya aikata nufin Allah shine dan'uwana da yar uwata da kuma uwa. Markus 3:35*

Haim ya dubi sojojin, "Yanzu kam mun shirya tafiya." Amma babu wani soja da ya iya jan kunamar bindigarsa, jim kadan sai wani hafsa ya iso wanda baiga dawowar yaron ba, ya zazzagi sojojin wai masu matattun zuciya ne, sai ya kashe Kristocin.

*An san wasu iyuli da zaman kwaici ainun. Wasu sukan yi alfaharin su masu dukiya ne. Wasu kuwa su kan nuna ingancin aikinsu. Koda shike Allah yana iya amfani da wasu abubuwa, ra'ayinsa na sani dabam yake ainun. Me yake sa iyali su zama masu amfani a mulkin Allah? Matsananciyar biyayya. Ba wai ana lissafi ne da girman motar iyali ba, amma ba da kai ga Kristi da suke yi. Allah ya shirya iyali a zaman wuri ne inda iyaye zasu yi jagoranci ta wurin nuna misalai domin yara su koya kuma suyi biyayya da Kristi. A yayinda misali na Haim yana da muhimmanci, muna iya zama masu biyayya a namu matsayin. Kaka zaka nuna naka iyalin? Iyalin wanene suka zama misali na matsanancin iyali?*

# Matsanancin Yin Amfani Da Karya

RUSSIA: WANI DALINBIN JAMI'A

**Rana ta 277**

**Yana kallon hoton lenin da aka rataya a jikin bango kusa da kofa sai wannan parfeso mara sanin Allah ya yi murmushi ya gusa gaba inda aka dora wata yar buta akan tebur cike da ruwa. Ya fito da wani dan kunshi na foda, kuma a yayin da ya bude kunshin sai ya fara zuba fodar cikin wannan ruwan, a hankali kuwa sai ruwan ya zama jawur.**

"Shikenan wannan shine al'ajibing da haka ya fara koyaswar sa. "Yesu ya boye foda a hannun rigarsa kamar irin wannan amma yake da'awar cewa yayi wata mu'ujiza ta juya ruwa zuwa ruwan-inabi ta hanyar ban mamaki. Amma ni ina iya yin haka fiye da Yesu; har ma ina iya sake ruwan-inabin ya saka zama ruwa sak.

Sai ya sake fito de wani kunshin fodar ya zuba a cikin wannan jan ruwan; sai ruwan ya haskaka babu ja kuma. Da sake zuba wata fodar kuma sai ruwan ya sake zama jawur. Daya daga cikin daliban sa da ke zaune akan kujeransa na aiji, ya kada kai domin rashin burgewar wannan batu na malaminsa. A karshe dai, sai ya kalubalanci parfeso: "Amma da karin tambaya daya kawai zuwa gareka - ka sha ruwan - inabin naka da kayi!" Sai parfeso ya yi yar dariya irin dariyannan da ake yi ba tare da bude baki sosai ba yace, "Ai wannan ne ba zan iya yi ba." Wannan fodar dafi ce."

*Suka musanya gaskiya Allah da karya. Rom. 1:25*

Shi wannan Krista sai ya amsa masa ya ce, "Wannan shine bambamci tsakanin ka da Yesu. Shi da mu'ujizar sa na ruwan-inabi, ya bamu farinciki, kai kuwa dafi kake bamu da naka ruwan-inabin". Wannan parfeso kuwa sai ya fusata ya fice daga cikin aji yasa aka kama dalibin nasa aka kaishi cikin kurkuku. Amma wannan labari ya bazu ko'ina kuma ya karfafa bangaskiyar mutane da yawa.

*Alkawarin abokin gaba na samun sauyi cikin sauki karya ne. Yawancin manya manyan kantuna sukan kirkiro hanyoyin fahintar da jama'a tsare tsaren su da zasu baiwa abokan cinikin su dama wajen musayarda wasu abubuwanda suka saya da zummar kyautata masu su gamsu. Mutane sukan shiga layi domin shiga suyi musayar tufa mai karamar lamba zuwa tufa mai babber lamba, ko kuma wani launin zuwa wani da zummar cewa wannan zai fi dacewa da su, ko kuma ya faranta masu rai. Kazalika, mutane da yawa suna tsaye a layi, tare da wai su musayarda gaskiyar Allah a hannu. Ana gaya musu abubuwa, kuma wannan zai gamsar da su. Duk lokacin da mukayi haka kuwa mukan kare da da-na-sani a karshe. Allah ya na bukatarka da kayi amfani da idanunka ka ratsa karyar abokin gaba. Ka tsaya tutturakan gaskiya ta Allah ko ta halin kaka.*

# Roko Matsananci

## INDONESIA: DELORES

Rana ta 278

**Wannan tsohuwa mai suna Delores ta gaji da gudu domin tsira daga magabta, sai ta fashe da kuka, ta ce "Ya Allah idan ka yarda, ka yi mana jinkai, mu ya'yanka!" Delores tana gudu ne domin tsirar da ranta, tare da wasu masu bangaskiya, a yayin da mahara suke jefawa kauyen su igwa. Ta wurin yin amfani da itace da ta rike a zaman matokara don ta dingisa taku taku sannu a hamkali ta hau dutse mai tudu ainun har sai da ta haura zuwa daya bangaren domin samun wuri a wani sansanin yan gudun hijira tare da daruruwan Krista da wannan hari ya kore su daga gidajen su.**

*Suka ta da murya da karfi suka ce, har yaushe zaka yi jinkiri da sharisa bira masam nan duniya da daukar funsar Jininmu? Ruya to Yoh. 6:10*

Delores tana daya daga cikin milyoyin Krista da suke zaune a kasar Indonesia - kasa wadda take da tsibirai fiye da dubu gomasha uku. Kuma Indonesia ita ce kasar da tafi ko wace kasa yawan musulmi a duniya. Duk da haka musulmi da Krista sun yi wanzuwa ta zaman lafiya shekara da shekaru, suna zaman tare na salama daga zamani zuwa zamani. Amma yanzu, sun fuskanci wani sabon magabci kungiyoyin yan gani kasheni na islama sun fito yanzu suna haddasa jihadi a wurare da yawa na wadannan tsibirai. A yau babu sauran zaman lafiyatsakanin Musulmi da Krista.

A wani binin su, Krista sun taru suna waka suna cewa "Na sallama Duka" a bakin ofishin gwamnan, a lokacin da suka yi zanga zanga ta lumana domin nuna salama irin ta Kristi. Suka yi ta rokon gwamnati da su yarda da cewar yan banga na islama sun kashe Krista da yawa. Kai har a lokacin da ake cikin wannan zangata lumana suna waka, yan bangan Islama sun kaiwa wani kauyen hari sunyi kaca-kaca da kauyen. Jama'a da yawa da suka saba zama na cigaba da arziki, a yanzu wuraren nasu sun zama tarin toka da buraguzai.

*Delores daya ce kawai daga cikin mutane masu bi da yawa da ake tsanantawa a kasar Indonesia wadanda a kullum suna kuka ga Allah domin kubuta daga tsanani. Littafin Ruya ta Yohanna ya yi magana game da dinbin shahidai wadanda suke begen zuwan shariar Allah da adalcinsa kuma. Amma fa bai kamata su yi wannan kuka su kadai ba. Muma da muke raye lallai ne mu tada muryoyin mu tare dasu game da rokonsu. Ko da shike muna iya zama nesa kwarai a wani bangare na duniya a cikin gidajenmu, amma nisar tsakaninmu babu yawa idan muka yi la'akkari da cewar addu'a tana kawo mu kusa da juna. A yayin da muka yi addu'a ta samun zaman lafiya da neman kubuta, sai mu kawo tunanin mu ga wadanda suke cikin wahala. Ko zakayi addu'a yau domin Delores da sauran masu bi na Indonesia? Zaka roki Allah da ya kare su a cikin tafiyarsu ta rayuwa, kuma ya ji addu'oin mu na neman kubuta?*

## Korea ta Arewa: Pastor Im

**RANA TA 279**

***Amma ai ni ba dan Kwaminis bane. Lalle ne ku gaskantarda haka. In ji Pasto Im a lokacin da Majilasar dinkin duniya ta sake karbe wannan yanki da aka mamaye a watan S atumba na 1950. Sojojin kwaminis na Korea ta Arewa sun bar Pasto Im a kulle cikin wani dakin kurkuku na daga-kai-sai na tsawon shekaru biyu domin ya wasu bisharar Kristi da kuma ki da yayi na canja salon wa'azinsa domin yau lafazin da zai yada gurguzanci.***

*Babba ne cikin shawara, mai iko ne cikin aiki abude suke cikin dukan al'amura.*
*Irmiya 32:19*

A lokacin da sojojin Majalisar Dinkin Duniya suka isa, yaji a ransa cewar zai sake samun yancinsa. Duk da haka sun dauka cewar shi dan Kwaminis ne, sai aka sake jefa shi cikin wani dakin kurkuku tare da yan kwaminis da aka kama. Da yake mutum ne mai tawakkali sai ya bar al'amuransa a hannun Allah. Pasto Im ya kanyi wa fursuna wa'azi. Dayawa sun karbi Kristi. Mun sha labarin wannan mai wa'azi na sansanin fursuna. "Inji wani mishan ba. Amirke yana gayawa abokinsa da ke shirin tafiya Korea a zaman shugab.. maikula da majami'a. "Tunda yasan fursunonin sosai. Gani nake ko zai taimaka mana wajen shirya yin bishara a can? Ya tambayi abokinsa da zai tafi Korea. Amirkawan mis ran dinnan suka nemi izinin kaiwa ga Pasto Im. Kuma mai wa'azin kurkukun nan ya amince kuma ya taimaka ya yi ta wa'azi a sansanonin kurkuku na cikin dukan Korea ta Arewa. Dubban kwaminisawa suka karbi Kristi. A cikin shekara guda kuwa aka sami fursuna dubu goma sha biyu da suke tashi duk safiya domin yin addu'ar asuba. Pasto Im bai kuma sake ganin iyalin sa ba amma dubbai sun zama yan uwansa a cikin Kristi a sa. isanonin fursuna.

***Menene ainihin nufin haka? Wannan ita ce tambayar da ke zuciyar kowa a yayin da muka ga ana wahalar da mutane ta rashin adalci da rashin imani. Amma duk da haka a kullum ba ma iya sanin manufar Allah. Abin da kawai zamu iya sani shine ma nufin Allah agaremu muhimmin abu ne kuma a karshe shine abu mafi kyau a garemu. Mu kamar hambaman daurin gwamai ne da aka watsa akan tabarma. Muna bude idanunmu muyi lura da nambaman da ke kewaye damu basu dace da tuninsu ba. Kukan zama da damuwa harma da tsoracewa. Amma shine masanin hadin daurin gwarmi shi ka dai ne mai iya ganin koina yana iya ganin dukan hambaman da ke cikin rayuwarka nan take. Shine mafi sanin mahadar su domin sufi dacewa da nufinsa. Zaka dubi allah da aminci da gamsuwa ko da a ina ya aijiyeka?***

## LABARIN KIRSIMETI MATSANANCI

# *Romania: Aristar*

**RANA TA 280**

***Yau a cikin birnin Dauda an haifa mana Mai Ceto a gareka kuma shine Kristi. Luka 2:11***

***"Ko ka taba sun-suna ingirici?"***

Aristar saurayi, manomi ya fara bada labarin sa "abin kamar wani ya janyea ainihin bazara ya kudunduneta don kada ta rabu da yanayinta. Sai kace da Maryamu da Yusufu sun sunsuna dadin ta a lokacinda suka sauka a turken dabbobi bayan doguwar tafiya. Sauran fursunoni suna saurare da doki a yayinda Aristar yake magana akan zafin kukan jariri Yesu a lokacin haifuwa a turken dabbobi, ko awakin da ke wurin zasu ji kukan Mai Ceto nan da nan bayan haifuwarsa. Su masu kunnuwan ji ne kwarai. Kamar yadda muna ya kamata mu zama masu saurare sosai a yayin da Yesu ya yi magana.

Anyi ruwan dusar kankara ainun a garin Tirgul-Ocna ta Kasar Romania inda har zurfin dusar hankara da ta zuba yakai kafa shida a daren Kirsimeti mai tsananin sanyi. Fursunonin basu da isassun tufafi. Abinci ma kalilan ne barguna kuwa dakyar a ce kowa na da guda daya mai kyau. Dukan kowa na jin kewar iyalinsa saboda haka suka maida hankalinsu garin saura ran labarin Arista na haifuwar Kristi domin sanyaya musu zuciya.

Ya cigaba babu mamaki a ce hasken tauraron da wata a wannan lokaci wanda ya haskaka ta kofar garke kuma ya sa zakara ga yin cara yana shelar haifuwar Kristi. Fursunonin suna saurare duka. Bayan jin labarin sai wani ya fara raira waka, a hankali kuw a suna karuwa har muryoyin da suka daga ya fara fita ana ji kowa ya tsaya yana saurare, kurkuku mara dadin zama labarin haifuwar Kristi yana dumama zukatan mutane da yawa. Domin Kristi shine tushe babu wanda zai iya kulle ruhaniyar Krista.

***Tabbas. Kirsimeti buki na na shekara. Kirsimeti ya wuce haka. Ko da shike hakan yana faruwa a zukatan dukan mutane wadanda sukan tsaya domin yin bukin shigowar Kristi a duniya mai al'ajibi ba wai lalle sai ranar Kirsimeti ba. Bukin tunawa da ranar haifuwar Kristi yana haskaka al'amura kuma yana yi mana tuni game da begen da muke dashi a cikin Kristi. Ba sai lalle mun ga dusar kankara a kasa ko fitilu masu haske ko itatuwan nan da aka yiwa ado na bukin Kirsimeti ba. Ko da a cikin wane hali kake ka sani cewa an haifi Kristine ta Kanas domin ya taimake ka a cikin dukan bukatunka. Jinkan sa na nan dukan shekara. Yaushe ne ka taba yin begen Kristi na cike a ranka? Dauki lokaci yau kayi bukin haifuwar Kristi zuwa ga duniyar ka kum zuwa ga zuciyar ka.***

# Tural: Wata Krista Fursuna

**RANA TA 281**

***An kawo fursunan a gaban mukaddashiyar kwamanda, wata mara tausayi mai murtuka fuska kuma maki magana akan Allah. Nazo ne domin na gaya miki lalle ne ki daina. Fuskart na dauke da fusata irin na kwaminis a kurkukun kasashen gabashin turai.***

*Ku tuba ga zancen irin zamani na da tsofon mutum wanda yana kara lala cewa bisa ga sabonta yaudara ku ta jikinku.*
*Afisawa 4:22-23*

Fursunan ta tsaya shiru amma da tsayayyen zuciya. Sai ta shaida wa kwamanda cewa ba bu abinda zai hana ta yin magana game da Mai Centonta. Ita mukaddashiyar kwamanda ta daga dunkulen hannunta don ta naushi fursunar amma nan da nan ta tsaya. Me kike wa murmushi? Ta tuhume ta, ina murmushi domin abin da nake gani a cikin idanunki. Me kika gani? Ni kaina a da mai zuciya ce kwarai na kanyi fushi har na kai ga bugu har sai da na sami koyon sanin abinda ake nufi da kauna. Tun daga nan kuwa bana dunkula hannaye domin kai bugu sam sam.

Ta cigaba, idan kika dubi cikin idanuna, zaki ga kanki kamar yadda Allah ya halicce ki, kamar yadda ya yi da ni. Fursunan ta tuna rayuwarta na baya na yadda take kare kanta, ta wajen rama zagi da zagi, amma sabili da sabuwar rayuwarta a cikin Kristi, alheri kadai take nunawa wanda yayi mata mugunta. Wannan kwamanda kuwa sai ba sauke hannayen ta. Ta nuna alamar mamaki kwarai sai ta fadi a hankali. Tafita daga nan, wannan fursuna ta cigaba da shaidar Kristi a ko'ina cikin kurkuku, batare da tsangwama daga mukaddashiyar kwamanda ba.

***Kokarin da kwamanda tayi na hucewa akan wannan fursuna ya zama kamar musu da mutum da ke matacce ne, abinda takeyi ya zama kamar tana taka mar gawa ce, a karshe ita kwamanda ta gane kuma ta fahimci cewar ko wacece wannan fursuna. Sabuwar halitta a cikin Kristi. Tsohon mutumtaka wanda ke maida murtani na kiyayya a da ya tafi. A madadinsa wannan fursuna ta bada damar kwamanda taga salama da jinkai irin na kamanta kristi kadai. Haka kuma lallene mu dubi kanmu a cikin sabon haske. Mun rigaya mun mutu ga tsohon rayuwar mu. A lokacin da aka tsokane ka aka cakune ka a lokacin da magabta suke fusatar da kai domin ka aikata wasu halaye da basu kamata ba, ka dauki darasi daga labarin wannan fursuna. Ka nuna kai mataccene ga halayen da na duhu.***

## MATSANANCIN KETAREN KOGI

# Thiland: Dan'uwa Ho

**RANA TA 282**

***Dan'uwa Ho bashi da lafiya, yana fama da zazzabi a lokacin da shi da abokinsa suka hau kan ruwan kan-kara na kogin Mekong. Su daliban Taunidi ne a Laos kafin sojojin kwaminis su mamaye makarantar.***

*Ka tuna da kamnar dokokin da nikeyi ka rayar dani bisa ga rahamar ka ya Ubangiji.*
*Zab. 119:159*

Da kyar suka tsira da rayukansu, akan hanyar su ta zuwa Thailand. Basu iya yin sallama da iyalansu ba, wadanda ba Krista ba ne, domin suna iya kama su su baiwa hukumar yan sanda. Sabo da haka sai sukayi addu'a ba tare da daga murya ba kuwa suka kama hanyar tafiya cikin sanyi da tabo dauke da hajjar su mai daraja a rataye ta baya a kafa dunsu watau Litattafai Masu Tsarki kanannade a cikin roba. Sauran kayan su da suka mallaka kuwa sun bari'a baya Ho yayi tunani a ransa. Ubangiji akalla idan ma har mun mutu zasu sani cewa mu Krista ne. Kuma da fatar in ma haka tafaru muna sa rai zasu karanta daya daga cikin wadannan Litattafai Masu Tsarki. Da suka kusan kai rabin ketaren kogin, abokin Ho ya ga bashi da ta yi ilia ya gusa da jakar litattafan zuwa kirjinsa domin ya yi iyo akai. A lokacin yin haka kuwa sai masu tsaro suka ji karar fantsamar ruwa da yayi ya jawo hankalinsu su da ke kan hasumiyar hange sai suka haskaka babbar fitilarsu a kogin fitilar ta haskaka daya jakar sai mai tsaron ya dauka kifi ne kawai yayi tsalle ya fantsama ruwa. Dauke filitar ya rage musu taraddadi. Ho da abokinsa suka fito daga kogin a gafen Thailand. Sun gode wa Allah da ya basu nasarar a kan litattafan su Masu Tsarki dake dauke da kalmomin samun rai na har abada, gashi kuma ya ceci rayukansu a daren jiya. Bayan sun kai ga isa lafiya sai suka bada kansu ga yin bishara a cikin sansanonin ya gudun hijira masu yawa a Thailand.

***Masu bishara na wannan labari suna dogara ga abubuwanda sukafi takarda da roba. Sun dogara ga Allah, kuma ketare kogi da sukayi da tsakar dare yana bamu kyakkayawar misali na matsayi da Littafi Mai Tsarki ke da shi a rayuwar mu ta dogara a kai. Dasu yadda zakayi mu sami kanmu a matsayin da wannan gaskiyar zata zama rubutacciyar gaskiya kuma aikatacciya. Dole ne mu mannewa alkawuran Littafi Mai Tsarki na kiyaye rayuwarmu. A lokacin da muke cikin damuwa ba zamu iya yin iyo mai nisa ba a karan kanmu da zai iya fitar da mu daga damuwar. Dole ne muyi iyo akan maganar Allah ko kuma mu nutse gaba daya.***

MATSANANCIYAR JARABA

## *Sabina Wurmbrand*

**RANA TA 283**

***A kullum tana biya*** 
***.aro tane na aminci*** 
***tana hakuri.*** 
***Kuma bata taba tabewa*** 
***ba.*** 
***I Kor. 13:708***

***A cikin dukan shekarunsu na aure, Sabina Wurmbrand bata taba nuna shakka game da kaunar da take yi wa mijinta ba. Amma kuma anyi shekaru da dama ba ta sami labarinsa ba domin yana kurkuku. Akwai ma jita jitar cewa ya mutu. Amma taji a jikinta Allah yana cewa ta dakata kuma ta gaskanta zasu sake saduwa wata rana.***

Sabina tana cikin karfin ta, ga kuma karamin yaron ta da ke bukatar kula, galibi takan sami jarabtar rashin kauna da rashin abokin zama. Sabo da haka a lokacin da wani kyakkawan Krista mai suna Paul ya fara zuwa yana taimakon danta wajen koya masa darusa, sai ta fara jin sha'awa. Wani lokaci sai ya rike hannunta suna tafiya tare ko kuma ya dubi idanunta da nuna sha'awa, to dole ne ta guje wa duk wani fasikanci domin alkawarin Allah zuwa gare ta, sai ta gaya wa Paul ya daina zuwa sam sam. Ya fahimta kuma ya tafi a cikin mutunci.

Bayan gajeren lokaci, Allah ya ba ta ladar bangaskiyar ta. Wata safiya a yayinda take aiki a cikin majami'a sai aka kawo mata wasikar gaisuwa ta hannun wani wai shi Vasile Georgescu. Amma ta shaida rubutun na mijinta ne babu tantama. Idanun ta cike da hawaye ta karanta lokacin da tazara suna kashe kaunar da ba ta da zurfine amma suna sa kauna mai zurfi ta zurfafa.

***Labarun majami'u da suka shiga tsanani labaru ne na mutane masu lamiri kamar kowa. Hotunan da ke cikin wadannan labaru ba takardar yar tsana bace. Muryar Sahahidai murya ce da baza a iya kuskure ta ga sanin cewa murya ce ta gaske kuma tá zahiri ba. Sabina ta yi kurde kurde cikin gwaji, I amma ita ma tana cikin gwajin bangaskiyar ta kuma tsanani yana fuskantar mu a matsayi danbam dabam kamar iyalin Wurmbrand karfin kaunarka ta karu tawurin shan tsanani in har zaka bari ta cika manufarta ta ainihi.***

***Idan kana da idanun hange babu abin da zai baka tsoro.***

***Tareda hangen sa kuwa Allah yakan ba da iko.***

***Lalle ne mu zama marasa tsoro.***

***Daga:***

***Pasto Dan Iran***

# Paskistan: Tara



***Tara yar makaranta ce a Pakistan tana cikin aji na biyu a sekandari inda ta nemu shiga koyon ilmin Tauhidi na Littafi Mai Tsarki ta hanyar koyo ta gidan waya domin tana so ta l.aru da sanin Allah, iyayen ta musulmi ne masu tsauri saboda haka basa amsar tambayyoyin ta game da yesu ita kuwa ta dage dason bincikawa tasani da kanta.***

*Kuma ko wane ne ya bar gidaje ko yan'uwa maza ko yan'uwa mata. Ko uba ko uwa ko yaya ne kasashe sabili da sunana, zaya sami riba dari zaya kuma gaji rai na har abada.*
*Matt. 19:29*

Amma lokacinda iyayen ta suka ganta tana karatun takardun Krista a dakinta sai suka fusata. A watan Nuwamba na 1992 sunyi mata mummunan duka da yakai ta ga suma adaki har kusan mako guda tana kwance a daki, ta bada gaskiya cewa mala'ika ne ya farfado da ita kuma ya kaita asibiti. Tara ta cigaba da girma a cikin bangaskiya kuma aka yi mata baptisma 1995 a boye

Daganan sai iyayenta suka yi shirin aurar da ita ga wani musulmi. Da Tara ta ki yarda sai aka sake yi mata duka kuma aka sa tayi tsayuwa na kwanaki ba bu barci. A wannan lokaci Tara ta ga budi sau uku inda taji murya na gaya mata ina tare dake nine Ubanki bayan karin duka saita fadi ta suma sai bayan kwana uku ta tashi kuma ta sami kanta jina jina sai ta sake jin wannan murya mai karfafawa tana cewa, nine Ubanki zan kiyaye ki.

Tara ta sami damar tserewa kuma yau tana zaune a matsera a wata kasa inda take bauta wa Ubangiji na cikaken lokaci tare da alkawarin Ubangiji na tsaronta.

***Wai shin Kristanci wani al'amarine na faduwa? Su da suke kasashe marasa yanci sun san yaya faduwa da rashi yake domin bangaskiyarsu ga Kristi. Sun san yadda suke rasa iyalansu ta hanyoyi da dama. Iyalin musulmi na iya kin wani nasu da ya karbi Kristi da cewar ya zama kafiri ya zama abin kyama. Iyalin Krista ma na fuskan tar haka ko da yake tu wata hanya dabam. Masu tsannanin ra'ayin Islama sukan kashe iyali guda gaba daya domin imanin su Rashin gagarumi ne amma muna da alkwarin Kristi ko da menene zamu rasa a dalilin sa. Zai dawo mana ribi kan ribi fiye da sau dari na rai madauwami a samaniya. Wannan ba caca bace. Wannan kididdigaggiyar kasada mara kuskure kuma tabbatacciya. Koka yarda da hada ko baka yarda ba.***

**VOICE OF THE CHRISTIAN MARTYRS NIGERIA**

**Stephen Publishing House**

STEPHEN HOUSE Sewage, Gowon Estate, Ipaja Lagos.
P.O Box 21078, Ikeja, Lagos, Nigeria
Tel: 0803 308 2342, 0805 444 0849, 0803 502 3229
www.stephens-persecution.com